UWA UWA CE

LITTAFI NA BIYU.

BATOOL MAMMAN.

UWA UWACE...21

GODIYA GA MASU KARATU.

Assalam alaikum wa rahmatullah wa barakatuhu.

Da farko ina godiya gareku masu kira da turo sako ta sms da whatsapp, wattpad da facebook. Nagode da shiruna bai sa kun manta dani ba. Allah Ya sakawa kowa da alkhairi. Na so sai na kammala labarin nan gaba daya zan sake post amma yawan tambaya da kuma rashin sanin me ya boyeni yasa ni fito da iya abin da ya samu.

Duk da haka ina mai baku hakuri domin daga wadannan shafukan zamu sake wani zangon kafin cigaba. Addu'arku nake roko don Allah. Akwai abu da ya tunkaroni, ina rokon Allah sa'a da salama a cikinsa. Allah Yasa a dace. Allah Ya biyawa kowa bukatunsu na alkhairi. Ina muku SonSo.

***

DAYA MAFARIN IRGA.

A zuciye Uwani ta isa gabansu tana muzurai. Kafadar Ummule ta riko ta yadda dole sai da tasa ta juyo suka fuskanci juna. Bata cire hannun ba ta nunata da dayan.

"Ke bariki ma fa iyawa ce. Naga kuma kamar baki iya ba tunda kin yi shuka a idon makwarwa. Idan sadaka ko taimako ki ke nema me ya hanaki tambayata ina mace 'yar uwarki? Ai mu biyu ne a wurin. Don tsabar is.. sai ki bi namiji?"

Dama Ummule tana fita daga adaidaita sahun ta gane Uwani. Akwai hotunanta a wayar Salihi. Kafadarta ta gotar hannun Uwani ya koma lilo.

"Akan me zan nemi taimakonki bayan ga mijina..."

Uwani ta kan ji ana cewa kunne ya toshe na 'yan dakiku sakamakon jin zance mara dadi. Ashe gaske ne. Daina ji ko gane komai tayi na wani lokaci sai kalmar miji dake neman mazauni a cikin kwanyarta.

Karfin hali Salihi ya yi ya ce "Uwani. Ummule. Ku shiga ciki muyi magana bai dace ana jin muryoyinku a waje ba."

A haukace Uwani ta isa bakin karamin gate din nasu wanda mota bata shiga, shi yasa suke ajiye motocinsu a waje. Tare shi tayi da hannuwanta biyu ta soma masifa ido rufe.

"In ta shiga Allah Ya ..."

"Kar ki karasa tsinuwar nan. Gida dai nawa ne kuma ku duka matana ne" cewar Salihi yayinda ya matso zai cire hannuwan da tasa ta tare hanya. Duhu ya mamaye unguwar sai hasken kwayayen fitilu. Su ukun duka babu wanda ya yi sallar magariba saboda ta riskesu a titi. Ga isha an soma kira. Baya son makotansu masu zuwa masallaci wani ya ga abin da yake faruwa a kofar gidansa.

Kallon baka da hankali Uwani tayi masa kafin ta iya hada labbanta ta ce,

"Su waye matan naka? Aure kayi da gaske ban sani ba?"

"Na ce miki mu shiga ciki ko" ya ce yana dan daga murya.

Mubasshir na cikin tura kudi a aljihunsa yaji muryoyin iyayensa kamar suna fada. Da sauri sauri ya tattara komai ya mayar inda yake. Aljihunsa kam bandiran dubu dai-dai guda uku ya tura. Ga sarkar da ya dauka daya. Ya kuma rufe mata daki kamar ba a shiga ba ya fito.

"Wallahi kayi kadan Salihi. Amanata ka ci? To ka je ka tambayi malamai wannan auren bai dauro ba tunda ban sani ba balle na amince."

"Ki ce kawai idan ki ka tsine masa za ta kama shi." Cewar Ummule, haushin lallabawar da Salihi yake mata a wannan yanayin da suke cik na kara kamata.

"Kar ki yi min rashin kunya! Bani da kyau wallahi" Uwani ta ce a harzuke kamar za ta kai mata duka.

Akan ce idan babba ya yada girmansa sai yaro ya taka ya hau. Ummule ba mai takalar rigima bace amma bata ga dalilin ragawa haukan da Uwani take musu ba.

"Daidai nake dake. Gidan mijina ne saboda haka a matsa min na shiga."

"Wanda ya auroki ma bai isa ya shiga ba."

Shi dai hankalinsa ya gama tashi saboda bai iya hayaniya ba. Da kyar ya cire hannunta ya janyeta suka shigo tare da Ummule. Ita haushi da tausayi ya bata. Yadda yake bin Uwanin a hankali har ta soma tara musu mutane ya kular da ita. Banda tana gudun bacin ransa da tuni ta hankadeta kowa ya huta.

Suna shiga suka ci karo da Mubasshir wanda rashin gaskiya ya fito a fuskarsa baro baro. Amma da yake suna tare da damuwa su duka babu wanda ya kula. Muryar Uwani a sama tana ta zazzaga masifa ba ji ba gani.

"Kaga Salihi ka sallami yarinyar nan kafin na illata ta."

"Mu illata juna dai" cewar Ummule tana jijjiga kafa.

"Kaji ko? A gabanka take yi min rashin kunya."

Ihu ne kawai bai yi ba amma kansa ya dauki chaji sosai.

"Uwani ki saurareni kiji."

"Anki a saurareka din..."

Mubasahir sai yaji wani iri. Mahaifinsa take yiwa magana haka a gabansa.

"Mama don Allah kiyi shiru..."

Dama a wuya take sai kawai ta janyo shi ta kai masa duka a gefen fuska ko ta huce. Ransa kuwa ya baci . Ta kara yiwa kanta bakin fenti a idonsa.

"Munafukai daga kai har uban naka. Saboda baka damu dani ba ko a jikinka an kawo 'yar shila da sunan kishiyata."

Bata tsaya kallon fuskar dan nata da miji ba bayan ta kira su munafukai ta harari Ummule.

"Idan ma dadiro kuke yi ya miki ciki a waje ake son kawo min cikin gida ne to kunyi karya."

Dama kallo daya ta fahimci Ummule tana da ciki. Sai da ta gaji da masifar don kanta ta

nufi dakinta ta soma dauko akwatuna tana budewa. Saboda gudun bacin rana da cin amana irin ta da namiji take ta tanadi. Gininta a Zawaciki filasta kadai ya rage da fenti. An kawata gidan sosai ya dace da zamani ta kowace fuska. Gida ne dan madaidaici wanda ta kudurta niyar komawa idan bai yi musu gyara a nasu na yanzu ba. To ashe mai gabadaya ya tasarma yi. Ajiyayyun kudadenta za ta dauko ta bayar a gama komai cikin watan da ake ciki. Tana ganin idan ta tashi daga shi har kurar da ta kwaso matarsa za tafi karfinsu.

Akwatin da kudaden suke ta durkusa ta bude kudi suka ce daukarmu inda kika ajiye mu!

***

Bayan tafiyar Uwani da aka idar da sallar Magariba wasu makotansu Innayo suka shigo. Zama na mutumci ne tsakaninsu shi yasa suka shigo tambayar ayyukan da take so su tayata na sunan gobe. Kafin ma ta fada musu babu taro suka fahimci halin da Zara take ciki. Sun tausaya mata sosai kuwa. Da yake Innayo ba mai yawan magana bace bata taba zaman sukar 'ya'yan nata ba. Sai dai wanda ya gani da idonsa ya fahimci irin zaman da suke yi. 'Yar hira suka taba yayinda su Hasiya suka gama kimtsa komai suna shirin tafiya.

Innayo ta fito raka bakinta kenan adaidaita sahun da ya dauko 'yan sakon gidan Salima ya tsaya a kofar gidan. Ihsan da kuka ta fito ta fada jikinta. Gabanta ya yi mummunan faduwa. Dago Ihsan din tayi daga jikinta hankali a tashe.

"Ina Salima? Me ya kawo ki da magaribar nan? Kukan me kike yi?"

Ihsan ta kasa magana sai shesshekar kuka. A tsorace take ko mutuwar gaske mahaifiyarta tayi.

Daya daga cikin 'yan rakiyar ne ya yi mata bayani. Kuka ne ya kwace mata, nan da nan idanunta suka dinga zubar da kwalla. Bata ga ranar hutu akan lamuran 'ya'yanta ba. Kuma tana tsammanin wannan ranar ba za ta taba zuwa ba. Daga ranar da mace ta fara amsa sunan uwa to har abada sunanta kenan. Da damuwar Zara ta wuni, bakincikin Uwani ga kuma tararrabin halin da Salima take ciki ya risketa a farkon dare. A yadda ta fito rakiyar nan haka ta kutsa kai cikin adaidaita sahun da ya kawosu ko cikin gidan bata koma ba. Silifas ne a kafafunta sai hijabin da tayi sallah wanda da shi makotan suka risketa. Hannun Ihsan kawai ta rike tana karanto addu'a a zuci suka koma cikin adaidaitan.

Su Hasiya sai ganin wadanda Innayo ta fita rakawa sun dawo su kadai suka yi. Kusan a tare suke rige rigen fada musu abin da suka ji da gani. Maimuna har ta soma kuka Hasiya ta tabata. Sai da matan suka fita ta sanar da ita yadda suka yi dazu.

"Duk da haka Hasiya idan kuma na gaske ne fa. Ni dai ki zo muje."

*

"Ban gane wannan sabon shishigi da ku ka soma yiwa matar nan ba ke da Munzali."

Ummakati shiru tayi ta dafe kanta da hannu daya kamar mai ciwon kai tana sauraren Asabe. Tun shigowarta dakin take ta yi mata fadan zuwan da tayi da magariba kamar dole. Sannan ana karo karon kudi ita ma ta dauka ta bayar ko shawara da ita bata yi ba.

"Tunda kin bawa banza ajiyata ai gara ki tashi ki tafi"

Asabe ta furta cikin fushi. Bata ga dalilin wannan binbini da Innayo ta fara yiwa yaranta ba. Ta dade da sanin darajar daukar ciki da haihuwa take ci a wurin Munzali amma bata gabansa. Ummakatin da take mace kuma cikin rufin asiri ita kuma bakar rowa gareta a nata tunanin. Amma don neman suna ta dauki kudi ta bawa Innayo.

Gatse ne ko shagube, kalaman ba suyiwa Ummakati dadi ba. Tayi bayanin har ta gaji amma Asabe taki yarda. Surukarta ta ninka Asabe a komai ma. Ga rigima ga fitina. Dan nata ma tsoronta yake ji. Kuma a haka kiris take jira ta saka shi sakin Ummakatin saboda wai gidan da ta fito bai yi mata ba. Daga Alh. Rabi'u har Asabe babu mai daraja a idonta.

"Ki yi hakuri."

Tsaki Asabe ta ja tana mai cigaba da sakin maganganu.

"Bani abin da kika kawo min ki tashi ki tafi kafin babanku ya san kin zo don cewa zai yi sai mun raba. Ko yana ina lokacin da nake fadi tashin gina ku ban sani ba."

"Hmmm" Ummakati ta furta a hankali hannunta a jikin zip din jakarta. Dubu biyar din da ta lalube aljihun mijinta ta dauko ta mika mata. Idan bata bayar ba ta san watan kwasar bakincikinta ne zai tsaya. Har gida za ta dinga zuwa tana zubar da mutumci a gaban jikoki da babansu. Ba za ta yarda cewa Asabe ta manta da yadda suka tashi babu kulawarta ba. Banda tsarewa ta Allah da ta dade da shiga duniya kamar kawarta da suka yi 'yammatanci tare.

A hanyarta ta fita ne ta tsaya yiwa su Innayo sallama. Nan ta ji abin da ke faruwa a bakin Maimuna. Ta ce su taso su tafi tare. Ayaah kawai aka bari a dakin ta kula da Zara da jinjirarta.

Asabe da ta san ba sauraronta Ummakati za ta yi ba ko ta ce kada ta kaisu sai cewa tayi,

"Yau dai ranar ta Innayo ce. Ana ta ganin bacin rai akan 'ya'yan da ake cika mana baki a kansu. An gama gulmata akan tarbiyar 'ya'ya sai gashi sune da arzikin da ake ci. Munzali ya sakar muku bakin aljihu yanzu gashi motar Ummakati za ku shiga. Duk wani asiri kuma da surkullen mutum zai yi ya gama ne. Kurkuwarmu kurrrr....." ta bisu har soro tana fada.

Dama can ba ayi musu tarbiyar mayar mata da magana ba ballantana kuma yanzu da 'yarta take wajen. Hasiya da Maimuna sai suka kama bakunansu. Murja da Ummi su ma basu tanka ba. Yaran Maimuna kuwa basa wurin. Su aka tura shigo da adaidaita sahu kafin shigar Ummakati dakin.

A zaune suka sami Salima da suka isa gidan. Fuskarta a kumbure ta sha kuka. Mata kuwa harda wasu mazan sun cika 'yar tsakar gidan babu masaka tsinke. Kowa bayanin abin da ya sani yake yiwa Innayo.

"Mama ku ma kun yi sakaci tunda abu ne na shekara da shekaru. Ba don tana da tsahon rai ba ma da tuni labari ya dade da shan bamban."

Matar da tayi maganar Innayo ta duba ta jinjina kai. Tabbas da laifinta. Duk da Salima bata fada ba amma ta jima tana hasashen hakan saboda irin ciwukan da take gani a jikinta. Karairayin Saliman na kare Ale Gambo dai ta zabi karba don ta

kwantarwa da kanta hankali. Damuwar 'ya'yan sai tayi mata yawa idan kowacce cikinsu bata da sukuni.

"Ina Gambon yake?"

Nan da nan aka shigo dashi a daddaure kamar huhun goro. Bata kula cewa ta wuto shi a waje ba inda samarin layin suka yi cincirindo. Motar 'yan sanda suke jira azo a tafi dashi.

Yana ganin Innayo da Salima a zaune ya fara kici-kicin son a kwance shi.

"Dama na fada! Sharri suke son kulla min ita da 'yan uwanta. Banda haka ai ba yau na fara dukanta ba amma suna tafiya ta zube min a kasa bayan ko rabin dukan da na saba ban mata ba?"

"La ilaha Illallahu..."

Mata suka hau sallallami don ga dukkan alamu bai san asirinsa yake tonawa ba.

"Kin ji yana fada da bakinsa ko Innayo? Wallahi na gama zama da shi ko kotu zamu shiga sai dai aje"

Cewar Salima cike da kwarin gwiwa ganin kowa ita yake karewa.

Don masifa Ale Gambo ji yayi kamar ya kwance daurin yaje ya mareta. Shi fa a tunaninsa bata isa ta taba ketare zancensa ba balle ta kaisu ga sa'insa.

"Ki bar ganin idanun mutane wallahi sai na tattakaki na taka banza idan suka tafi. Ni dake aure yanzu aka fara."

Hasiya da Maimuna harma da Ummakati sun so mayar masa da martani amma fafur Innayo ta hanasu magana. Yaran kawai ta cewa su shiga daki su dauko kayan sawarsu. Washe gari sai a dawo a kwashe kayan gidan.

Hankalin Ale Gambo sai lokacin ya tashi da yaga sun fara fita. Mutane irinsa masu mulkin mallaka ga wadanda suka fi karfi basu fiye son a gudu a barsu ba. Duk wannan power din da yake takama da ita dama na samun wuri ne a jikin Salima. Yau da tayi bore sai yake jin yafi kowa kaskanci. Kiran sunanta ya dinga yi da karfi da kalaman tsoratarwa akan irin hukuncin da zaiyi mata idan ta dawo.

Babu wanda ya waiwaye shi har 'ya'yansa. Innayo ce kadai ta dakata sai da iyalinta suka fice sannan ta dawo inda yake tsaye an daure masa hannuwa ta wanka masa wani irin gigitaccen mari. Kamar an dauke wuta haka mazan da suka yi saura a wajen suka dauke numfashi. Shi kuwa hantar cikinsa sai da ta kada domin bai taba zaton za ta iya yi masa wani abu sama da mugun kallo ba.

"Idan takamarka wanda ya baka aurenta bai san darajarta ba shi yasa kaima kake takawa to kayi karya. Muddin ina numfashi da yardar Allah ka gama taba lafiyar Salima. Shari'a kuma akan hakkinta da ka dade kana dauka ko zamu shekara anayi in Allah Ya so ba za mu karaya ba."

Juyawa tayi ta fita ran ta yana kuna. A bakin kofa suka yi kicibis da 'yan sandan da aka kira. Haka suka bi bayansu domin sun ce dole Salima taje ta bada statement kafin su daure shi.

*

Daki guda Abbati ya zage da kansa yana gyarawa Baaba Mari. Gidansa kato ne. Akwai rashin adalci idan aka ce matar gidan kullum sai ta bi dakuna da bandaki ta gyara. Shi yasa ya sa rai da ganin kura kadai ta rashin amfani. Shi ma kuma ko don kada kaya su lalace a kalla ko sau daya a sati ne ya kamata ace an share. Sai ya sha mugun mamaki. Datti dakal-dakal ya tarar da kura harda yana. Basu fiye bakin kwana ba saboda kishinta duk da masu zuwan duka 'yan uwansu ne. Bandakin kuwa harda kwari suna yawo wasu kuma sun mutu. Bawan Allah bai hango laifin

kowa ba sai nasa. Da bai salwantar da rayuwarsa wurin yawo ba kila da yafi kula da lamuran gidansa. Yanzu kuwa ko sannu bai samu ba daga Hanne tayi hayewarta sama.

'Yashshafa ma duk shirmenta sai da taga rashin dacewar haka. Dukkaninsu sun gaji musamman Hannen da tayi jeka ka dawo a rana daya. To amma har ace ta manta mijinta a ranar aka sallamo shi daga asibiti? Akalla ko da ba yi za ta yi ba ai ta nuna masa cewa tana da hankali ta hanyar cewa ya bata tsintsiyar ta share. A yadda ta fahimti Abbati ta san da kansa zai ce taje ta huta. Jinjina kai tayi ta tashi daga kan doguwar kujerar da ta dan kwanta tabi bayansa bayan ya wuce da tsumman goge-goge.

"Ina zaki kuma?" Deluwa ta tambayeta da sauri.

"Karbar gyaran dakin zan yi."

"Dawo ki zauna ai ba sanin darajarki ya yi ba. Na gano miki miji dan gidan arziki ba taka haye irin na wasu ba."

Ta furta tana kai dubanta ga Baaba Mari wadda maganar ta yiwa dirar mikiya. Ko a farcenta don Deluwa ta hana 'yarta taya Abbati gyaran daki. Abin da ya tsaya mata bai wuce kiransa wanda ya yiwa arziki taka haye ba. Kenan ba ita kadai sauri da habbakar arzikinsa yake yiwa kai kawo a kirji ba? Kamar Deluwa taji tunaninta ta bata amsa tana faman tabe baki.

"Kar fa kiji haushin maganata Mari kin san ba karya nayi ba. Almajiri da tamfatsetsen gida irin wannan akwai ayar tambaya. Anata cewa yana kasuwanci gashi har rana irin ta yau bamu taba ganin samfurin hajar tasu ba."

Baaba Mari bata iya cewa uffan ba har Habi ta shigo daga bangaren Munzali inda aka yi musu masauki. Daki ya basu a cewarsa bai yarda su dawo tare a barshi a nasa gidan shi kadai ba. Iya Kande ba zama take sosai ba indai Qibdiyya bata nan.

Habi ce ta karbi gyaran dakin a wurin Abbati shi kuma ya hau sama. Deluwa ma da 'Yashshafa suka shige dakin da aka basu suna jiran kuku ya gama girki.

Tunani, damuwa da zancen zuci aka bar Baaba Mari tana yi akan tarin dukiyar Abbati. Kasantuwarsa dan fari ba shi ne ya sanya soyayyarsa tafi ta 'yan uwansa a zuciyarta ba. Saukin kansa wanda mutane musamman na gidan suke amfani dashi wurin cusguna masa tun kuruciya ne. Tunda aka gane lagonsa ake saka shi kuka. Tun tana kawaici har ta koma musayar yawo da duk wanda zai taba shi saboda bashi da baki. Wannan saukin kan yasa ta guji ya tafi almajiranci. In an barta ma za ta ce wannan halin zai janyo masa wahalar rayuwa fiye da a gabanta. Sai gashi abin mamaki maimakon ci baya sai ya yi gaba. A gaban ma ya yiwa da yawa fintinkau. Wata irin zabura tayi ta mike lokacin da taji takunsa yana saukowa daga sama. Haka ta kura masa idanu tana kallonsa cike da firgici. Tsoron yarda da hasashenta take yi. A cikin zuciyarta take addu'a kamar haka.

"Ya Allah Kasa ba sata ko fashi yaron nan yake yi ba."

BIYU IDANUN...

***

Su uku ne zaune a dakin Alh. Rabi'u. Shi, Innayo da Asabe. Tray din abinci ne a gabansa yana ta kwasar girki yana gumi. Hannun malum-malum dinsa yasa ya goge shi bayan gama ya janyo tsintsiyar kwakwa a gefen gadonsa. Dan tsinke ya karyo ya danna a baki yana sakato naman da ya makale yana tofarwa.

Magana ya kirasu suyi wadda gabadaya akan 'ya'yan Innayo ne. Shi yasa taji haushin kiran Asabe da ya yi dakin nasa. Ta san ya yi ne domin neman fada a wurin Munzali tunda dan Asabe ne. Duk tsiya idan ya kyautata mata ta hanyar nuna mata gazawar Innayo za ta yiwa Munzali magana akan bukatunsa. Ya kula yanzu bakin gwargwado Munzali yana dan yi mata magana da tattausan lafazi.

Hirar arzikin Munzalin ya dauko suke ta yi da Asabe har sai da Innayo ta magantu.

"Zan koma idan kun gama tadin ayi min magana."

Mikewa tayi abinta za ta fita Alh. Rabi'u ya dubeta fuska a hade kamar ba shi ya gama yiwa Asabe dariya ba.

"Bakin halin da ki ka koyawa 'ya'yanki za ki gwada min?"

Dadi ya kama Asabe ta karbe zancen don ta kara zuga shi.

"Ka dai bi a sannu kar ka manta da bakinka ka fada min Ale Gambo ya ce ta mare shi."

Kamar an kunno shi kuwa ya hau masifa yana fadawa Innayo maganganu.

"Banda lalacewa ace har kin iya dora hannuwanki a fuskar baligi kamar Ale Gambo kamar baki san haramcin yin hakan ba?"

Saboda yadda take jin ta muzanta sai take gani kamar tsirara ya yi mata a gaban matarsa. Jikinta ya yi sanyi kalau yayinda zuciyarta take tafarfasa. Haka nan idanunta suka rine da bacin rai mara misaltuwa.

"Yanzu Alhaji me ya kawo magana irin wannan? Gambo tamkar dan cikina fa yake tunda ya auri Salima."

"Tamkar 'yar cikinki dai...ke da baki san ma'anar haihuwar namiji ba ina ke ina kwatanta dan wata da naki?"

Asabe ce tayi maganar dankwalinta a gaba tana neman takalar fada. Haushin yadda su Munzali ke bin Innayo take son fanshewa.

"Fada mata dai. 'Ya'yan da ta cusawa kiyayyata basa ganin girmana. Gashi tun ba aje ko ina ba an fara dawo min gida."

Asabe ta murmusa cike da jindadi.

"A'a fa Alhaji. Kar kayi butulci. Nima shaida ce ana kawo maka dari da kwabo idan Hasiya mai lalle tayi ciniki. Su kankamoji (Zara da Uwani) dai ko ita sha-wuyar basa bawa."

Dariya suka washe da ita wadda tayi sanadiyar zubowar hawayen da Innayo take ta kokarin dannewa. Habar zaninta ta saka ta goge idanunta amma haka wani hawayen ya maye gurbinsa. Dan kuka mai ja wa mahaifiyarsa jifa. A haka ta fita tana jiyo sautin dariyarsu.

Bata karasa dakinta ba ta juyo a fusace ta koma dakin Alh. Rabi'u. Tuni ta fahimci cewa sadaukarwa da hakuri daban suke da kawar da kai. Ta sadaukar da kuruciya, lafiya da jindadinta a bautar aure da kula da yara. Tayi hakuri da rashin kyautatawar miji da wasu cikin 'ya'yanta. Duka wadannan akwai riba a duniya da lahira. Amma kawar da kai akan abubuwa na bacin rai kam cutarwa ne gareta dasu wadanda take kyalewa. Anyi abin da aka yi a baya. Yanzu kuwa daidai take da kowa. Bata da nufin cutar da kowa, sai dai ba za ta yarda tayi ta hadiyar bakincikin kowa ba.

Bankada labulen tayi ta shiga ta zauna a gaban Alh. Rabi'u. Hannayensa duka biyu ta kamo ta shimfida tafukan akan fuskarta. Asabe mamaki ne ya kamata na zuci da zahiri. Shi kuwa sai ya sami kansa da shiga taitayinsa ya kasa yi mata magana.

Cikin muryar lumana babu wani hargagi kamar yadda ta yiwa su Zara ta soma magana.

"Kaji dumin hawayena?"

Ya gyada kai kamar sakarai.

"Bai kama kafar zafin zuciyata da barazanar bugawar da take a kirjina ba. Alhaji...."

"Na'am" ya amsa da rawar baki.

"Allah zai bi min hakkin hawayen da na zubar maka ba da hakki ba."

Ta tashi ta juya za ta fita sai ta tsaya ta kara da cewa " 'ya'ya amana ne kuma daidai iyawata nayi kokarin sauke wannan amanar. Ba komai da nayi bane zai zama daidai amma nayi imanin Allah zai sakawa kokarina. Zai shirya min 'ya'yana. Zai daidaita min lamurana."

Da ta koma dakinta duka 'ya'yanta suna nan harda Uwani da ta shigo bayan fitarta. Kare musu kallo tayi daya bayan daya tana tuna ranar da ta haifi kowacce. Uwar dakin ta shiga ta barsu ba tare da ta amsa maganganun da suke yi mata ba. Hannu na rawa ta tura kofar ta rufe da sauri sannan ta zube a kasa saboda zafin kirji. Miji babu dadi, kishiya ba zaman lafiya, 'ya'yanta kuma kowacce da tata matsalar. Matsalolin nasu da suka zame mata abin tunani da shiga damuwa.

Kwana biyar kenan da ta dauko Salima. Ga Zara har yau mijinta bai zo ba. Maimuna nata mijin ya ce ya gaji da yawan zarya da take yi zuwa gidan iyayenta, ga talaucinsa da yafi na Ale Gambo. Uwani tun washegarin zuwan Ummule ta fada mata anyi mata kishiya. Gabadaya ta sauya tana neman susucewa. Sai dai taki fada mata ba zuwan kishiyar bane kadai damuwarta ba. Kudin da take yawan cewa babu ta nema ta rasa. Ta kuma kasa cigiya a gida saboda babu wanda ya san dasu. Hasiya kuma nauyi ya mata yawa. Bata morar kudin sana'arta ko kadan yanzu. Duk ta rame saboda wahala da rashin isasshen bacci. Sannan rashin haihuwarta yana matukar damunta.

Ita ce uwa garesu. Bata hango ranar hutun jiki da na zuciya ba kila sai ta bar duniyar.

Alh. Rabi'u da Asabe kuwa har Innayo ta ware a dakinta basu dawo daidai ba. Maganarta takaitacciya ce amma ta zauna saram a kwakwalensu.

***

"Kace masa Habu ne."

Masinjan ya bishi da wani irin kallon kwaf kafin ya ce "Habun ai da yawa. Baka da inkiya ko cikakken suna?"

Honorable ya yi dan murmushi don fushi ba nasa bane. Satinsa guda yana zuwa ma'aikatar wurin shugabansu Alh. Bala ana jirga shi. Ba kuma zuwan kansa bane. Mutumin ya kasance abokinsa lokacin da yake da abin hannu. Tunda ya sami karayar arziki bai taba bibiyar tsofaffin abokan huldarsa neman taimako ba. Wulakanci ne baya so. Yanzu ma dole ce ta kawo shi. Ya boyewa duka iyalinsa ne musamman Hasiya amma likitan da yake duba Abbas a asibitin kwakwalwa na Dawanau ya tabbatar masa da cewa idan ba ayi masa aiki cikin kankanin lokaci ba da wuya ya warke ko anyi. Jijiyoyin da suka sami matsala sun fara gajiya a yanayin da suke ciki. A wannan yanayin ne ya hadu da tsohon abokin nasa a wajen daurin aure. Bai yi kasa a gwiwa ba ya nemi taimako kuma ya yi sa a ya amsa masa. Fatan samun warakar Abbas din shi ne albishir din da yake ta boyewa Hasiya. Sai gashi har yau ko ciki bai sami shiga ba. Kullum da abin da ake fada masa. Yau ne ma ya yi sa'ar haduwa da masinjan Alh. Bala din shi ne har aka tambayi sunansa.

"Habu Danmalam za ka ce masa. "

Masinjan ya sake kura masa ido kamar me neman wani abu. Cikin 'yan dakiku ya sanya hannu ya bugi kansa da takaicin rashin gane shi da wuri. Sakin fuska ya yi sosai ga mamakin yanayin da ya ganshi.

"Habu Danmalam dai da na sani?"

"Ni ne" ya amsa da murmushi.

"Ikon Allah. Ai wallahi da na san kaine da tun zuwan farko nayi cuku-cukun hada ka da Yallabai" Hannu ya mika masa suka gaisa ya ce " Amma ina zuwa. Bari naje na fada masa idan Minista ya tafi sai ka shiga."

Wani karamin ma'aikaci a wurin yana jin furucin masinjan ya janyo shi gefe.

"Yallabai fa ya ce kada a bar kowa ya shiga yau. Idan Ministan ya tafi shi ma tashi zai yi."

Honorable Habu yana jinsu ya ja gefe da nauyin zuciya. Gwargwadon iyawarsa bai yi amfani da mukamansa na baya ya wulakanta kowa ba. Amma duk da haka yanzu idanunsa sun kara budewa da bambancin masu mukami da talakawa. Mafi yawan masu kawo korafi basu da yadda zasu yi ne. In an barsu ba za sy zabi kaskantar da kai suna roko ba. Amma sai su keta billensu suyi rokon bayan an hanasu a kara da wulakanci.

Masinjan ya amsawa mutumin da cewa "Honorable Habu Danmalam ne fa."

"Kai ka san shi" cewar wancan irin 'yan rijiya ta bayar guga ta hana dinnan.

"Ni kuwa na san shi. Kuma Yallabai ma ya san shi domin tare suka yi siyasa."

Bai kara saurarar mutumin ba ya wuce cikin ofishin Alh. Bala. Ya san suna tare da Ministan (Land, Housing and Urban Development) sai dai kuma idan har bai sanar dashi bakon nasa ba karshenta ya fice ta baya idan sun gama tattaunawa.

Sallama ya yi ya sake gaishe da Ministan kamar ba shi ya yi masa rakiya har nan din ba.

"Yallabai dama na ce bari na leko ko kuna bukatar wani abu."

"Idan ina bukata ma ai ka san Surayya (sakatariyarsa) tana nan."

Masinja ya gyada kai

"Eh haka ne kuma. To ku tashi lafiya." Juyawa ya yi kamar zai tafi sai kuma ya dawo "af...Yallabai kar na manta kana da bako fa."

Alh. Bala ya kirne fuska saboda wannan shishigi zai iya sawa ya rasa alkhairin da Ministan ya zo dashi. Hannuwansa ya dora akan teburin gabansa yana maganar da babu kofar ja'inja cikinta.

"Ba zan ga kowa ba idan mun gama tafiya zan yi. Ko waye ka ce ya dawo gobe."

Ya san za a rina shi yasa ya ce "babu komai. Yau da gobe duk daya ne. Don ya kara kwana daya akan ragowar kwanakin da ya yi yana zuwa babu matsala."

Wani mugun kallo Alh. Bala ya jefa masa kafin ya kai ga ambaton sunan bakon a dole ya fita. Addu'a yake shi kadai yana fatan bai yiwa kansa sanadin aiki ba.

Sai bayan fitar Masinjan Minista ya ajiye karamin kyakkyawan kofin shayin da yake rike dashi tun shigowarsa. Yadda ya buga kofin ya tayar da hankalin Alh. Bala domin alama ce ta bacin rai.

"Kayi hakuri Ranka ya dade. Na san ka ma fini haduwa da 'yan maula masu hana mutane hutawa. Mutumin da ya zo din na san ba kowa bane illa wani tsohon dan siyasa da muka zauna jam'iyya guda a baya. Gwamnatin da ta maye gurbin tamu

tun a wancan lokacin tayi watsi dasu. Shi kuma bai iya kwantar da kai irinmu ba...hahahhha"

Har lokacin fuskar Minista babu wani annuri sai ya dora da,

"Harda laifinsa gaskiya da ya kasa samun wani mukami da aka sake samun canji tsohuwar gwamnatinmu ta dawo. Ya dauki girman kai da dagawa shi a dole mai tsantseni. Ashe abin nasa duk buge ne, gashi daga haduwa wurin daurin aure ya makale min."

'Allah na gode Maka da Ka nuna min waye Alh. Bala tun kafin na sanar dashi makasudin zuwana.' Furucin Minista kenan a zuciyarsa.

Idan yawan aiki ne da yawan 'yan maula ya ninka Alh. Bala nesa ba kusa ba. Sai dai shi mutum ne da ya tsani wulakanci. Tarba mai kyau wadda ta dace da matsayinsa ya samu kuma akan idonsa wani ya sami kishiyarta. Wannan abu ne da ba zai iya dauke kai ba. Maganar aure ce ta kawo shi. Ya hadu da wata yarinya a gidan abokinsa wadda bayan gajeren bincike aka fada masa 'yar Alh. Balan ce. Muradinsa na son auren mata biyu yaso cikewa akanta. Dalilinsa kenan na zuwa ya same shi saboda shi mutum ne mai tsari. Ba ya son ya fara yi mata magana a waje ta amince saboda mukaminsa bayan akwai wani. Halin mahaifin nata da ya gani yasa shi yanke shawarar zurfafa tunani da bincike.

Tashi ya yi ya gyara zaman babbar rigarsa.

"Ba dai tafiya ba? Bamu tattauna maganar da ka ce mai mahimmanci bace ba ma" Cewar Alh. Bala shi ma yana tashi tsaye.

"Kada ka damu zan kira ka a waya. Ina da appointment ne da naso mantawa dashi gashi har lokaci ya kusa."

"Au tohhh..." Alh. Bala ya ce yana sakin fuska "ai na zata zuwan dan anacen can ne ya bata maka rai."

Minista bai ce komai ba har suka fito waje. Alh. Bala kuwa sai zuba masa surutu yake yana ta kwantar da kai kamar ya durkusa masa.

*

Da Masinjan nan ya fito bai iya komawa wurin Honorable Habu ba. Zaman jiran bai dame shi ba. Ya zabi ya fadawa zuciyarsa aiki ne ya yiwa Alh. Bala yawa ba wai da gangan yaki ganinsa ba.

Tashin wasu security da sassarfa suna komawa wurin jerin wasu bakaken motoci da ya samu a wurin yasa shi kallon hanya. Farinciki ya wadatu a fuskarsa yayinda ya yi tozali da Alh. Bala. Da sauri ya tashi yana son yi masa magana kafin ya shiga mota. Da ya tashi sai yaga ba shi kadai bane ya nufi Alh. Bala din da wanda suke tare. Sai kalaman fadanci ake ta zubawa ana cewa

"Allah Ya kiyayeka"

Da dai ya gane ba da ubangidansu suke ba sai ya kalli abokin tafiyar sosai wanda shi ma kallonsa yake yi. Baki ya hangame sai kuma dariya da murna suka hana shi magana.

Ministan ne da kansa ya ambaci sunansa cikin wani irin shauki da kewa.

"Habu Kansila? Honorable Namu? Kai ne?"

Honorable ya dinga gyada kai har suka cimma juna. Hannuwansa Minista ya rike yana ta murmushi.

"Abdulkarim kaine haka?"

Sunkuyar da kai ya yi na kunyar rashin kyautawarsa kafin ya ce,

"Naji kunya sosai Honorable duk da dai wallahi na nemeka sosai bayan dawowata aka ce ka bar unguwar. Laifina shi ne na rashin mayar da hankali wurin binciken inda ka koma din."

Alh. Bala sai yaji kamar an sare masa gwiwoyi. Alamun sanayyar dake tsakaninsu barazana ce a gareshi. Hanyar da suka baro ya nuna da hannu yana kiransu.

"Ku zo mu koma ciki don da alamu kuna bukatar zantawa cikin sirri."

Minista Abdulkarim Mamman Diso bai bashi amsa ba sai nunawa Honorable motar da zasu shiga ya yi.

"Bismillah. Kodayake ban tsaya naji uzurin da ya kawoka nan din ba."

Honorable ya kalli Alh. Bala ya kawar da kai

"Wanda nazo gani bai saurareni ba"

Da haka Minista ya gane shi ne wanda yazo ganin Alh. Bala.

A motar suna tafiya Minista yake sake bashi hakurin yankewar zumuntarsu. Ba abokai bane domin kuwa Honorable ya girme shi nesa ba kusa ba. Lokacin da yake ganiyar cin zamarsa ne su Abdulkarim suka fitini unguwa. Rashin kudi ya hana iyayensa tura shi makarantar gaba da sakandire. Kafin wani ya kai zancen kunnuwan Honorable Habu shi ya gani da idanunsa. Har gida ya tura aka kira masa iyayensu maza ya ce zai dauki nauyin karatunsu shi da abokansa su uku. Haka kuwa aka yi. Suka sake JAMB cikin ikon Allah shi kadai ya haye. Yaji dadi sosai ya biya masa kudin karatun. Abokan masa kuma ya basu jari.

Rayuwa tayi ta tafiya har ya kammala digirinsa na farko. Honourable Habu ya soma cuku cukun nema masa aiki sai ya sami tallafi na zuwa kasar waje karo karatu. A can ya zauna ya yi masters da Phd. Kuma nan ne dai ya hadu da dan wani mai bawa shugaban kasa shawara. Da taimakonsa aka sama masa aiki ya fara yana dawowa. Ya nemi Honorable Habu a ranar da ya sanya kafarsa a unguwarsu Diso sai ya sami labarin ya tashi. Da zuci zucin ya kara nemansa ya koma Abuja. Daga nan kuma kujiba kujibar duniya da kai kawo suka dauke masa hankali. Sai gashi sun sake haduwa a inda bai yi zato ba.

"Ina su Abbas kuwa? Ya gama karatu yanzu ko?"

Tambayar sai ta zama fami ga Honorable. Nan ya labarta masa halin da suke ciki.

Abdulkarim sai ya kara jin haushin kansa. Bai ce masa komai ba amma tuni ya gama yanke shawarar irin taimakon da zai yiwa Hoborable da iyalinsa.

***

A gidan Alh. Tahir kuwa Mami Khadija ta cigaba da shirye shiryen bikin autansu. Mama Nasima kuma ta matsawa Mardiyya lamba da tambayar yaushe Munzali zai dawo.

"Kinga ya tafi kafin mu samu ayi maganar da ta dace. Ni ba so nake kuyi ta batawa juna lokaci da hirar waya ba." Ire iren zantukanta kenan kullum.

Ita kuwa Jiddo ta shiga tsaka mai wuya a wurin kawaye. Karyar da ta zuga musu akan hadin kai da jindadi da ta samu a wurin Danliti makanike ce take neman tarar da ita. Mutum biyu cikinsu kuma harda shugabarsu a ciki sun nemi ta hadasu dashi. A cewarsu harka da talakawa marasa galihu tafi dadi. Komai kika yi musu yanzu sai su ji kamar duniya babu kamar ki. Ladabi da biyayya da kuma bin hanyoyin farantawa mace sai kin zaba kin darje. Sannan uwa uba sun fi rike sirri.

Zancen da ake yanzu dai shugabar tasu tana son yaje Abuja ya sameta sati mai zuwa. Mijinta zai yi tafiya kasar waje kuma tana da yakinin da daya daga cikin 'yan matansa zai tafi. To ita ma ta kirkiri tata tafiyar ya kuma amince. Nan kuwa dan gidan holewa ta saya ba tare da saninsa ba inda take kai kwartayenta. Dubu hamsin ta turawa Jiddo ta ce ta bashi ya yi kudin mota.

Jiddo ta rasa inda za ta saka kanta. Tun ranar da ta tura masa hotuna bai kara nemanta ba. Ta saka masa kati na dubu goma babu godi bare na gode. Yanzu kuma har shugabar wadda ake yiwa lakabi da Sarauniya ta fara cewa idan ma taki hadasu ne saboda tana kishinsa zasu saita mata zama. Ai ta san dokarsu babu rowa. Kowacce tana da damar neman saurayin 'yar uwarta. Shi yasa ma suke fadawa juna yadda ta kaya ko wata za ta so.

Uban gayya Alh. Tahir kuwa yana cikin fushin Yakumbo. Ya tsayar da duk wata magana ta auren Yumna saboda abin da tayi masa. A yadda ya tsara idan an fasa akalla nauyin Farha zai ragu a ransa har ya samu su yi magana. Rabin hankalinsa a kwance yake tunda sauran 'ya'yansa babu wanda ya canja masa fuska. Ya san bata fada ba. Ita kadai ce dai har yau bata yarda sun hadu ba. Motsin motarsa ma idan taji daki take shigewa ta kulle kofa.

Yakumbo kuma tayi rantsuwar idan bai auri Yumna ba to ya shirya ganin bacin rai domin babu shi babu ita.

A can wani bangare na zuciyarsa wanda soyayyar 'ya'ya ta rinjaya sai yake jin gara fushin Yakumbo akan na 'ya'yansa. Yakumbo uwa ce. Uwa kuwa a saninsa za ta iya jure komai kuma ta hadiyi komai domin 'ya'yanta. Idan ta kama ya yi mata kuka ne ma zai yi don ya san za ta yafe masa ta janye zancenta.

*

Dan madaidaicin akwati mai taya hudu Farha ta daga ta saka a booth din motarta. Idanunta ta kai kan motar Abbati wadda take lullube a wurin ajiye motocin gidan taji zuciyarta ta harba. Zai yau zai zo gidan daukar motar amma ba zai sameta kamar yadda tayi masa alkawari ba. Sakon da ya turo mata jiya da daddare ta sake maimaitawa a cikin kanta a hanyarta ta zuwa wurin Maminta.

(Zan zo mu yi magana Ya Farha. Maganar baki da baki kafin nayi shirin daukar mataki na gaba wurin mallakawa Auwal muradinsa. Kin mamaye ko'ina a tare dani. Allah Yasa kina tuna ni ko sau daya ne a rana.)

Wani abu mai kama da ana yiwa mutum yawo a ciki taji ya tsirga mata a lokacin don dadi. Ita kadai ta dinga zuba murmushi tana kuma jin kunya kamar yana gabanta. Ashe sunansa Auwal ta fadawa kanta kamar da wani take. Sai da ya soma fitar da rai da samun amsa sannan tayi masa reply.

(Ban san Auwal ba shi yasa bana tunaninsa)

Da wurwuri ya sake turo mata wani

(Amma dai kin san Abbati?)

Kasa rubuta komai tayi tana dariya kasa-kasa.

A bangaren Abbati shirunta sai ya dame shi. Shi fa kaifi daya ne baya son jan rai. Kiranta ya yi kai tsaye ta dauka da wayar da kusa tsinkewa.

"Ya Farha baki san Abbati ba?"

Yadda ya yi tambayar da damuwa yasa ta fasa cigaba da ja masa rai.

"Na san shi." Ta rage murya sannan ta kara da cewa " Kuma ina tunaninsa kullum."

Ajiyar zuciya ya saki tare da lumshe idanu

"To ai ni ne Auwal din. Suna na na gaskiya na fada miki."

Bata san lokacin da tayi dariya ba har tana tunanin ko dan fari ne. Dariyar da ta dinga kurdawa ko ina a cikin Abbati tana saka shi daukar dumi. Tun yanzu yake fatan idan ya sami Farha Allah Ya bashi ita har aljanna. Da wata irin murya mai dadin amo da tsayuwa a rai ya ce

"Ina sonki Ya Farha"

Yadda ya dauke numfashi yana jiran amsarta haka ta dauke nata saboda girman lafazinsa. Ta dade kwarai da cire rai da jin wannan kalmar a kanta.

"Kin barni da faduwar gaba."

"Nima nawa gaban faduwa yake" ta bashi amsa da dukkan gaskiyarta.

"To yanzu ya za ayi kenan? Da sai nan da kwana uku zan zo daukar motata amma na fasa. Tunda gabanki na faduwa gobe zan zo in sha Allahu."

Kunya ta ji ta sake yin shiru har sai da ya tambayeta me yasa bata son yi masa magana sosai. Bai san hira irin wannan gabadaya bakon abu bane a gareta. Kawar da zancensa tayi ta sako wata hirar daban.

"Yaya su Baaba? Don Allah ka ce ina gaisheta."

Sai da ta yi dariya ya ce "ba damuwa don kin bagarar da zancen. Gobe kinga sai ki bani amsa muna kallon juna. Kinga ni na huta tunda dama ba iya fada zan yi a gabanki ba don nima ina jin kunya. Baaba kuma tana lafiya. Zuciyata tana ninka son mai mutunta Baaba. Ki gaishe min da Maminmu."

Katse wayar ya yi ya barta da murmushin da masana zasu gane na sabon shigar soyayya ne.

Sai dai nishadin da take ciki bai dade ba ya rugurguje. Alh. Tahir ne ya kirata sau biyu bata daga ba sai ya kira Mami Khadija ya fada mata sako ta bata. Suna gama magana kuwa ta kirata ta sanar da ita.

"Abbanku ya ce ki same shi a falonsa goma na safe."

Kuka ta soma tun kafin ta gama jin sakon.

"Mami don Allah..."

Daurewa Mami Khadija tayi domin ta san abin da zata fada mata shi ne daidai.

"Wasan buyar da kike dashi ya isa haka. Kije kiji kiran me yake miki"

"Mami?" ta furta da kyar saboda kukan da yaci karfinta.

"Sai da safe Farha."

Ita ma kukan ne ya taho mata shi yasa ta katse kiran.

A daren Farha ta hada kayanta a akwati. Gari na wayewa ta karasa shiryawa. Ita ta tashi Mami Khadija da ta shiga dakinta.

"Gidan Mama zan tafi na zauna har a gama bikin Kawu."

Ta san za a rina dama. Farha can be stubborn idan abu bai yi mata ba.

"Da izinin wa za ki tafi?"

Zubewa tayi a gaban gadon ta marairaice mata.

"Don Allah ki barni in tafi Mami. Idan naji zuciyata za ta iya daurewa inyi magana da Abba zan dawo." Tayi maganar kwalla na zubo mata.

"Au...bama ki da niyar dawowa in an gama bikin kenan?"

"Please Mami"

"Naji. Allah Ya tsare. Kada dai ki manta duk dadi ko rashinsa ba a canjawa tuwo suna."

Kai ta gyada ta mike. Har ta fita bata bar fassara kalaman Mami na karshe ba. Jinjinawa mahaifiyarta ta tayi domin ta fahimci ko da bata fadi me ta gani ba ita ma ta san ko meye. Ita kam bata son fasiki kuma bata jin zuciyarta tana da kwarin daukar cin amanar namiji. Kofa a bude take yayi aure amma banda yawon bin matan titi. Bata fatan abin da zai zo ya gifta har ya sata hakurin zama da mazinaci!

UKU DUWATSUN...

***

Da mukulli Jiddo ta rufe kofarta bayan mai yi mata aiki ta fita ta shige daki. Missed calls din Sarauniya sun fi goma. Sai sakwanni wadanda tun bata bude ba ta san kwanan zancen. Surutu ne da zagi duk akan rashin hadasu da Danladi. Kayanta ta cire bayan ta rurrufe tagogi ta haye gado ta dauki hotuna kala kala wanda muninsu yafi na farko. Ta dai tabbatar bata hada da fuskarta ba. Wayar Danladi ta kira yana gani bai dauka ba sai kawai ta tura hotunan tare da sakon magiyar ya amsa gayyatarta. Ta kara da fada masa nemansa da Sarauniya take yi.

(Ta bani dubu hamsin na baka kayi kudin mota zuwa Abuja. Ladan aikinka zai iya fidda kai daga talauci. Ni da kai duka zamu karo da abin da za ta biya. Sai naji shawarar da ka yanke.)

A kwance yake ya gama karewa hotunan kallo ya karanta sakon nata. A gigice ya tashi har ya barar da dan kofin silba din da matarsa ta ajiye masa ruwa a ciki. Dubu hamsin kuma kudin mota kadai?! Hannunsa kaikayi ya kama yi yana son kiranta amma wata zuciyar ta hana. Wai kada ya nuna mata shi din kwadayayye ne.

Jiddo kuwa da ta tabbata yaga hotunan sai ta kira shi. Da irin salonsu na gogaggun mata take masa magana.

"Danladi mata aka sani da jan aji amma sai gashi lokaci guda kana ta dagula min lissafi. Shin ko dai abin da na turo bai burgeka bane?"

Sai da ya hadiyi yawu da kyar saboda muryar ta tuna masa irin hotunan sannan ya dan yamutsa fuska ya amsa mata kamar ba ya so.

"No ba haka bane. Kawai ina busy ne."

Jiddo ta murmusa. Dan hannu ne babu tantama. Kyale shi za tayi ya ja ajin sannan ta fadi bukatunta.

Danladi ya gama kwanakwanarsa ya mika wuya. Ba wai son zuwa ne baya yi ba tun farko dama. Kawai dai yana tsoro ne ganin cewa matar manya ce. In bai manta ba, motar da ya gyara musu da kayan jikinta babu alamar talauci ko kadan a tare da ita.

"Ku sa min rana amma banda satin nan."

"An gama" cewar Jiddo cike da nishadi.

Jan shi ta dinga yi da hira har ya dan saki jiki. Suna gama wayar hankalinsa ya karkata kan Ayaah. Ita ce irin macen da ya dade yana muradi. Irinsu Jiddo sai dai

aje aci kudi kawai a dawo. Ayaah kuwa su ake kashewa kudin idan akwai su. Dakin matarsa Raiha ya shiga tana zaune da yaransu biyu tana basu kunu.

Aikin sa yana kawo masa rufin asiri daidai gwargwado amma saboda karya da yawon bin 'yan mata ya kasa wadata gidansa. Yau tashi suka yi babu ko sisi a jikinsa sai makota ta shiga ta karbo bashin kunu. Shi ne suka sha da safe, rana da kuma yammacin yanzu da ya gama sanyi kalau.

"Wani abin kake so ne?"

Ta tambaye shi a ladabce ganin ya tsaya a bakin kofa yana ta binsu da kallo.

Tabe baki ya yi kafin ya ce "bani darin da na baki dazu zan dan fita."

Danne zuciyarta tayi ta ciro darin daga cikin riga ta mika masa. Bai ce mata komai ba ya juya abinsa. Ludayin da take bawa yaran kunu taji ya mata nauyi ya sabule daga hannunta saboda bakinciki. Dan kudin da ya bata take cancanawa za ta saya musu awara suci mai dan nauyi da daddare shi ne ya karbe.

Kamar kiftawar ido da bude shi don ko gyara zama bata yi ba ya sake shigowa ya wuce dakinsa. Katin naira dari ya siyo ya saka a wayar ya dannawa Ayaah kira. Yaci alwashin yau zai fara dorata akan manufarsa. Ba zai bar gidansu ba sai ya rungumeta.

*

Wanki take ta kunna rediyo tana sauraron wani shiri da akeyi a tashar Freedom mai suna Sabon Shafi. Shirin yana burgeta matuka domin ana hira ne da mata da suka yi fice a fannoni daban daban. Burinta wata rana ace za ayi hira da Hajara Habu Danmalam, fitacciyar....

Tunaninta ne ya katse ba tare da ta gama tsara matakin da take son kaiwa a gaba ba sakamakon shigowar waya. Daga kai tayi kan dan dakalin da suke ajiye guga inda wayar take taga sunan mai kiran. Da sauri ta goge hannunwanta da zanin jikinta ta amsa kafin ta katse.

Sai da tace hello sau hudu Danladi bai amsa ba. Yana jin ciwon tafiyar kudinsa a banza amma dole ya hakura idan yana son cin wannan yakin. Wani jan numfashi ya yi kamar wanda ya yi muguwar gajiya sannan ya kira sunanta da kwantacciyar murya.

"Ayaahhhh. Me na yiwa mata suke guduna haka?"

Daburcewa tayi da salon maganarsa. A lokaci guda kuma kalamansa suna tayar mata da hankali. Duk yadda akayi matarsa ta kuma guma masa wani abin.

"Mata har nawa ke gudunka?"

"Wadda kika sani dai ta gidana, sai kuma ke da na daukeki wata babbar jigon rayuwata. Kwana nawa baki ji daga gareni ba amma ko dan tes dinnan ya gagara ki ji lafiyata."

Kanta yayi gingirin kamar an dora farantin kwai tana tsoron ya fado ya fashe. Zuciyarta kuwa shawagi ta dinga yi mata a kirji saboda tsananin farinciki. Da tattausan lafazi ta soma bashi hakuri. Da ya san katin yana daf da karewa sai ya katseta.

"Na san dai ina takura miki da matsalolina amma don Allah I am sorry. Bana son Mom ta sani. Ke kadai zuciyata ta amince ta dinga fallasawa sirrinta. Idan kina gida zan zo da anyi magariba."

Cikinsa a take ya bada wani sauti kamar yana rokon shi ma a kaishi gareta ya sami abinci. Shu'umin murmushi ya yi ya dan daga murya,

"Dalin, kin dafa min indomie din ne?" Ya dan yi jim kadan "naji. Allah Ya baki hakuri. Idan na fita zan nema. Kina son wani abu ne na taho miki dashi?" Ana fara warning

na yanzu kudin zai kare ya ce da Ayaah "sorry na barki ina magana. Idan nazo zan kiraki."

Mace mai tunani za ta fassara hirarsu Ayaah da cewa Danladi (Dani) ya cancanci a tausaya masa saboda rashin samun kulawar iyalinsa. Da kudinsa da komai amma abinci ma sai dai ya saya. Mai zurfin tunani kuwa za ta tausaya masa da farko. Idan an gama wayar sai ta koma tunanin dalilinsa na fada mata laifin matarsa. Daga nan za ta gane akwai wata a kasa. Sauran binciken zai nuna mata shi abin yarda ne ko akasin haka.

Wankin da Ayaah bata gama ba kenan. Inda Hasiya take tare da 'yan lallenta taje ta durkusa. Sosai alakarsu tana ta gyaruwa yanzu sai dai duk da haka aure Ayaah take so. Ita dai ta bar gidan ta huta da zugar su Anti Fati kannen mamanta da kuma mitar yayyenta. Sannan ta kula baban nasu ba iya biya mata zai yi ta cigaba da karatu yadda take so ba.

"Anti me za a dora ne? Naga yamma tayi sosai."

Hasiya tayi murmushin jindadi. Canjin da Ayaah tayi yana faranta zuciyarta sosai.

"Kin manta yau Ummita ce a kitchen? Kice tayi mana jallof din shinkafa."

Ta zaro dari uku ta mika mata ta ce a siyo kifi a saka a ciki.

Ayaah ta karba harda godiya ta shiga ciki. Mayafi ta dauko ta tafi ta siyo kifin ko Ummita bata nema ba.

Kifin dari biyu da hamsin ta siyo sai alayyauhu da albasa mai lawashi na hamsin. Sauran kayan bukatar duka akwai a gidan. Albasa ma suna da ita sai da mai lawashin take bukata. Wankesu tayi ta yanka tare da alayyahun ta sake wankewa ta ajiye ya tsane. Ta debo wake yadda take bukata ta dora. Sannan tayi jajjagen kayan miya da citta da tafarnuwa ta soya ta tsayar da ruwan abinci. Kamshin ne yasa Ummita lekowa daga daki. Tun dazu take son fitowa dora girkin ciwon kai ya hana.

Ta dauka Murja ce ta gama kitso ta zo taimaka mata sai ganin Ayaah tayi. Wani dadi ya shigeta na canjin kanwar tasu tayi mata gofiya ta koma ciki.

Da ruwa ya tafasa Ayaah ta zuba shinkafa tare da waken da ya soma dahuwa su dahu tare. Sai da ta kusa gama turara bayan ta rage wutar ta zuba lawashin da alayyahu tare da kifin da ta ciccirewa kaya. Yau ma kafin kowa ya farga ta dibarwa Dani sannan ta kwashe sauran. Tayi sa'ar gama komai kafin a fara kiran sallah. Sai ta fake da alwala ta samu ta wanke fuska taje tayi kwaskwarima.

*

Honorable yaga ranar taimakawa na kasa a lokacin da bai zata ba. Da suka bar ma'aikatar su Alh. Bala, gidan Minista Abdulkarim suka wuce. Tamfatsetsen gida wanda ko lokacin da yake ganiyar arzikinsa bai taba tunanin mallakar irinsa ba. An kawo masa abinci mai rai da lafiya ga kuma girmamawa ta musamman daga maigidan. Matarsa tana Abuja da yara shi kadai ya zo ganin iyayensa da magana da Alh. Bala. Wannan yasa masu hidimar gidan su ma suka zage damtse anata kai kawo.

"Naga kamar umarninka kadai suke bi. Don Allah ka ce kada ta zubawa wallahi na koshi."

Furucin Honorable kenan bayan duk abin da yaci kuma aka sake kawo masa farfafesun jelar saniya.

Abdulkarim ya dagawa mai aikin hannu da murmushi a fuskarsa sannan ta fasa zubawa. Kallon Honorable ya yi yana mai kara jin tsoron Allah ta yadda rayuwa take jujjuyawa ga bayi.

"Gani nayi duk ka rame. Don Allah ka sake cin wani abu."

Honorable ya tuntsire da dariya "banda abinka kuma sai aka ce a cin abinci guda zan yi kiba?"

Dariya suka yi tare suka taba hira sannan Honorable ya tashi zai tafi. Abdulkarim ya ce bai san zance ba. Yana son jin me ya faru dashi tsayin lokaci har rayuwa ta koma haka.

Tiryan tiryan ya labarta masa komai. Ba kuma don maula ba sai don dalili guda wanda ya fada masa kamar haka,

"Duniya bata da tabbas Abdulkarim. Ba komai ne yake zama tabbatacce ba a rayuwa. Saboda haka ka daure ka rike gaskiya a duk inda ka sami kanka. Idan duniya ta ciyar da kai gaba fiye da nan sai ka dinga kallon kasa kana kara godiya ga Allah. Bana maka fata amma ko da za ta kawoka inda ta ajiyeni to kada ka karaya da samun rahama. Allah ba Ya dorawa bawa abin da yafi karfinsa. Ba zan boye maka ba da farko na shiga kunci saboda rashin sabo da babu ga Abbas a kwance. Da ilimina na fara hasashen ko auren Hasiya ne ya jaza min talauci. Sai gashi ashe ita za ta rike gidana da 'ya'yana. Duk zafin talauci idan Allah Ya baka mace ta gari to tabbas Ya kwashe maka radadinsa."

"Zan so ganinta. Muje da kaina zan kai ka gida." Cewar Abdulkarim, zantukan suna shigarsa da kyau.

Honorable ya dage baya so. Shi ma Abdulkarim ya dage sai yaje. Daga nan ya tashi ya bi wata hanya zuwa bangarensa. Da envelop ya dawo ya mika masa.

Allah Sarki! Yawun bakinsa ya kafe. Idanuwansa suka kada suka yi ja....a wani shudadden lokaci shi ne yake bawa Abdulkarim. Yau duniya ta nuna masa cewa tables can always turn. (Ya Allah Ka rabamu da talauci da karayar arziki. Duk abin da zai taso mana na kudi Allah Kasa mu fi karfinsa.)

"Duk ni kadai? Basu yi yawa ba?" Ya ce da murya tana rawa. Raba kudin ya yi gida biyu ya mika masa rabi.

Abdulkarim sai yaji wani abu mai nauyi a zuciyarsa. Honorable Habu yafi karfin wulakanci a wurinsa. Laifin kansa ya gani da ya yi sakaci da zumunci har ta kai bai

san mawuyacin halin da tsohon ubangidansa yake ciki ba. Ace har ya kai matsayin da dubu dari za ta kawo masa kwalla a ido.

"Kada kayi min haka Honorable. Ban kyauta ba a baya na sani amma ka dauka Allah ne bai shirya haduwarmu ba sai a yanzu da muke sa ran alkhairi ya biyo bayanta."

"Haka ne. Nagode.."

Godiyar ma katseta Abdulkarim ya yi suka fita zuwa mota tare. Wannan karon daga su biyu a bayan mota sai direba. A hanya ne yake tambayarsa irin sana'ar da yake son yi. Lokaci ya ja babu batun komawa siyasa. Idan an manta da mutum sai ya zo da kwakkwara kuma kyakkyawan shiri tafiyar take sake armashi. In ba haka ba kudinsa kawai zai yi asara.

"Zan yi shawara da Hasiya sai na fada maka" Ya ce da murmushi a fuskarsa.

Abdulkarim ya kama dariya sannan ya ce "Allah Yasa bata aurar da duka 'ya'yanta ba ta bani guda. Don naga alama idan na auri rainonta kila sai nayi shugaban kasa."

Honorable ya girgiza kai "abin kuma harda zolaya?"

Abdulkarim bai ce komai ba. Ba kuma zai ce ba har sai yaje gidan ya ga 'yan matan da ya sani a baya tun suna yara. Kudurcewa ya yi a zuciyarsa indai ba rashin tarbiya wanda baya tsammani ya gani ba ko su suce basu son aurensa ba zai nemi guda.

***

Mardiyya da Sauda ne tare da Suhaib da Lilu tsaye a jikin motar Abbati. Sun rako su bakin mota shi da Munzali bayan sun shiga sun gaisa da Mami Khadija. Mama Nasima bata nan kuma Mardiyya sai addu'a take yi su yi su bar gidan kafin ta shigo.

Sau biyun da ta zubar da kimarta a gaban Munzali bata yi a gaban yayyenta ba. Ba kuma ta son a fara daga yau.

Hirar motoci suke yi wadda Lilu da Munzali ne karfinta.

Lilu ya shafa motar yana binta da kallon bege

"Ni dai ba don yau za ku tafi ba ai da na dana ko zuwa karshen layinmu ne in kashe arna."

Keyarsa Suhaib ya kwade ya kuma ce idan bai kama kansa ba sai ya fadawa Mami. Mardiyya da Sauda zasu yi dariya ya hade rai zai yi kaza huce kan dami.

"Wai me ma ya fito daku ne? Wurinku suka zo? Ku koma ciki."

Munzali ne ya shigar musu domin Abbati kamar baya wurin. Hankalinsa yana kan hanya yana dakon ganin ta ina Farha za ta bullo.

Da sauri Munzali ya ce "Ya za ka korar min kanne?" Dan nesa kadan da inda suke tsaye ya nuna da hannu yana mai cewa "In ganki mana Diamond girl."

Karashen maganar ya yi ne idanunsa a cikin na Mardiyya. Kawar da kai tayi da sauri gabanta na wata irin faduwa ta daban. Bata san yadda akayi yau take jin Munzali a ranta haka ba. Tun dazu take satar kallonsa sai ta ga shi ma ita yake kallo.

Juyawa tayi za ta gudu saboda kunya Sauda ta rike mata hannu. Shi kuma gogan ya basar kamar ba daga bakinsa maganar ta fito ba. Abbati ma dake son tambayarsu game da Farha amma ya kasa sai da yaji kunyar.

Wato duk yanzu halinsu yake fitowa game da mata da suka hadu da wadanda suke so.

Suhaib ma dai daskarewa ya yi don kusan yafi kanwar tasa jin kunya. Gyaran murya ya dinga yi ba kakkautawa don ya kasa magana. Lilu kuma ya dinga kikkifta idanu na shakiyanci sannan ya ce,

"Diamond dai da na sani mai shegen tsadar nan ka kira Mardiyya?" Hannu ya sakalo a kafadarta ya tako kusa da Munzali dake ta murmushi ya tsaya da ita a gefensa. Hannuwa ya hada kamar mai shirin daukar hoto yana aunosu ta cikin zagayen da yatsunsa suka bayar. Ya dawo kunnenta yayi magana kamar rada amma kowa na ji

"Baby Sis kin matso mana class wallahi." Ya koma ga Munzali " Kai ma Alh. Munzali ka more. Hummm don ma kada ka ce yabon kai da sai in ce duk 'yan matan Kaduna babu kamar na gidanmu."

Hannun Mardiyya ya fara kamawa suka ti musabaha sannan ya saki ya koma kan na Munzali yana faman murmushi gami da nanata kalmar "congratulations."

Suhaib ji ya yi kamar ya daga shi a kafada su bar wurin. Lilu ba ya jin magana ya ce a ransa kafin kuma a zahiri ya biyo shi. Zillewa Lilu ya yi bai bari ya kama shi ba ana ta dariya.

"Baka da kunya ko kadan." Suhaib ya furta yana fuskantar bangaren Abbati. Nauyin Munzali ne ya kama shi saboda a gabansu yake yiwa Mardiyya wani irin kallo. Gashi sun girme shi sosai balle ya yi irin jan idon nan na yayan budurwa.

Abbati kafadar Munzali ya ture da tasa har sai da yasa shi rankwafawa yana mita.

"Munzalin ma ai ba kunyar gare shi ba da ya yi mata magana a gabanmu."

Daure fuska Munzali ya yi cikin wasa yana hadawa da hararar Abbati.

"Ai dama ba ayi maka gwaninta. Sharar fage nayi maka don duk su watse kafin ta fito."

"Wa?" Lilu da Suhaib suka hada baki wurin tambaya.

"Ya Farha" Sauda da Mardiyya suka basu amsa a tare.

Suhaib bai san lokacin da wani irin murmushi mai cike da tsantsar annashuwa ya bayyana akan fuskarsa ba. Farha ce yau da kunnuwansa yaji ance namiji yana jiranta? Ganin murnar na neman yi masa yawa kuma bashi da tabbacin me yake faruwa sai ya ce,

"Yanzu duka nan dama zance ku ka zo ba daukar mota ba?"

Sauda da Lilu har ma da Munzali sai dariya.

"Diamond girl kanwata ce kuma abokiyar shawara ko?" Munzali ya yi magana yana kannewa Mardiyya ido sannan ya dora da cewa "wasu ne dai har a cikin bacci za ka ji suna kiran Ya..."

Bakinsa Abbati ya rufe da hannu su Lilu aka sami nayi sai dariyarsu suke. Munzali na kokarin kwatar kansa Abbati kuma yana faman yi masa alkawura akan idan ya kama bakinsa zai cika masa su.

"Zan tuka motar har Kano!" Ya fadi abin da ya san zai yiwa Munzali dadi.

A take Munzali ya daina kokarin janye hannun Abbatin ya nutsu. Yana sakinsa yasa dariya. Da gaske wautar Abbati bata wani buya lokuta da dama.

"Riba biyu kenan. Kaga dai kowa ya fahimci menene baka son na fada. Alkawari kuma dole ka cika tunda ban fada da bakina ba" Mukullin ya dorawa Abbati a tafin hannu ya yafito Mardiyya da hannu.

"Kina ta sani dibar kunyar Ya Suhaib kuma kin ki zuwa."

*

Gate din gidan aka wangale direban Alh. Tahir ya shigo ciki. Wurin ajiye nasa motocin ya dan yi nisa da inda yake hango 'ya'yansa da wasu baki biyu suna dariya. Motar da ya gani a kusa dasu kuma a bude ce tasa ya gane su waye. Mami Khadija bata tauye masa hakkinsa na maigida ba, ta sanar dashi game dasu tun ranar da suka ajiye motar a gidan.

"Ga sirikinku nan" cewar Lilu yana yin gaba wurin mahaifinsa.

Mardiyya da Sauda ma da sauri suka mara masa baya suna kiran "Abba" tamkar wanda ya yi tafiya. Kafin su karasa ya ware hannuwansa ya rungume kowacce a bari daya. Kirjinsa yaji ya takure saboda rashin Farha. Indai su uku suka zo tarbarsa to ita a bayansa take tsayawa ta riko wuyansa da hannuwanta biyu. Daga nan haka suke raka shi har daki. Wani lokacin ma su taya shi cin abinci. Lilu kuma idan yana gida shi yake dauko masa jaka da wayoyi. Yanzu ma ya dauko harda babbar rigar da ya bari a motar ya ratayota a kafada. Tun tashinsu Suhaib baya zuwa sai suke ganin kamar irin abin nan ne na babban yaya. Farha kuma tunda taga bidiyon nan take kirkirar abin da zai hanata fitowa idan ya dawo ko ya aika a kirata.

Yanayin soyayyar uban da 'ya'yansa ya burge Munzali da Abbati matuka saboda basu tashi a haka ba. Gara ma Abbati ya san nasa mahaifin yana dan kokartawa amma babu zancen wata runguma ko sakin fuska makamanciyar wannan. Duk ranar da suka kwatanta haka karshenta Mal. Sa'idu sai ya tsire masa uba. Shi kuwa Munzali ina ma suka hadu balle a nuna an damu dashi.

"Manyan yayye basa zuwa oyoyo?"

Munzali ne ya tambayi Suhaib amma Abbati ne ya lura da yanayinsa a lokacin da yake bayarda amsa.

"Mu ai mun girma an barwa kanana"

Ba da niyar nuna musu komai ya yi ba amma bakidaya annurin fuskarsa ya bace. Irin kallon da ya yiwa mahaifin nasa ya kawar da kai Abbati ya kasa fassarawa. Kamar kallon tsana, kiyayya ko jin haushi. Kallo mai nuni da cewa akwai wani kwamtaccen abu na bacin rai tsakanin uban da d'ansa. Bai bar tunanin ma ya zauna masa ba ya kawar dashi ta hanyar sakin fuska suka karasa wurinsu shi da Munzali.

Da fara'a ya tarbesu ya kuma dinga jansu da hira. Dama ransa a bace yake daga office amma ganin yaransa kadai ya wanke masa komai. Wata sabuwar ma'aikaciya suka dauka shi ne daga zuwanta ta fara nuna masa alamun tana so su kulla mu'amala. Matsalarsa da Farha ta janyo masa rashin kwanciyar hankalin neman yarinyar duk da ya kwadaitu da ita tun farkon zuwanta. Abin da ya bashi haushi kuwa bai wuce kukan da ta saka masa a office ba bayan ta gaji da dabarunta ya daka mata tsawa ya ce ta fita.

"Amma sauran duk sun ce ba haka kake yi musu ba. Ni me na rasa?"

Wannan magana ta hana shi hadiyar yawu a lokacin saboda dacin da ya taso masa. Sauran da take nufi ba wasu bane illa matan kamfanin nasa da ya nema a baya. Kenan duk kudaden da yake kashe musu da gargadin su rike bakunansu ya tashi a iska. Suna hirar da juna harda yi masa cune...in ba cune ba ta ya akayi yarinyar ta san ta nemi jan ra'ayinsa tunda ba shi ya fara nemanta ba? Har suka iso gida yana tunanin mutum nawa aka fadawa? Mutane nawa ne suke yi masa kallon tsirara mara kima ba tare da ya sani ba?

Farha da baya tsammanin gani a cikinsu ya tambaya Sauda ta fada masa tana gidan Mama.

Ba shi kadai yaji babu dadi ba harda Abbati da suka yi alkawarin haduwa yau.

Alh. Tahir murmushi ya yi ya ce "ta fi ku dokin bikin nan naga alama."

"Abba bata fada maka za ta tafi ba?" Mardiyya ta tambaye shi don tayi mamakin tambayar tasa.

"Yau meeting muka yi tayi amma naga missed calls dinta zan kira."

Sallama ya yiwa su Munzali ya wuce nasa bangaren kafin a kara wata tambayar da za ta fallasa karyar da ya musu. Abbati kam jikinsa ya yi sanyi tunda bata sanar dashi ba kuma ta san zuwan a yau dominta ne. Farha ta fi karfinsa ta kowacce fuska idan ya dubi tarayyarsu. 'Yar masu kudi duk da dai ya san indai don kudi ne ba zai wahala ba. To amma cikakkiyar 'yar boko ce mai tsaftataccen asali. Sirrin rayuwarsa ya sanya bai sami damar jin bacin ran kin fada masa ba. Zuciyarsa dai ta raya masa cewa bashi da wannan matsayin. Tunani ne ya yi masa yawa sai kawai ya yi sallama dasu Suhaib ya shige mota bangaren direba . Munzali dake son magana da Mardiyya sai ya fasa ya ce zai kirata.

"Mutumina kayi hakuri. Karshenta inda taje din ba za ta iya haduwa da kai ba shi yasa bata fada maka bata nan ba ko ta ce ka biyota" Munzali ya fadi a kokarinsa na kwantar masa da hankali bayan ya zauna.

Da sanyin jikin da bai so ko Munzali ya gani ba ya ce "Kar ka damu."

Suna tafiya Suhaib ya tafi wurin Mami Khadija. Albishir ya yi mata don yafi kowa sanin damuwarta akan Farha.

"Amma Mami yarinyar nan don wulakanci sai ta tafi gidan Mama bata fada masa bata nan ba? Wallahi duk yadda yaso boyewa sai da na gane rashin jindadinsa."

"Ai kuwa zan gamu da ita. Ta barmu da damuwa Allah Yasa ba ita take korarsu ba muke tunanin su suke kin zuwa."

Zancen yana da mata da kuma tsoron kada a sami matsala a gaba ta fara yi masa suka shiga wata hirar daban.

A waje kuwa sai da kowa ya tafi sannan Lilu ya nufi dakin Abbansu da kayansa da ya dauko a mota. Tunawa ya yi da katin daurin auren wan abokinsa a dakinsa ya juya. Ya san ba zuwa zai yi ba tunda rana daya ne da na kanin Mami da za ayi a Kano. Duk da haka amintarsa da abokin nasa tasa yana son Abban nasa ya sani kuma ya kira baban angon ya masa fatan alkhairi.

Akan gadonsa ya ajiye kayan Alh. Tahir ya bude durowar gaban madubi ya dauko envelop din katin. Jakar office din ya fara dauka sannan wayoyin. Ya dago babbar rigar biruka da wallet suka fado daga aljihun jakar. Guntun tsaki ya yi na bata lokaci ya duka ya daukosu. Hannu kawai ya zura a aljihun ya mayar dasu sannan ya kama zip din zai ja sai yaji ya rike yaki motsawa. Jibge kayan hannunsa ya yi ya juyo da jakar yadda zai ga zip din da kyau. Abu ne kamar takarda ya makale yasa taki zuguwa. A lokacin da ya zube kayan hannunsa akan gadon ne wayar Alh. Tahir wadda yake amfani da ita wurin kiran 'yan matansa ta fado daga aljihun babbar rigarsa. Lilu bai kula ba ya gama gyara zip ya kwashe wayoyin da yazo dasu a hannu ya yi gaba.

Alh. Tahir bai tashi sanin wayar bata nan ba sai dare bayan Jiddo mai girki a ranar tayi bacci. Hankalinsa kuwa a take ya tashi. Ko a office ba zai so barinta ba saboda gudun fadawa hannun da zai ji kunya, ballantana kuma gida. A daren nan wurin daya saura ya fita yaje motar ya dudduba tunda ya san a hanya ma ya amsa waya da ita.

Motsin wucewarsa Lilu yaji a lokacin yana kallo ya tashi ya leka taga. Ya yi mamakin me Abban nasu yake nema a mota a daren. Kamar ya fita tambayarsa sai yaga ya koma. Laptop dinsa ya kashe ya kade bargonsa ba tare da kula da wayar da ta fado daga kai ba ya haye gado ya kwanta.

Wurin karfe tara ya fito zai tafi makaranta yaga Alh. Tahir tsaye da jallabiya ga direbansa yana ta bankade mota yana dube dube. Karasawa ya yi ya gaishesu duka.

"Abba me ake nema ne? Jiya ma cikin dare na ganka kana duba motar nan."

Murmushin dole Alh. Tahir ya yi saboda kada ya nuna ya damu da wayar.

"Babu komai jeka abinka" ya ce masa. Shi kuma direban ya ce "wayar Alhaji" a lokaci guda.

"Abba ka duba. Jiya duka wayoyinka na kawo maka daki."

Kamar gaske Alh. Tahir sai ya saki fuska "bari naje na duba. Sai ka dawo."

Ana rufe gate din gidan ya dawo da idanunsa da suke nuna tsantsar bacin rai ga direbansa. Hankalinsa ya matukar tashi.

"Idan wayar nan ta fada hannun wani saboda sakacinka a bakin aikinka."

Direba cigaba da bincike ya yi yana mamakin wannan abu. Shi ko kalar wayar ba zai ce ya sani ba amma an dora masa laifin batanta.

Ana gobe zasu tafi Kano Mami Khadija ta kafa sharadin duk wanda bai gyara dakinsa ba babu inda zai je. Kamun amarya ne wanda aka hada da mother's eve da dinner za ayi a Kanon. Babu mai son a barshi da kallon hotuna yana cizon yatsa. Ita kanta ta san da wa take dama. Lilu ne dakinsa sai tayi da gaske yale gyarawa. Alh. Tahir ya so masu aiki su dinga gyara musu ta ce sam bata yarda ba. Tana barin wurin ya fice daga gidan. Shawarma ya siyo guda biyu manya manya da robobin yoghurt ya shige wurinsu Sauda. Mardiyya ce ta fara jin kamshin shawarmar ta tashi da murna za ta karbi ledar ya boye abarsa.

"Kun dai ji me Mami ta ce. A gyara min palace dina a ci dadi. Bari na saka muku yoghurt din a fridge kafin ku gama."

Da gudu gudu suka bi bayansa. Wasu kaya ya dauka a leda ya tafi dakin Suhaib ya shirya. Dinner din gidansu abokinsa ya tafi.

Sauda ta fada toilet aka bar Mardiyya da uban shirgin kayansa. Tana cikin ninki taci karo da waya a kasan gado. Lilu bai san da ita ba balle ya kula da faduwarta. Daukewa tayi ta jona masa tunda taga chaja a jikin bango. Da suka gama aikin ta kunna masa kafin ta fita. Shi kuma da ya dawo ko bi ta kan wurin bai yi ba ya kwanta saboda gajiya. Da safe bayan sun gama shiri sun dauki hanya Yumna ta dinga kiran wayar.

***

HUƊU KAFAFFUN...

***

Flashing ya kai shida Danladi ya yiwa Ayaah. Tsabar kwarewa wasu a ciki ma bata jin karar wayar sai dai taga haske kamar walkiya ya bace. Hakura tayi da son dauka ta kira shi da kanta. Abin da ya fara cewa yana daukar wayar shi ne,

"Gaskiya kuna da matsalar netwok a unguwar nan. Zuwana nan na kira ki ya fi sau goma. Har na fara tunanin turo yaro a kira min ke tunda ba zan iya tafiya ban ga murmushinki ba."

Da sanyin murya ya yi magana. Cikin wani irin yanayi mai sa mutum ya ji kamar ya aikata gagarumin laifi. Ayaah taji babu dadi ta shiga bashi hakuri duk da a bangare guda tana cike da farinciki game da kalamansa. Da ya nuna mata kamar komai ya wuce sai ta ce ya ajiye mota a bayan layinsu za ta zo nan ta same shi.

"Yanzu Babanmu ya kira Anti cewa yana hanya tare da bako. To ban sani ba ko bakon da zai kai ciki ne ko mai tsayawa a soro. Kuma kaga baku taba haduwa ba zai fi kyau ku hadu yana shi kadai."

Cije lebe Danladi ya yi ransa na kuna. A soron nan nasu mai dan duhu ya so ya fara koya mata gurbatacciyar soyayyarsa. Gashi bai sami motar da tayi masa a garejin ba. A ina zai sami wannan damar idan suka hadu a filin Allah? Da muryarsa da ya

kware wurin kwantarwa domin ya sanyawa 'yan mata tausayinsa ya yi mata magana.

"To babu komai Ayaah. Ba zan so na takuraki ko na sanyaki cikin yanayi mara dadi ba. Banda zuciyata da ta kasa sukuni saboda tunaninki da na hakura sai lokacin da kike so na zo."

Numfashi taja wanda ya bashi damar yin murmushin samun nasara tun kafin ta furta ta bakinta. Yadda yaso haka ta ce za ayi. Duk da tana jin nauyi haka ta daure taje ta fadawa Hasiya za tayi bako. Murmushi Antin tasu tayi gami da 'yar tsokana.

"Gilashi zan saka domin na tantance ko ya cancanci zama surukina. To amma wani hanzari ba gudu ba. Ki bashi hakuri ya jira zuwa gobe. Kinga Babanku yana hanya da bako."

Ko kadan Ayaah bata son batawa Dani rai. A tunaninta zai fassara rashin sauraronsa daidai da abin da yake fada mata matarsa tana yi. Zai shiga damuwa idan basu hadu ba kuma bata son haka.

"Anti ko inje gidan Mal. Tasi ya sameni a can sai na bashi hakuri tunda ya riga ya zo?"

Katangarsu daya da ta gidan Mal. Tasi din. Yadda ta marairaice fuska sai Hasiya ta amince. Dakin Abbas ta koma suna hira da Murja mai bashi abinci. A zuciyarta take tunanin lallai Ayaah tana son bakon nata. Za ta sanar da Honorable tun wuri ayi binciken da ya dace.

Ayaah kuwa da saurinta ta sake kiran Dani ta fada masa inda zasu hadu. Ba haka yaso ba amma ya fiye masa waje. Tana cikin gaisawa da matar Mal. Tasi tare da fada mata abin da ya kawota taji sallamarsa. Wani iri ta dan ji tunda ta zata zai kirata ne. Da babu alaka mai kyau tsakanin gidan da nasu kuma ba ayi mata izini ba haka zai zo kenan? Ta tambayi kanta. Haka nan dai ta tashi da ledar da ta sako madaidaicin filas din da ta zuba masa abinci. Tana doso soron kamshi ya dinga

hawa kanta. Yau ma turaruka 'yan duri ya bulbula sai dai hannu ya so zarcewa. Kamshin ya yi yawa har yana neman sakawa mai shaka mak'ak'in wuya.

Suna hada ido ta manta da komai sakamakon murmushin da ya sakar mata. Yana da nashi kyawun amma babban abin da ya zame masa jari bai wuce yanayin jikinsa ba. Ga tsayi ga kaurin da bai kai a kira shi kiba ba. A idonta gani tayi kamar ya fad'a. Haushin matarsa ya kamata. Ta yaya mace za tayi sake mijinta ya dinga ramewa saboda rashin kulawa da abinci?

"Mom dina tana gaishe ki"

Rausayar da kai tayi gefe tana murmushin jindadi ta ce "ta sanni ne?"

Dariya ya yi mata yana mai cewa babu wani abu nasa da mom din bata sani ba.

"Idan ta dawo daga Dubai har gida zamu je ki gaisheta."

Ayaah sai tayi murmushi. Ina ita ina zuwa gaishe da uwar saurayi? Ba Anti Hasiya da Babansu ba ko su Anti Fati da kakarta Larai sai sun kusa yankata. Yawo ba tarbiyarsu bace. Idan ya sake tayar da zancen a gaba za ta kirkiro hanyar fitar da kanta don babu inda za ta je.

Ledar hannunta ta mika masa ya dinga godiya da shi mata albarka. Harda cewa wai ya akayi ta san yana jin yunwa? Filas din wan can karon da na yau ya yi mata alkawarin kawowa duka a washegari.

Wurin karbar ledar ne ya samu ya hada da hannunta ya matse. Gabanta taji ya yi mummunar faduwa taja hannun da sauri amma ta kasa kwacewa saboda ya rike gam. Ja ta sake yaki saki sai ma wani irin shafawa da ya dinga yi a hankali yana mai bin kwayar idanunta da kallo da nasa da suka yi alamun tausayi. Ilahirin jikinta babu inda baya rawa kamar mazari. Cikin dabara ya rage tazarar dake tsakaninsu.

"Ki dago ki kalleni Ayaah" ya ce a kasalance.

Kasawa tayi sai girgiza kai da take yi tana son cewa ya saketa. Danladi sai ya saka yatsunsa biyu ya dago kanta. Runtse idanu tayi da sauri taji ya yi karamar dariya.

"Kunya ki ke ji? Gashi ni kuma mutum ne mai son kulawa. Kulawar da na rasa a gida. Ina fata da addu'ar ki cike min wannan gurbin ki hanani tunawa akwai kowacce mace bayan ke. Idan kin amince min zan yiwa Mom magana kawunnai na su zo ganin Baba."

Runguntsumi sunan abin da Danladi ya yiwa Ayaah domin yaji dadin isar da mummunan kudurinsa. A lokacin da yake son bude mata ido da haramtacciyar mu'amala ya kama zuciyarta a hannu ta hanyar nuna mata yana sonta. Banda haka ya hada da maganar aure da mata ke so a wannan zamani. Sannan ya rufeta ruf da ya nuna mata cewa za ta zo gidansa a matsayin mai share hawaye. Wannan tunani ke sanya mata mugun tausayin namiji da ganin ba zai rayu babu su ba.

Da kyar ta iya mallakar tunaninta ta ja jikinta baya. Muryarta ko fita bata yi sosai ta ce,

"Ka sakar min hannu don Allah. Kaga babu kyau."

"Nima ba zan so yin abu mara da ke ba. Kiyi hakuri" ya ce yana sakin hannun.

Ko sallama bata yi masa ba ta fita daga soron. Ya kwashe da dariya

"Kin kusa samuwa."

Ficewa ya yi abinsa da ledar abinci ya tafi gida. Yana zuwa ya bawa Raiha yana wani cin magani.

"Sai ki saki ran ai. Baki san irin kokarin da nake domin samar muku abinci ba. Don na karbi darin dazu ki ke ta kumbure kumbure. Ki zuba min ku ci sauran"

Bude filas din tayi ta ganshi shakare da abinci sai kamshi yake. Cikinta ya bada wani uban sautin yunwa. Da sauri ta samo faranti ta dibar masa sannan ta taso yaranta tana basu tana ci. Tambayar inda ya samo abincin bai zo mata ba don ta zata sayowa ya yi.

*

A dakin Abbas iyalin Honorable Habu suka hadu ya nuna su ga Abdulkarim wanda tausayin Abbas ya kusa saka shi kuka. Addu'ar samun lafiya ya yi masa tare da jaddadawa Honorable lallai ranar litinin a mayar dashi asibiti. Duk abin da ake ciki a sanar dashi. Hasiya tsabar farinciki sai da tayi kuka. Da zai tafi tayi masa tayin abinci sai ya ce a zuba masa ya tafi dashi. Dan filas din da yake madaidaici mai kyau shi Ayaah ta kai wa Danladi. Aka yi neman duniya aka rasa. Murja sai rantsuwar ta wanke shi take yi. Hasiya ta ce babu komai su bar maganar kada bakon yaji. Na maigidan ta saka a leda aka bashi. Bayan tafiyarsa ne ta rutsa Ayaah a kitchen ta tambayeta inda ta kai shi.

"Lokacin da zaki fita wurin bakonki na ganki da leda da abu kamar shi sai dai ban zata abinci ki ka diba ba shi yasa ban miki magana ba."

Sunkuyar da kai Ayaah tayi. Hasiya ta daure fuska saboda bata so hasashenta ya zama gaskiya ba.

"Na zata mun wuce wannan matakin Ayaah. Kin sani sarai rowa ba halin gidan nan bace amma ba zan lamunci yiwa saurayi girki ba! Wato dalilinki na karbar girkin Ummita kenan? Bai ji komai ba ya karbi abinci a hannunki ko mahaifinki bai taba gaisarwa ba?"

Tuni zuciya ta soma tunzurata. Ba za ta iya jure kalamai marasa dadi a kansa ba. Idan ba a tayata tausayinsa ba ai bai dace a aibata shi ba.

"Anti matarsa ce fa bata girki. Shi ne na zuba mishi ba roka ya yi ba. Bata yi masa komai ko ya roka sai taga dama."

Hasiya sai ta hadiye fadanta ta kirkiro murmushi ganin abin ya girmi abincin da ta bayar.

"Kin kyauta da ki ka taimaka masa amma nan gaba ki dinga tambayata kinji ko? Kuma ki ce lallai zuwa na gaba ya zo mu ganshi."

Ayaah sai murmushi. Tasa hannu ta rufe fuska sannan ta tashi a guje tana yiwa Hasiya godiya. Ita kuwa bayan tafiyar Ayaah daki ta koma ta rafka tagumi. Gabadaya saurayin bai yi mata ba daga jin furucin Ayaah. Maza masu tonawa iyalansu na gida asiri ba mazan kwarai bane mafiya yawan lokuta. Ta kuma fuskanci ya riga ya fara dasa mata wani tunani. Tashi guda idan ta nemi rabasu za a iya samun matsala. Gida za taje suyi shawara da Salima don ta fita fahimtar halayyar yara. Shawarar data bata kwanaki ita ce ta taimaka wurin kara kusantasu da juna.

***

Ginin shopping mall din su Abbati ya yi nisa. Hankali kwance komai yake tafiya yadda suke so. Ga tafiyarsu Italy asibiti tana ta matsowa. A lissafi nan da kwanaki goma sha bakwai zasu tashi. Suna fata idan an dace babu wani abu da zai yi saura a tare dasu na bukatar jinsinsu. A gefe guda suna cike da farincikin daina jin motsin Shazali. Tun zuwan da Munzali ya yi gidansa ya masa dukan nan akan tafiyar Abbati bai sake nemansu ba. A zatonsu an rabu kenan...

Yau ta kama Alhamis suna site din gininsu tare da masu aiki ana ta lissafin kudaden da zasu kawo domin siyan wasu kayan aikin. Hankulansu sun raja'a kan abin da ke gabansu wayar Abbati ta soma ringing. A hannunsa take ya juyo da ita yaga sunan Farha ya bayyana a screen din. A take zuciyarsa ta doka dan tsalle sai kuma ta koma ta kwanta. Tun zuwansu Kaduna da bai hadu da ita ba yake kiran wayarta a kashe. Yau kwana biyar sannan za ta kira shi. Yana son dauka yana jin tsoron me za ta ce. Muryar Munzali yaji wanda ya zuro kai ta kafadarsa.

"A haka dai kamar za kayi abin arziki amma daukan waya ya gagareka. Tsoron me kake ji ne?"

"Ni kar ka kara min tension ka matsa ka bani wuri" Abbati ya bashi amsa yana kokarin matsawa gefe domin yaji dadin amsa wayar.

"Ita ma fa tana sonka"

Tsayuwa Abbati ya yi ya juyo ya kalli Munzali da murmushi kamar Farha da kanta ta fada masa.

"Ai fa na kasheka da dadi to dauki kada ta kuma tsinkewa" Munzali ya ce yana kara yi masa dariya.

"Kaima ka ce wani abu. Bari na sallameta zan gamu da kai."

Gefe ya matsa don idan Munzali ya saka shi a gaba kila hirar ba za tayi armashi da kyau ba. Yana dauka yaji zazzakar muryarta mai taushi tana magana.

"Ya Auwal"

Shiru...Abbati ya sake nutsewa cikin kogin son Ya Farha.

"Ko dai wrong number na kira?" Tayi tambayar da murmushin da yake kan fuskarta tun lokacin da ta yanke shawarar kiransa da sunan gaskiyarsa idan ya dauki wayar.

"Ki ka ce baki san shi ba" Abbati ya fada a hankali da ya rasa me zai ce.

"Na san shi. Kararsa ma na kawo maka"

Sai da ya jingina da bango ya cigaba da sauraron bayaninta. Korafi tayi masa na rashin nemanta ranar da yaje Kaduna a wurin 'yan uwanta. Ta tabbata da ya yi

hakan dole zasu kai shi gidan kakaninta. Ita kuma wayarta ce gida na taro aka nema aka rasa a ranar. Ba ita tayi sabuwar waya ba sai da safe kafin su taho Kano. Kin fadawa Alh. Tahir wanda zai saya mata sabuwa a guje tayi. Sai da safen Mami Khadija ta bata kudi ta saya.

"Kina nufin iskar gari daya muke shaka? Shi yasa yau nake jina daban."

"Uhummm. Wane canji aka samu?"

"Iska mai dadi, gari yana kamshi, zuciya kuma sakayau."

Farha sai ta kama dariyar yadda yake magana. Kwatancen inda suka yi masauki ya nema ta ce ba za ta iya gane komai a hanyar ba. Wata 'yar uwarsu ta samu 'yar gidan da suke tayi masa kwatancen. Hira suka yi inda take fada masa daurin auren kanin Maminsu ne za ayi ta kuma gayyacesu. Hoton IV din za ta tura masa ta whatsapp don bata san unguwannin Kano ba.

"Idan kun fita ki dinga kallon hanya tunda zama ya kusa kawo ki."

Kunya kuwa ta kamata ta ce "Ni sai anjima".

"Mu jima da yawa Ya Farha sarkin kunya. Yau dai tunda bikin na yamma ne ba zan zo ba. Amma gobe da jibi kafin ku koma in sha Allahu zan zo."

*

Anyi kamu ranar Alhamis din tare dasu Mami Khadija da suka iso ita da sauran yaran. Ranar Juma'a kuma sai bayan magariba za a tafi wurin dinner. Farha ta sami Lilu tayi masa famfo akan ya tambayi Mami ko zasu sami kati guda biyu tunda event din card admit ne. Shakiyanci ya yi mata kuwa son rai tana shanyewa sannan

ya tafi wurin Mami. Yana gama fada mata zancen da ya tsara ta girgiza kai tana murmushi.

"Dama kai ai ko ba aiko ka aka yi ba nayi tunanin za ka iya nema musu."

Shafa kansa ya yi yana dariya "wallahi Mami don ba ki yi musu kallon kwaf bane amma sun hadu."

"Allah Ya tsareni da yi musu kallon kwaf" ta ce tana mikewa da dariya. Babu wanda ya san irin farincikin da take ciki sakamakon soyayyar da taji akwai a tsakanin Abbati da Farha.

Sun yi sa'ar samun katuna a wadace daga wurin dangin amarya masu shirya dinar. Hakan kuwa ya faru ne saboda suma zasu yi tasu a Kaduna idan an kai amarya. Yadda suka basu da yawa shi ne aka ramawa kura. Guda biyun ta bashi ya tafi yana murna. Suhaib ya kaiwa domin su ji dadin karbar gayyatar shi kuma ya kira ya fada musu.

*

Kafin lokacin masallaci dama Munzali yake da nufin zuwa dauko Qibdiyya yau. Tunanin zuwansu dinner din gashi Kande bata dawo ba sai washegari sai ya kira Abbati ya fada masa.

"Kada ma ka fara tunanin soke daukota zuwa gobe. Ko so kake a fara ganin kamar akwai uzurin da za ka dinga fifitawa akanta?" Cewar Abbati yana tsaye a cikin wani bakery. Duk wani cake da ya san tana so ya saya yana jiran turn dinsa ya biya.

Munzali ya sha kunu kamar suna tare ya ce "Ka gama kashewa yayarmu murya ni kuma ka dinga yi min masifa. Ya yi kyau!"

Daga inda Abbati yake har hasko fuskar tasa ya yi. Dariya ya dinga yi masa,

"Ai kaine da wani zance kawai don za ka je tsara budurwa baka son babyna ta bata show."

Shi ma dariyar ya yi "Dadin abun kaima tsarin nan dai zaka je. Tun wuri na fada maka idan mun tafi da ita a wurinka zata zauna ku kare kalau."

Da haka suka yi sallama. Munzali ya kira Mardiyya shi kuma Abbati gudun kada Munzali ya shashantar da dauko Qibdiyyan yau ya kira Zakiyya ya ce mata yana hanya.

Abu ne da suka saba dama. A wajen kaita gidan ko daukota daya daga cikinsu ke zuwa ko suje tare. Tunda Zakiyya ta san da tafiyar tun kwanaki biyu ta riga ta hada mata 'yan kayanta. A can dinma tana da kaya domin dakinta guda. Hatta uniform akwai koda watarana dalili zai sa ba a mayar da ita da wuri ba. Fitowa tayi daga daki tana kwala mata kira domin ta zo ta shiryata.

Duk inda take tunanin samunta ta duba babu Qibdiyya babu dalilinta. Hankalinta tuni ya fara tashi tunda ta tabbatar tare suka shigo gidan daga gidan kitso. Dakin mahaifiyarta ta sake shiga ta gama tashin hankalinta.

"Umma kamar fa bata gidan nan. Kuma ga kofar gida a rufe."

Umman tasu kanwa ga Asabe ta mike ita ma cikin firgici.

"Taso min Daddy ya zo ya fita a dubota. Ba har gara Munzali ya zo ace bata nan ba da wannan Abbatin."

Daddy din kanin Zakiyya ne. Hanyar dakinsa ta nufa da gudu gudu sai gashi tana kama kofar dakin shi ma ya kama ya bude. Wata mayyar jallabiya ce da ya nacewa a jikinsa yana murmushin yake. A gefensa kuwa Qibdiyya ce tayi tsilli tsilli da ido.

Dariyar da bata kai zuci ba Daddy ya yiwa yayarsa.

"Oji-oji (hide and seek) muka yi miki kuma baki kama mu da wuri ba ko Qibdiyya?" Ya furta yana tsare yarinyar 'yar shekara biyar da idanu.

"Eh" ta amsa babu wani kuzarin kirki a tare da ita.

Zakiyya haushi ya kamata duk bata kula da yanayin fuskokinsu masu dauke da labarai iri-iri ba. Hannunta tasa ta tankado kan Qibdiyya gabanta.

"Bana son irin wannan wasan, kada ki sake. Wuce muje ki canja kaya."

Tana sake turata Qibdiyya taji wani irin azababben ciwo ya tsirga ta tsakanin kafafunta.

"Washhh Mama."

Kafin Zakiyya ta gama juyowa har Daddy ya sunkuceta ya yi gaba.

"Daga yi miki wasa sai ki dinga hankadeta? In wasan ne ba kya so an daina yi dake."

"Ku wasa ya dama. Kayanta suna kam gado. Kayi sauri ka shiryata kafin azo daukarta, dama karatu nake Abbatin ya kirani."

Falo ta koma inda ta bar wayarta ta dauka ta cigaba da karanta novel din da aka yi update gabanin wayarsu da Abbati. Bata ji komai ba ta nutse cikin karatun ta bar kankanuwar 'yarta a hannun baligin namiji wai ya shiryata don kawai tana takamar shakikinta ne.

Ba yau ta fara ba. Son jiki ne ko sakaci? Allah Masani.

"Saka mata pant."

"Jeki Uncle Daddy ya yi miki wanka kafin na gama."

"Daddy shafa mata mai."

Aikin Zakiyya kenan. Idan ka bibiya kuma zaka samu ba wani abin kirki ne ya tsareta ba da har kula da tilon 'yarta yake yi mata wahala. Gashi bata son takura. A haka ma don anyi sa a Ummansu tana tsawatarwa duk lokacin da ta gani. Ta kan ce mata wannan zamani da uba yake haikewa 'yar cikinsa bau dace tana sakacin sakarwa kaninta ragamae Qibdiyya haka ba. Kowane dan Adam baya rasa makusa. Wannan dabi'ar ita ce ta Zakiyya.

To shi ma Daddy ba yau ya fara latse 'yar yayar tasa ba tare da barazana. Na yau dinne sai yaso wuce gona da iri. A cikin dakin daure fuska ya yi katamau yana yiwa Qibdiyya kallo mai ban tsoro.

"Kina fadawa wani zan sani kuma sai nasa wukata mai kaifi na yanka wuyan Daddy dinki (Munzali) da Papa (Abbati)."

Girgiza kai tayi da sauri tana mayar da kwallarta. Bidiyo din da yake nuna mata na yadda aka yanka wani mutum ta tuna ta runtse ido

"Allah ba zan fada ba."

"Ko kefa " Ya dan kalli jikinta "babu zafi ko?"

"Uhmm" ta ce da saurinta tana gyada kai.

"Good girl."

Abbati na zuwa Daddy ne ya rakota har mota suka gaisa sannan ya ja suka tafi. Abin mamaki a gareshi bai wuce rashin kuzari ko digo a tattare da Qibdiyya ba. Kafin su isa gida ta cure jikinta a bayan mota tayi bacci.

BIYAR NA YATSUN...

A kafada Abbati ya saba Qibdiyya daya hannun kuma ya dauko ledar kayan ciye ciyen da ya siyo mata suka shiga gida. Hanne tana zaune a falo tana kallo. Ganinsa da 'ya a hannu da kaya bai sa ta tashi ba balle ta rage masa wani abin. Sannu kawai ta ce masa ta mayar da idanunta kan tv.

Ko ta kanta bai bi ba ya shiga dakin da Baaba Mari ta zauna kafin su koma Kirikasamma ya kwantar da ita akan gado. Sama ya haye ya yi shirin masallaci ya sauko har lokacin Hanne bata motsa ba. Shi ya fara yi mata magana yana daura links. Sallahun kula da Qibdiyya ya bar mata ya fita.

Tsaki ta buga bayan taji tashin motarsa. Yadda ya bata mata rai shekaranjiya da tafiyarsu Baaba Mari ita ma ba zai ji dadinta ba kuwa. Sama ta haye ta bar Qibdiyyan har suka dawo. Allah Yasa Munzali gidansa ya shiga da tare zasu ji kukanta tana ta kiran Abbati da Anti Hanne. Ransa kuwa ya sosu ba kadan ba. Yana gama rarrashin ya kaita wurin Munzalin sannan ya dawo ya sameta rai a bace.

"Idan Qibdiyya 'yar cikinki ce haka zaki tafi ki barta ta tashi tana kuka?"

Baki ta murguda bata san ya gani ba ta bashi amsa da rashin kunya.

"Sai kaji in da dadi mutum ya nemi abu aki yi masa bayan akwai halin yin hakan."

Ya fara gane inda ta dosa amma ya kyaleta ta cigaba da magana domin ya tabbatar. Zancen shekaranjiyan ne dai ta tayar. Tunda Baaba Mari ta zo tayi 'yan kwanaki ita ma sai tata uwar ta zo.

"Ai uwa bata fi uwa ba"

Daure fuska ya yi da takaicin halayenta.

"Gwaggo Jumai ba kishiyar Baaba bace kina jina. Haka kawai idan ta so zuwa gidan nan ba zan hana ba. Amma ba zan yarda ki tsiro min da abin da zai iya zama rigima a gaba ba. Zuwan daya ba zai zama dalilin zuwan daya ba."

"To kuwa wallahi...."

Dan murmushi ya yi sannan ya katseta "ki cigaba da biyewa Gwaggo Deluwa ta kashe miki aure."

Gabanta ne ya dan fadi saboda bai yi kuskure ba. Gwaggo Deluwa ce zugata akan cewa ya kamata innarta ta zo ta kwashi romon arzikin gidan. Abbati sai ya sami damar cigaba da fadin abin da yake jin zai taimaka masa ya dan dawo da ita kan hanya.

"Ki bar ganin tana ta cewa ta samarwa 'Yashshafa miji a Kaduna. Idan yaki aurenta kin san ni din dai za a kuma kawowa. Shi yasa take so tayi sharae fage yadda idan can bai samu ba nan din ba za ki kawo musu matsala ba."

"Cabdijan" ta furta cikin bacin rai "amma Gwaggo Deluwa ta raina min...."

Bai tsaya jin sauran sababin nata ba ya sake ficewa yana murmushi. Sai da suka yi magariba suka tashi shiryawa zuwa dinar. Hanne da rawar jiki yana cewa ta shirya Qibdiyya ta kamata tayi mata wanka. Wurin tsarki ne ta kula tana kanne ido sai ta alakanta hakan da zafin ruwan. Tsaf ta shiryata cikin riga da skirt na lace tayi mata dauri. 'Yar kwalliyar da taso yi mata da ja gira a hada da jambaki da foundation ba tun yau Abbati ya hana ba. Ya kan ce mata komai da lokacinsa. A bar yarinya taci kuruciyarta idan ta isa adon ba sai an koya mata ba.

A mota kwanciya Qibdiyya tayi a jikin Munzali, Abbati kuma yana tuki.

"Wai ni baka ga canji a wurin Mamana ba? Dan taba wuyanta ko zazabi take yi? Shirun ya yi yawa."

Dago kanta Munzali ya yi ya taba wuyan da goshi.

"Babyn Daddy akwai inda yake miki ciwo?"

Kamar ta nuna masa sai ta tuna kashedi ta fasa. Yanzu ma dai da sauki sosai tunda bai yi mata mai gabadayan ba. Firgici ne ya zauna mata a rai ta rasa walwala saboda bidiyo din da Daddy ya nuna mata. Kai ta girgiza ta sake kwanciya.

Gajeren tsaki Abbati ya yi yana cewa "ka gani ta sake kwanciya ko? Kawai kar mu dade mu biya a dubata. Ni dama saboda shirun ne ma nace mu fito da ita ko ta sha iska."

***

"Nifa ba soyayya muke ba" Mardiyya ta sake nanatawa Farha da Sauda mai bada labari.

"Shi yasa naji yana kiranki Diamond girl" Sauda ta fada tana hararta ganin za ta raina musu wayo.

"Saboda a diamond plaza muka hadu ko kun manta?"

Sauda bata hakura ba ta sake cewa "Amma ai ke ya fadawa zasu zo da 'yarsu."

"Saboda yaga kamar na fiki son yara ne."

"Tunda a rubuce yake a goshi ba! Ke dai idan biki ya tashi kada ma ki nemeni don ba zan miki komai ba tunda tsakaninmu an fara boye boye."

Farha dariya tayi yadda suke hararar juna kowacce tana son a yarda da zancenta. Su ukun sanye suke da skirt da riga na lace fari da purple. Kowacce kamar sauran 'ya'yan dangi taci gwaggwaronta da kwalliya irin ta zamani saisa-saisa. Dokar Maminsu kuma ta tabbata a kansu don bata yarje musu yawo babu lullubi ba saboda biki.

"Duk wadda ta ajiye tarbiyarta tayi yadda take so a bayan idona Allah na kallonta."

Da haka ta kashe musu jiki domin da fari har Sauda da Mardiyya sun fara son bin sahun 'yan mata 'yan uwansu. Da suka kiyaye mutumcinsu kuwa sai suka dinga jinsu a sama a wurin bikin sabanin marasa mayafi. Sun yi matukar kyau kamar a daukesu. Hankalinsu kwance basu da damuwar komai. Jiddo da Mama Nasima ma duka sun zo saboda biki dai na kanin Alh. Tahir ne ko bai auri Mami Khadija ba.

Inda suka zauna ma dai taron 'yan uwa ne daga masu sabbin goyo sai marasa aure anata hira. Kiran Abbati da sanarwa Farha da ya yi cewa sun iso ya kara karfin shewarsu.

"Farha da saurayi? Lallai yau zamu yi farin gani a wurin nan." Cewar wata sa'arta wadda a yanzu take da ciki na biyu.

Idanu suka dawo gareta kowa na fadin albarkacin bakinsa. Abin ne da mamaki saboda duk lokacin da ake haduwa irin haka ana hirar samar sai dai tayi murmushi. Idanu suka saka mata suna jiran ganin waye ya ciri tuta. 'Yar kwallarta ta samu ta danne saboda ganin yadda suke ta murna. A baya din ma basu san babu bane ba wai tana boye shi ba.

Zuga guda ce ta biyo su suka tsaya daga bakin kofar shiga inda ake nuna kati ana jiran su shigo da bakinsu. Farha da ta fisu tsiya sai ta fadawa Lilu ta ce ya shigo dasu. Idan akwai saukin mutane ma ya fara kaisu su gaisa da Mami Khadija. Shi kuma sai ya kira Suhaib saboda katinansu suna wurinsa.

*

Ba tare da wata shan wahala ba Danliti ya iso venue din da Anti Jiddo ta fada masa ya zo ya sameta. Yau bai yi karambanin daukar motar garejinsu ba saboda ta san ko shi waye. Gara ma ya nuna mata fakirancinsa da kyau domin ta kara sakar masa bakin jaka. Yana sauka daga adaidaita sahu ya kirata ta fito waje. Ba karamar kwalliya tasha ba. Mayafinta a kafada daya ta rataya shi sai karamar jaka a daya hannun. Ba ciki take son su shiga ba. Hasali ma idan ta sami faraga so take su dan zaga hotel kafin a tashi daga taron. Shi yasa ma ta san yadda tayi Alh. Tahir ya yarda aka taho da motarta. Dan kanwarsa ne ya tuko kuma ana zuwa ta karbe mukullinta.

(ZINA kenan. Ma'abocinta baya taba cin bulus. Da wuya ne idan bata dawo jikinsa yadda zai yi masa ciwo ba.)

Kasa dauke ido daga kallonta Danliti ya yi har ta iso tana girgiza masa jiki.

"Ka san kana so amma nake turo maka hotuna kana ja min aji" Jiddo ta furta tana kashe masa idanu.

Busassun labbansa ya lasa cike da shu'umanci a zuciyarsa ya ce "ba so ne bana yi ba karfina kawai aka fi."

A kagauce ta ce "Akwai inda zamu iya zuwa kurkusa don na dawo da wuri?"

Da ka ya amsa mata saboda irin kallon da take masa da motsin jikinta duk sun hargitsa masa lissafi.

Danna remote tayi motarta dake gefe tayi kara alamun lock din ya bude. Da ido ta nunawa Danliti ya shiga tana wani irin kakkashe masa idanu kamar wadda ta sha kayan maye.

Danliti ya kama hannun kofa zai bude kenan Suhaib ya isko su. Ta gabansa Anti Jiddo ta fito tana waya da Danliti ya zo bata kula dashi ba. Fitowarsa kenan zai shigo dasu Munzali. Uzurinsa yaso karasawa da ta wuce sai dai karairayar da ya hango tana yi da girgiza jiki ya matukar kada hanjinsa. Yau ko mahaifinsa ne baya jin akwai dacewar tayi haka a gabansa a waje irin wannan ba. Jikinsa ya yi matukar sanyi da yaga irin kallon da Danlitin yake binta dashi shi ma. Maganganunsa basu isa kunnuwansa ba sai dai ganin suna neman shiga mota ya karar da hakurinsa. Baya son dasa musu zargi bisa hasashe amma duk da haka baya jin zai iya dauke kai.

"Anti Jiddo ina zuwa haka ana ta nemanki a ciki."

Sakin mukullin tayi ba shiri sakamakon gumin da ya karyo mata ba shiri har tafin hannu. Daburcewa tayi gabadayanta ta juyo.

"Me ya fito da kai ana tsakar taro Suhaib?"

Kallon tuhuma ya yi musu duk suka ji kamar ya yi musu tsirara a waje.

"Baki gareni zan shiga dasu."

"Oh...to sai ka dawo." Anti Jiddo ta ce da murmushin yake tana fatan ba zai yiwa Danliti magana ba.

"Kai kuma fa?" Ya ce da Danliti fuska a murtuke.

"Am, ammm"

Wani mugun kallo Suhaib ya dinga yi masa sai ya rasa abin fada duk kwarewarsa a karya. Anti Jiddo da ta san koma meye ita ce a ruwa sai ta ce makanike ne zai duba mata mota.

"Waye ya turo miki shi?"

Tambayar ta fito babu digon fara'a a fuskar Suhaib gareta.

"Kawata. Eh kawata ce ta turo shi." Ta amsa da rawar murya.

Hannu kawai ya mika mata "bani mukullin naki. Idan na raka bakin ciki sai na bi shi. Gani ga Lilu ace kin tafi gareji a daren nan Abba ma ba zai barmu ba."

Jikinta sanyi ya yi ga wani irin bacin rai da yake cinta. Danliti zuciyarsa kamar ta fado don tsoro. A haka ya daure ya ce,

"Kawo na tayar na fara dubawa kafin ka dawo. Idan dole sai mun je garejin zan gani."

Shiga motar ya yi ya tayar ya shiga danna totir ya leko da kansa da ya jike da gumi.

"Ina jin ma ba sai mun je ba." Ya dubi Anti Jiddo "Hajiya bakin mai kawai za ki canja."

A firgice ya mikawa Suhaib mukullin ya kara gaba ko waige babu. Suhaib ma sai ya bawa Anti Jiddo ya tafi inda su Abbati suka yi parking ko kallon kirki bai kara yi mata ba. Kwafa kawai tayi tana tsine masa a ranta. Uban da ya haife shi ma yawo yake bata ga wanda zai hanata more rayuwarta ba.

*

Gaban Farha ne ya fadi da su Abbati suka shigo hall din. Bata jin rashin samun masoyi da wuri ne yasa take ganin ya burgeta a komai. Yanzu kam shigarsa take kallo. Kayansu iri daya da Munzali. Yadi ne ruwan toka anyi musu dinki mai gajeren

hannu. Kawunansu da hula ita ma iri daya babu bambanci. Wurinsu Mami Khadija Suhaib ya fara kaisu suka gaisheta. Lilu yana wurin ya dauki Qibdiyya wadda take makale a hannun Abbati yana tambayarta sunanta.

"Lilu sarkin yara. Tun yanzu zan fara yi maka addu'ar bibbiyu da uku uku." Cewar matar wani kanin Mami din.

"Ai kuwa matata ba sai ta dauko mai raino ba Anti. Ta dauki daya na dauki daya."

Mami Khadija ta girgiza kai tana kiransa mara kunya su Abbati suka yi murmushi. Iyayensa dake wurin kuwa dariya suka dinga yi masa anata tuna kuruciyarsa da yadda yake daukar musu yara yana musu wasa.

"Kaisu su zauna mana" Mami ta ce da Suhaib wanda ya kafe Anti Jiddo da ido a inda take zaune.

Bayan sun zauna Lilu ya kira Farha ya kwatanta mata inda suka zauna. Tare suka mike da yan uwanta har mutum hudu. Duk yadda taso sai da suka bi bayanta suna dariya.

"Gashi can mai sajen" Sauda ta nuna musu shi.

Kan kace meye wannan sun riga Farha isa. Kunya ta kamata da taji suna ta yi masa tsiya.

"Allah banga laifinki ba Farha. Wannan da ya bayyana da wuri ai da tuni an miki kwace." Wata mai baki ta fada.

Abbati kuwa sai ya kada baki ya ce "ba zan kwato ba fa. Ni nan sai Ya Farha."

Kafin kowa ya farga Suhaib ya bar wurin saboda wata irin shewa da suka saka. An tara masu baki ne a wurin wadanda duk taro sune iyayen zance. Farha kamar ta nutse a kasa ta juya zata bar wurin.

" 'Yan uwanmu kunga ban gama shigar da kaina ba kuna neman korar min ita ko Mun...."

Yana waigawa babu alamun Munzali a wurin sai Lilu da yake bawa Qibdiyya meatpie. Ashe wurin zama daban ya ce Mardiyya ta sama musu tun kafin su shigo. 'Yan matan suka gama dariyarsu suka watse. Ya rage su hudu har Qibdiyya.

Lilu ma sai ya mike ya dorata akan cinyar Farha.

"Zan bika" ta ce da sauri tana daga hannuwa.

(ABIN LURA: Yaran da kan gamu da sharrin makusanta ta fannin fyade ko koya musu munanan dabi'u sukan saba da abin fiye da tunanin iyaye. Ba ranar Daddy ya fara taba Qibdiyya ba sai dai ranar ne ya fara nufin zarcewa. Wannan ne ya haddasa masa tsoronsa har ta kaishi ga yi mata barazana. Idan uwa bata kula da 'yar alawa da biskit kadai ake toshe bakunan yara musamman masu wayo ace kada su fadawa kowa. Ba tare da sani ba kwakwalwar Qibdiyya ta saba da abin da Daddy yake yi mata. Lilu da yake kusan tsaransa kuma lokaci guda ya jata jiki sai wancan abu yake neman tasiri a kan karamar yarinya. Gani take abin da Daddy yake mata shi ma kila zai yi. Kuma tunda ya fara da kyautatawa me yiwuwa ba zai kaisu da zancen yanka iyayenta ko ya yi mata mai zafi ba.)

Girgiza kai Lilu ya yi ya bata hakuri cewa zai je ya dawo ne sai ga Sauda tazo ta dauketa.

Shiru kan Farha yana kasa haka kawai take jin kunyar Abbati fiye da ta kullum. Nasa shirun bashi da nasaba da kunya sai nazarin yanayinta. Zuciyarsa ce take kara nanata masa lallai yabi a hankali saboda ba lallai bayan anyi binciken asalinsa a mallaka masa ita ba.

"Ya Farha dago kanki muyi magana"

***

Kayan daki gabadaya Uwani tasa Mubasshir fitar mata wurin neman kudadenta. Ko digo bata zargin Salihi saboda haka bai taba faruwa ba. Mubasshir din kuma ta san da wuya yake shigar mata daki. Tafi yarda da cewa wuri ta canja musu amma har yanzu shiru. Ga dadin bakincikinta yadda Ummule take tararta gaba da gaba babu shakka ko tsoro. Da taga wankin hula yana neman kaita dare kawai sai ta nemi Habibu. Ta kikkira wayarsa a iya kwanakin da take neman kudin bata samu ba. Shi ne yau kawai ta same shi a office.

"Hajiya, Hajiya" ya dinga yi mata kirari tun kafin ta iso gabansa.

Murmushi tayi kanta na fashewa ta sami wuri ta zauna. Bayan sun gaisa ta bijiro masa da bukatarta. Kudinta take so na Hajji ta fasa zuwa. So take ya bata taje ta karasa gyaran gida ta tashi.

"Ikon Allah. Metiron lafiya kuwa? Wannan indai ba fitar rabo ba waye ya taba fasa Hajji saboda gyaran gida?"

Cike da bacin rai ta ce "ba za ka gane bane Habibu. Wai ni Salihi ya yiwa kishiya? Kishiyar ma kuma wai gida daya zamu zauna. Bana son yin wani tashin tashina dasu domin nafi karfin haka. So nake ya gani a aikace cewa na haifu cikin uwa da uba. Sannan wannan aikin ba gumin banza nake fitowa nayi ba."

Yawu ya hadiya. Ta ina zai fara nemo wadannan makudan kudade yanzu? Dama jira yake a fara kiran maniyata ya samfe ba za ta kara jin duriyarsa ba sai an gama dawowa. Wannan ba za ta har ina?

"Gaskiya Metiron akwai matsala. Kudi ba zai dawo ba. Na fada miki cewa na riga na biya har Agents sun gama komai. Lokaci ake jira a baku passport dinku."

Huci ta kama sai ta ya tsorata. Ta buga ta raya ya daure ya cigaba da cewa sai dai tayi hakuri. Haka ta hakura ta koma wurin aikinta tana ta tufka da warwara. Da

shigarta ba dadewa aka kawo mai haihuwa. Matan manyan mutane sun fi ganewa asibitin kudi akan na gwamnati. Yau sai ga tsuntsuwa daga sama gasashshiya. Matar kwamishinan raya karkara ce da kanta ta kawo surukarta. Nakuda ta kamata kuma suna ganin kafin su isa asibitin da take awo za a iya samun matsala saboda ta soma zubar da jini. Shi yasa suka kawota nan saboda yafi kusa. Uwani kuwa sai tayi uwa tayi makarbiya ta hana kowa tsayuwa kan mai nakudar.

Kafin likitoci biyun da aka sanar su shigo har ta gama shirinta. Kudi kawai take gani har ta samu indai tayi aikinta yadda ya kamata.

"Haihuwa ta nawa ce?"

Da kyar yarinyar ta amsa mata "ta biyu."

Rage murya tayi ta matsa kusa da ita kamar cikin za ta taba sai ta duka yadda za ta ji ta sosai.

"Naga babu dinki a haihuwarki ta farko kuma da alama da kanki ki ka karu."

"Washhh Allah..."

"Ko"

"Likitan ta ce ban karu shi yasa ba ayi ba."

Uwani ta dago kai kamar gaske "wace irin likita ce wannan mai neman kashe miki aure? Ke baki dinga jin jikinki a sake ba?"

"Innalillahi...wayyo Mamaaa"

Jira tayi ciwon ya dan kara sauki ta kuma ingizota.

"Zan taimaka miki. Idan kin haihu yanzu da kari kada ki yarda ko kadan ayi miki dinki. Zan jira ki haihu na baki nambata. Wallahi gyara zan miki giredi amma a gida. sai kinfi budurwa a wurin mijinki."

"Lahaula wala quwwata illa billah....ki rabu dani don Allah" yarinyar ta furta cikin tsananin azabar ciwo.

Ana haka likitocin suka iso. Kafin ma su fara dubata kan d'a ya danno. Ba haka Uwani taso ba haka tana ji tana gani likitocin suka karbi haihuwa. Abin dadi ga maijego wannan ma bata karu ba ko kadan. Uwani sai ta makale a dakin da sunan taimaka mata ta gyara jikinta kafin a fito da ita.

"Kar ki cuci kanki na san zafi ne babban abin da yake saka ku gudun dinki. Allura zan miki wadda zata kashe duk wani ciwo. Mazan yanzu masu dan banzan yawo sai da gyara ake samun kansu."

Bacin rai muraran ta gani a fuskar yarinyar a lokacin da ta tashi za ta fita daga dakin haihuwar tana cewa

"Baiwar Allah ki kyaleni don girman Allah"

Tana fita Uwani ta ciji lebe za ta fara zaginta sai ji tayi ance "ni ina so. A nawa za ki min na dawo kamar budurwa?"

"Dubu ...." ta soma cewa bayan ta bude labulen da ya raba gadon wadda ta haihu da na mai maganar. Ita ma tsohon ciki ne da ita. Ta sanar da ira cewa an kawota tun dazu anyi inducing amma har lokacin bata fara jin ciwo ba.

"Barshi ma. Zan baki dubu hamsin kiyi min aiki mai kyau." Sama ta kalla tayi kwafa "sai na shayar da kai mamaki. Wallahi nafi karfin zama da kishiya."

An tabo inda yake yiwa Uwani masifar kaikayi. Nan ta zauna tana yiwa matar da bata sani ba famfo da nuna mata illar rashin gyara irin wannan ga matan aure.

Ranar fafur taki tafiya gida sai wuraren uku na dare matar ta haihu. Ta so suyi magana tun lokacin amma ganin manyan likitoci suna ta kai kawo sai ta hakura. Ranta fari kal domin ta tabbata dai matar wani ce.

Bayan ta kimtsa an kaita dakin hutu da kanta ta ce a kira mata Metiron Uwani. Da zumudinta kuwa ta shiga ta kara yi mata barka. Matar ta karbi nambar wayarta.

"An riga anyi min dinki amma."

"Karki damu. Kwancewa zanyi nayi miki nawa. Wallahi na yiwa mata sun fi a kirga masu haihuwa a nan da haihuwar gida ko wasu asibitocin."

Ajiyar zuciya ta samun nutsuwa matar tayi sannan suka yi alkawarin ana sallamarta washegari za ta kirata ta bata kwatancen gidanta. Jikin Uwani har rawa ya dinga yi saboda taji kudi. Tana fita matar nan ta dauki waya ta kira maigidanta. Hakuri ta bashi saboda yana ta kiranta lokacin da suke maganar da Uwani bata dauka ba. Farincikinsa na sake samun karuwar zuri'arsu ya nuna mata da tambayar bukatunta idan akwai a lokacin.

Murmushi tayi ta gyarawa jaririnta kwanciya sannan ta ce "Akwai mai girma CMD (Chief Medical Director). Ana badakala a asibitin nan karkashin shugabancinka baka sani ba. Nayi karambani na kama maka daya. Za dai muyi maganar a gida. Amma please my dear ya kamata kasa ido sosai."

Dariya ya kwashe da ita ta tausayin mai tsautsayin da tayi shuka a idon makwarwa. Matarsa lauya ce mai zaman kanta wadda take hadawa da aikin sa kai na kare hakkin bil adama.

Karfe shida da kwata a kofar gidan Alh. Rabi'u ta yiwa Salihi. Garin da sauran duhu hasken rana bai fara fitowa ba. Wasu magidantan ma basu riga sun koma

muhallansu daga masallaci ba. Daga ganin yadda ya ajiye mota zaka san baya tare da nutsuwa. Kasheta kawai ya yi ba tare da ya rufe ba ya fita ya soma doka sallama a kofar gidan.

Sallamar tasa ba karamin tsinka zuciyar Salima wadda ko tashi daga kan abin sallah bata yi ba tayi. A hanzarce ta mike suka kusa yin karo da Zara don ita ma ta gane muryar waye. Innayo kuwa iccen da take kokarin turawa a murhu tayi jifa dashi su ukun suka hado a kofar gidan da ko budeta ba ayi ba.

"Karbo min mukulli a wurin Alhaji"

Innayo ta furta muryarta tana fallasa fargabarta. Babu wani abu ko daya da zai kawo Salihi gidan nan da duku dukun asuba mai dadi.

Tare da Alh. Rabi'u Salima ta dawo ya sako babbar riga yana murza idanu don ko sallah bai yi ba. Innayo ya kalla ta jingina da bango zuciyarta tana ta dukan kirjinta.

"Aka ce Salihi ne yake sallama."

"Ni ne Alhaji" ya amsa daga waje.

Nasa hannun ma rawa ya kama yi sai Zara ce ta iya budewa Salihi ya shigo. Daga soron ya durkusa ya gaishesu sannan ya dan sosa keya.

Salima da Zara sai suka bar wurin tunda kowa ya fahimci ba tashin hankalin da suke taraddadi bane.

"Innayo ki bata hakuri tazo mu koma. Indai akan Ummule ne zan raba musu gida."

Alh. Rabi'u ya kalli Innayo kallo na wulakanci sannan ya yi wata irin banzar dariya.

"Hajiya Hauwa kenan. Kin nunawa kowa a gidan nan cewa kin fi kowa iya tarbiya da kyawun hali. Rannan har magana ki ka fada mana ni da Asabe akan 'ya'yanki. Sai gashi a tsukin abin da bai kai wata guda ba uku sun dawo gida. Allah Ya kyauta."

Wucewarsa ya yi ko waige babu. Salihi kunya ta lullube shi yaji kamar ya nutse a wajen.

Numfasawa Innayo tayi ta dube shi da murmushin da ya tsaya a fatar bakinta saboda bacin ran Uwani.

"Salihi aure kayi?"

Da sauri ya kalleta ba tare da ya iya boye mamakinsa ba.

"Uwanin bata fada miki ba?"

"Bata fada ba. Allah Ya sanya alkhairi. Sai dai kuma bata zo gidan nan ba."

Kansa da ya yi niyar yin kasa dashi ya sake dagowa da sauri hankalinsa a mugun tashe. Jiya bata da aikin kwana. A ka'ida ma kafin la'asar take dawowa a ranaku irin wannan. Sai gashi har bayan isha babu duriyarta. Ya dinga kiran wayarta babu amsa, wanda kuma tana sane don kada ya katse mata jiran mai haihuwar da zata zame mata alkhairi. Abu kamar wasa har goman dare. Nan fa yaji ba zai iya bacci ba dole ya tafi asibitin nemanta. Nos din da suke da aikin kwana ranar suka ce masa ta tafi. Basu san tana nan ba tunda kafin zuwansu ma 'yan yamma sunyi nasu sun tashi. Sai da ya tafi ne daya daga cikinsu ta ganta take fada mata wani yazo nemanta. Haka nan taji a ranta maigidanta ne amma sai taki kiransa. Dole zai yi mata ta dawo gida ita kuwa bata cikin masu wasa da neman kudi. Haka ya koma gida ko runtsawa bai yi ba. Tunaninsa ya tafi akan ko tayi yaji ne saboda zuwan Ummule. Shi ne ya taho gidan da sassafe saboda baya son kowa ma hatta Ummule ta fuskanci da b'araka irin wannan tsakaninsu.

"Ikon Allah" ya ce lokacin da yake jin wani irin tsoro a ransa "nima nayi jinkirin zuwan ne saboda tunanin ko ta karbarwa wata aikin kwana ne..."

Innayo ba shiri tayi 'yar dariya tana cewa "banda abinka Salihi yaushe zaka dinga magana kamar yau ka san Uwani? Ita da ba wasu kawayen kirki ba ai da wuya ne ta karbarwa kowa aiki."

Murmusawa ya yi shi ma. Wayar suka sake kira shiru dai ta ma daina shiga. Innayo daurewa kawai take yi amma gabanta sai faduwa yake yi. Salihi yana tafiya taje ta ballo magungunan hawan jininta tasha. Sun yi dashi zai koma asibitin ya sake dubawa. Idan an tabbatar masa ba a nan ta kwana ba zai kirata ya sanar da ita su san matakin dauka na gaba. Jiri ne ma ya yi mata sallama dole ta nemi wuri ta kwanta.

*

Wuraren bakwai da rabi Metiron Uwani ta fito daga dakin Haj. Salma wato matar CMD. Bakinta kamar gonar auduga domin Hajiyar tayi mata alkawarin idan aiki ya yi kyau tana da mutane a kalla shida wadanda zata hadata dasu. Duka kawayenta ne a cewarta da suka hayayyafa ana neman tayar da komad'a. Kudin aikin kowacce sun tsayar a dubu talatin. Nuna mata tayi duka matan manya ne sannan ai suna sayen kayan gyara na sama da wannan kudin sosai. Kai tsaye dakin da suke kwanciya ko ajiye kayansu ta nufa ta dauko wayarta. Tabe baki tayi ganin yawan kiran da Salihi ya dinga yi mata. Da yana sonta ba zai munafunceta ya karo aure ba ta ayyana a zuci. Kiransa tayi yana bakin danja zai karaso asibitin.

"Naga missed calls ne" ta ce dashi da ya dauki wayar da yanayi na nuna kosawa da kiran nasa.

Haushi ya kama shi ya daure ya boye fushinsa.

"A ina kika kwana?"

"Wace irin tambaya ce wannan bayan ka san ina zuwa aiki? To ina asibiti yanzu zan taho gida."

"Sai kin dawo"

Yau kam ya yi niyar nuna mata idan ma da gangan take wannan rashin hankalin to bashi da juriyar cigaba da dauka. Ace ko kadan bata ma san tayi masa ba daidai ba? Ta kwana a waje ba waya ba text sai amsa waya da gadara. Wayar Innayo ya kira ya fada mata sun yi magana sai ta roke shi da ya kawo Uwanin gidanta idan ta koma.

Ita kuma Uwani wayar kafintanta ta kira cikin sa'a kuwa ya dauka. Kayan gado da kujerun da ta saya a wurinsa ta ce tana bukatar aje a kafa mata yau. Dama ta saya ne saboda tayi gyaran daki idan ta dawo daga Hajji.

"Idan kun kusa titin Kofar Famfo ga nambar dana ku kira zai kaiku gidan."

Bayan ta gama dashi ta kira mai labule shi ma ya dinka mata ne na iya falo da dakin baccinta. Karin yadi ta ce ya nema irin wadancan za ta zo bayan la'asar suje ya auna labulen sabon gidan a kara. Kafin nan ta san masu gado sun yi nisa a nasu aikin. A son ranta a gama komai cikin kwana biyu ta tare.

Ginin da kuma wadannan kayayyakin da ta saya su suka cinye mata kudade. Dalilin da yasa ta shiga rudani kenan akan bacewarsa sarka da kudadenta na daki. Shawarar da ta yanke tun kwana biyu da bacewar kudin ce ta sake fado mata taji kwarin gwiwa. A jikin Salihi za ta fanshi kudinta komai runtsi.

Da wadannan lissafe lissafen ta kama hanyar BUK oldsite inda Mubashir yake karatu. Da ta kira shi a waya tsorata ya yi da farko sai yaji ba zancen kudinta bane. Haduwa suka yi ta bashi mukullin gidan nata da bayanin abin da zai yi. Saboda halin rayuwa ta jima da nuna masa gidan tun yana fuloti. Daga nan gida ta nufa zuciyarta kamar an yayyafa ruwan sanyi. Tana tura gate din suka yi ido hudu da Salihi.

"Fita zaka yi ne?" Tayi masa tambayar rainin wayo a zuwan ita har lokacin bata san tayi masa laifi ba.

"Ke nake jira"

Kallonsa tayi shekeke ta wuce ciki tana cewa "wai meye ne kake ta wani bata rai don na kwana a asibiti kamar wani bakon abu?" Dan tunani tayi ta dawo da baya ta ce "Idan saboda ban kiraka bane aiki ne ya min yawa. "

Tsabar takaicinta bai bashi damar amsa mata ba. Daki ta wuce tayi wanka ta fito ta sha shayi a gurguje saboda kada Haj. Salma ta kirata bata gama ba. Tana tashi Salihi da Ummule suka fito daga dakinsa. Dakin nata ya bita shi kadai ya sameta tana sauko da akwatuna.

"Lafiya?"

"Lafiyar kenan" ta ce a yayinda ta dauko wata leda da 'yan mukullaye a ciki. Kwancewa tayi ta dauko wasu masu guda hurhudu ta cirar masa d'ai-d'ai ta damka masa.

"Gasu nan mukullin gate ne da na kofar gida. Idan kayi kwanakin cin amanarka a nan sai ka dinga biyoni nawa muhallin ranar girkina."

Mamakinta yana neman zarta bacin ransa. Sam ya kasa fahimtar inda ta dosa.

"Ban fahimceki ba."

Kugu ta rike da hannu daya bayan ta turo dauri gaban goshi.

"Na gama gini na ina shirin saka 'yan haya kazo min da waccan abar wai kishiyata kuma kana sa rai na karbeta mu zauna a nan. Sai dai ina so ka sani cewa nafi karfin wannan wulakancin. In Allah Yaso ba zan kara sati ba a gidan nan zan koma nawa. Ba kuma zan yafe maka hakkina ko daya dake kanka ba."

"Yanzu Uwani har gida ne dake ban sani ba?"

Kwaikwayonsa tayi tana dariya "yanzu Salihi har aure ne da kai amma sai da matar tayi ciki na sani?" Ganin ya kasa cewa komai ta dora da cewa "da ne maza suke taka mata su zauna lafiya amma yanzu kan mage ya waye. Ko an fada maka kudin da nake nema ina yi ne don na mutu ku ci gado kai da 'ya'yanka?"

"A tare lafiya Uwani"

Daga yanayin fitar muryarsa ma ta gane ba da niyya ya yi mata adduar ba. Shi yasa ita ma ta amsa masa yadda zai ji haushi.

"Amin dai. In ka sami sukuni sai ka kawo kudi ko ka sayo gadon da zaka sa a dakinka na can."

Ya daina mamaki kamar yadda ya daina jin bacin rai. Hukuncinta sai ya zauna ya yi shawara da kwakwalwarsa sosai. Tafiya ya soma yi ta biyo bayansa da sauri.

"Af...baka ji ba. Na ce akwai lissafin da zan maka na abubuwan da bakuwarka ta sace min." Dage gira taga ya yi sai ta hau bayanin cewa ranar da ya kawo Ummule gidan bata ga alamun bakunta a tare da ita ba. Shiyasa rake ganin ba ranar ya fara zuwa da ita ba. A takaice tana zargin ita tayi mata satar kudi da sarka.

Katse zantukan da yake ganin matsalar kwalwalwa ce ta kawo mata su ya yi

"Idan kin gama shiryawa ki zo muje Innayo tana nemanki."

"Ina da uzuri zan biya idan na gama. Maganar sark...."

"UWANI!"

Hadiye sauran maganarta tayi ba shiri saboda karfin tsawar da ya daka mata.

"Ki dauko mayafinki yanzun nan ina jiranki a mota."

Bata gama dawowa daidai daga firgicin da ta shiga ba Mubashir ya kirata. Saurin dawo da nutsuwarta daga tunanin me ya sami Salihi tayi ta amsa wayar.

"Umma gamu a bakin gate amma KNUPDA sun yi alamar a dakatar da aiki a gidan."

Kwakwalwarta ce ta toshe na 'yan dakiku ta dinga maimaitawa Mubashir tambaya daya kamar mai bitar karatu.

"Su waye kuma KNUPDA?"

***

Farha bata dago da kanta ba har Abbati ya gama fada mata asalinsa da musabbabin zuwansa Kano. Labarin nasa ya sami sauyi ne a wurin silar arzikinsa inda ya ce mata kasuwanci suke yi amma yanzu sun balle daga jikin ubangidan nasu. Ya fada mata unguwar da suke ginin shopping mall da ire iren kayayyakin da suke son zubawa a ciki.

A lokacin da yazo gabar da dole karya ce kadai za ta iya rufa masa asiri sai da ya hadiyi yawu mai daci. Da kansa yake jin tsana da kyamar dabi'ar da suka rayu cikinta. Yana son Farha so mai girma. Burinsa idan har ya mallaketa su zamewa juna tamkar warin takalma masu cike junansu. Yadda bashi da sirri da Munzali yana fatan kusancinsa da ita yafi wannan. Ba don komai ba kuwa face sanin cewa duk matsayin aboki matar aure ta fishi. Ita da mijinta aminai ne, masoya kuma ma'aurata.

Kimanin minti uku da yin shirunsa amma har lokacin bata dago kanta ba. Tuni ya fara sarewa yana jin ya rasata kenan har abada. Magana mai girma irin wannan ya

so ace a gida aka yita. Sai dai kuma tazo masa bagatatan ne da Farha tayi masa tambayar cikin hirarsu.

"Don Allah ki dago kan ki ko sallamata zaki yi kada ki ce ba za ki sake iya kallon wannan almajirin dan kauyen wanda ko kwalin primary bai mallaka ba." Muryarsa ce tayi wani irin rauni mai fallasa ruhi da zuciya tana raurawa saboda tasirin soyayyarta a zuciyarsa. Bai gaji ba ya sake yi mata magana domin ya kagara ya san matsayinsa duk da ya gama sallamawa.

"Ni ba tsaran aurenki bane Ya Farha, amma wallahi ina sonki da dukkan zuciyata."

Farha bata san yadda zata kwatanta halin da Abbati ya jefa zuciyarta ba da kalamansa na karshe. Zuciyarta kara fadi take a cikin kirjinta tana kuma cikewa da wannan bawan Allah dake gabanta.

Kosawa ya yi da rudanin da zuciyarsa ta shiga a sakamakon shirunta.

"Ko in tafi?"

Sai lokacin ta dago da taji ya dan tura kujerarsa baya alamun zai tashi.

"Idan ka tafi kana tunanin tsaran auren nawa zai zo?" Ta ce a raunane.

Kansa ya gyada da murmushin da ya tsaya a labbansa. Wurin kawai yake son ya bari kafin ya tsinci kansa a kan gwiwoyinsa yana rokon soyayya.

Hawaye ne ya zubo mata ba shiri da ta hada ido dashi. Wannan wace irin zazzafar soyayyace suke yiwa juna haka? Da jikakkun idanunta ta dube shi.

"Yazo ya aureni kana ji kana gani?"

"Kin yarda idan yazo na kore shi ko waye?"

Ita ma kai ta gyada masa amma nata murmushin mai sauti ne da jindadi.

"Kina ganin su Mami zasu yarda ki aureni?" Ya tambayeta da sabuwar damuwa.

"In sha Allahu babu matsala."

Gyara zamansa ya yi gami da sakin ajiyar zuciya. Suka kalli juna suka yi murmushi a tare. Abbati ya kasa dauke ido daga kan kyakkyawar fuskarta.

"Kin san me?"

"Ina dai so in sani" ta lumshe idanunta sannan ta bashi amsa.

"Na dan kware a Ingilishi."

Farha bata san lokacin da ta kama dariya ba.

"To ko mu kara ne?"

"Me ya yi zafi daga wasa"

Dariya suka yi tare a idanun Mami Khadija wadda ta zo wucewa can nesa dasu da kawayenta. Murmushi tayi ta dauke kanta kafin su farga cewa ta gansu. Fatanta Allah Ya cikawa 'ya'yanta farincikinsu.

A zuciyar Abbati kuwa tunani yake kada Allah Ya kawo abin da zai raba shi da Farha. Shi kan shi tsoron girman soyayyar da yake yi mata yake yi. Idan ya rasa ta.....baya son sanin halin da zai shiga idan ya rasa ta.

*

Can daya bangaren inda Munzali da Mardiyya suka zauna suma tasu hirar suke gwanin sha'awa. Hirar irin son da Abbati yake yiwa Farha yake mata tana bashi amsa da tabbacin yayarta ita ma tana kaunar aminin nasa.

"Da gaske dai ba sona kike ba ko Mardiyya?"

Ya furta daga sama suna tsakar magana. Gabanta ne ya fadi domin tun haduwarsu bai taba kiranta da sunanta ba. Kallon ma kamar tayi masa laifi haka ya tsareta da idanu duk sai ta daburce.

"Me nayi don Allah?"

Yanayin tsoratar da tayi sha'awa ya bashi. Yarintarta ta fito sosai sai kara shiga zuciyarsa take yi.

"Tunda muka zauna nake yi miki zancen su Abbati amma ko ki bata rai ki ce a canja hira. Kamata ya yi nima naci ribar lokacin nan nayi miki hirar zuciyarta da yadda take kaunarki."

Sunkuyar da kai tayi tana wasa da wayar hannunta. A haduwarsu da yawan wayarsu ta gane Munzali yana da son wasa da tsokana. Wannan ma yana daga cikin abubuwan da suka sa take son sa.

"Baki ce komai ba."

Mardiyya sai ta zabi ta rama ita ma ta nuna masa wace ce ita.

"To ni me zan ce? Ka kebe 'yar karamar yarinya kana yi mata zancen soyayya."

Dariya sosai ya dinga yi yana bude baki ya rufe kafin ya ce "kin ce wani abu. Wato yarinya ko? Bari na tashi na nemi daidai dani a cikin taron nan"

Hannuwanta ta daga kamar mai addu'a da ya mike ta soma cewa "Allahumma..."

Tsayuwa ya yi yana kallonta cikin wani irin yanayi mai kashe jiki "karasa mana."

Sai ta daure fuska ta cigaba

"Allah Kasa duk wadda Daddyn Qibdiyya ya gani ya yiwa magana ta ce an kawo kudin aurenta."

"Diamond girl" ya ce yana dariya sosai "I love you."

A guje ta tashi ta bar wurin har tana tuntube da kujera akan hanya.

Munzali ya dinga murmushi yana mai mamakin yadda zukatansu suka zama mallakin yaya da kanwarta lokaci guda.

*

Filin rawa Lilu yaje ya yi abarsa son rai ya dawo inda Sauda take tare da Qibdiyya. Yarinyar ta sake abinta tana ta yi musu hira. Tana ganin Lilu ta gudu wurinsa. Sauda ta ce.

"Baban yara ita ma ka sayeta kenan"

Ranar har su Abbati suka tashi tafiya Qibdiyya tana hannun Lilu. Kowa sai da ya shaida yadda tasu tazo daya daga haduwa. Da ya zo sakata a mota shi da iyayen nata babu wanda ya kula cewa kiss ta so yi masa a baki. Dama ce bata samu ba saboda tana yunkurowa ya sauketa a jikin Abbati.

Kuruciya bata barta ta dauke shi komai ba. Uncle Daddy ne kadai yake yi mata. Sai kuma mutanen cikin ire iren bidiyo da yake kunna mata ya ce tayi masa abin da ta gani. Ta fanin kallo Zakiyya tana matular kokari don ko fim ta daina kallo a gaban 'yarta saboda kaifin basirar yarinyar. Shi yasa bata da aiki sai karatun waya. Sakacinta a bangaren saka ido ne a cikin gida. A zatonta tunda suka fito ciki daya da Daddy ba zai taba cutar da ita ba balle 'yarta.

(Ya ke UWA mai dimbin daraja da martaba. Ba a ce ki sanya zargi da kokonto a tsakanin mu'amalar 'ya'yanki da 'yan uwanki ba. Nagari masu sonmu da gaskiya sun ninka shaidanun. Yana da kyau amma ki kula da irin shakuwarsu ko tsoronsu da yara ke ji. Idan tayi yawa to wajibi ki bi abin cikin laluma ki gano musabbabinsa. Ita alakar da aka gina da taba jikin juna a waje tana da wuyar bari. Shi yasa ma yaran da ake yiwa fyade ko koya musu mummunar dabi'a ake samun wahalar hanasu. Sai kin dinke baraka tsakaninsu da mai koya musu sai suje suna nema a wurin wasu da kansu. ZINA MASIFA CE GA BABBA DA YARO! Rabuwa da ita sai an dage sosai.)

***

KIRIKASAMMA

Dakin Baaba Mari babu haske sosai saboda ta gama shirin bacci. A kwance take tana ta juye juye akan gado. Jikarta ta wajen Atine da suke kwana tare sai munshari take abinta. Gajiya tayi da tunanin da ya addabeta ta tashi za ta dauro alwala kamar yadda aka koyar dasu a islamiyya. Babu wani abu da ya gagari addu'a, musamman a hada da qiyamul laili.

Alwala taje ta dauro a bandakinta wanda Abbati ya yi mata a falo. Da yake fitilar chaji ta kunna tana iya hango tsakar gidansu sosai. Maigidanta ne har yanzu shadaya da kwata na dare zaune tare da Mal. Sa'adu wanda ya yi uwa ya yi makarb'iya akan bakon da suka yini dashi. Su uku har bakon hira suke suna dariyar wani abu da ya fada.

Daki ta wuce ta dauki hijabi da abin sallah. Komai a sanyaye take yi saboda wani kwantacwn abu da bata san a ina yake ba yana fada mata akwai matsala. Ko Munzali bai taba zuwa Kirikasamma shi kadai ba. To me zai sa 'yan satittika da nad'in sarautar Abbati shi wannan Shazalin ya dawo?

SHIDA RANAKUN...

***

Gari ya waye, rana ta fito tun karfe shida da rabi. Zuwa goma na safiyar Asabar jama'ar dake waje har sun fara jin zafinta. Sai dai wannan zafin ba zai hana masu uzuri a waje fita su gabatar dashi ba. Kamar kowacce rana ga dan Adam, ita ma wannan Asabar ta zo a matsayin ranar kuka, farinciki, dariya, bakinciki, fargaba, alhini da kowane irin yanayi da mutane ke tsintar kawunansu.

A safiyar wannan Asabar din ne Uwani ta amsa wayar Mubashir mai tafe da mummunan labari akan gininta.

A ranar ne kuma Shazali ya wayi gari a Kirikasamma bayan ziyarar bazata da ya kaiwa gidansu Abbati.

Ita ce kuma ranar da Hasiya ta zaba domin kai wa Salima kukanta akan saurayin Ayaah.

Duka dai kuma a wannan ranar ne Abbati da Munzali suka je daurin auren kanin Mami Khadija bayan dinner din da suka je ranar Juma'a da daddare. Dinner din da basu baro ba sai da suka tabbatar an sami musayar zukata tsakaninsu da 'ya'yan Alh. Tahir guda biyu.

***

Ana kiraye kirayen sallar Magariba Shazali ya isa Kirikasamma. Girkin abokiyar zaman Baaba Mari ne. Tana jin an ce abokin Abbati ne ta fito daga rumfar da suke girki tana fadin maganganu. Ciki har tana cewa

"Ban san da zuwan bako ba saboda haka ban girka dashi ba."

Baaba Mari ko tari bata yi ba har ta juya ta tafi. Bakinciki da hassada ba bakon abu bane gareta daga wurin kishiyar dake morar arzikin Abbati. Niyarta idan an kawo mata nata abincin ta bashi. Sai gashi an hada masa gara guda daga bangaren Mal. Sa'adu. Atine da Habi su ma ba a barsu a baya ba saboda kada mahaifiyarsu ta wahala. Kowacce ta aiko da abinci.

Ashe kusan karfin girkin ma 'Yashshafa ce tayi. Deluwa ta rasa inda za ta saka ranta domin a burge wannan bako. Mahaukaciyar motar da yazo da ita kadai ta ishi bawa shiga rudani. Akan Shazali ita mai iya hakura da Sha'aib ce kamar yadda take kiransa.

Kafin lokacin kwanciya baccin da Baaba Mari ta kasa runtsawa Mal. Inuwa ya shigo dakinta. K'aidarsa ce zaga matansa da asuba da kuma bayan Isha. Da murna ya shigo mata yana yabawa baiwar dansu wanda har masu kudi ke ziyartar iyayensa.

"Idan aka kirani da Uban Abbati sai naji duk garin nan babu ya ni. Dubi dai ace mutum mai arziki kamar wannan ne a gidanmu..."

Kula ya yi hankalinta ba ya gare shi ya bata rai.

"To yanzu kuma me ya faru? Tunane tunanenki na banza akan arzikin danki ne ya sake dawowa?"

Murmushin yake tayi tare da kawar da kai domin ko za ta kwana tana bayani baya taba fahimta.

"Malam kenan."

Komawa ya yi ya zauna yana dubanta cikin yanayin da yaki jinin ganinta.

"Ki fadi damuwarki tunda nayi imanin akwai. Yau da ace ba Inna Mairo ce ta karbi haihuwar dan nan ba sai ince ba naki bane shi yasa kike gwada masa halin matar uba ko dan riko. Ni ko da wasa ban taba jin uwar da take yiwa dan cikinta bakincikin samun arziki ba sai ke Mari."

"Har yanzu kana ganin laifina don na damu da son sanin silar kudin da mu da danginmu muke ci? Daga zuwa almajiranci sai kudi kamar suna zuba daga sama?"

Ransa ya soma baci amma ya danne domin baya son rigima a daren nan.

"To meye a ciki? Arziki ba na Allah bane? Kuma yana baiwa wanda ya so bi ghairi hisaba. 'Yan kasuwa nawa ne suka fara a matakin da yafi bara kaskanci amma yanzu sun wuce sa'a?"

"Cikinsu kuma kowanne idan an tashi zaka ji an cewa abu kaza yake sayarwa ko yake kerawa. Shin ka taba tambayar kanka me Abbati yake sayarwa? Ka taba ganin wani abu cikin kayan sayarwarsu ya kawo gidan nan?"

Shirunsa ya bata damar cigaba da magana cikin lumana.

"Malam ni da kai mun sani cewa yaron nan duk fadi tashinsa yana yi ne domin ya inganta rayuwarmu. Kafatanin gidan nan babu wanda Abbati bai shiga rayuwarsa ba." Muryarta sai ya karye tun kafin ta fadi abin da ke zuciyarta "dan nan yaron kirki ne ba don ni na haife shi ba. Amma ina tsoron kada haram..."

"Ya isa!" Mal. Inuwa ya furta yana mikewa. Zargin ta dasa masa wanda ko kadan bai so ba. A duk lokacin da son bincikar dan nasa ya bijiro masa sai tsoron abin da zai

tarar ya hana shi. Amma yau yaji wani irin nauyi ya sauka a zuciyarsa mai tayar da hankali.

"Allah Ya huci zuciyarka. Mu kwana lafiya."

Daga wadannan kalaman ya shige uwar daka ta barshi. Ya fita zuciyarsa tana ta wasiwasi. Amma yana zuwa wurin Mal. Sa'adu da ya same shi da Shazali suna hira sai ya tura zarginsa baya.

Da safe Deluwa har dakin da aka sauke Shazali ta tura 'Yashshafa ta kai masa abinci. Ta hada mata da hududbar kwarkwasa domin daukar hankalinsa. To 'Yashshafa ko kadan baiyi mata ba daga kallon farko. Akwai kudi ta gani daga sutura da motarsa. Bashi da wani muni amma mummuman nufin dake zuciyarsa ya tasirantu a cikin ji da ganinsa. Ko murmushi yake idan ka kalle shi zuciya sai ta harba saboda shaidan ya gama dashi. Da zumbura baki tayi sallama kuma yana amsawa ta ajiye a bakin kofa ta gudu abinta. Gara dai a mayar da ita Kadunan ko sa saba da Suhaib. Matsalarta daya akansa bata wuce kaninsa da ya kirata Iya duba-duba ba. Idan ta auri yayansa sai ta tashi tsaye ta saita shi don kada ya rainata.

Wajajen biyu da rabi aka raka Shazali bangaren Baaba Mari zai yi mata sallama. Ita kadai ce a falon nata tana sauraron rediyo.

'Saboda ke Abbati bai isa ya jika min aiki ba. Munzali baya ketare maganarsa. Idan ya ce su komo gareni karshenta da gudu zai biye masa ya amince.'

"Zauna mana"

Baaba Mari ta furta da dan karfi domin ta dawo dashi daga duniyar da ya luluk'a. Jikinta har sanyi ya soma yi da ya shigo saboda kallon da ya kafeta dashi yana tunanin yadda zai bata mata da.

Gaisheta ya yi da girmamawa da zai tafi ya kawo dubu hamsin ya ajiyeta a kusa da ita. Kudin ma tsoro ya bata tunda bata san manufarsa ba. Haka kawai ya zo ya kwana kuma gari ya waye zai tafi ya hadata da kudi.

"Daukesu don Allah."

Nunawa ya yi kamar bai ji dadi ba ya yi magana cikin rashin walwala.

"Don Allah ki dauka kisa mana albarka. Na san da Abbati ne ba za ki ce ya dauke ba."

"Duk da haka ai kai bakonmu ne. Ni dai don Allah ka dauke nagode."

Wayarsa ya zaro yana cewa "tunda baki daukeni d'a ba bari na kira Abbati da kansa ya fada miki matsayina."

Matsawa tayi daga inda kudin suke tana sauraron alamar shigar kira saboda speaker ya saka. Sau hudu ya kira Abbati bai dauka ba saboda suna zaune da Munzali suna amsa tambayoyin Alh. Tahir da wasu yayyensa. Sakon text Shazalin ya tura masa wanda ya saka shi kira hannu na rawa bayan ya tashi ya fita.

(Ina dakin Baaba Mari a Kirikasamma)

Shazali sai ya dauka ya kuma danna speaker a lokacin da Abbati yake magana hankali a tashe. Ya gama birkicewa gami da tsorata. Magana kawai yake yi yana mai jin inama zai iya bude ido ya ganshi a gidan.

"Ban gane kana dakin Baaba ba? Shazali me zai kaika gidanmu."

"Zumunci mana."

"Zumunci? Ko da can ka taba jin na nemi yin zumunci da kai da balle yanzu?"

Shazali sai ya kalli Baaba Mari ya marairaice kamar kalaman sun bashi mamaki shi ma.

"Ka bari na fita nan ba wurin wannan maganar bane. Ni kararka na kawo mata akan kasuwancinmu. Sana'ar tana kawo kudi kana neman durk'usar damu."

Daga bayan fage (background) Abbati yaji ana kiran sunan wata ya kuma gane muryar mai kiran da sunan wadda aka kiran duka 'yan gidansu ne. Hankalinsa sai ya nemi gushewa saboda tsananin tashin hankali da ya gane da gasken yana gidan. Gargadin da yake yi masa ma a raunane ya fito domin yana daf da fita daga hayyacinsa.

"Shazali! na rantse idan ka fada mata wata magana sai ka raina kanka. Hummm....Kai bari kaji in fada maka, idan ka sake ka fada mata abin da zai tayar mata da hankali sai na dauki mummunan mataki a kanka."

Baaba Mari tana daga zaune amma jiri ke dibarta. Hannuwanta ta sanya ta rike gefe da gefen kujerar two seater da take kai a zaune. Idanunta a rufe taji muryar Shazali yana bawa Abbati amsa. Tasa muryar a nutse take fita da wani abu da za a iya kira da nasara.

"Kwantar da hankalinka ni hanya ce ta biyo dani na zo muka gaisa. Ban san sadar da zumunci da iyayen aboki laifi bane da ban zo ba."

Kashe wayarsa ya yi ya juya ya fita ko sallama bai yiwa Baaba Mari ba. Bukatarsa ta riga ta biya. Ko yanzu kasuwa ta tashi Dankoli ya ci riba. Bukatunsa akan Abbati biyu ne. Ko dai tsoron tonon asiri a wurin mahaifiya da danginsa yasa shi komawa ruwa ko kuma asirin ya tono ya zubar masa da mutumci kamar yadda ya hana shi cigaba da samun kudi. Yadda ya san Munzali yana jin maganar Abbati ko uwar da ta haife shi baya jin ta isa dashi. Umarnin da hani a hannunsa suke. Shi yasa ya zabi biyo masa ta bayan gida.

Abbati ya dinga kiransa wani kiran na tarar da wani amma yaki dauka sai da ya shiga mota. Idanunsa na kallon Mal. Inuwa da Mal. Sa'adu tare da wasu kawunnan Abbatin suna ta dago masa hannu. Murmushin mugunta ya yi sannan ya amsa wayar. Shi ya fara magana bai ma saurare shi ba, kuma yana gamawa ya katse kiran.

"Zabi ya rage naka Abbati. Kafi kowa sanin cewa ina da abubuwan da zan nunawa tsohuwarka wanda zai sa ta tsine maka yau dinnan ba gobe ba. Ka fadawa Munzali na ce ku same ni a Port Harcourt jibi."

***

Awanni uku da rabi kafin waccan mummunar wayar sun zo wa Abbati da Munzali tare da masoyansu da abubuwa daban daban. Ga Abbati da Farha, wata kofa ta karin sani da fahimtar juna ce ta bude musu bayan an dawo daga daurin aure.

Sai ta kurewa Suhaib a waje yake yarda magana ta hada shi da mahaifinsa. Sai dai yau ta sha bamban da kowacce rana. Jiya bayan sun dawo daga dinner Farha ta fada masa yadda suka yi da Abbati. Shi da Mami wadda ya fadawa zancen duk sun yi mamakin jin bai yi karatu ba sai na yaki da jahilci.

Tabbas Mami Khadija za ta so 'yarta ta auri mai ilimin boko bayan na addini sai dai kuma ta duba abubuwa da yawa. Na farko dadewar Farha a gida babu wanda ya taba cewa yana sonta (kadan daga cikin shukar Alh. Tahir da zuri'arsa suke girbewa). Yabawa da hankalinsa da mutumcin mahaifiyarsa. Sai kuma ganin girman soyayyar da Farha take yi masa.

Dasu aka daura auren sannan suka bi su Lilu gidan Kawunsu inda aka shiryawa Ango reception. Suhaib ya hango Alh. Tahir cikin mutane. Sai da yaga ya bar jama'ar dake tare dashi ya fito daga karkashin katuwar canopy din ya bishi a baya.

"Ga bakin Farha da Mardiyya zasu gaisheka."

"Suhaib kenan. To ina kwana?" Cewar Alh. Tahir yana mai jindadin maganar da dan nasa ya yi masa ko a wane yanayi ne.

Shi ma Suhaib sai yaji kunya ya dan rissina da murmushi a fuskarsa. Murnar alakar dake tsakanin Abbati da Farha ta cire masa damuwa sosai. Wannan kuwa ya biyo bayan nishadin da yake ganin Mami Khadija tana yi saboda ganin walwalar 'yarta. Kansa ya dan shafa ya ce,

"Abba ina wuni? Ya taro?"

Bai iya boye jindadinsa ba kuwa "Lafiya kalau. Suna ina bakin? Ko na rannan ne da suka zo gida?"

Da Suhaib ya tabbatar masa su din ne sai ya ce su dan jira shi minti kadan zai je ciki ya gaisa da kakaninsu da suka zo. Sannan tunda akwai 'yan uwan Alh. Tahir din mazauna Kano, zai fi son su gaisa dashi a gabansu domin a taya shi bincike.

*

Munzali ya kasa nutsuwa da Suhaib ya fada musu zasu gaisa da Alh. Tahir da kawunnansu.

"Idan wani ya san mu ko wanda ya san mu fa?"

Ya ce jikinsa a sanyaye ga wani tsoro yana shigarsa. Idan ka cire Qibdiyya, to Mardiyya ce mace ta biyu da yake matukar so. Asabe darajar haihuwa kadai ta samu a wurinsa saboda watsi dashi da tayi.

"In sha Allahu babu komai"

Abbati ya sami kansa da karfafawa Munzali gwiwa duk da a zahiri ya fi shi jin tsoro.

Manyan mutane sun halarci daurin auren saboda baban amaryar dan siyasa ne. Shi kuma ango danginsa manya ne a ma'aikatun gwamnati daban daban. Dole su tsorata saboda ire irensu sune abokan mu'amalarsu a baya.

*

Mardiyya ta gama shiri za ta fito su gaisa da Munzali kafin Alh. Tahir ya kirasu Mama Nasima ta tsayar da ita. Dakin da babu kowa ta shigar da ita ta damka mata wata 'yar leda.

"Yi maza ki bude ki saka kwallin kafin wani ya shigo."

"Kwalli kuma? Kinga idona fa na saka." Ta matso da fuskar gaban mahaifiyarta sosai.

Mama Nasima ta daure fuska da sauri ta kwance ledar ta miko mata abubuwan dake ciki.

"Kwallin mallaka ne. Ki saka sannan ki shafa hodar ki fita wurin Alh. Munzali."

Ja da baya Mardiyya tayi da sauri bayan ta mayar da kullin ledar tafin hannun mamanta.

"Ba zan saka ba."

Kiris ya rage Mama Nasima ta mareta

"To shashashar banza. An fada miki mazan yanzu ana sanya a kansu ne? Tun yanzu idan bamu tashi tsaye ba kina ji kina gani wata za ta kwace shi a hannunki. Yau da sassafe Dini (kaninta) ya shigo mota domin ya kawo amma za ki fara yi min shirme."

Kwalla sai ta taru a idon Mardiyya. Tana son mahaifiyarta amma taki jinin halayen da ta tashi ta ganta a kansu.

Mama Nasima da ta fuskanci kamar abin bai mata dadi ba sai ta wayance ta koma lallabata.

"Kafin ki fara yi min wa'azi tun wuri ki sani ba kayan boka bane. Haba Mardiyya, kamar baki sanni ba? Wannan wani malami ne wanda ya dogara da Qur'ani. Ko kasa zai buga miki sai ya kama sunan Allah."

"Mama ni dai ki daina wasa da lahirarki a kaina. Malamin Allah babu ruwansa da duba ko buga kasa."

Ba don bakunta da idanun mutane ba da Mama Nasima ta kai mata duka don haushi.

"Baki ji na ce yana Bisimillah kafin ya fara don ya kori shaidanu ba?"

Cigaba da maganar zai iya saka Mardiyya yi mata rashin kunya wanda ba halinta bane. Sai kawai ta zabi fita daga dakin cikin kunar rai ta iske Munzali da Abbati a inda Suhaib ya ce suna tsaye.

Tun daga nesa Munzali ya gane tana cikin bacin rai. Wurin wata mota ta tsaya ya ka a ya sameta. Yana isowa wayarta ta hau ruri. Sunan (Mama) ya gani a jikin wayar kafin tayi saurin kashewa. Murmushin yake tayi masa wanda akan ce yafi kuka ciwo. A zuciyarta kuwa tana tararrabin kada Maman ta biyo bayanta. Yanayinta na mai son boye zahirin halin da take ciki ya fi komai damunsa. Karamar yarinya ce da ta dauki nauyin saita mahaifiyarta da boye aibunta. Abin da shi Munzali mai shekaru da suka kusa rubanya nata bai yi ba duk kuwa da shawara da fadan amininsa. A lokacin da Abbati yake masa wannan fadan yana ganin tamkar bai gama fahimtar matsalarsa bane tunda ya tashi gaban uwa tagari. Sai gashi ya hadu da Mardiyya cikin yanayin dake kusanci da wanda ya taso a ciki. Kuma tana gwada sabanin abin da ya dinga yiwa tasa mahaifiyar.

Girmanta ne ya karu a idanunsa tare da wata irin soyayya mai ratsa zuciya. Murmushi ya yi mata ganin duk ta takura kanta tana ta waige waige.

"Ashe nayi kuskuren tunanin zan zama mai baki shawara game da abin da ya shafi rayuwarki Diamond girl."

A razane ta dube shi sai ta sadda kanta kasa saboda kallon da yake mata ya nuna maganarsa ta jindadi da yabawa ce.

"Idan baka bani ba wa ka samu da zai bani?"

Ido cikin ido ya kalleta ya kuma kada yatsansa yana mai gargadinta da kada ta kaucewa kallonsa. Daurewa tayi ta cigaba da kallonsa zuciyarta tana rawa.

"Zuciyarki ce za ta dinga bamu shawara Mardiyya. Da ka nake tafiyar da personal matsalolina. Amma na gane kan yana kuskure domin a zuciya ne akwai jin kai da tausayi. Tawa zuciyar kuma karama ce akan taki ta wannan fanin. Shin za ki karbi amanar wannan bawan Allahn dake neman hasken bin iyaye ki gyara masa rayuwa? Kin amince na gabatar da kaina a matsayin manemin aurenki? Za ki iya aurena nan da wata hudu da kin kammala secondary?"

Murmushi tayi ta cukwikuye fuskarta cikin mayafi. Ga duka tambayoyinsa tana gyada kai na amincewa.

*

Farha kuwa da ledoji biyu masu dauke da abincin da aka raba na reception ta fito. An yi packaging abincin cikin mazubin roba mai kyau sai lemon ginger da zobo a robobi suma duka masu kyau da dadin rikewa. Ledar da aka saka su a ciki ta gaba sunan ango ne da amaryarsa. A baya kuwa tana dauke da tambarin /D Delight/ kwararru wajen girkin taro tare da abin sha (online cooking classes for Ramadan coming soon in sha Allah. Come and patronize Batul Mamman please.)

Abbati kadai ta hango saboda Munzali yana tare Mardiyya. Tun kafin ta karaso suke yiwa juna murmushi.

"Ya Farha kin tayar min da duka kishina da wannan kwalliyar. Ina tafiya ki je ki goge indai ba a ciki zaki zauna ba."

Dariya tayi a hankali "so ka ke na dauka da gaske kake har na fara jin nima na isa?

Hararta ya yi da jin furucinta ta cigaba da yi masa dariya. Dolensa ya soma tayata domin gabadaya yana neman shagala da kallonta.

"Kin yi yawa ma. Kin kuma san da haka. Fatana kawai kada Allah Ya kawo abin da zai iya shiga tsakaninmu."

"Kana ganin akwai?" Sai kuma tayi murmushi "kodayake yawancin kullum sai naci karo da sakon Malama hide my ID idan an kawo kararku."

"In sha Allahu ba zan taba yi miki abin da zaki kaini kotun social media ba." Ya furta da alamun tsoron da ta zata na wasa ne.

"Allah Yasa"

Kasa hakuri ya yi ya dora da cewa "ko kin ji wani abu nayi miki rantsuwa ko meye ya zama tarihi. Zan zame miki miji nagari in Allah Ya so."

"Allah Ya yarda" ta amsa da karamar murya.

"Da gaske nake sonki Ya Farha. Burina na zama mijin da babu abin da zaki ji a kaina ki yarda kai tsaye ba tare da bincike ba."

Kalaman nasa sun fara bata tsoro. Shi kuma firgicinsa akan tunanin idan gaskiya tayi halinta watarana ne. Rokonsa tayi da sigar da bai ga kofar kubucewa ba.

"Kayi min alkawari daya Ya Abbati..."

"Kina son wani abu ne bayan ni?"

Girgiza kai tayi tana murmushi "kwantar da hankalinka ba mutum bane."

"Au tohh. Ina jin ki. Nayi alkawarin."

"Babu zancen sirri ko rufe wani abu da zai zo tsakaninmu nan gaba. Ko aure ka ke son karawa ka fada min da wuri ba don neman izini ba sai don bani da boye boye kuma bana son ayi min."

Jikinsa ya yi sanyi kalau yaji tsana fiye da ta baya game da rayuwarsa.

"In sha Allahu irin zaman da zamu yi kenan. Kuma tunda kin amince min zan sanar da iyalina game dake tun kafin iyaye su zo."

Hira suka soma gwanin sha'awa basu ankara ba ashe Alh. Tahir ya fito kiran Suhaib domin kiransu Abbati cikin falon. Da ya hango Farhansa tare da Abbati sai da yaji zuciyarsa ta wani takure a kirjinsa. Abu ne dai bai taba ji ko gani ba tun tasowarta. Damuwar da suke da ita shi da Mami akan wannan matsala yana sa ran cewa ta kau. Tahowa ya yi garesu fuskarsa a sake ya ma manta da fushin Farha.

Ita ta fara ganinsa ta daure fuska sosai. Bata da yadda zata yi da zuciyarta akan bakincikin hoton da kwakwalwa ta kasa gogewa. Mahaifinta dauke da kawarta akan cinya daga shi sai dogon wando da singeleti. Wannan abu har ta koma ga Allah bata jin zai taba fita daga ranta. A yadda kuma abin yake mata ciwo har yanzu ta san bata da karfin gwiwar fuskantarsa ba tare da tayi abin da za ta yi nadama a gaba ba.

Gajeren tsakin da zuciya tafi karfinta a kai ne ya fito ba shiri a lokacin da take cewa Abbati,

"Don Allah zo mu koma daga can saboda idon mutane."

Yaji tsakin sannan kuma muryarta ta sauya lokaci guda. Juyawa ya nufi yi domin ganin wanda ya bata mata rai sai yaji ta ce,

"Kar ka juya mana.."

Sai dai ya riga ya ga Alh. Tahir din wanda fuskarsa take tamkar gonar auduga. Ya juya ga Farha ita kuma tata babu annuri ko digo sai ma kwalla da ta cika mata ido. Sai yaki motsawa daga inda yake. Yana ganin ta fara tafiya bai san lokacin da tasa muryar ta fito da sigar umarni ba.

"Dawo ki tsaya."

Sau daya ta kalli fuskarsa wadda ta sauya shi ma babu wasa ko kadan taji kafafunta sun daskare a wurin.

Alh. Tahir yana karasowa Abbati ya durkusa cike da ladabi ya gaishe shi. Ya amsa masa tare da mikar dashi tsaye ta hanyar dago hannuwansu da suka yi musabaha. Wanda kuma Alh. Tahir din ne ya mika masa.

"Tashi tashi ai ka zama dana."

Wajen sati guda sai yau yasa Farha a idonsa. Amfani ya yi da albarkacin idon Abbati ya janyota barin jikinsa.

"Farhan Abba wato tun yanzu za ki min ritaya ko?"

Da kyar ta saki jiki ta rabu da jikinsa amma har runtse idanu tayi saboda tsigar jikinta da ta tashi. Mahaifi! Sanin mahaifinka yana zina daban da ganin mahaifinka a yanayin da ya kusanci zina. Yanayi mai nuni da cewa anyi ko ana gabar yi. Its devastating! Kada Allah Ya hadamu ko zuri'armu da mummunan gani irin wannan.

Abbati dake dariyar kalaman Alh. Tahir bai fasa la'akari da yanayinta ba. Hakan ya tuna masa da abin da Suhaib ya yi rannan a gabansu na kin zuwa gaishe shi. Ko ba a fada ba ya gane akwai matsala kenan.

"Ki bamu aronsa kakaninki da baffani zasu gaisa dashi." Cewar Alh Tahir. Sannan ya dubi Abbati "ina fata kai da abokinka da gaske kuke akan 'ya'yana. Idan akasin fahimtarmu ne a gabanku don Allah kada ku yaudaresu."

"In sha Allahu ba za mu baka kunya ba" Abbati ya furta kai a kasa.

Alh. Tahir sai ya murmusa "Allah Ya muku albarka. Bari na nemi Suhaib a waya ya shigo daku wurin 'yan uwana."

Da haka ya tafi. Farha ma sai ta daga kafa tana shirin barin wurin. Da muryar dazu ya ce,

"Farha."

Kiran ya fadar mata da gaba. Ya tuna mata cewa Abbati babba ne ta kowacce fuska akanta. Ko Suhaib bai isa ya kara dashi a shekaru ba balle ita. A hankali ta juyo suna hada ido sai hawaye ya soma gudu a kumatunta. Kallon roko da magiya tayi masa sannan ta fadesu da baki.

"Don Allah kada ka tambayeni komai."

Sai ya sami kansa da yin murmushi "bani da niyar tambaya. Amma duk da haka ina da abin cewa idan kin bani dama."

Sai ta dawo ta tsaya sosai lokaci lokaci tana goge hawayenta da bayan hannu.

"Yanzu kin ga idan ba ni ba babu wanda zai ce kin burge shi da wannan fuskar da ta baci da kwalli."

Sai da yaga murmushinta ya soma magana a nutse.

"Ya Farha darajar mahaifi da mahaifiya ta girmi komai da kowa banda da'a ga Allah da ManzonSa SAW."

"Na sani" ta ce a raunane wani hawayen yana zubowa.

"Ina mai baki shawara da kiyi amfani da wannan ilimin ki bi hanyar da ta dace ta mu'amalarki da Abba."

Babu wasa ko damar tayi masa musu a maganganunsa. Cigaba ya yi har sai da ta fashe da kuka sosai.

"Allah SWT Ya yi mana dukkan gata da bai watso mu cikin duniya ba tare da iyaye ba. Daga Mahaliccinmu sai Annabinmu sannan iyaye a girman daraja. Allah Ya ambaci yi Masa biyayya tare da da'a ga iyaye a wurare daban daban cikin littafinsa mai tsarki. Karshe ma dai iyayen nan kin sani saboda adalcin musulunci ya horemu da kyautata musu ta kowacce siga koda mushirikai ne. Illa iyaka kada mu yi musu biyayya wurin saba Masa. Tunda sune abu mafi kusanci da suke tuna mana da Girma da Buwayar Allah. Cikin hikimarSa ya hado mutane biyu mabanbanta jinsi da komai Ya ce musu ga amanar bayiNa wato 'ya'ya. Sai ki ga mutum har sata ya kan yi domin ciyarwa ko dauke wata lalurar wannan amanar. Wani ayi ta cin zarafinsa a wurin aiki amma ya yi ta jurewa saboda albashinsa shi ne abincin 'ya'yansa. So many things dai da ba sai na fada ba. Wasu irinmu mu da bai bawa 'ya'yan ba har kuka muke muna fargabar ko girman zunubanmu ne yasa Allah bai bamu amanar bayinSa su zo a matsayin 'ya'yanmu ba..."

Kuka ta fashe dashi domin ya gama daureta da jijiyoyinta. Ta san Qibdiyya ba 'yarsa bace kuma bai ce mata yana da d'a ba. Amma da ya fada da bakinsa sai da ya tabata fiye da zato.

"Kayi shiru don Allah, za ka haihu in Allah Ya so....na fahimci kuskurena kuma Allah zan gyara."

"A yau ba gobe ba?"

"A yau ba gobe ba."

Murmushi ya yi ya ce "Allah Yasa ke dinnan rabona ce ta duniya da lahira"

Amin ta ce yadda zai ji domin ita kam bata jin kunyar ya san cewa tana yi masa soyayya mai girma. Duk mutumin da zai gan ka a irin yadda ya ganta ya kuma zauna yana kokarin ganin ka gyara lahirarka baka da na biyunsa.

Basu gama hirar ba Suhaib ya zo suka wuce cikin falon tare da Munzali. Da wasa da dariya dattijan suke yi musu tambayoyi har aka gangaro kan sana'a. Bakinsu a hade suka ce kasuwanci suke yi. Iyayen sun yaba da halayyar da suka gansu a kai aka shiga barkwanci.

Wannan lokacin Shazali ya zaba ya kira Abbati. Kiran da Munzali ya fito ya same shi a mawuyacin yanayi a dalilinsa. Jijiyoyin kansa duka sun fito sai gumi da yake tsatstsafo masa saboda firgici.

"Allah mun tuba. Allah Ka rufa mana asiri"

Kalmominsa kenan har suka shiga mota a gigice suka tafi ko sallama basu koma sun yiwa kowa ba.

"Idan ya fada mata wallahi da kyar in bata tsine min ba. Munzali yaya zanyi da rayuwata kuma? Me zai rage min idan Baaba taji wannan zancen?"

Abbati kuka yake yi. Kuka kamar karamin yaro. Irin kukan da ya manta rabonsa da yin makamancinsa. Bai hada iyaye musamman Baaba Mari da kowa ba. Ita ce mafi girman gatan da Allah Ya bashi domin ba don ita ba kila bayan waccan dabi'a sai ya hada da wasu munanan alfashar.

Munzali ma kukan yake yi ya kuma kasa rarrashin Abbati. In ta kwabewa daya ta kwabe musu ne su duka. Hanyar Kirikasamma ya dauka ba tare da tunanin komai ba.

BAKWAI RANAKUN...

***

Kallon jan fentin da aka yiwa alamar (×) a jikin gidanta Uwani tayi taji jiri yana dibarta. Tambayar Salihi ta dinga yi cikin sarkewar harshe kamar ya san wani abu a kai.

"Me nayi? Ina da takardun filin nan da sa hannu wanda na saya a wurinsa. Kai hatta Mai unguwa sai da muka je yasa hannu a matsayin shaida."

Duk da yana cike da haushinta sai ta dan bashi tausayi a lokacin. Ba kuka take ba domin tana da bala'in dakakkiyar zuciya. Jikinta ne kawai ya saki sannan sautin muryarta ya fallasa tsoro da tashin hankalinta.

"Ki kwantar da hankalinki tunda akwai takardu za a warware cikin sauki in sha Allahu."

Sambatu ta dinga yi kamar ba da ita yake ba. Katangar gidan ta nuna masa inda tasa aka yi baya da ita kawai don tana son ayi mata rela samma tana tsoron kar ta shiga filin gwamnati. Shi dai hakuri ya bata har suka koma mota tare da Mubashir a baya. Niyarsa su je gida ta amsa kiran Innayo sai ta kafe akan lallai ofishinsu can Ministry of Health zata je ta sami Habibu.

"Shi ne ya jagoranci sayen filin da komai. Zuwa zai yi ayita ta kare don wallahi asara bata kamani ba."

"Waye kuma Habibu?" Salihi ya tambayeta. Bacin ransa na dawowa sabo fil.

"Abokin aikina ne. Shi ya tallata min filin ya kuma shige min gaba."

"Tunda kin auri lusari ai dole wani kato ya fini sanin halin da kike ciki Uwani."

A kausashe Salihi yayi maganar wanda yasa Uwani shan jinin jikinta. Borin kunya ta soma yi masa saboda ta san bata da gaskiya.

"Damuwa kayi dani da zaka san me nake ciki? Ko kai ba aure kayi ba tare da sanina ba? Habibu duk inda yaji harkar karuwa zai nemeni. Kafin ka ce ban fada maka ba ma shi na bawa ya biya min kudin Hajji. Bana damu za ayi 'yan bakinciki su daina hura mana hanci."

Da kannensa mata take ya sani. Shi yasa bai ce komai ba har suka isa gate din BUK ya sauke Mubashir. Kai tsaye ministry din ya nufa sai ga waya an kirata. Koda ta duba sunan (Costumer) ta gani ya bayyana. Murmushi a take ya maye gurbin bacin ranta. Amsa kiran tayi taji muryar Hajiyar nan da ta haihu tana yi mata magana cikin nutsuwa. Uwani ta ajiye komai a gefe ta saurari kwatancen gidan da matar tayi mata.

"Ka saukeni 'Yan Kaba zani" cewar Uwani ga Salihi.

"Ai ko direba nake ya kamata ki rissina lafazinki gareni."

Yatsina fuska tayi ta gyara lullubi sannan ta hayyako masa da fada tana jin kanta daidai da kowa tunda ta tabbatar zata sami kudi. Cikin kudin za ta bawa Habibu a kashe kurar dake neman tashi a gidanta su sallami KNUPDA.

"Sau nawa nake cin arzikin shiga motar taka da har zaka min gori? "

Girgiza kai kawai ya yi "wurin wa zaki a 'Yan kabar?"

"Stitches zan yiwa wata."

"Allah Ya kiyaye hanya."

Sauketa ya yi ta fita ta shiga adaidaita sahu. Yadda yake jin bacin rai ba zai juri ja in ja da ita ba. A yau kadai ya gane har yawon dinke mata take zuwa bai sani ba. Sai yake jin kamar ma bai san wace ce yake aure ba. Karya kwana ya yi ya nufi Ministry din yana son ganin wannan Habibun domin zuciyarsa taki nutsuwa. Ba wai zarginta yake ba domin ya yarda da ita dari bisa dari. Duk bakin halinta ya yarda za ta tsare

mutumcinta duk inda take. Harka dai ta kudi ce bashi da tabbas. Idan yana son gyara lamuranta ya kamata ya fara da sanin abokan huldarta.

Da kwatance da kiran waya Uwani ta isa gidan CMD. Bata wani sha wahala ba saboda kwatancen dalla dalla ne duk da ba a fada mata sunan maigidan ba. Hankali kwance ta shiga wani makeken falo bayan anyi mata iso. Gida ne babba irin wanda take burin mallaka wataran. Nan da nan ta sake ganin kimar hajiyar tana tunanin yadda za ta tatsi naira jikinta da kawayenta matan masu kudi.

"Haj. Umma ta ce ki shigo ciki"

Muryar mai aikin da ta shigo da ita ta katse tunaninta. Sai lokacin taji sunan matar. Wata kofa suka bi sai gasu a wani falon da ya shafe shafin inda ta baro. Sai da ta zauna akan wata luntsumemiyar kujera sannan matar ta tafi. Kimanin minti bakwai sai taji sallamar Hajiyar. Fuska ta saki tana mai kara raina kanta. Kama daga sutura zuwa su sarka babu ta inda Haj. Umma bata burgeta ba. Tashi tayi cikin girmamawa tana yi mata sannu.

"Ya karfin jiki da jaririnmu?"

"Alhamdulillah Matron Uwani. Ya gajiyarki?" ta amsa fuska a sake.

Zama suka yi Haj. Umma ta ce bari ta kira Maigidan su gaisa sai su shiga daki ayi. Uwani taji kamar kakarta ta yanke saka yau. Idan tayi sa'a mijin mai alheri ne ai kila

shi ma ya bata wani abu. Irin wannan mutanen idan sun yi maka kyauta baka cewa a'a.

Kamshi ta fara ji kafin sallamar babban mutum cikin wani irin yanayi na seriousness. Kasa dagowa tayi har ya zauna ta gaishe shi.

Muryarsa babu alamun wasa ko digo taji ya kirata da cikakken sunanta. Wani abu da yasa hanjin cikinta kanannadewa da juna cikin azama.

"Matron Uwani Rabi'u!"

Haka ta daga kai jiki na tsuma. Fuskar da ta gani sai da ta kusa sakin zawo. Basu taba haduwa kurkusa ba amma karya take ta ce bata san kamannin CMD dinsu ba.

"Innalillahi wa inna ilaihi raji'un" ta dinga maimaitawa ba ji ba gani da karfi ga gumi yana bin sassan jikinta.

Dakewa ya yi domin ba abu bane mai wuya ya tausaya mata ya fasa hukuncin da ya dauka. Bai manta da zantukansu da maidakin nasa ba. Inda take cewa yiwa Uwani sako sako tamkar an ce ita ko wasu su cigaba da haka ne. Dole ne ya tauna tsakuwa domin aya taji tsoro. Laifin Uwani mai girma ne. Gara ace matan ke nemanta da abin da take yi. Akalla idan su suka nemeta a waje babu ruwan asibiti. Yanzu kuwa ana samun tangarda basu da mai kwatarsu a hannun hukuma tunda ma'aikaciyarsu ce.

Envelop ya nuna mata akan karamin teburin gilas na gabanta.

"Dauki ki tafi."

"Ranka. Ranka. Ya dade. Ranka ya dade.." ta soma magana tana waigawa ko matar tasa zata fito.

Katseta ya yi ganin za ta bata masa lokaci. "Idan hukuncin da yake ciki bai yi miki ba kina iya kai batun Ministry."

Kafin ta samu bakin magana ya fice abinsa. Kasa bude takardar tayi saboda faduwar gaba. Kafafunta kamar an kwashe mata kasusuwa don kiris ya rahe ta zube a kasa. Kirjinta kawai ke dukawa tare da azababben ciwon kai. Ko a mafarki abubuwan da suka faru yau suke samunta ta san cewa sai ta tashi da hawan jini. Shigowar Haj. Umma wannan karon fuska a tamke ya kara tayar mata da hankali.

Ita mamakin kasadar Uwani ma take yi.

"Allah Yaso ki duk wadanda kike yiwa aiki ta wannan sigar babu wadda nata ya baci ta shigar da kara kotu. Da license dinki ya dade da barin hannunki. Idan private practice kike son budewa kin san akwai hanyoyi da matakan da ya kamata ki bi domin samun sahalewar gwamnati. Amma son zuciya ya hana. Ace mace tana tsakar nakuda don tsabar rashin tausayi kina tallata mata muguwar sana'arki?"

Kalaman cin mutumci ne suka taba fita daga bakinta ga abokiyar aikinta lokacin da ta taba yunkurin hanata wannan sana'a. Ashe kura ta san gidan mai babbar sanda. A gaban Haj. Umma ko tari bata iya yi ba har ta gama magana.

"Ki bashi hakuri Hajiya. Tunda ki ka ga ina wannan abu kin san cewa kudi nake nema."

"Kiyi me dashi? Yasa anyi bincike akanki Uwani don kar ya dauki hukunci bisa rashin uzuri. Kina da miji mai rufin asiri. Har mota gareki balle ace kuncin rayuwa ne ya tasoki a gaba. Neman kudi ba hauka bane so kar ma kiyi kokarin justifying laifinki. Ko kina da wata kebantacciyar bukata hanyar da kika biyo bata dace ba."

A shekaru wannan matar bata fi kanwarta ta uku ba Salima. Don tana auren maikudi shi ne za ta tasata a gaba da bakaken maganganu? Wannan abu ya tunzura zuciyarta taji ba za ta bar gidan bayan an koreta daga aiki ba tare da ta rama ba.

Yatsina fuska tayi tana hura hanci ita a dole girmanta bai zube ba.

"Don kin sa an koreni daga aiki kina tunanin zan daina walwala ne? Ana kiran ciwon 'ya mace na 'yar uwarta ne kamar ba a san mata sun fi kowa son ganin karshen junansu ba? Banda munafunci ai bake nake yiwa tallan ba jiya amma kika yi katsalandan kika ce kina so. Auren maikudi ba zai raba mace da talauci ba ehe. Idan kina son burgewa ki nemi na kanki ki wuce wulakancin namiji."

Tun farko Haj. Umma bata ga alamun mutumci a tare da Uwani ba. Sai dai ko kadan bata kawo a ranta abin ya kai haka ba. Ranta ya sosu matuka amma haka ta daure taki magana har Uwani ta dire tana yi mata kallon banza. Hannu ta kai ta dauki envelop din da Uwanin bata kai ga dauka ba ta yaga shi gida hudu ta watsar a kasa.

Uwani tabi takardun da kallo tana kissimawa a ranta rashin nuna tsoronta ya yi rana. Karshenta matar ta tsorata ne taga gara a bar mata aikinta. Murmushi ta soma yi sai dai bai kai ko ina ba idanunta suka soma cikowa da kwalla sa'ilin da Haj. Umma ta soma magana.

Tsaye take kyam kana ganinta ka san mace ce da ta san kanta. Sai tayi mata wani irin kwarjini.

"Suspension ne na wata hudu hukuncin da aka yi miki ba tare da kai zancenki ministry ba. Anyi miki haka ne domin kada mu rabaki da aikin da bamu san irin WAHALAR DA IYAYE suka yi wurin karatunki ba. To amma Uwani kin yi kuskuren fada min maganganu son ranki a cikin gidana. Ki koma bakin aikinki daga yanzu idan kin so. Sai dai ina so ki sani cewa in sha Allahu indai ni Barr. Umma Jibril ina numfashi sai kin rasa license dinki ba ma aiki ba."

Wuta ce dif ta dauke a kwanyar Uwani

'Barr. Umma Jibril din da kusan duk mai jin Rediyo Kano ya sani?' ta tambayi kanta a zuci. Amsa ta bawa kanta domin tana jin sunan ta alakanta muryar da wadda take ji a rediyon.

Da tangadi ta bar gidan don ji take kamar duniyar da ta sani aka kifar. 'Yan uwa da iyaye da mijinta bata ga wanda ba zai yiwa halin da take ciki dariya ba. Zasu samo mafita ko ta wane hali ita da Habibu. Ya san manya a matakai daban daban na

gwanati. Idan ta rasa aikinta ta rasa matattakalar rayuwarta ne. Shi ne abin da ta dogara dashi wanda zai kangeta daga talauci.

Habibu ta kira. A lokacin yana tsaye a gaban Salihi yayi tsilli tsilli da idanu. Tambayarsa ya yi akan ya hada shi da ainihin dillalan filin da tayi gini sannan ya bashi shaidar biya mata kudin kujera.

Mintuna arba'in da suka wuce Salihi ya tambayi masu gadi ko akwai Habibu a wurin. Tashi daya suka amsa da cewa akwaisu har uku. Biyu manyan ma'aikatane. Daya kuwa sub-staff ne mai shigewa manyan. Yana jin haka ya ce a nuna masa shi. Da ya sanar dashi cewa shi ne mijin Uwani ba karamin mamaki da tsoro ya gani a tare dashi ba. Tambayoyin da ya yi masa suka sashi daburcewa ya kasa bada kwakkwarar amsa. Sai gashi ta kira a wannan lokacin. Gefe ya dan matsa da niyar bude mata wuta da borin kunya.

"Habibu akwai matsala. Zan shigo ministry yanzu."

Tana cikin tashin hankali a yadda yaji muryarta. Sai ya fasa fadan ya ce

"Don akwai matsala sai ki turo min mijinki ya titsiyeni a cikin mutane?"

Adaidaita sahun da ta tare ta hau. Abin da ya dameta daban da zancen da yake yi shi yasa ta amsa shi ba tare da nuna damuwa ba

"Zuwa ya yi? Yace maka me?"

Habibu sai ya murmusa ya zabi amfani da amsarta ya tada tarnaki tsakaninsu. In ba hakan ya yi ba yau shi za ta karewa.

"Takardun filinki ya ce na bashi da kuma kudin kujerarki. Har yana ikirarin ban isa na fishi sanin matarsa ba. A matsayinsa na mijinki yaba da hakki akan dukiyarki amma ke ce harda yin gini bai sani ba."

Abin ya zo mata bambarakwai saboda sanin Salihi shi yasa ta ce "inji Salihin?"

"Yasin gashi a nan, na baro shi a gefe da zan amsa wayarki. In kin ce na bashi kwafin takardun sai na bayar." Ya rage murya yadda za ta tausaya masa.

"Ka barni dashi. Kada ka bashi komai. Kai kaga ma yi tafiyarka ka bar saurarensa. Wannan wace irin masifa ce?"

Maimakon ya wuce gaba sai ya dawo gaban Salihi ya tunkuda hularsa gaban goshi.

"Da kai bada izinin matar taka kazo yi mata kutse a harkokinta ba? Ta ce kada na baka komai. Ko kunya baka ji ba bayan kayi aure matar ta sami ciki sannan ta sani, shi ne za ka lallabo rabata da arzikinta. Ku kuke janyowa ana zaginmu ace bamu da

tausayi. Haka fa kwanakin baya ka matsa mata da sai ta ranta kudin makarantar yara."

Salihi bai taba danasanin auren Uwani kamar yau ba. Banda barin Habibu ya zama uwa da uba gareta yana juyata da sunan shawara harda sirrin gidansa duk ya sani. Allah Kadai Ya san yawan abubuwan da ta sanar dashi. Kala bai iya sake cewa ba ya kama hanyar motarsa yana jiyo dariyar Habibu. Yana hanya Uwani ta kira shi da tambayar rainin hankali.

"Me kaje yi wurin Habibu?"

"Na baki rabin awa duk inda kike ki sameni a gidan iyayenki."

Da ya ajiye wayar sai kawai ta kama a'uziyya domin ta yarda dari bisa cewa jifa ne ko sihiri aka yi mata. Idan komai zai kwaba bata taba kawowa harda Salihi ba. A zatonta har abada zai kasance tare da ita yana hadiyar bacin rai. Kwafa tayi tare da mugun tsaki lokaci guda da wani tunani ya fado mata.

"Tsafi gaskiyar mai shi. Lallai Mulmule kike ko wa? Ni zaki tarwatsawa rayuwa daga zuwanki?"

Sai kawai ta soma dariya wanda har ya janyo direban adaidaitan ya dinga kallonta ta madubi. Ita kuwa karfin halin amaryar Salihi ne ya saka ta dariyar. A bayyane yake gareta Ummule ce tayi mata asiri. Banda haka me yasa komai bai faru ba sai da tazo gidan? Wata kwafar tayi ta ce da direban Adaidatan ya kaita Dala.

***

"Hummm inji mai ciwon hakori. Ka magantu azo a fara narai-narai da ido ana neman janyo maka zunubin da ba naka ba."

Furucin Asabe kenan bayan Hasiya da 'yan matanta sun gaisheta sun wuce dakin Innayo. Alh. Rabi'u sai ya zata dashi take saboda sun yi sa'in'sa akan 'yar dangin wa ya kamata a sake hadawa da Munzali cikinsu.

Labule ya daga ya leko da kansa ya watsa mata mugun kallo.

"Dake da Munzalin duka kuna karkashin ikona. Sannan Zakiyyan da suka rabo ba 'yar kanwarki bace ciki daya?..."

Dakatar dashi tayi ta nuna masa dakin Innayo da bakin da ta turo gaba.

"Maida wukar. 'Ya'yan matarka ne naga suna ta sintiri a gidan nan abin ya soma yawa."

Ta tashi ta koma dakinta yana biye da ita. So tayi ta daga murya wurin fadin maganganu amma Munzali ya ce mata ko labari yaji ta sake takalar Innayo sa rigima zai hanata kudin wata.

"Kwanaki Zara ce ta haihu kullum sai sun zo. Auren Salima ya mutu shima kamar wata uwar zasu iya yi mata suka dinga zuwa. Dazu kuma akan idona Maimuna tazo ta wuce da ledoji harda jakar bacco. Ga Hasiya ita ma ta wuce yanzu. Kar ka manta zuwan mijin waccan kankamojin Uwani shi ma ya ce bai ganta ba. Ni dai ka dauki mataki kafin a fara zaginmu a unguwa."

Buguzum buguzum ya fice daga dakinta ya tafi na Innayo. Ta saka dariya ta zauna jiran tashin muryarsa idan yana fada.

Hira ya samu suna yi ga kayan kad'in miya danginsu kuka da daddawa ana ta zuzzubawa a ledoji. A gefe ma akwai ledojin viva biyu cike har baka da danyar masara. Sai kwan zabi cike da katuwar kwarya.

Fuska a sake Innayo ta nuna masa uban kayan dake gabansu.

"Idan kun hadu da Musbahu (mijin Maimuna) kayi masa godiya. Kauye yaje shi ne ya hadomu da abin arziki."

"Ya hadoki dai ke da kike shagwaba shi. Duk wata dawainiyarsu kin dauka kamar ke ki ke auren Maimunan" cewar Alh. Rabi'u cikin fushi yasa kafa ya shure ledar masara guda daya "wai masara kamar wasu mabarata?" 'Ya'yan nasa yabi da kallo

saboda duk sun dinke fuska yaja dogon tsaki. Duk tsiyarsu dai shi ne ubansu. Kuma dadin abin yana da Munzali. Tabe baki ya yi kamar anyi masa dole kafin ya fita ya ce "In kun dafa ki miko min inji idan noman ya yi kyau dai."

Tun a gida Maimuna take cikin farincikin wannan kyautatawa ta mijinta ga iyayenta. Kullum sune masu karba a hannun Innayo ko Hasiya, yau gashi ita ma tana da abin kaiwa gìda asa albarka. Sai gashi tun ba aje ko ina ba Alh. Rabi'u ya yi nasarar kawar da murmushinta. 'Yan uwanta duk sun kawar da kai basa son hada ido da ita don kada su karasa sarar mata da gwiwa.

"Ina da itace. Zara tashi kije ki dora masarar nan."

Idanuwan sai suka koma kan Zara. Salima ta mike da hanzari tana cewa bari ta dora. Ga mamakinsu sai Zara ta tashi da rawar jiki. Irin rawar jikin nan na mai son burge wanda ya bashi umarni ba na tsoro ba. Ledojin ta kwasa tayi waje ga uban murmushi ta kasa dainawa.

Sai da ta fita Innayo tayi murmushi tana girgiza kai ta furta kalmar "Zara kenan" da kulawa.

Ita kuwa Zara tana isa waje sai da ta share kwalla. Shareta da Innayo take yi yafi duk wani abu da ya sameta ciwo a yanzu. Daki daya suke kwana amma takaitattun kalmomi ke shiga tsakaninsu. Ta riga ta sauke duk wani dakon rashin albarka da ta dauka akan ahalinta. Shiri take nema da kowa a cikinsu. Da ta dora kin komawa ciki tayi tana ta faman tura icce don tayi saurin dahuwa. Sa'arta daya ma iccen bai nuna mata kurenta ba. Tashin farko ya kama ba tare da ya hada mata hawaye da majina na yaushe gamo ba. Tana jin kukan jaririyarta taki shiga ciki har sai da Hasiya tazo ta kirata.

"Ke kuma daga hura wuta sai kiyi zamanki ki barta tana kuka?" Cewar Maimuna tana mika mata 'yar.

"Naga duk kwadayin cin masara ya kamaku shi ne na zauna ina ta fifita don ku samu da wuri."

Wasa take son shigarwa tsakaninsu. Basu sace mata gwiwa ba kuwa suka dinga dariya suna cewa ko dai akwai sauran bebi a cikinta.

"Ku barta dani take tunda ni na ce a dora."

Zara sai idanu suka raina fata. Gabanta ya fadi. A tsorace ita dasu Mqimuna suka kalli Innayo ta fara cewa

"Wallahi, wallahi..."

Innayo sai tayi dariyar da ta bawa 'ya'yan nata mamaki.

"Lallai ma Zara. Ke ki tsokani 'yan uwanki amma ni ba zan tsokaneki ba?"

Ajiyar zuciya Zara ta sauke su Hasiya ma duk sai suka saki rai. Sun san yadda Innayo ta dauki zafi da ita. A gaban ido da baya duk suna bata hakuri da son ganin ta sakarwa Zara.

"Tsoron bata miki rai nake Innayo." Ta ce a sanyaye wanda ya soki zuciyar mahaifiyar da bata da tamkarta.

Hararta tayi cikin wasa ta ce "Ai kuwa dai ya soma baci tunda kin bar min jika da yunwa."

A gaggauce Zara ta gyara zama ta rungume 'yar a jikinta sosai. Ta kalli su Salima kowa murmushi yake mata. Innayo ta sake shayar da ita mamaki da ta ce,

"Komai ya wuce Zara ki daina saka damuwa a ranki. Allah shaida na yafe miki duniya da lahira. Rashin zuwan maigidanki da yara duk ba wani abu bane indai kin sami lafiya. Muna nan da yardar Allah zaki ganshi dasu."

Allah Sarki, Zara sai hawaye "na gode Innayo. Salima kuma ku yafe min. Don bakin halina yarinyar nan ko suna bai saka mata ba har yau."

"Allah Ya san sunan da Ya halittota dashi. Kada ki sake tambayarsa." Cewar Innayo ta sake sako wasa don ta kawar da damuwarsu "ni dai a dafa min masara in mayar da mugun yawu."

Kusan tare yaran nata da ita kanta suka saka dariya. A zuciyarta tana jin wani irin farinciki wanda yafi kudi da duk abin da kudi zai saya.

Dariyarsu ce ta kawo Asabe wadda take mamakin ko Alh. Rabi'u bai yi musu yadda ta ce ba. Zuwanta ya yi daidai da tambayar da Hasiya ta yiwa Innayo akan dalilinta na cewa a dafa masara bayan abin da babansu ya yi mata. Su duka sun kasa gane dalilin rashin nuna fushinta da abin da ya yi. Asabe ta kasa kunne da kyau domin kwasar gulma ta kara hada fada.

"Allah ne fa Ya ce kada mu zata don mun ce munyi imani ba zai jarabcemu game da 'ya'ya da dukiyoyinmu ba. Da rayuwa tana tafiya da burin dan Adam da babu wanda zai yi kuka da komai. To amma yawan jarabawa da hakuri da ita karin daraja ne a aljannah. Tunda Allah bai bani kudin yin sadaka ba ba zan butulce don Ya dora min wannan rayuwa ba."

Hawaye ta sanya 'ya'yan nata. Suka kara ganin kima da darajar mahaifiyarsu. Ana haka Salihi ya iso. Bai jira isowar Uwani ba ya ce da Innayo idan ta zo ta ce mata ta zauna.

Abin da ya fadi ya tabata sai dai dama ta san dole akwai ranar da tura zata kai bango. Ya yi hakuri na ban mamaki a zamansa da Uwani.

"Wani abin ta sake yi?"

Murmushin bacin rai ya yi "ta dai zauna. Idan zuciyata ta sanyaya zan zo ki mana hukunci. Mubashir zai kawo mata kayanta."

Bata taba ganin suruki irin Salihi ba. Nauyinsa ta kara ji. Yana da iyaye da 'yan uwa amma har kullum bai gazawa wurin kokarin rufa asirin matarsa. Ta rasa wace irin zuciya ce a kirjinsa mai matukar hakuri da zurfin tunani. Ba shi ta haifa ba amma ya iya zuwa debe mata kewar 'yarta yana kuma bata hakuri akan halayyarta. Yau kam ta tabbatar Uwani bata yi masa da wasa ba wajen bata masa rai. Za ta bashi hakuri ya ce don Allah ta bari. Uwani ce mai laifi don ta haifeta ba za ta dauki nauyin laifinta ba. Bai jima da fita ba uwar gayyar ta iso.

Innayo taji kamar ta rufeta da duka akan amsar da ta bayar bayan ta fada mata abin da Salihi ya ce.

"Ba zan yi mamakin duk wani abu da zai yi min ba yanzu tunda ya auro matsiya... "

"Rufe min baki shashashar banza. Kina girma halinki yana kara tabarbarewa. Akanki ni ba sai dai na ce banga ranar boko ba? Ke kadai kika same shi mai yawa a cikin 'yan uwanki amma banda hauka bai kareki da komai ba."

Haukan ta nuna ziryan inda ta kada baki tana hurawa kannenta hanci ta ce "ai kuwa boko ya min komai Innayo. Na sayi mota, nayi gini sannan na biya kujerar Hajji."

'Ikon Allah' Innayo ta sami kanta da cewa cikin wani irin yanayi a zuciyarta. Bata cikin iyaye masu saka ido akan kudin 'ya'yansu amma bata jin duk hakurinta zata so

ace bata san cigaban yaranta ba. Babu abu daya da Uwani ta lissafa wanda zata yi mata shamaki da mallakarsa. To me ya hanata fada mata ko addua ta tayata da fatan alkhairi. Abin bai yi mata dadi ba ko kadan. Murmushin fatar baki tayi mata tare da fadin,

"Sai ki wuce gidan naki kafin mijin naki ya sakko."

"KNUPDA sun kwace" Uwani ta ce tana tura baki kafin kuma cikin sauri ta dora da yi musu bayanin cewa zata je a daidaita don kada suyi mata dariya.

Dariyar da ta guda ita Innayo tayi.

***

Bayan tafiyar kimanin awa daya da rabi sai ga wayar Suhaib. Munzali ya samu a lokacin. Ya jima yana kiran layukansu shi da Abbati amma duka sun ki shiga saboda raunin service na hanya. Da ya same su kuma aka rasa mai daukar wayar cikin su biyun. Gara ma Munzali tuki yake. Abbati kuwa ragowar karfin halinsa ne yaji yana neman kufce masa da yaga sunan mai kiran. Kira hudu ya musu a jere ta wayar kowa sau bibbiyu sannan ya hakura.

A gidan bikin iyayen nasu duk sun damu saboda an san cewa wayar da Abbati ya amsa ce ta tayar musu da hankali har suka tafi.

Yayinda Mardiyya take ta kiran Munzali saboda halin da ta shiga na taya shi jimamin damuwar da ake tsammanin suna da ita, Farha bata kira Abbati ba ko sau daya. Ko ma mene ne ta fahimci gagarumi ne tunda ya bar gidan ba tare da ya yiwa iyayensu da suke tare sallama ba. Za ta jira zuwa gobe idan ba a ji daga garesu ba ta bangarenta ko 'yan uwanta kafin ta kira. Addu'a kawai ta zauna tana yi don bikin ya fice mata a kai. Da Suhaib ya ce wayoyinsu na shiga ba a amsawa sai ta tura masa text.

(Allah baya dorawa bawa abin da yafi karfinsa. Wannan alkawari ne daga Mamallakin dukkan halitta. Ina fata Allah Ya kawo muku saukin abin da yake gabanku. Luv, Ya Farha)

Karar shigowar sakon ya kada duk wani abu dake yawo a jikin Abbati. Fargabar barnar da yake tunanin Shazali ya yi masa ta shafe komai a kwakwalwarsa. Wayar tana aljihunsa amma jikinsa ya bashi daga ina sakon yake. Jiki a sake ya dauki wayar ya bude sakon. Numfashi kawai ya dinga ja yana saukewa da sauri da sauri.

"Shazali ne? Me ya ce?"

Munzali ya tambaye shi da yaga yadda ya kara birkicewa.

"Farha ce."

"Nima tun dazu Mardiyya take kirana."

Shiru suka yi na lokaci har suka isa Gumel. Fadan irin tashin hankali da tsoron da suka sami kawunansu a tsukin lokacin ma bata baki ne. Gidan mai suka shiga suka kara mai tare da yin sallah. Sun kusa barin garin Abbati ya ce da Munzali ya yi parking. Gefe ya gangara ya fuskanci Abbati ba tare da kashe motar ba.

Yana tsayawa Abbati ya kama kofar ya bude. Kafarsa daya a waje ya juyo ya kalli Munzali mai binsa da ido da alamun tambaya.

"Ka koma Kano zan wuce ni kadai."

A razane Munzali ya dube shi maganar tana dukansa ta ko ina.

"Me ka ke nufi?"

Kadaici yake bukata? Tsoron haduwarsa da Baaba Mari? Tabbacin rasa Farha na har abada? Hasashen girman tashin hankalin da zai wanzu a gida da garinsu? Babu abin da ahi kadai bai isa ya haukata tunanin shi ba. Sai gashi su duka da ma wasu suna jiransa. Bai san ta ina zai fara ba, amma gara ko meye ya tunkareshi shi kadai tukunna.

"Don Allah Munzali ka koma. Tunda kaji na ce ka barni ni kadai ka san bani da zabi ne."

Yawu mai daci ne ya wuce ta makoshin Munzali. Ko ba a fada ba ya san cewa Abbati ya gama sarewa da komai. Yau din rana ce da za ta zama mafarin wani abu da bashi da suna a rayuwarsu. Kuma har ga Allah Yafi kowa sanin cewa tonowar asirin Abbati ba kamar nasa bane. Abbati ya tashi cikin dangi da iyaye. Duk wani rikicin cikin gida bai raba kan iyayensa ba. Shi kuwa ko yau iyayensa suka ji bashi da abin da ya wuce dora musu alhakin komai. Darajar Qibdiyya da kuma 'yan uwansa da ya fara sabunta zumunci dasu ne ababen dubawa. Sai kuma masoyiyarsa Mardiyya wadda ko kadan baya son abin da zai shata layi tsakaninsu. Mafi girman damuwarsa kuwa tana tattare da bakincikin shi ya batawa Abbati rayuwa. Numfasawa ya yi bayan ya dan yi nazari.

"Kana nufin za ka je ka tonawa kanka asiri ne ni kuma na zauna? Waye silar shigarka wannan rayuwa."

Hannu Abbati ya nuna masa "kada muje nan wajen."

Rai ya soma baci Munzali ya ce "to ina zamu je? Ba ni bane? Ba don ka hadu dani ba da yanzu kana rayuwarka cikin kwanciyar hankali."

Kafin ya gama maganar idanunsa sun yi jajir. Zuciyarsa a kuntacce take yana jin yadda take zafi. Ya sake bude baki zai yi magana Abbati ya dakatar dashi da cewa,

"Don Allah kayi tuki a hankali."

Duk yadda Munzali yake son yi masa musu haka ya hakura ya tafi bayan shigar Abbatin motar haya.

***

Mummunan faduwar gaba ne ya sami Baaba Mari har ta saki butar hannunta da taji muryar yaran gidan suna yiwa Abbati barka da zuwa. Sake dibar ruwa tayi cikin rawar jiki duk tana zuzzubarwa ma ta kuma cika botar ta zauna za tayi alwalar Isha'i. Jikinta har wani karkawa yake saboda tashin hankali. Tunda ya iya biyo dare ya taho garin a yau da basu kwana da shirin zuwansa ba ta san babu lafiya. Tabbas babu ko tantama Abbatinta bashi da gaskiya. Da babu wata a kasa tun dazu zai kirata ya karyata zantukan da taji sunyi a waya da Shazali. A yadda zuciyarta take dakan lugude a kirjinta kuwa a lokacin ko me ya fada a waya zata amince. Yardar ta zame mata wajibi ko don kada bakincikin jin gaskiya ya kwantar da ita.

Shi kuwa a bakin kofar da zata sada shi da sashen mahaifinsa ya tsaya tun shigowarsa. Idanunsa da suke cike da kwalla suka sauka akan Baaba Mari tana alwala. Ya gama karanta da fahimtar duk wani motsinta. A firgice take! Alwala take yi amma sam hankalinta baya jikinta. Shafar kai kadai wadda da wuya ake kuskure adadinta saboda sau daya ce sai da tayi biyar akan idonsa. Ya lura duk gabar da ta kama sai ta dawo hayyacinta take tafiya ta gabanta. Bai san kuka yake ba sai da yaji ruwan da zafinsa yafi wuta a zuciyarsa yana bin kumatunsa. Asalin kunci da damuwa ne suka rufe shi ya juya a hankali ya fita daga gidan.

Kofar gidansa yaje tun daga dan nesa yake hango hasken tocilan din wayoyi guda uku a wurin. Bai yi mamakin ganin 'Yashshafa da wasu 'yan mata sa'o'inta biyu ba. Su ma duka kannensa ne kowcce da tsintsiya a hannu.

"Gwaggo Deluwa ce ta aikomu muyi maka shara kafin a kawo abinci."

Guda cikinsu ta fada bayan ta gaishe shi. Mukullin kawai ya mika musu ya juya masallaci. 'Yashshafa bata manta gargadin Deluwa ba tayi saurin cewa a dawo lafiya.

"Ki kwantar da kai ki kyautata masa domin mu sami biyan bukata."

Cewar Deluwa mintuna kalilan da sallamar Abbati cikin gidan.

'Yashshafa tana dirzar kafarta da dutsen goge kaushi ta daga kai tana zumburo baki.

"To wai ni Inna haka za kiyi ta min ne? Yau ki ce in daina sakar masa fuska gobe in saki? Yaushe zai soni a haka?"

Deluwa ta murmusa tana wani jijjiga kai

"Yaro man kaza. Banda abin ki 'Yashshafa idan baki kwantar da kan ba ta yaya zamu samu ya baki lambar shi Sha'aib din cikin sauki?"

Cigaba da dirzar kafarta tayi cikin yanayin ko in kula ta ce "Inna ki bar batunsa don a ranar ko kallo ban ishe shi ba."

Harara mai kyau ta samu kuwa sannan cikin fushi Deluwa ta ce mata,

"Ta yaya zaki san me yake faruwa a lokacin nan kina can kina kukan shanu? Kar ma ki zata dominki na damu. Tausayin yaron da mutumcin uwar tasa ne yasa nake ta kokari. Ni kadai na san me na gano a kwayar idanunsa game dake. Jikina ya bani suna ta nemanki ta wurin Abbati. Amma don mugunta yaki hadaku. Su kuma 'yan birni ba wuya ciwon zuciya ya kwantar dasu saboda da gaske suke soyayya."

Tabe baki 'Yashshafa tayi bayan tafiyarsa tabi 'yan uwanta cikin gidan. Daga Abbatin har Suhaib ta san bata gabansu. Ita din ma ta turesu daga gabanta. Kwanakin nan mutum daya take yawan tunawa tana jin ina ma zasu hadu ta rama dariyar da ya yi mata.

Da Abbati ya dawo bai koma gidansu ba. A waje ya gaisa da sauran iyayensa maza ya ce kansa ne yake ciwo zai kwanta. Harda nanatawa Mal. Inuwa ya sanar da Baaba bashi da lafiya kada ta ji shi shiru. Nan kuwa karfin gwiwar hada ido da ita a daren ne bashi dashi. Abinci kala biyu ya gani a falonsa. Wanda ya tabbata daga wurin Baaba Mari aka turo ya tsakura kadan ya yi shirin bacci. Sun dan taba shawarwari da Munzali a waya sannan ya kwanta.

***

Tafiyarsu Munzali ta gaggawa ta dagawa iyaye da 'yan uwan Alh Tahir wadanda Allah Yasa suka gamu dasu jiya hankali. Saboda haka suka dinga kiransa ana tambayar ko yaji daga garesu. Shi ma ya damu haka Mami Khadija da Mama Nasima. Wuraren tara na safe yaci sa'a Munzali ya dauki waya.

TAKWAS GOMA BA BIYU.

Tafiyarsu Munzali ta gaggawa ta dagawa iyaye da 'yan uwan Alh Tahir wadanda Allah Yasa suka gamu dasu jiya hankali. Saboda haka suka dinga kiran Alhajin ana tambayar ko yaji daga garesu. Shi ma ya damu haka Mami Khadija da Mama Nasima. Wuraren tara na safe yaci sa'a Munzali ya dauki waya. Munzalin kwanan zaune yayi inda yake ta tufka da warwara. An wayi gari kansa yana wani irin ciwo saboda rashin bacci da alhinin me zai faru tsakanin Abbati da Baaba Mari. Irin wannan lokacin sallah da kankantar da kai a gaban Allah SWT shi ne yafi dacewa da bawa. Sai aka yi rashin sa a munin dabi'ar da suka rayu cikinta ya danne tunaninsu daga shi har Abbati. Asalin kalmar da bature yake kira despire ita ce ta wanzu a kawunansu. Suna jin tamkar basu da sauran rabo. A duniyar sai sun ji kunya sannan a lahira da wuya su sami dacewa da rahama. Wannan shi ne tunanin kowannensu. Shi ne fargabar da suke da yakinin ganin ranar faruwarsa.

Da farko bai yi niyar amsa wayar kowa ba sai ta Abbati. Amma karar kiran da ya shigo tamkar ana kada kararrawa a cikin kansa ya saka shi mika hannu ya daukota a gefensa. Katse kiran yaso yi tunda bai san nambar ba, bisa kuskure sai ya zamana ya amsa ne.

"Alhamdulillahi ya dauka"

Shi ne abin da Munzali yaji an fada daga dayan bangaren. Bai sha wahalar gane mamallakin muryar ba. Hakan ya tilasta masa tattaro duk wata nutsuwarsa ya gyara murya suka gaisa sosai.

"Me ya faru jiya Munzali? Kun tafi kun barmu da fargaba. Ina shi Abbatin?"

Murmushin fatar baki Munzali ya yi da ya hasko tonuwar asirinsu da irin yadda zasu wulakanta bayan rabuwa da masoyansu. Karya ce kadai rufin asirinsu kuma ita ya gilla kamar yadda suka saba domin kare kai.

"Ku yi hakuri. Wan Baban Abbati ne aka kira babu lafiya ...."

Alh. Tahir ya katse shi tun kafin ya gama da cewa "Subhanallahi, ciwon ya yi tsanani kenan duba da yadda ku ka tafi."

"Eh suma yake yi kamar ba zai tashi ba."

"Kuna ina ne yanzu?"

Munzali sai da ya dauke wuta na wucin gadi kafin ya iya bayar da gamsashiyar amsa. A yadda suke dai bai kamata ya ce Abbati ne kadai ya tafi ba. Sannan idan ya yi gaggawar binsa yanzu bai san me hakan zai janyo ba. A takaice ma dai dole ya zauna domin ya dakile yunkurin da yake hasashen Alh. Tahir ya fara.

"Muna Gumel nima aka kirani Qibdiyya ta fadi ana zaton karaya ce." (Da safe ranar ta fadi amma ko kuka bata yi ba)

"Sannunku kaji. Ya jikin nasu?"

"Kawu Sa'idu ya fara samun sauki. Qibdiyya kuwa mai kula da ita ce ta firgita. Buguwa ce kawai."

Nutsuwar da Alh. Tahir ya rasa tun jiya ce ta dawo masa. Ya sake jajantawa Munzalin sannan suka yi sallama.

Munzali har ya fara jin sanyi a ransa na rabuwa dashi lafiya sai ya sake kira. Bayan ya fada musu me yake faruwa ne Mama Nasima ta ce ayi musu kwatance zasu je dubiya. Ita a nufinta taje har gidan Munzali ta kara gane ina zata kai Mardiyya. Alh Tahir bai ki ba saboda shi ma baya son wadannan zaratan matasa su kufcewa zuri'arsa. Tunda Allah Yasa suna Kanon gara ma da aka yi haka. Sai suje domin a karfafa magana.

"Amma ya dace muje gidansa? Babu mace fa a ciki. Idan akwai ma kuma ai bai kyauta iyayen wadda yake son aure suje duba mata 'ya ba."

Mami Khadija ce taja hankulansu kan kuskuren zuwa gidansa. Mama Nasima sai ta hau borin kunya.

"Mutum kullum burinsa ya nuna yafi mu sani da iyawa. Da an fimu din kuma da bamu zo gidan ba. Ki kwantar da hankalinki bance sai kinje ba. Yanzu nake shirin cewa a fada masa ya kaita gidan iyayensa sai muje can."

Mami Khadija sai ta girgiza kai kawai. Ba don tayi magana ba tsaf gidansa zasu je. Yanzu kuwa ko don a bata kunya dole a canja salo.

Ba bata lokaci Alh. Tahir ya kuma kiransa ya fada masa shawararsu. Suna gama wayar Munzali ya tashi a gaggauce ya fada bandaki. Cikin mintuna biyar har kaya ya saka. Yana makala links din hannun riga wayarsa tana gefen kunne ya danneta da kafada. Asabe ya fara kira ya tambayeta ko tana gida ta ce ta tafi sunan wata 'yar uwarsu a kauyen Kuyen Ta'inna da sassafe.

"Idan zuwa zaka yi bari in taho gida yanzu. Ka san kauyen a cikin gari yake zan iso da wuri."

"A'a yi zamanki. Zan zo da daddare ko gobe."

A wurinsa gara ta zauna kada su hadu da Mama Nasima ayi abin da shi da Mardiyya zasu dade basu manta ba. Zara ya kira ya fada mata bakin da zai yi da matsayinsu.

Asabe kuwa sai ta kasa zama. Idan kudi ne gara ta koma gida tayi masa waya ya zo ya kawo mata. Kada tayi sake goben ya ce ya taba. Takalmanta ta saka ta sallami maijego ta fito neman abin hawa.

***

Yau ma Abbati ya kasa shiga bangaren Baaba Mari. Ya leka ya gaisar da kawunnansa. Ita kuwa yana zuwa kofar dakinta ya tambayi wani yaro dan wajen Habi ko ta tashi.

"Ta tashi tun dazu. Kunu take sha."

Kirjin Abbati ya sake matse zuciyarsa saboda tsoron hada ido da ita. Cikin hanzari ya ce da yaron

"Tunda kunu take sha ka ce ina gaishe ta. Bana son shiga in katseta. Zan dawo anjima."

Daga cikin dakin Baaba Mari tana sauraronsu tun farkon tsayuwarsa a wurin. Maganarsa ta karshe tasa ludayin hannunta ya yi mata nauyi a hannu. Abbatin da ko wanka take yi yana jiranta shi ne mai cewa baya son katse mata shan kunu? So take ya bata dalilin karyata duk wani zargi da ya darsu a zuciyarta amma ya kasa. Daga wayarsu ta jiya kafin yazo zuwa yanzu bai yi komai ba sai tarwatsa mata zuciya da fargaba. Akwai matsala ta riga ta sani sai dai bata san girmanta ba. Wannan shi ne tashin hankalinta.

Tsayuwa Abbati ya yi a jikin bangon dakin ya kasa tafiya. Komai na duniya ya tsaya masa cak. Baaba Mari kawai yake so ta dube shi, duba na tsausayi da soyayyar uwa ta ce masa ta yafe. Ta roka masa rahamar Allah wadda a yanzu yake taraddadin samu. Idanunsa ya rufe sa'ilin da kwala ta cikasu har tasa suke zafi. A sanyaye ya juya zai tafi sai yaji wayar Baaba Mari tana ruri.

Sautin ne ya dawo da ita daga duniyar tunani tayi saurin share kwallarta sannan ta dauka da sallama. Muryar mace mai kamala ce ta amsa mata cikin walwala da son janta a jiki.

"Wa alaikum salam wa rahmatullah. Allah Yasa baki manta Khadija kanwarki ta Kaduna ba."

Baaba Mari tayi murmushin jindadi "yaushe zan manta mace mai kirki da mutuntunta dan Adam kamar ki Mami Khadija?"

Innalillahi wa inna ilaihi raji'un. Cikin sakan daya Abbati ya bayyana a gaban Baaba Mari a hargitse.

Kallo guda taji ya matukar bata tausayi. Duk ya sauya babu komai a idanuwansa sai fargaba da tashin hankali. Bakinsa na rawa saboda bai san me aka ce musu ba tunda ya gama tsorata da Shazali ya ce,

"Baaba kashe wayar don Allah" a hankali.

Dauke kai tayi kamar bata ganshi ba tana tambayar Mami Khadija yara.

"Kowa lafiya kalau Alhamdulillah. Ya mai jiki kuma? Jiya Abbati ya tafi ya barmu da fargaba. Ashe kawunsa ne babu lafiya."

Kallonsa Baaba Mari tayi ta tabe baki. Abin har ya kai ga karya kenan. Shi da bai ma san abin da Munzali ya fada musu ba sai ya daburce ganin tana masa kallon tuhuma. Da bakinsa ya kasa hada kwakkwarar kalma balle ya yi magana sai ta cigaba da wayar.

Rufa masa asiri tayi kamar yadda kowace uwa za ta yi ta ce "Ai jiki ya yi kyau sai hamdala. Tsorata muka yi shi yasa aka kira shi."

Cikin jimami Mami Khadija ta ce "haka Munzali ya ce. An kira an ce yana suma ai dole hankula su tashi. Don Allah kiyi masa sannu."

"In sha Allahu Mami. Mun gode sosai."

"Haba ai an zama daya. Allah Ya kara hada kawunansu."

Amin ta ce sannan suka yi sallama. Abbati ya kalleta cikin sauri ya sauke ido. Inda ya tashi ya koma ya gurfana gabanta hankalinsa ya sake tashi.

Baaba Mari ta kasa tambayarsa komai. Tsoron amsarsa take ji ga kuma tausayin yadda ya firgice mata. A hasashenta ma daga maganganun Mami Khadija ta fahimci akwai alaka tsakaninsa da daya daga cikin 'yan matanta. Wayarsu ta karshe kafin zuwan Shazali dama ya fada mata akwai maganar da yake son yi da ita. Kawar da tunanin tayi domin bashi da muhalli a yanzu cikin damuwarsu. Can ta nisa tayi masa tambaya amma a sakaye.

"Kai da Munzali sana'arku daya?"

Sai da taji hadiyar yawunsa tare da hawa da saukar Adam's apple dinsa kafin ya iya bata amsa.

"Eh" ya dora da cewa "amma wallahi Allah mun tuba mun daina" yana mai nunin girman maganar da yatsansa.

Hannu ta daga ta dakatar dashi nata jikin yayi sanyi kalau. Kunnuwanta kuwa kamar an toshesu domin bata jin komai sai karar bugun fargabar zuciyarta.

"Bana son jin koma mene ne Abbati. Duk wanda yake kan tafarkin gaskiya ya sani. Wanda ya saba ma yana sane. Ka tashi ka koma gida. Zamanka a nan ba zai karemu da komai ba."

Samun kansa ya yi da fashe mata da kuka. Babu sauti sai dai ilahirin jikinsa duka rawa yake kamar an kwara masa ruwan sanyi.

"A tare dake aljannata take Baaba. Idan kin yafe min ina sa ran samun gafarar Ubangijina."

Nata kukan ta danne. Ya zama wajibi a gareta ta karfafi zuciyarta indai tana son danta ya sami karfin gwiwar tuban da yace ya yi.

"Na yafe hakkina idan akwai a cikin sana'arka. Sai dai ban san yadda zaku yi da hakkin mutane ba."

"Baaba ban fahimta ba." Ya tambayeta da dukkan gaskiyarsa. Rikicewarsa ta kai ya manta bata san ainihin sana'ar ba.

"Ba da sana'arku ku ka yi kudi ba?"

"Da ita ne." Ya amsa kansa a kasa.

"Kuma sana'ar haramtacciya ce?"

Kai ya sunkuyar ya gyada shi a hankali.

Yanayinsa sai ya soma bata haushi. Yafi ta sanin me suke aikatawa to don me zai nuna mata rashin sanin girman laifin? Duk mai daukar kayan da ba nasa ba yafi kowa sanin hakkin wasu ne yake dannewa. Hakkin da sai an tambayeshi ranar lahira.

"Kafi ni sanin cewa dukiyar haram ce kake kwance a kai. Idan akwai halin ka mayarwa wasu cikinsu dukiyoyinsu gara ka gaggauta yin hakan."

Abinka da dan fari kuma mutum wanda tun asali bashi da saurin fahimtar abubuwa makamantan wannan. Da Munzali ne tabbas zai cigaba da tafiyar da Baaba Mari ne akan zarginta na cewa sata ce suke yi. Abbati kuwa cikin kidima da tsoron zargin da take musu sai cewa ya yi bai taba satar kudin kowa ba.

Baaba Mari taji zuciyarta ta daka wani mugun tsalle a kirjinta yana fadin haka. Da sassarfa ta tashi ta tura kofar dakinta ta saki labule sannan ta dawo ta kama hannunsa suka zauna. Kallon ido cikin ido take yi masa cikin yanayi na fargaba da taraddadi.

Muryarta a shake ta fito saboda nauyin tambayar da take shirin yi masa.

"Yankan. Yankan? Kai? Yankan kai? Abbati ku 'yan yankan kai ne?" Bata jira amsarsa ba ta shiga yarfe hannuwa "na shiga ukuna ni Mariya. Abbati rashin imanin naku ya tsallake sata ya hada da zubar da jini?"

Sakin hannuwansa tayi ta hanyar bigesu daga cikin nata tayi baya a zabure. Hakan yasa shi yaji kamar ba za ta kara son ya kusanta gareta ba. Ita kuwa zafi ta soma ji fiye da kima ga gumi yana tsatstsafo mata kamar an kunna famfo. Wannan kaddara

da nauyi take. Dan cikinta ne a gabanta amma bata san shi ba. Tana tuhumarsa da daya daga cikin masifun wannan zamani amma yaki cewa komai sai ido da yake binta dasu. Tana hawaye ta doki gefen kirjinsa, cikin gunjin kuka ta ce,

"Bakinka zaka bude kayi min magana. Wato da baka da niyar fadin gaskiya sai ranar da aka bukaci jininmu a kungiyar ...."

"Baaba ki yarda dani wallahil Azeem bana cikin kowacce irin kungiyar asiri ko yankan kai" ya fada dalla dalla duk da kukan da yake cinsa domin ta yarda da gaskiyarsa.

Komai ya kulle mata. Ta rasa tudun dafawa. Tsoron abin da zai fada yasa take jin gara ma ace satar ce. Sassauta murya tayi ta sake mika hannu ta damko hannunsa daya. Da dayan hannun nata ta share kwallarta sannan ta fuskance shi da kallo na tausayi garesu baki daya.

"Fada min sana'arka!"

Saukar aradu yaji. Zuciyarsa ta tsaya na 'yan dakiku kafin ta cigaba da bugu cikin yanayi na faduwar gaba.

"Baaba...."

Sai kuka. Kuka. Kuka...sannan ya fayyace mata komai tun daga haduwarsa da Munzali. Ko da ya gama ya sake kiran sunanta bata amsa ba. Dama kansa a duke yake sai ya dago a hankali. Shi take fuskanta amma ba shi take kallo ba. Bakin kwayar idanunta a birkice ya gansu, sun juye kamar babu su. Suman zaune tayi bai sani ba.

***

Datar MTN ta dari uku wadda suke bayar da 1GB na kwana daya Danliti ya saka a wayarsa. Whatsapp ya bude cikin rashin sa'a bai ga sunan Ayaah ba. Guntun tsaki ya yi domin ya so ganin hotunanta yau. Kwana biyu kenan da zuwansa wurin dinner inda ya hadu da Suhaib amma har yanzu bai manta da fuskarsa ba. Sai da ya koma gida haushi ya ishe shi. Da gani ya girme shi wai amma shi ne ya yi masa barazanar da ta tsorata shi haka.

"Idona idon matsiyaci sai na nuna masa tashancin 'yan Kano."

Danliti ya yi kwafa gami da jinjina kai cikin bacin rai. Duk da cewa baya jin akwai wata mace da ta kama kafar Ayaah cikin matan da yake son mu'amala dasu, amma yaci burin samun hajiyar Kadunan nan wato Jiddo.

Da bukata bata samu ba. Ya laluba babu halin ganin hoton Ayaah a yau. Sai kawai ya saka katin dari biyu ya kirata.

Shirin fita suke ita da Murja zuwa gidan Innayo. Murja ce za ta yiwa Zara kitso kamar yadda ta fadawa Hasiya jiya. Shi ne ita kuma ta hadasu da Ayaah ta ce su tafi tare.

Shake murya ya yi yana magana ciki ciki irin na mayaudara.

"Baby nayi missing dinki da yawa. Anjima zan zo. Me ki ke so na taho miki dashi?" Ya fada a karshe don ya san ba za ta ce komai ba.

Ita kuwa sanyi taji a ranta da sabon sunan da ya rada mata.

"Babu komai. Fita ma za muyi da Murja."

"Ina zaku je baki fada min ba? Nifa gaskiya bana son kina fita ana gane min ke. Da kin fada min sai na zo na kai ku. Anywhere dai ku jirani please zan taho now now."

Satar kallon Murja tayi ta bar wurin da sauri kafin taji me yake cewa.

"Ka barshi bani kadai bace. A gida fada za ayi min. Gidan kakanninmu zamu."

A lissafinsa anci rabin kudin wayar sai kawai ya fake da nuna bacin rai ya mata sallama. Hankalinta sai ya tashi tayi maza ta kira shi da ragowar canjinta.

"Kayi hakuri mana don Allah."

Kamar ba zai ce komai ba har ta fara kosawa sannan ya ce "Naji. Amma har ku isa muna chatting. Ki kwatanta min gidan sai na sameku a can ko fuskarki na gani naji dadi. Da kudi a wayar ko na turo miki?"

"Akwai" ta bashi amsa duk da ta san sun kare.

A danja ta sayi kati ita ma na dari biyu ta saka ta tura masa amsar sakonsa wanda ya rubuta kamar haka,

(Wane kaya ki ka saka?)

(Atampa ce)

(Kwatanta min daga sama har kasa domin naji kamar kina gabana.)

Kwatancen tayi masa na riga da skirt da hijabin da ta saka mai hannu wanda ya zarta gwiwarta kadan. Abin bai yi masa armashi yadda yake so ba. Wanda a idon namiji mai mutumci zai ga tayi matukar kyau. Canja salo ya yi cikin kwarewa da iya hillata.

(Da wane irin kaya ki ka fi son yin bacci?)

Kallon wayar tayi kamar ba tata ba na dan lokaci har sai da Murja ta tambayeta ko akwai matsala ne. Dena juya wayar tayi a kasan ranta tana yi masa uzuri da cewa kila lefe yake tunanin fara hadawa.

(Doguwar riga)

Danliti yaja tsaki ganin taki daukar haske.

(Ni kuwa kinga nafi son kwanciya da wandon bacci kadai. Idan ma sanyi ake nan gaba kadan na san kina kusa dani ba zai dameni ba. Kema ki shirya ba zaki zo min da doguwar riga bed ba.)

Wani dumi dumi Ayaah ta fara ji. Ita kadai ta dinga tsarguwa ko Murja ta fahimci irin sakwanin da yake turo mata. Hirar ta daina yi mata dadi amma ta rasa me ya hanata dakatar dashi ko ta daina bashi amsa. Wani sakon ne ya sake shigowa sai da ta dan zabura da ta karanta.

(Ina son mace mai kunya. Shirunki yasa na kara sonki. Amma fa ki sani nan gaba kadan zaki nemi kunyar ki rasa. Zaki fara rungumeni da kanki ba sai na nema ba. Kafin aurenmu ina son mu sake da juna sosai ta yadda tun yanzu zamu san abubuwan da zasu faranta mana.)

Ayaah bata iya sake tura masa amsa ba. Tambayoyin nauyi suka yi mata. 'Yar fara'ar da ta soma ta nema ta rasa.

Danliti da kansa ya gano zai yiwa kansa sagegeduwa ta wannan hanyar. Kifin rijiya ce ba kamar yadda ya yi zaton irin makwadaitan 'yan matan nan bane masu mummunar wayewar zamani a soro.

(Kiyi hakuri Baby. Ina jin kamar na dauko hirar da bata kamata mu fara tun yanzu ba. Ina tsananin kewar irin wannan kusancin da iyalina. Ke kadai ce zan iya fitowa da damuwata hankali kwance domin nayi imanin zaki saurareni kuma ki fahimceni. I love you)

Shi kenan! Kyakkyawan tunanin da ya fara ginuwa a zuciyarta ya rugurguje da sakonsa na karshe. Tausayinsa ya sake kamata. Ta kara jinsa a rai fiye da kullum. Matarsa kuma ta sha bakaken addu'o'i domin har gani take ba don haduwarsa da ita ba kila da yanzu ya fara bin matan titi.

*

Dubu ashirin Alh. Tahir ya baiwa Mama Nasima domin yiwa Qibdiyya sayayyar dubiya. Ita da Mami Khadija zasu je. Sai 'ya'yansu. An nemi Jiddo a waya bata dauka. Tana can gidan wata 'yar kungiyarsu 'yar Kano an kawo musu samari suna keta dokar Allah. Ta gama tsara karyar da zata yi idan ta dawo kafin lokacin tafiyarsu Kaduna.

Mota biyu suka yi. Daya direban gidan da ake bikin ne yake jan Mama Nasima da Mami Khadija tund shi dan gari ne.Ta bayan kuwa motar gidan Alh. Tahir ce. Suhaib ke tuka kannensa suna biye dasu a baya.

A son ran Mami Khadija su biyu kadai zasu je sai ko 'yan mazan. Saboda mata da kunya aka sansu. Tana ganin iyaye da 'yan uwa sun isa su wakilci 'yarsu kafin a daura aure. Dadin dadawa ma maganar bata riga ta zama ta gemu da gemu ba. Zai iya zama kamar suna son cusa 'yarsu ne ta karfi. To Mama Nasima ta dage sai Mardiyya taje. Shi yasa ta hada da Farha da Sauda don kada ido ya yiwa Mardiyyan yawa idan aka fahimci matsayinta.

***

Kayan tarbar baki lodi guda Munzali ya kawo dakin Innayo. A nan ya sami Uwani tana ta buge bugen waya tana tsaki. Tun safe take kiran Habibu waya taki shiga. Za ta fita kuma Innayo tayi rantsuwar idan bata nemi izinin mijinta ba in ta fita kar ta dawo. Ita Salima dama yaji labarin komai. Sunyi magana da ita a waya ya kwantar mata da hankali tare da goyon bayanta akan son raba auren.

Zara ce ta gyara falon Innayo ta sakewa Qibdiyya kaya sannan ta jera komai a tray. Salima ta shimfida tabarma saboda basu san mutum nawa bane. Haj Uwani tana uwar daka ta kira Mubashir a waya tana kwatanta masa kamanin Habibu. So take yaje ministry ya kira mata shi. Innayo kuma tana gefe ita da Munzali yana yi mata bayanin Mardiyya da iyayenta.

"To amma duk wannan bayanin da kake ni banga farinciki a fuskarka ba. Baka son

yarinyar ne ko akwai wata matsalar ne daban?"

Ta tambaye shi bayan ya gama. Bata ga wani doki ko murna a tare dashi ba. Kusan ma kamar rabin hankalinsa yana wani wajen daban.

"Ba haka bane Innayo. Abbati ne ya ce min zai taho daga Kirikasamma yau. Shi ne nake tunanin zuwan bakin da isowarsa. Kada ya iso basu tafi ba. Kinga babu mai dauko shi daga tasha."

Zancen bai yi tasiri a kanta ba saboda bashi da madogara. Abbati ba yaro ba kuma ba bako ba me zai same shi idan ya shiga mota daga tasha zuwa gida? Akwai damuwa sosai tana gani a idanunsa. Munzali mai yawan fara'a yau idanunsa kamar an dauke wuta. Rabuwa zata yi dashi har bakin su tafi sai ta kuma tuntubarsa. Idan ba abin da ya kamata ta sani bane zata bishi da addua.

*

Uku da rabi saura suka isa kofar gidan Alh. Rabi'u. Sauda ce mai tsokanar Mardiyya tana cewa,

"Ke zaki shiga gaba mu take miki baya tunda gidanku ne."

"To parrot kaddai mu shiga ki dinga nunata."

Farha da tayi maganar ita ma bata tsira daga tsokanar kanwarta ta ba.

"Kai Ya Farha daga wasa? To ko daga nan a biya garinsu ne shi ma."

Suhaib da Lilu aka bari da dariya. Suka taka zuwa inda iyayensu suke tsaye bayan sun fito daga mota. Tsayuwarsu keda wuya Munzali ya fito tare da Ayaah a gefensa. Ita za ta rakasu dakin Innayo shi kuma zai shiga dasu Suhaib falon Asabe tunda babu kowa a ciki.

TARA DAGA KE SAI GOMA.

Innayo da 'ya'yanta sun karrama su Mami Khadija fiye da zaton Munzali. Shi ya kawo duk wani abin ci da sha to amma bai kai rabi rabin kyautatawar su Salima garesu ba. Farha tana ganin jaririyar Zara ta karbeta. Mardiyya da Sauda suka karaci nacinsu suka hakura. Uwani har lokacin tana daki ko lekowa a gaisa bata yi ba. Duniyar ce take ta hajijiya da ita. Bata da lokacin kanta balle na wani.

Lokacin da suka shigo Murja tana ta sauri sauri ta kai karshen kitso biyun da ya rage musu, saboda haka kan Zara a bude yake. Suna sallama ana gamawa. To bayan sun zauna an gama gaisawa Sauda ta dinga taba Mami Khadija har sai da Innayo ta kula da hararar da Mamin take yi mata. Da hannu ta kira Saudan fuskarta dauke da murmushi. Bakin da gani sun baiwa kalmar 'babu' hutun shekara da shekaru ma. Amma babu alamun wulakanci ko girman kai. Mama Nasima ce ma dai ta hadiye rashin gamsuwarta ta hanyar kama bakinta tana jiran tabbatacen bayani game da gidan da matar dakin.

"Zo ki fada min me kike so ake hanaki kamar ba dakin mamanki ba."

Mami Khadija tayi saurin cewa "don Allah kar ki biye mata."

"Sai dai a tari gaba."

Yadda Innayo tayi maganar sai ya basu dariya. Sauda na tsoron batawa Mami Khadija wadda bata daina hararta ba, sannan tana kunyar badawa Innayo kasa a ido.

Su biyun duka idanunsu na kanta. Ta kalli wannan ta kalli waccan ta dukar da kai. Farha da Mardiyya da ma su Zara da Ayaah wadda 'yan matan suka burgeta ana ta dariya. Mama Nasima kuwa cin magani take rai a bace sai ga Munzali ya shigo. Sauda ta hau murmushi da ajiyar zuciya.

"Yauwa don Allah taimakeni."

"Da me?" Ya amsa yana dube duben fuskokin mutanen dakin.

Mami da Innayo ma sai da suka yi dariya wannan karon. Salima ce ta labarta masa me yake faruwa.

"Saboda haka ka taimaketa idan ba haka ba daya daga cikinsu zata hukunta ta."

Halin rashin nutsuwar da yake ciki bai hana shi biye musu ya yi murmushi ba.

"Nima dai babu ruwana. Kawai ki kwato kanki don duka ina tsoron fushinsu."

"To ke kinji, kin kama kafar wala" cewar Mami Khadija da murmushi.

Sauda ta turo baki ta soma cewa "Ai don dai ba Mar....."

Kafin ta gama shi da Mardiyya sun kama kansu domin cikin sauri suka dinga cewa ta fadi abin da take so. Nan da nan dakin ya sake kaurewa da dariya. Sai da suka nutsu ne ta fada musu kitson da ta gani ne ya burgeta.

Ayaah ta mike da sauri tana cewa "bari na kirawo miki wadda tayi."

Sauda ta kalli Mami ita kuma ta ce ba za su jira ayi mata kitso ba.

Munzali na jin haka ya ce "Mami ba a waje za a nemo mai kitson ba. 'Yata ce ita ma. Bari su zo na gabatar muku dasu" ya kare maganar da murmushi.

Zara da Salima harda Innayo ne suka hadu suna rokar alfarmar Mami ta bari ayi kitson. Murmushi kawai tayi domin nauyinsu ne ya kamata ta kasa kafewa akan bakanta. Halayyarsu ta burgeta matuka don daga uwar har 'ya'yanta sun iya saka bako yaji kamar a gida yake. Shi yasa ta ce ba hanawa tayi ba sai dai da kunya zuwan farko su zauna ayi kitso.

"Duk gida ne Hajiya kuma na fahimceki sosai. Amma don Allah ki bari ko manya tayi mata. Ki ajiye dalilin zuwanku ki dauka mu daku daya ne."

Mami Khadija ba yadda ta iya da furucin Innayo wanda tayi cikin sigar rarrashi da sanin ya kamata. A dole ta ce ta hakura amma fa manyan za ayi kuma tun wuri Innayo ta sani cewa idan sun je gida sai ta yiwa Sauda fada.

"Ba zan hana wannan ba. Amma dai kar kiyi da yawa. Na tabbata jin da tayi kamar tana tare da 'yan uwanta ne yasa bata boye abin da take so ba. In wani gidan ne ita ma ba za ta soma ba ko Saudatu?".

Sauda ta gyada kai tana kallon kasa. Farha ta tashi ta ce bari ta fadawa Suhaib. Saudan sai ta bita aka bar Mardiyya da ta karbi baby din Zara da Munzali tare da sauran mutanen falon.

Mardiyya kunyar kasancewar Munzali a wurin ta hanata sakat. Sau biyu suna hada ido. Murmushi yake mata wanda a kasan ransa yake jin zai iya zama na bankwana. Tunda Shazali ya kunno musu wuta yanzu basu san iya inda zata tsaya ba. Don kada kowa ya fahimci kallon me suke yiwa juna sai ta dubi Zara ta tambayeta sunan baby.

Kafin Zara ta san me za ta ce mata Mami Khadija ta sako tambayar waye babba tsakanin Munzali dasu Salima. Ba kuma haka kawai tayi ba sai don ta kawar da hankulansu daga tsakin da Mama Nasima take yi jifa jifa. Sautin na yanzu yafi karfi shi ne tayi tambayar da dan karfi ita ma. Har kasan ranta bata da niyar idan sun zo ta zake da yawa tunda ta san halin abokiyar zaman nata. Kar ta ce surukanta ne Mamin take shige musu. Kyawun mu'amalar 'yan uwan Munzalin ya bata sha'awa amma ta kula ba haka bane a wurin mai shirin zama surukarsu. Yatsine yatsine take ta yi da tsaki na gajiya da kosawa daga zamansu. Dalilinta kenan na jan maganar kitson da Sauda ta nuna mata kawai don kada su kunyata kansu.

Munzali ya nuna mata Salima ya ce ta girme shi amma Zara kanwar bayansa ce. Ai fa nan suka soma musu da Zara akan waye babba har ya hakura ya karbi kankantarsa.

*

Da Ayaah ta fito kiran Murja samunta tayi tana waya. Gira ta dage tana yi mata dariyar shakiyanci saboda gane wanda ake wayar dashi. Mahiru ne saurayin da ya kai kudin aurenta.

"Haba nifa naji shiru daga kaiwa baki abin sha baki dawo ba ashe ashe..."

Sallama Murja tayi da Mahiru tayi dariya "gulmammiya indai ba labe ki ka yi min ba me ki ka ji na ce da zaki gane da wa nake waya?"

Ayaah ta rausayar da kai hannunta daya akan kugu ta ce "gani nayi kina ta bin bango kina malalewa kamar ruwa irin abin nan na Indiyawa a lambun soyayya. Na ce duk yadda aka yi Yaya Mahiru ya fadi abin da ya susuta Murjanatu 'yar Baba."

Haushi ya kama Murja da Ayaah ta kwatanta irin tsayuwarta a jikin bangon harda waka.

Iska ce ta debi maganganunsu har falon Asabe saboda sun fi kusa da wurin. Lilu ya kama dariya harda rike ciki. Suhaib ya kai masa duka yana nuna masa alamar ya yi

shiru da dan yatsa. Shi ma hirar nishadi ta sanya shi har yaji yana son ganin fuskar mai tsokanar.

"Kai fa baka da kan gado wallahi."

A lokacin wakar da Ayaah take yi ta shiga kunnuwansa sai da ya murmusa. Gyara zama ya yi yana saurarensu tare da kallon Qibdiyya da Lilu yana biye mata kamar yaro dan uwanta. Waka take abinta babu kyakkyawan kari. Duk baitin da yazo kanta take fada.

"Sai ruwa ruwa na malaleeeee. Ashe ruwan bana ya ci su Murjaaaa. Kinsan ya dade yana sonki ruwa na ...."

"Zan malale bakinki a wurin nan" cewar Murja a fusace tana galla mata harara sai kuma ta kama dariya "murya kamar gogen tsumma."

Ayaah ta sha kunu tsiwar ta motsa ta ce "kin dai fada ne kawai don kiji dadi amma ke kin san muryata da dadi. Idan ina magana Dani kasa dauke ido yake daga kaina."

"Waye kuma Dani kamar wani arne?"

Furucin Murja kenan domin yau ta fara jin sunansa. Ran Ayaah in yayi dubu kuwa a take ya baci. Maganar tayi mata zafi don sai da taji kwalla na neman kwace mata. Dani din nata ake kamantawa da arne.

A bangaren su Suhaib ma sai suka hada ido da jin kalmar Murja ta karshe da shirun Ayaah. Ba tantama ya da kanwa ne. Sai da Farha ta fito tana tambayarsu inda su Lilu suke sannan Ayaah ta fadawa Murja sakon da ya kawota.

Rashin sanin da mutane a kurkusa dasu ya sake bawa Ayaah haushi da Murja ta nuna falon Asabe. Da suka fito bayan gama jin bayanin Farha suka fito Ayaah ta basu baya tayi hanyar kofar gida da waya a kunne. Danliti ne ya iso yana neman karin kwatance. Basu ga fuskarta ba har suka karasa ciki wurinsu Innayo.

***

Mami Khadija bata son barin 'yan matan dasu Lilu kadai a gidan. Sannan take taken Mama Nasima tun farkon zuwansu ya nuna mata zasu iya samun matsala akan jiran kitso. Cije lebe tayi ta rasa me zata ce da Innayo ba tare da ta bata mata rai ba.

To ita ma Innayo din duk ta karanci rudanin da Mami Khadijan ta shiga. Ita kadai a zuciyarta ta yabawa wannan uwa. Tunanin maslaha ta tayata inda bayan dan nazari na kankanin lokaci ta bude baki tayi musu magana.

"Munzali ko zaka bisu da Murja sai Ayaah ta rakata. Kitson mutum daya dai na san kafin Magariba in Allah Ya so sun gama. Ko kuwa? Kunga sai a sami zumunci sosai tsakaninsu ko?"

Kai Mami Khadija ta daga ta kalleta da murmushi sannan tayi mata godiya sosai.

"Haka ne. Nima ba zaman kitson ne bana so ba amma kinga ..." tana son cewa su matsayin dangin mata suke kuma gashi ko iyaye maza basu gana ba. Ita da tun farko bata goyi bayan zuwan ba kuma harda Mardiyya bai kamata ta assasa dadewarsu ba.

"Karki damu duk na fahimta. Bari ta kirawo kanwarta sai su biku tare."

A lokacin Lilu ya bukaci Suhaib ya bashi mukullin mota yana da chakulet zai daukowa Qibdiyya. Nan ta soma tsalle. Munzali ya ce shan zakinta ya yi yawa kada ya dauko. Da ido Lilu ya yiwa Suhaib alamar ya taimaka ya dauko masa. Shi kuma sai ya sami kansa da biye masa yabi bayan Murja da ta fito kiran Ayaah.

***

Turare Danliti ya sake mitsikawa a hannunsa yabi jikinsa ya shafe sannan ya sako kai soron da Ayaah ta shiga bayan ta hango shi. Tuni ya ce mata a bakin titi ya ajiye mota saboda ya zata layin nasu mota bata shiga. Ita ma a ciki hijabinta ta gyarawa zama tasa hannu ta dan goge fuska. Idanun iyayenta da bakin dakin Innayo ne suka hanata sabunta kwalliya domin tarbarsa.

A tare suka sakarwa juna murmushi da ya shigo. Idanunsu sarke da juna kunya duk ta kamata.

"Baby kin yi min kyau sosai."

Kalman da Suhaib yaji kenan da ya tunkaro kofar. Can ya baro Murja tayi cikin gida tana ta kwala kiran Ayaah. Bai san wace ce ba amma zuciyarsa ta bashi abokiyar fadanta ta dazu ce wadda aka ce zasu tafi tare.

Fari tayi masa da ido sannan tayi godiya.

"Na gode Dani."

'Dani?' Suhaib ya ambaci sunan a ransa yana mai tuna abin da ya hada 'yan uwan rigima. Curiosity bai barshi ya cigaba da tsayuwa inda ya dakata ba. Yanke shawarar wucesu don yaga fuskokinsu su biyun ya yi. Murmushi ya bayyana akan fuskarsa da ya ayyana me Lilu zai yi da shi ne ya fito. Ya daga kafa zai cike tazarar dake tsakaninsa da kofar soron sai yaji abin da bai zata ba. Muryar mai suna Dani ce take fita a raunane cike da makirci irin wanda ba kowa zai gane ba.

"Baby yau ma ina cikin damuwa. Shi yasa ma kika ga na matsa sai mun hadu." Bai kuma jira jin cewarta ba don ya kula ta fara yi masa kallon tausayin nan ya dora da "wai ko kinsan yanzu matar nan ta daina zuwa shimfidata sai na biya?"

A saukar aradu maganar ta shiga kunnuwan Ayaah da Suhaib. Ita nauyi da kunya ne suka kama ta gami da fara jin haushin me yasa hirarsa bata wuce irin wadannan maganganun. Suhaib kuwa zuciyarsa yaji ta soma tafarfasa. Ya yiwa zina da duk wani ma'abocinta mummunar tsana. Salon hirar nan kuwa ba komai bane illa dauko hanyar bude kofar da za a iya fadawa gareta. Yarinyar da yaji muryarta kila ba za ta wuce sa'arsu Sauda ba ita ake fadawa wadannan kalamai. Jikinsa har yana tsuma

don bacin rai ya iso daidai bakin kofar amma sun juya masa baya sannan yaji amsarta.

Muryarta har raurawa take yi saboda an kure rashin kunyarta ta ce "Dani ina ga ba ni ya kamata ka fadawa wannan matsalar ba. Gara dai ka kaiwa magabatanku a nemi mafita."

Danliti ya gane ta fara jin tsoro daga muryarta ya yi murmushin gefen baki. Da tsoron wanda bai hana cigaba da soyayya ake samun kan irinta. Sake kwantar da murya ya yi abinsa harda langabe kai.

"Wa zan fadawa matsalata bayan Mum idan ba ke ba? Ita kuma saboda bata kasar bana son yawan tayar mata da hankali. Kece dai wadda nake shirin aura nake ganin ya dace ki san matsalolina tun yanzu domin ki tanadi hanyoyin magancesu."

Maganar tasa tana fita ne daidai da takunsa da yake ta kusanto shi gareta. Idanun Ayaah sun yi wuri wuri amma ta rasa me ya hanata ja da baya. Tausayinsa take ji har kokon ranta tana kuma gudun kar ya nemi wata idan taki taimaka masa. Bata yi aune ba ta ji shi daf da ita har tana jin dumin numfashinsa.

"Baby ko dan huk (hug) ne don Allah in samu domin na rage zafi. Ina tsananin bukatar mace. Jiya na tura mata dubu dari ta ce ya mata kadan. Ni kuma shi ne naji haushi ban sake yi mata magana ba. Kudin bai dame ni ba amma na gaji da rainin wayo."

Sai ga Suhaib yana tafa hannuwa kamar mace saboda tsabar mamakin da ya sarke shi. Bai taba ganin dan is... kamar wannan mai sunan arnan ba. Duk da haka ya tsaya yana son ganin irin tarbar da Ayaah zata yiwa yunkurinsa domin ya san matsayin da zai ajiyeta. Duk abin da ake yi ko fuskarta bai gani ba har yanzu.

Akan idonsa ta ja baya kadan tayi magana kamar mai shirin kuka.

"Ka kara hakuri. Ba ka ce idan Mum din ta dawo za a turo ba? Ka bari ayi auren."

Hannu ya daga yana son shafa fuskarta ta goce da sauri. So yake su wuce wannan matakin ya sami yadda yake so. Yawancin mata wuyarta a sami kansu na farko. Daga basu da zabin da ya wuce amincewa a gaba saboda gudun kada a ki aurensu. Ya dade da yadda da wannan shi yasa yake cin karensa babu babbaka.

Cikin muryar dake nuni da tsantsar karaya da neman agaji ya ce

"Har sai wannan lokacin Ayaah? Idan na shiga wani hali kafin nan ba laifinta bane ita kadai har dake. Naki ma yafi nata domin zuciyata da gangar jiki duka ke suke so. Nayi zaton zuwa yanzu nafi karfin komai a wurinki. Ashe ni kadai nake haukana. Yadda na daukeki daban da matsayin da kika bani."

"Ba haka bane. Kai ma ka san ina sonka."

"To ki nuna min a aikace. Ki mantar dani bakincikin da matata take kunsa min. Ki cire tsoro a ranki domin wallahi ko raina ki ka nema zan iya baki. Sannan kada ki manta dama ya halatta na ganki tunda maganar aure ce tsakaninmu. Gani babu hijabi balle mayafi. Hakkina ne kike neman dannewa Baby. Kin yi min adalci kenan?"

Runtse idanu Ayaah tayi da ya sake daga hannu zai shafa fuskarta. Bata so ko kadan amma zuciyarta ta gama aminta da halatta haramun din da yake neman yi. Ba zina zata yi ba. Nutsuwar da yake nema kawai take son taimaka masa ya samu.

Suhaib bai san lokacin da ya iso gabansu ba. Danliti da ya gama sakawa ransa cewa daga shafa fuskar zai zarce da koya mata wani karatun daban sai ji ya yi hannunsa ya makale a iska. Daga kai ya yi yana kallon gefen fuskar mutumin da ya rike shi a firgice.

Ayaah kuwa da taji shiru bai taba ta ba sai ta bude idanunta a hankali. Nan suka yi ido hudu da mutumin da bata sani ba. Kwayar idonsa tamkar maganadisu aka zuba saboda yadda ta kasa dauke nata. Mugun kallo yake yi mata mai kama da na tsana. Zuciyarta sai da tayi wani irin tsalle don tsoratar da tayi. Suhaib ya kuma ware mata idanuwansa da suka kara firgita ta.

"Get out of here (bar wurin nan)" ya umarceta da tsawa.

A guje tayi cikin gida tana haki. Murja har ta fitar da rai da ganinta suka yi karo. Bata kula da yanayinta ba ta fada mata sakon Innayo.

Bayan tafiyarta Suhaib ya kalli Danliti wanda yake ta kokawar kwace hannunsa ya kasa. Tuno inda ya san fuskarsa ya yi ba shiri ya saki hannun baki a bude.

"Kai? Ba kai bane makaniken...."

Bai iya karasa magana ba sakamakon ture shi da Danliti ya yi da karfi ya kwasa a guje ya fita daga soron. Tunda ya fita ba shi ya tsaya ba sai da yaje titi. Ya tsaya mayar da numfashi bai yi aune ba wani mai kurar ruwa ya kwashe shi ya watsar a gefe.

*

Innayo da iyalinta har bakin mota suka rako su Mami Khadija. Su suna godiyar ziyara ita tana ta kyautata musu da aka yi. Ita dai Mama Nasima mota ta shige kai tsaye ko waige babu. Tuni ta fara musu da zuciyarta akan amincewa alakar Munzali da Mardiyya. Ta raina gidan da ahalin gidan.

An rarrabu kowa ya shiga mota. Ayaah kamar wadda ta yiwa Sarki karya gabadaya ta kasa sakewa. Duk inda ta motsa sai taga kamar idanun mutumin da taji Kawunta ya kira Suhaib suna kanta. A gaban motar Munzali ta zauna ta hade hannuwanta a tsakiyar cinya. Murja tana baya suka bi bayan motar Suhaib din. Ita dai har suka isa gidan bata san inda tunaninta yake ba. Tsakin da taji lokacin da ta fito daga motar ne ma yasa ta karewa gidan da suka iso kallo. Ido suka kuma hadawa da Suhaib ya sake yin tsaki a karo na biyu sannan ya kawar da kai tamkar yana kyamar kallonta.

Hawaye taji yana neman sauko mata ta daure ta hadiye shi. Da tabi 'yan matan cikin gidan shi tsayuwa ya yi wurin Munzali suna magana. Hankalinta a tashe tana tsoron ko abin da ya gani yake fada masa. Ana ta janta da hira sai dai tayi yake. Cikin abin da bai kai minti talatin ba har an gama kitson. Mami Khadija ta basu kudi suka ki karba. Har ta nuna bacin rai amma suka ki. Sai suka sake burgeta. Dama da a gida suka hadu ba kudi zata bayar ba. Kyauta zata yi musu irin wadda ta dace da 'yan mata.

"Ku karbi nambar juna ku dinga gaisawa. A haka ake fara zumunci."

Abin da tace musu kenan sannan ta juya ta barsu dasu Sauda. Da yake 'ya'yan nata babu girman kai a take suka fara aiwatar da shawararta, aka yi musayar nambobi tsakaninsu. Ayaah jiki ya kasa daina rawa saboda ganin har lokacin Munzali da Suhaib suna magana. Da Munzali ya kallo inda take kuwa sai da taji kamar ta saki fitsari a wurin.

"Ku zo mu tafi"

Kasa daga kafa tayi sai da Murja ta ja hannunta. Da suka isa bakin motar Suhaib ya bata mamaki da ya bude mata gaban sannan ya hada da yi mata murmushi. Kura masa idanu tayi ba shiri domin tabbatar da abin da take gani. Ya kuwa sake yi mata

murmushi a karo na biyu. Farha tana yi musu sallama shi ma ya yi harda cewa su gaida gida.

Murmushinsa bai hanata satar kallon Munzali ba a hanya tana jiran ya fara fada. Gani take kamar na mugunta yake mata bayan ya gama hada mata bomb.

Kallon hanya da zurfi cikin tunani da take ganin Munzali ya yi bashi da alaka da abin da take tunani. Suhaib ya yi masa magana ne akan baffaninsu maza da suka yaba dasu har suka bukaci a sanar dasu cewa su turo iyayensu indai da gaske suke. Ya kira Abbati yafi sau shurin masaki amma bai dauka ba tunda gari ya waye. Abin ya karu domin yanzu wayar ko shiga bata yi. Haka ya rufe ido ya kira layin Baaba Mari shi ma shiru. Kafin ya isa kofar gidan Hasiya ya kira mutum ya kai shida a gidansu Abbati. A kalla kowanne ya kira sau uku ko hudu. Hankalinsa ya tashi sosai har ta kai kwatancen gidansu da Murja take yi masa baya ganewa sosai. Sau biyu yana yin kwana sabanin wadda take fada masa.

Tsayuwarsa da mota ke da wuya Ummita ta fito rike da Hasiya a jikinta. Tangadi suke duk su biyun. Hasiya na ciwo, Ummita na firgicin irin aman da taga tana yi. Cikin kankanin lokaci ta fita daga hayyacinta. Ko kashe motar bai yi ba Ayaah da Murja suka fita da sauri.

"Me ya sameta?"

Ummita tana kuka ta fada masa yadda Hasiya ta dinga amai daga kwabin lalle. Babansu kuma tun safe Abdulkarim ya turo aka tafi dashi asibiti tare da Abbas. Duk wannan bayanin a hanya aka yi shi. Gudu irin na ganganci ya dinga yi saboda kakarin da Hasiya take yi a galabaice.

Kiran Abbatin da bai sake samun damar yi ba kenan a ranar domin suna zuwa asibitin emergency aka nufa da ita.

***

"Gabadaya na kasa fahimtar bayaninka Abbati. Haka kawai ta suma bayan bata kwana da ciwon komai ba?" Mal. Inuwa ya furta hankalinsa yana ga Baaba Mari dake kwance akan gadon asibiti rai kwakwai, mutu kwakwai.

Atine ce tayi karfin halin cewa "Ya ce magana suke fa yaji ta daina amsawa"

Duka 'ya'yan Baaba Mari suna dakin da aka kwantar da ita a babban asibitin garin Kirikasamma. Abbati ya rasa me yake masa dadi a duniya. Gefe guda ya samu ya zauna ya hada kai da gwiwa cikin tunani. Tare suke da mahaifinsu Mal. Inuwa da wasu cikin Gwoggoninsu matan 'yan uwansa. Shi Mal. Inuwa yafi kowa nuna gigita saboda yadda yaga Abbati ya fito da ita waje a hannu ko motsi bata yi. Daga shi har 'yan majalisarsa sun dauka bata da rai.

Kowa yana tofa albarkacin bakinsa game da ciwon da ba a san silarsa ba likita ya dawo. Wasu gwaje gwajen jini ya sake rubutawa ya bukaci Abbati ya biyo shi waje.

Da sauri Mal. Inuwa ya ce "Fadi ko ma mene ne Dafta. Nan wajen duka babu bare. Me ya sami Mari?"

Likitan ya dubi Abbati wanda ya gyada masa kai sannan ya fada musu abin da suka gano.

"A gaskiya jininta ya hau fiye da kima har yana barazanar taba mata zuciya. Idan ba a dauki matakin da ya dace ba zata iya samun stroke (mutuwar barin jiki) ko …."

"Allah ma Ya kiyaye" cewar Mal. Inuwa da rawar murya "indai kudi ne sha Allahu ba zai gagara ba. Ayi mata duk abin da ya dace ga danta nan."

"Malam. Malam"

Ba Mal. Inuwa da ta kira ba, duka wanda yake dakin sai da ya juya da farincikin ganin Baaba Mari ta farfado.

Da hannu ta yafito shi ya matso kusa da gadon ya duka kansa ganin tana ta motsa baki.

"Ku mayar dani gida."

Wani irin kallo ya mata cikin tashin hankali ya daga kansa ya yiwa Abbati inkiya da ya matso. Su Habi duk sai suka fice.

"Kaji taurin kan mata ko? Wai a mayar da ita gida."

Murmushi tayi masa "Idan an kaini asibitin waye zai biya kudin?"

"Wace irin magana ce wannan? Ko kin sami makuwa ne saboda ciwo?"

Muryarta ta kara dusashewa ta ce "kana da sauran kadara ne Malam da zaka sayar ka nema min magani?"

Duk da ya soma harzuka haka ya daure saboda ba lafiya gareta ba ya ce

"Wai ba ga Abbati ba? Mari lafiyarki kuwa?"

Idanun Abbatin ta lalubo da nata. Ya zabge tamkar shi ne kwance a gadon asibitin. Kalamanta na gaba a gareshi ita kanta basu yi mata dadi ba sai dai babu gudu ba ja da baya.

"Ban yafe ba idan ya sake kashe min kwandalarsa. Ban yarda kaima ka kashe min daga kudin da ya baka ba. Sannan idan ban tashi ba ka isar da sakona ga dan uwanka Sa'idu. NI MARIYA BAN YAFE MASA BA!

TARA DAGA KE SAI GOMA.

"Anya Mari baki yi gamo ba? Yaya Sa'idun kike ja wa Allah Ya isa?"

Wani bacin rai ne ya turnuke kirjinta. Wato bai ma damu da abin da tace akan dan cikinsa ba sai yayansa wanda ya zama silar rushewar rayuwar 'ya'yanta maza.

"Ko in hada da kai ne?"

Mal. Inuwa ba arziki ya saita fuskarsa daga fushin da ya yi da farko

"Ni kuma me nayi?"

Ko kula shi bata yi ba ta dubi Abbati da murmushi. Wannan karon kallon yana cike da soyayyar uwa da danta. Yadda ya koma yafi mata ciwo akan shi kansa. Dukiyarsa take son ta raba shi da ita domin babu amfani su cigaba da ninkaya cikin haram. Sabuwar rayuwa za ta tura shi da taimakon Allah wadda bai taso cikinta ba tunda ya fara sana'arsa. A yanzu yafi bukatar soyayyarta da tausayawa kuma a shirye take ta nuna masa domin yaji dadin tuba.

"Kirawo 'yan uwanka su taimaka min na tashi."

Kai ya gyada daidai da saukowar hawaye a idanunsa. Tana kallon yadda yasa bayan hannunsa ya dauke hawayen sai dai bai hana wasu gudana suna maye gurbin wanda yake sharewa ba. Haka ya fita bai yi musu akan rashin son zamanta ba. Ya fahimceta sarai. A shirye yake ya bi umarninta. Da hannu ya kara goge idanunsa sannan ya kira kannen nasa.

Da ya fita Mal. Inuwa kallon tuhuma ya dinga yi mata. Tabbas akwai abin da yake faruwa tsakaninta da Abbati. A matse yake da son ji. Sai dai yanayin fuskarta ya sanya tayi masa kwarjinin da ba zai iya yi mata titsiye ba.

Likitan da ya dubata har bakin mota ya bisu yana nanata musu gangancin dake tattare da dauketa a yanzu.

"Bai kamata ku biye mata don ta ce ba za ta zauna ba" ya dubi matan da ya tabbatar 'ya'yanta ne saboda kukan da suke da rokon yayansu akan su zauna "za ta iya shiga yanayin da dukkanku nan sai kun yi dana sanin kin karbar shawarata."

Habi sai ta koma kusa da mahaifinsu tana kuka.

"Kaji abin da yake cewa Baba. Don Allah ka tilasta mata ta zauna."

"Abbati?"

"Baba muje gidan. Da kaina zan dawo da ita asibiti in Allah Ya yarda."

Iyakar abin da yace kenan ya shiga gaban motar da zata mayar dasu gida.

*

Deluwa ce kan gaba wurin zuwa bangaren Baaba Mari bayan sun dawo. Daga ita sai daurin kirji da dankwali a ka. Tabe baki tayi tana soshe-soshen jiki.

"Yo aka ce mana ranga- ranga aka fitar dake ashe ma ciwon ba wani na azo a gani bane."

Ci-kan-ki wannan bata samu daga bakin kowa ba. Ta gaji da maganganunta ta kama hanya za ta fita.

"Ki kirawo min mijinki idan kin fita"

Wata irin juyowa Deluwa tayi ta kalli bakin Baaba Mari da ya furta wannan maganar. Har wani duka ta kaiwa kunnenta domin tabbatarwa.

"Ki ka ce?"

"Ki turo min mijinki! Da jikina da kwari da kaina zan je na same shi."

Mal. Inuwa dama ya matsu yaji me yake faruwa. To amma shi ma yadda tayi maganar ba karamin tsorata shi ya yi ba. Musamman da ta sallami duka 'ya'yanta da jama'ar gidan da suke sashen nasu ta bar Abbati shi kadai. Dadin dadawa kuma sai shi ma Abbatin ya yi wata magana da ta sabule masa kuzarinsa ya kara shiga firgici akan me yake faruwa.

Hadiyar yawu mai masifaffen daci ya yi, idanunsa duk sun shige ciki ya dubeta.

"Baaba tona min asiri zaki yi? Na rantse miki ba yau na tuba ba. Ni da Munzali har..."

Runtse idanuwa tayi da ya ambaci sunan Munzali. Allah Ya sani ko sunansa bata son ji balle ayi hirarsa. Ya fice mata a rai lokaci guda kamar anyi ruwa an dauke. Akwai laifin mijinta da yayansa dumu dumu amma nasa mai girma ne. Bata jin zata taba manta cewa shi ya koya masa....karshenta ma har yanzu suna yi. Tsigar jikinta a take ta mimmike da wannan tunanin.

"Idan ban yiwa tufkar hanci ba ka san irinka nawa zasu samar mana a dangi?"

Abin da ta ce kenan. Sai ya koma jikin bango ya tsaya tare da jingina bayansa. Babu wani abu ko digo da yake yi masa dadi a duniyar nan. Nadama iyakar nadama ya kara yi. Ya tsani ranakun da ya mika jikinsa ga marasa tsoron Allah cikin manyan mutane masu fada a ji a kasar nan. Farincikin da kudaden suka saka shi ya koma bakinciki.

Sallamar Mal. Sa'idu da kakkaurar murya mai nuni da girman bacin ransa sai da tasa hanjin cikinsa kanannadewa. Zazzabi mai zafi har cikin 'bargo ya afka masa. Daga wannan lokacin zai sanya kafa guda da sabon shafin rayuwa. Idan har zai iya cigaba da rayuwar.

Shikenan!

***

"Wa nake gani kamar Mariya?"

Asabe ta takawa kafafunta burki a daidai kofar dakin Innayo. Laluben dakin da yake sakale akan dokin kofa ta sake dagawa da hannunta ta leka ciki. Tabbas jikarta ce take hangowa zaune akan cinyar Salima tana ta zuba surutu. Ranta ya sosu ta taka cikin falon ko sallama babu sai ganin hannunta Salima tayi tana kokarin fincikar Qibdiyyan.

"Tashi ki wuce muje."

Noke kafada tayi ta kwace hannunta. Salima ta murmusa kawai ta ce mata "tashi mana Qibdiyya. Sannu da zuwa Asabe."

"Ban son munafunci. Ki rike sannunki ki sakar min jika"

Sababi ta hau yi akan dalilinsu na riketa a dakin.

"Shi ma Munzalin zai zo ya sameni. Akan me zai kawota bai fada min ba?"

Innayo da Zara duka suna falon amma yadda bata nuna ta gansu ba haka su ma basu kulata ba. Ta gaji da fadanta ta dauki Qibdiyya da karfi ta nufi bangarenta.

Ihunta suka ji da ta tura kofar ta bude ba tare da ta saka mukulli ba.

"Jar uban nan! Wallahi gidan nan baku so zaman lafiya ba. Wace mai kokarin ce ta bude min daki?"

"Daddyna ne ya budewa su Uncle Lilu."

Asabe ta gatsina fuska "waye kuma Unku Lihu?"

"Uncle Lilu da yake min doki a bayansa... " Cewar Qibdiyya da mamakinta irin na yara idan aka kasa gane abu mai mahimmanci a wurinsu.

Asabe hakura tayi da neman ba'asi. Duk inda yake ta san dole zai dawo daukan 'yarsa. Zata nemi karin bayani a wurinsa. Sannan kuma ta samu ta karbi kudin da take tunanin shi ya zo bata.

Mayafinta ta kama za ta cire Qibdiyya ta ce zata yi fitsari. Sunkutarta tayi gabadayanta ta shiga bandaki. Yarinya fes da ita amma saboda son burge mahaifinta kamar ba dan cikinta ba ta tube mata kaya.

"Wanka zan miki kada ya dawo ya ganki haka kamar wadda tayi dambe."

Bata da ruwan dumi amma don kar ya dawo bata gama ba idan ta tsaya dafawa sai tayi mata da mai sanyi. Qibdiyya harda kukanta don garin babu wannan zafin da zai sa mutum wanka da ruwan sanyi. Aka zo shafa mai tabi ta mulketa da man kadanya sai kyalli take. Ta kawo kwalli aka rambada mata a ido. Ta tafi dauko pant din da ta cire mata a bandaki Qibdiyya ta kai hannu gabanta tana susa. Wanka ne aka yi aka koro maikon jiki amma ba ayi mata tsarki ba. Dan datti da ruwan sabulun da ya wuce ta wajen da fitsarin da tayi ba a wanke ba.

Wannan susa akan idon Asabe da ta dawo daga bandakin.

"Kalau kike kartar jiki haka da karfi? Kwanta mu gani ko kurji ne a wajen."

Da kanta ta kwantar da ita ta kai hannu za ta raba kafafunta taji ta cafke mata hannun. Idanuwa Qibdiyya ke binta dasu tana yi mata kallon tsoro.

"Kema hannu zaki saka min a nan? Kiyi min a hankali ba mai zafi ba. Kuma ba zan fadawa kowa ba don kada ki yanka min Daddy da Papa."

Asabe ido kawai ta zuba mata ta kasa kwakkwaran motsi saboda firgici.

Qibdiyya kuwa tuni ta rufe ido tana jira ayi a gama. Da taji shiru sai ta bude idon a hankali. Da karamar muryarta ta ce da Asabe,

"Ni ce zan yi miki?"

Kamar wadda aka kwadawa mari sai lokacin Asabe ta dawo hayyacinta. Kuka ta kama yi ba tare da ta sani ba ga jikinta ya soma rawa kamar mazari. Furucin Qibdiyya ya matukar tayar mata da hankali fiye da tunani. Shi yasa bata ma san lokacin da ta d'aka mata wani mugun duka a cinya ba.

"Ki yi min uwar me? Na bonu ni Asabe. Kiyi min me? Tashi don uban...."

Qibdiyya ta tashi zaune a razane tana son yin kuka amma tsoro ya hana. Daddy ya hanata kuka ko taji zafi idan yana yi mata abu irin wannan. Cewa yake hawayenta na fita za a saka mamanta a rami a rufe da kasa. Tun bata iya ba har ta kware wurin danne hawayenta. Idanu tsilli tsilli ta kafe Asabe dasu babu alamar kuka duk zafin dukan.

"Daina kallona" wani tunani tayi ta sake kwantar da Qibdiyya ta soma dubata. Allah ne kadai Ya taimaketa bata suma ba akan abin da ta gani. Kankanuwar yarinya ta kusa gama budewa.

Kafafunta kasa daukarta suka yi bata ankara ba tayi zaman 'yan bori a kasa. Kai ta dago dankwalinta ya karkace saura kadan ya fadi ta kalli jikarta.

"Waye yake taba miki nan?" Ta nunawa Qibdiyya inda take tambaya da hannu.

Razanar da tayi a dalilin dukan da tayi mata dazu da kuma tsoron kada a rufe mata uwa a rami sai taki fada. Jikinta yana bata cewa idan ta fada din ma ba tsira zata yi ba.

Asabe ta gaji da tambaya ta soma dukanta. Amma ko digon hawaye babu sai ajiyar zuciya. Hargagin muryarta tana cewa "ba za ki fada min ba?" har tsakar gida. Uwani ta fito tana waya taji. Hanyar dakin ta nufa sai dai kafin ta isa Innayo ta fito daga nata dakin ta ce mata kada ta soma zuwa.

"Bana son gulma ki zo ki wuce naki uzurin kada ki ja min magana".

Komawa tayi din amma haka kawai taji ta kwadaitu da son sanin me yake faruwa. Maganar dai kamar da Qibdiyya ake yi amma bata ji ko tarin yarinyar ba.

*

"Munzali kana ina?"

Sautin muryarta banda alamun tashin hankali harda kuka yake iya ji.

"Muna asibiti da Hasiya ne amma na kusa tahowa. Wani abin ne?"

Karo na farko a rayuwar Asabe da ta dakata tayi tunani kenan da kwakwalwarta. Wannan sam ba maganar waya bace.

"Ka taho da sauri ina son ganinka yanzun nan."

Bayan ajiye wayar hankalinsa ya kasa kwanciya. Yasa rai da jin mitarta akan zuwa wurin 'ya'yan Innayo. Kudi ya damkawa Ummita kafin shigowar Hon. Habu ya ce musu zai je gida ya dawo.

Akan hanya ya dinga kiran Abbati shiru bai dauka ba. Kansa ya sake daukar chaji kamar ana buga guduma. Ya san Abbati ba yaro bane da za a zane bayan ya fadi gaskiya. To amma me ya biyo bayan fadin tunda ya tabbatar da wahala idan bai fada din ba.

***

Sanyi da daddadan kamshi ke tashi a wani katafaren falo. Duk inda ake neman ni'ima mai shiga zuci an gama samu a nan. Mazauna wurin maza ne su biyar wadanda shekarunsu suka tura. Ga kuma shaida a jikinsu na cewa sun kama kasa. Daga 'yan siyasa sai 'yan kasuwa sai kuwa masu manyan mukamai a gwomnati.

Dukkaninsu sanye suke da manyan kaya harda babbar riga illa mutum daya. Daga gani shi ne mai masaukin baki saboda yadda ya bararraje. Hula da babbar rigarsa duk suna gefe guda can nesa dashi. Bayani yake yiwa babban bakonsu. Amininsu ne ta fanin harkokin 'yan mata. Sai gashi a Kano garin yake gida ga sauran hudun.

"Yanzu sai da kana shirin komawa Kaduna zaka sanar damu zuwanka Alh. Tahir? Karramawar nan da ake yiwa manyan baki ma baka bamu damar yi maka ba."

Cewar mai gidan hutun (guest house) din da suke ciki.

Dariya Alh. Tahir ya yi masa "banda abinka ni da na taho da taurarina guda uku ina ni ina bin kwararo?"

Kwashewa suka yi da dariyar shakiyanci suna zolayar juna. Nan hira ta kacame da ciye ciyen kayan abinci na alfarma. Maigidan aka kira ya amsa ya bayar da umarni ga mai kiran da ya shigo.

Alh. Tahir na jin haka ya san ba zai wuce mace aka kawo ba. Murmushi ya yi yana gyada kai.

"Ni dai bari na gudu don na tuba."

Wani Alhaji mai tulun ciki ya tafa da na kusa dashi suka yi masa dariya "Kowa ya tuba don wuya ba lada."

Alh. Tahir ya kada kai "da lada fa. Abubuwa sun cabe min. 'Yar banzar yarinyar nan kawar Farha da nake fada muku yanzu fa Yakumbo ta rantse sai na aureta. Yarinyar da take yawonta da kananan yara kuma duk na sani."

Mai gidan yaja guntun tsaki "duk laifinka ne. Na fada maka wallahi Malamina yana aiki akansu maganar nan zata bi ruwa. Ita Yakumbon da kanta za ta ce a bar maganar. Yarinyar kuwa duk iskancinta sai an sauke mata shi. Ba za ta sake yin wani yunkuri domin bata maka suna ba."

"Wai kai Alh. Tahir tsoron me kake ne? Ka amince mana ka yar da kwallon mangwaro. Yarinyar nan a bariki ta sameka tayi kadan ta kawo maka cikas da girmanka da komai." Wani da bai ce komai ba tun dazu ya tofa albarkacin bakinsa.

Mai neman kuka ne aka jefe shi da kashin awaki. Basu wani jima ba suka shawo kansa. Nan take Maigidan wanda aka fi sani da Comared ya kira Malamin tsibbunsa a waya. Suna kan magana wani mutum sanye da kufta da wando ya zo ya shige cikin dakin Comared din da dan matashi da bai fi shekaru sha takwas ba.

Bayan ya gama wayar ne Alh. Tahir ya tsare shi da idanu yana nuni da dakin nasa.

"Comared ba dai kaima ka fara daya harkar ba da maza?"

Kkamar dazu, yanzu ma dariya sauran suka yi masa. Comared ya gyara zama yana shafar gemunsa.

"Wannan Malamin da na kira shi ya dorani a harkar nan. Naki fada maka ne kawai saboda naga kamar kana kyamar abin. Magana ta gaskiya wani aiki aka yi min shi ne yace na nemi namiji. Washegari aikin ya ci to amma abin ya zarce...." Ya kare da shu'umar dariya.

Alh. Tahir ya kada kai "kace ya hadani da mata goma ni dai akan namiji guda."

Wata dariyar Comared ya yi domin aikinsa kenan. Dariya kamar dan akuya.

"Ai kuwa ka makaro domin kuwa namiji ya ce ka nema ranar laraba kafin rana tayi zawali. Indai kayi yadda ya ce da kanka za ka nemeni. Zai aiko da magani da zaka hada kafin kayi abin."

Hula Alh. Tahir ya cire ya shafi sumar kansa wadda ta fara samun bakin furfura. Ko kadan baya son auren Yumna musamman saboda abin da ta nunawa Farha. A bangare daya kuma ko yana shan giyar wake ba zai so tsinuwar Yakumbo ba. Sau daya dai don ya nemi namiji ba zai rage shi da komai ba. Yana tunanin abin yaji tsigar jikinsa ta mike har amai na neman taso masa. Wayarsa ya dauka ya tashi yana yi musu sallama.

Comared ya dakatar dashi daga tafiya "bari nasa ayi maka booking wanda ya san me yake yi tunda kai sabon shiga ne" waya ya dauka ya sake kira sai ga mai kuftar da ya shige dakinsa ya fito.

Zubewa ya yi kamar mai rokon gafara a gabansa "Yallabai kana da wata bukatar ne?"

Kofar dakinsa ya kalla ya hadiyi yawu "yaron da ka kawo daga gani ya yi kawai. Kwararre a harkar nan nake so kayi min booking ranar laraba mai zuwa. Ina son irin wanda idan sabon kamu ya samu gobe da kansa zai koma. Daga aljihuna kadai zan baka dubu dari biyar. Shi kuma uban gayyar ba mai rowa bane. Ka sa rai da farin gani."

Shazali ya saki murmushi har hakoransa suka fito. Ya san inda zai samo musu kalar wadanda suke so. Shi da yake da shaidar da zata tarwatsa musu rayuwa, dolensu su zo ko sun ki ko sun so.

GOMA ƊAYA GOMA.

Akwai uwa kuma akwai uwa! Wadansu uwayen sun san cewa 'ya'ya amanar Allah ne kuma suna kokari wurin ganin sun sauke in nauyin. A cikinsu wasu suna yin nasara wurin aikata daidai a wannan tafiya mai dadi da wahala. Wasu kuwa kuskure suke aikatawa wanda soyayyar 'ya'yan ne yake zama sanadiyarsa. A shagwaba 'ya'ya fiye da kima. A kasa tsawatarwa kurakurensu, sannan a karshe a biyewa ra'ayoyinsu koda zuciya da kwakwalwa sun san hakan bai dace ba. Kaso na biyu cikin uwayen bayan wannan rabe raben na masu son sauke nauyi sune masu fifita kawunansu da bukatunsu akan na 'ya'yansu. Irinsu ake yiwa lakabi da ballagaza.

Kwakwalwarta kalau take balle ace lalura ke hanata bawa 'ya'yanta kulawa. Ita bata ma san cewa kuskure take aikatawa ba. A lissafinta kodayaushe ita ce farko kafin danta. Shi yasa take gabatar da farincikinta kafin na danta. Ita fa ko yunwa ke damunsu ita da 'ya'yanta sai ta fara koshi take tunawa dasu. Idan abincin babu yawa sai su kare da sudin hannu. Kulawa wadda ke karkata zukata ga nuna tausayi da damuwa ga mai bayar da ita bata fiya shiga tsakaninta da nata ba. Wannan sakacin nata zai iya zama kalubale kuma babbar jarabawa ga 'ya'yanta da duk wanda ya rab'e su. A karshe da za ta rigasu komawa ga Allah da wahala su ji kewa irin wadda 'ya'ya ke ji idan sun rasa uwa. Albarkacin wata tara, nakuda da shayarwa kadai za ta ci.

Ya ke Uwa!

Ki koyawa 'ya'yanki sonki ta hanyar kulawa, tausayi, jinkai, ladabtarwa da soyayya. Idan a gaba kin sami sabanin tarbiyar da kika yi musu ki sani cewa kowane bawa yana tafe da kaddararsa. Ke dai ki tabbatar cewa kin yi iya yinki har a gaban Allah

ta yadda ba za ki zama wata Asaben ba. Kin bata naki ki bata na wasu da basu ji ba basu gani ba.

Kada ku manta laifin ba na Uwa bane ita kadai.

***

Ya dauki kimanin minti goma sha biyar a dakin bata ce komai ba. Hasali ma ko motsi daga inda take bata yi ba. Qibdiyya ce a gefenta idanunta a kumbure sun yi ja, da gani tasha kuka. Ya yi mata magana bata amsa masa ba. Tun shigowarsa da ta taso a guje Asabe tayi mata tsawa ta koma ta zauna.

Gajiya ya yi da shirun. Ya san halin mahaifiyarsa. Karshenta kudi take son karba a hannunsa take ta kirkiro wannan dabarar. Hannu ya zira a aljihu ya zaro dubu goman da ta rage a hannunsa ya dora mata a hannun kujera.

"Qibdiyya taso mu tafi" ya furta a yayinda ya mika mata hannunsa don ta kama.

Sannan Asabe ta tashi da fada bayan ta kwashe kudin "ince ka zo amma don raini baka tsaya kaji me ya faru ba za ka tafi."

Hannu yasa ya matse kansa da yake ciwo. Haka ya soma magana kamar zai yi kuka. Bai san wata damuwar da ta zarce rashin ji daga Abbati ba. Washegari yake son bin sa, ko ma me za ayi gara ayi musu tare. Ko kuma ya bishi a yau....tunaninsa ne ya katse lokacin da Asabe ta sakar masa harsashin da ya bula kwakwalwa da zuciyarsa.

"Ban san wane irin sakaci kake yi da 'yarka har wani tsinanne ya..ya" sai taji bakinta ya sarke sakamakon idanun da Munzali ya zuba mata.

"Me aka yi?" Ya furta da sautin da yafi kama da umarni. Bai ma san ya yi amfani dashi ba saboda yadda ya soma tsorata tun kafin yaji karshen zancen.

Asabe ta hadiyi yawu "ina jin fyade aka yi..."

"Qibdiyyan???" Ya tambaya a razane kafin ma ta kai karshe. 'Yarsa ya dauka da zafin nama yana neman dubata mata jiki.

Asabe tayi azamar karbeta "baka da hankali ne za ka bude mata jiki? Na riga na duba kuma wallahi namiji ya kusanci..."

Innalillahi wa inna ilaihi raji'un....hawaye ne suka ballewa Munzali. Zancen ya dinga bin sassan jikinsa tamkar ana huda shi da alluran da aka kona a wuta. A wurin ya durkushe yana kuka mai sauti. Kuka irin wanda bai taba yin kwatankwacinsa ba. Da zai ci karo da ko ma waye ya tabbata sai dai ayi masa takwara a dangi domin shi kam tasa ta kare. Kashe shi zai yi idan ya so shi ma a hukunta shi.

Asabe gani tayi ya dora hannu a kahon zuci yana bugun kirjinsa. Idanunsa basu bar fitar da hawaye ba.

"Kashe kanka zaka yi ko kuwa zaka tambayeta waye ya mata wannan aikin?" Sannan ta kara da cewa "kuma ina zargin ba abin kwana daya bane domin kuwa alamu sun nuna ta soma sabawa."

Runtse idanuwansa kawai ya yi. Yawancin maza idan 'ya'yansu mata suka isa aure sai kaga suna ja wa manemansu aji. Ba don komai ba kuwa illa tunanin cewa idan ka auri 'yata fa ga abin da zaka yi mata. Wannan kishin yadda uba yake yiwa 'yarsa haka 'ya'ya maza suke yiwa uwayensu idan kaddarar sake aure ta gifta musu. Munzali yaji zuciyarsa tana suya a kirjinsa. 'Yarsa mai shekaru biyar ake cewa ta saba...ta saba da namiji a kananun shekarunta. Shi da ransa, mahaifiyarta ma da ranta. Garin yaya???

(Zina bashi ce Munzali. Kaga Allah Ya bamu 'ya. Idan bamu tuba ba wata rana ita za ta girbe abin da muka shuka)

Kalaman Abbati a wani lokaci da yake yi masa maganar tuba daga wannan alfashar suka dawo masa. A hankali ya tashi yaje gaban Qibdiyya ya durkusa. Ya mika hannuwansa gareta duk ta firgice. Asabe tayi mata dukan da ba a taba yi mata ba a dalilin kin fadan wanda yake mata. Shi yasa ta tsorata ko shi ma dukanta zai yi. Ga mamakinta da Asaben sai ya rungume Qibdiyya. Riketa ya yi sosai a jikinsa yana jin kamar ranar suka fara haduwa bayan haihuwarta. She will always be his baby duk girmanta. Kasancewarta tsatsonsa bai kara mata komai ba sai masifa. Ya cuceta cuta ta har abada domin an bar mata tabo daga barnar da ya kasance yana aikatawa.

"Ki yafe min Mariya. Ki ce kin yafe min."

A razane Asabe ta taso har tana tuntube da kujera.

"Me kake cewa. Na shigesu. Munzali kai ne ka bata..."

Magana ya cigaba da yiwa Qibdiyya da taushin murya.

"Ki yafewa uban da bai bar alkhairin da zaki mora a rayuwarki ba sai sharri. Nayi miki alkawarin gyarawa. Zan yi ta tuba har karshen rayuwata. Ina fatan Allah Ya haskaka rayuwarki Ya wanke miki duhun da na janyo miki."

"Munzali kayi min gwari gwari don Allah. Shin kai ne ka bata 'yar nan?"

"Allah ba zai dora min wannan kaddarar ba in sha Allahu."

"Washhh har hankalina ya kwanta" tace tare da sauke ajiyar zuciya "yadda ka ke magana ne sai a zata kai ne."

Da Qibdiyya a hannunsa ya juyo ya fuskanceta

"Hankalinki kar ya kwanta Asabe. Ke ki ka assasa komai."

"Kar ka dora min laifin da ba nawa ba. Dubata fa kawai nayi na sanar da kai. Banda sakarci ita kadai kwal amma kun kasa kula da ita."

Murmushin bacin rai ya yi "kamar yadda ki ka kasa kula dani da 'yan uwana?"

Ba ta zaci wadannan kalaman daga bakinsa ba shi yasa ta dinga bude baki tana rufewa don mamaki. Da kyar ta iya yin magana muryarta tana fita kamar an shake mata wuya.

"Me kake nufi?"

"Bayan haihuwata da suna da ku ka saka min ke da Baba kuna da wani abin kare kai a wajen Allah game da tarbiyyata? Kin san sana'ata? Kin san silar arzikina?" A yanzu sababbin hawaye sun cika idanunsa har suna zuba amma dariya yake yi "ina dauke da zunubina ga na Abbati da nayi silar fadawarsa mummunar rayuwa. Ba mamaki shi yasa Allah Ya jarabceni akan Qibdiyya."

'Kada kayi sab'o' ya fadawa kansa da ya tuna da cewa da a gaban Abbati ya fadi wannan maganar haka zai ce masa.

Tunanin Asabe sai ya luluka da ita duniya daban da wadda Munzali yake son haska mata. Gani take kamar abin da ya sami Qibdiyya ne yake neman taba masa kai. Banda haka kaf zantukansa basu yi ma'ana ba a cewarta. Tana kallo ya murda kofar dakinta ya fita. Sai dai me?

Yana fita suka yi ido hudu da guda cikin 'yan uwansa mata. Idanunta kadai ya kalla ya san ta gama jin komai. Abin mamaki shi ne yadda zuciyarsa bata ji komai ba. To

me zai ji bayan ciwon da yake ciki a yanzu? Matsalarsa bata wuce rashin sanin halin da Abbati yake ciki ba. Sai kuma tunanin irin hukuncin da zai yiwa wanda ya soma ketawa diyarsa haddi.

***

Zaune akan kujera Mal. Sa'idu ne yana karkada kafafunsa. Su hudu ne a falon Baba Mari. Daga ita sai Abbati, Mal. Inuwa da shi babban bako na musamman. Bacin ransa baya bukatar ya bude baki ya yi magana. Yanayinsa kadai ya isa tsorata jama'ar gidan.

Mal. Inuwa kansa a takure yake don idan fadan ya tashi babu mai tsira. Da ya dubi Baaba Mari sai ta bashi tausayi. Duk yadda aka yi zafin ciwo ne ya kaita ga yin wannan kasadar.

Gyaran murya Mal. Sa'idu ya yi gami da yin kwafa.

"Inuwa gani a gaban isasshiyar matarka. Ka umarceta da ta fadi abin da yasa ta aika NI SA'IDU in zo inda take."

"Mari..." Mal. Inuwa ya fada a hankali kamar yana rokonta da ta kawo karshen zaman nan.

Mal. Sa'idu ne ya katse shi

"Idan kuma takamarta haihuwar Abbati ne to ka tuna mata cewa ni da ake zagi, ni ne silar arzikinsa. Bayan duk tijarar da ta gama yi akan tura shi karatu gashi tafi kowa girbar samunsa" ya daga hannu yana kadawa domin kashedi "duk da haka babu wata mace da ta isa ta nuna min iko da danta domin iyayensu maza ma umarni na suke bi. Abbati da duk abin da ya samu nine sila..."

"To Alhamdulillahi..." Baaba Mari ta katse shi.

Kowa sai ya kalleta da tayi magana. Abbati kuwa ji yayi kamar kasa ta bude ya shige ciki kada a sake jin ko da sunansa balle labarinsa. Ya amince da ko ma me zata yi amma hakan ba zai hana shi jin tamkar tsirara yake a gabansu ba.

Kamar tana jin rurin da zuciyarsa take yi sai ta kira shi da hannu. Kafafunsa da yake ji kamar ba nasa ba haka suka kaishi gefenta ya sulale ya zauna. Dan murmushi tayi masa wanda ya sake nutsar da zuciyarsa sannan ta fuskanci Mal. Sa'idu.

"Fashin baki nake son yi muku akan wani abu da kuke yi mara tushe kafin na fadi illar da ya janyo min."

Mal. Sa'idu ya yi dariya

"Magana kike son yi akan zuwa almajiranci ko? Ke a dole ba za ki karbi addini a yadda ya zo miki ba?"

"A yadda yazo muku dai. Wannan fitinar da kuka farlanta bata cikin shika shikan musulunci. A takaice ma dai baku yiwa addinin komai ba sai bacin suna."

"Mari wai sai yaushe zaki daina janyowa kanki matsala da Yaya Sa'idu?" Cewar Mal Inuwa cikin fushi.

"Kila yau! Yau din da nake so kai dashi ku san cewa kun dade ana rubuta muku zunubi a matsayin wadanda suka jagoranci aikin alfashar da dansu yake yi saboda mummunar akida."

Falon sai ya yi tsit. Baka jin komai sai hawa da saukar numfashi. Kan Abbati a kasa yayinda Mal. Sa'idu yaji lokaci ya yi da zai saurari Mari. Kalamanta ba karamin zargi bane wanda yake jin dole sai da hujja za ta yi shi.

"Addinin Musulunci da kalmar Karatu ya fara zuwa garemu. Wannan yake nuni da cewa ko kadan jahilci bashi da muhalli a cikinsa. Allah ma Ya ce mu san Shi kafin mu bauta Masa. Duk musulmin kwarai bai dace ya yi gaba da neman ilimi ba."

Mal. Inuwa ya ce "to amma ai ke kina yi."

"A fahimtarku ba" ta nuna Abbati da yatsanta "ga danku nan. Kamar kowane bawa shi ma da tasa kaddarar yazo duniya amma kune sila. 'Ya'yanmu amana ne. Babu inda aka ce mu sakesu da kananun shekaru neman karatu ba tare da kyakkyawar kulawa ba. Kun turasu gidan malamai da sunan neman ilimi amma babu abinci. Yunwa ba kanwar uwar kowa bace. Idan ta taso dole a kawar da ita ko a ji jiki. Babba ma idan ka kai shi karatu babu abinci ka hada shi da jidali balle yaro. Wani sai ya wuni yana barar bai samu ba. Mutane su ci karo dasu wasu su zagesu wasu su tsine musu tare da mu iyayensu saboda sun dame su da bara. Ba dole su nemi abinci ta hanyar da ta fi musu sauki ba? Wasu su dace da halal, da yawa su fadawa haram. Hatta masu kwacewa na kasa dasu kana ganin laifinsu? Sun yi girma da bara kuma da gaske babu abincin. Sannan sun tafi babu tunanin ranakun da zasu tashi ba lafiya. Waye zai kula dasu idan suna ciwo? Wa zai basu magani? Ko kun manta ranar da na shigo garin nan da gawar Sani ba tare da na san ya rasu ba?" Sai ta fashe da kuka. A haka ta cigaba da cewa "Uwa uba baku ajiyesu a inda za a basu tarbiyya ba. Iyakarsu da malamansu a biya musu karatu su bayar da hadda. Idan sun yi laifi a zane su. To amma tarbiyyar fa? Sai abin da suka tsinta a titi? Da yawansu basu tashi sun ga jinkai da tausayi ba. Dan shekara shida yana yawo a unguwa neman abinci a lokacin muku-mukun sanyi ko damuna. Wani idan ka ganshi saboda rashin kulawa da zama cikin hazo sai dai ka dinga ja masa Innahu min Sulaimanu. Wallahi zato zaka yi aljani ne. A makarantar babu mai tausaya musu sai kalilan idan anyi sa'a. Mu da muka haifesu mun riga mun bata rawarmu da tsalle da muka rabu dasu da kuruciya. A karshe zukatansu su bushe. Idan anyi dace yaro ya zama nagari, idan ba a dace ba ya buwayi al'umma."

"Yanzu ki ka ce kowa da kaddararsa. Ni tun tasowata banda Sani da jikan Mai-adua ban taba jin labarin yaron da yaje karatu ya rasu ba. Gidan nan yara nawa muka tura kuma gasu nan duk sun dawo kamar ba ayi ba?"

Mal. Sa'idu kenan. Ya fadi haka ne ba don zuciyarsa bata soms zuwa inda Baaba Mari take son kai shi ba. Ba dai ya son ya karbi gyaran ne daga gareta.

"Ashe baka ji lokacin da nace kowane bawa da kaddararsa yake zuwa ba? Amma akwai sila. Kuma dole ne silar ya karbi sakamakon abin da ya zama tushen faruwarsa mai kyau ko akasinsa."

"Kai Abbati. Wace irin sana'a kake yi? Sata ko fashi?" Cewar Mal. Sa'idu muryarsa ta soma sauyawa daga dakiyar da yayi da farko.

Abbati bai iya amsawa ba. Ba zai iya cewa ga takamaimai abin da yake cikin zuciyarsa ba.

"Ba da kai nake ba!" Ya daka masa tsawar da zata firgita mai karamin tunani "nace wace irin sana'a kake yi?"

Baaba Mari ta daga masa hannu duk da kwarin jikinta yana ta raguwa.

Tsawar da ya yi ta bata rai itama ta koma yi masa magana tana daga murya.

"Baka da hurumin yiwa dana tsawa Yaya Sa'idu. Wannan damar ta saraya a wuyanka. Abin da ya rage tsakaninmu bai wuce ALLAH YA ISA ba. Ni da d'ana bamu yafe mak...."

"Mari!" Mal. Inuwa ya kirata da karfi.

"Kaima da ka kasa tsayawa 'ya'yanka ka tanadi amsar fitar da kai ranar lahira."

Dakin ya yi shiru na wani lokaci. Iyayen maza biyu mamakin kalamanta ya ishe su. Baaba Mari kuma ciwo ke neman dawowa sabo. Abbati ya matsa kusa da ita da sauri. Filo ya kara mata a bayanta domin ta zauna da kyau.

Mal. Sa'idu ya rasa me zai ce ya kare kansa sai "Yanzu ke da ace barinki aka yi da yaran nan za ki iya kula dasu ba tare da uba ba? Uwa ai ba ita kadai ce madogarar 'ya'yanta ba. Sannan karatun nan da kike ta suka ba shi ne yake taimaka musu

wurin iya rike kawunansu a duk inda suka sami kansu ba saboda sun horu?" maganar ma a hankali ta fito.

"Rike kai..." Baaba Mari ta furta da murmushin da tun dazu take yawan yi domin ragewa Abbati damuwa "Allah bai halicci kananan yara domin su rike kawunansu ba. Da haka ne kuwa to kowannemmu zai fado daga sama idan lokacin haihuwarsa ya yi. Yaya, cikin daukar ciki da haihuwa akwai mabanbatan wuya irin wadda bakunan mata kadai ke iya labartasu. Wannan azabar mai kama da mutuwa bata taba hana uwa mai cikakken hankali son 'ya'yanta ba. Ashe baka san.." ta dubi idanun Mal. Sa'idu babu tsoro ko shayi "soyayyar uwa da 'ya'ya aya ce cikin ayoyin Ubangijinmu ba? Cikinsu ya hanamu lafiya, haihuwarsu ta gadar mana da ciwo da sauyin halitta, tarbiyarsu ta janyo mana zagi da aibatawa komai kokarinmu amma duk da haka bamu fasa son kayanmu ba. Me yasa karatu yazo mana da cewa Allah Yana kunyar wadanda bai bawa haihuwa ba? Kuma Ya umarcemu da kyautatawa marayu domin samun lada. Lallai Ubangijin da Ya samar da wannan ladan ba zai so a tauyewa uwa zamewa 'ya'yanta uwa ba. Munfi kowa son cigaban 'ya'yanmu. Idan suka zama manyan malamai sai nafi kowa cikinku farinciki. Amma zama malamin ko wani kwararre a fannin da Allah Ya dorasu yana tafe da kulawarmu. 'Ya'yanmu suna bukatarmu kafin su shiga duniya su iya rike kawunansu. Baka bani damar kulawa dasu a lokacin da suka fi bukata ta ba. Yaya Sa'idu jawabina da yawa. Gashi na gaji bana jindadi. Kuje kai da dan uwanka na barku da ...."

Caraf Mal. Inuwa ya hanata karasa magana "haba Mari karki karasa mana. Ni duk zancen ma baki fada mana me yake yi ba."

Ta kalli fuskar Abbati sai kawai ta tashi ta barsu a wurin ta shige dakinta. Shi da ta bari taji nauyin karasa labarin da kansa ya zayyane musu komai. Mahaifinsa ya dinga kukan da ko ranar da iyayensa suka bar duniya bai yi irinsa ba. Daga cikin dakin Baaba Mari tana jinsa ita ma kukan take yi. Hawaye wani yana min wani babu kakkautawa. Mal Sa'idu ne ma bata ji koda tarinsa ba sai daga baya taji alamun faduwa da kuma kiransa da karfi da Abbati da Mal. Inuwa suka yi.

***

Honourable ya kai ya kawo a dakin asibiti ya kasa zaune ya kasa tsaye har likitan da ya sake shiga ya fito.

"Baku yi min bayani ba sai shiga kuke kuna fita. Me ya sameta?"

"Alhaji muje ofis muyi magana."

'Yan matan aka bari a kanta yabi bayan likitan. Ana cewa ya zauna bai ji ba don hankalinsa baya tare dashi.

"Yallabai matarka ciki gareta na wata uku."

Cikin wani gigitaccen farinciki Honourable ya ce

"Allah Hakimu, Hasiya ke da ciki? Alhamdulillah. Allah Ka karawa Annabi SAW daraja."

"Amin" cewar Likitan "sai dai akwai 'yar matsala."

Nan da nan Honourable ya zauna hannuwansa akan teburin likitan. Murna tana neman komawa ciki.

"Zubewa ya yi?"

Gamsashen bayani likitan ya yi masa akan halin da take ciki. Mahaifarta bata da kwari ne tana barazanar zubar da cikin. Idan ba a daure mahaifar ba zai iya zubewa. Sannan tana bukatar bed rest na wani lokaci. Kuma ta daina komai har ya yi kwari a gani.

Honourable ya ce musu ya amince ayi duk abin da ya dace. Yana fitowa masallacin asibitin ya nufa ya yi sallah raka'a biyu domin godiya ga Allah. Hasiya ke rike da gidansa da sanaarta. Da ace wata biyu da suka wuce ta sami cikin nan mai matsala bai san yadda zai yi ba. Yana neman kudi sosai amma kamar kofofin samun sun

toshe masa. Yanzu gashi tayi cikin a lokacin da yake da abin kula da ita. Minista Abdulkarim ya bashi kudi a hannu banda wanda ya zuba a account din asibitin da aka kai Abbas.

"Allah Ka kara mana hakuri da kaddara kowace iri."

Daga nan bai koma cikin asibitin ba. Adaidaita sahu ya tare ya ce a kai shi Dala. Sai dai akira shi duk abin da aka ga dama amma da bakinsa zai yiwa Innayo wannan albishir. Ita ce mutum ta farko da ya san Hasiya za ta so gani idan ta tashi. Kuma bai ga wanda zai yi masa tattali da jinyarta kamar mahaifiyarta ba.

***

Kankanin daki ne kamar akurkin kaji, ba taga ko daya sai kofar shigowa. Babu komai a cikinsa sai tarkacen gyaran mota irinsu spanner, sukun direba da matattun tayoyi. Iskar dakin kuwa warin fetur take da bak'in mai. Daga bayan inda aka jere wasu tayoyi suka yi tsini muryoyi ke tashi a hankali. Daya tana magiya dayar kuma tana bayar da hadin kai. Cikin sassarfa Suhaib ya shigo dakin ya isa bayan tayoyin ya leka. Mummunan gamun da ya yi bai sa shi ja da baya ba sai ma cakumo wuyan rigar namijin da ya yi.

Dani ne sanye da kayan makanikai ya yi duqun-duqun. Suturarsa da fatar jikinsa duka suna neman agajin wanka da wanki. A tare dashi kuwa ba kowa bace illa Ayaah. Fuskarta babu kwalliya amma tayi kyau. Hijabin jikinta kuwa dama shi Dani ya kamo saura kadan ya gama cire mata shi. Ya gama hillatarta da alkawarin aure idan ta yarda ta bashi hadin kai kamar yadda Suhaib yaji.

Kunnenta Suhaib ya murde iya karfinsa yana yi mata fada cikin bacin rai.

"Ban yi miki magana ba dazu?"

Ayaah ta turo baki "wai kai ina ruwanka? Kuma ba ya ce zai aureni idan Mummy ta dawo."

"Mooooommiiii"

Yaji an ce daga gefensa. Kunnen Ayaah ya saki ya juya. Yarinyar nan mai kwalliyar aljanu cousin din Abbati ya gani. Bata fasa kiran Mooomiii ba. Lilu a kusa da ita ya dinga dariya yana kiranta Iya duba duba.

*

A zabure Suhaib ya tashi daga bacci yana salati. Kansa ya yi wani irin nauyi kamar an dora masa dutse. Baccin dauke shi ya yi bai sani ba. Fuskar Ayaah ce ta zauna masa daram a kansa lokacin da ya gansu Dani zai cire mata hijabi. Murmushi take yi kamar abin da suke niyar yi daidai ne.

"You have the guts to smile (har kina da damar yin murmushi)" ya furta tare da yin kwafa ya yi wurgi da filo.

Sake kwanciya ya yi niyar yi wani tunanin ya fado masa. What if yarinyar nan ta bi mutumin yaje ya bata mata rayuwa? Daga hirarsu ta dazu ya fahimci kamar yanzu ne yake neman amincewarta.

"Wannan kanta baya ja da gani"

Tsaki ya yi ya tashi a gurguje ya zura takalmi ya fita zuwa cikin gidan. Yawancin 'yan biki sun watse tunda yau aka tafi da amarya Kaduna. Yana shiga suka yi kicibus da Mardiyya.

"Bani wayarki."

"Wallahi Ya Suhaib babu komai a ciki mara kyau."

Murmushi ya mata duk hankalinsa yana kan wayar.

"Karki damu Auta na yarda dake."

Wayar ta bashi ya laluba contact dinta. Da yazo kan numbar Ayaah da sunanta da ya zauna masa daram a ka ya ganeta. Yana wurin suka karbi nambar juna. Kallo biyu ya yiwa numbar ya haddaceta. Mardiyya tana jiran taga me zai yi sai gani tayi ya miko mata wayar.

Dakin da suka yi masauki ya koma ya samu wuri ya zauna a gefen gado. Yana danna kira ta shiga. Sai yaji wani bakon yanayi ja sarkewar harshe ya ziyarce shi. Me zai ce mata matsayin dalilin kiran?

Kunyarku nake ji wallah. Haka dai zaku dinga hakuri dani saboda Son So dake tsakaninmu. Allah Ya barmu tare har aljanna. Amin

BABI NA GOMA SHAƊAYA.

***

"Ranka ya dade kana da bako."

DPO Yahaya ya dago kai cikin bacin rai ya kalli Sergent din da ya yi maganar a tsorace.

"Me na ce muku dazu?"

"Duk wanda yazo ace ka dan fita" ya ce sannan ya gyara tsayuwa rabin jikinsa a bayan kofa "Yallabai mun nemi ya sanar damu matsalar da ta kawo shi ya kafe lallai kai yake son gani."

Girgiza kai ya yi ya fasa yin fadan da da ya yi niyya. Yau din kamar hadin baki tun sassafe ake abu daya. Daga wannan case din sai wancan. Wani abin ma sai kayi tunanin al'ummar tamu ta rasa alkibla. Cuta, ha'inci, mugunta, magudi da uwa uba zina. Kansa ya dauki caji yana ta ciwo. Shi yasa ya bayar da umarnin ace baya nan domin ya huta. Tunda an riga an fada masa bashi da zabin da ya wuce sauraron mutumin.

Sallamar kadai yaji ya gane surukinsa, babban wa ga matarsa. Ba shiri ya mike domin nuna girmamawa a gareshi. Mutumin akwai mutumci da halin girma.

Ilai kuwa da shigowarsa kalmar hakuri ya fara amfani da ita "ayi min hakuri Yahaya. Na san aikinku babu hutu."

"Haba Yaya Salihi ai sai kasa naji babu dadi" ya amsa masa a yayinda suke musabaha.

Bayan 'yan gaishe gaishe Salihi ya zayyane masa duk abin da ya sani game da Habibu na ma'aikatar lafiya. DPO Yahaya ya dinga gyada kai har ya gama.

"Akwai wani mugun dan ta kife mai cin kudaden mutane a cikin ministry of health. Ka san ai jurisdiction dinmu ne .."

"Dalilin kenan da na kawo maka case din."

DPO Yahaya ya ce ya kwantar da hankalinsa zai bi kanun komai

"Sunan ne naji ya zo daya ina tsammanin wanda nake zargi ne. Sau biyu yana zuwa nan amma sai kaji daga sama an ce a sake shi."

Salihi ya dan cije lebe "kana nufin idan shi ne sakinsa zaka yi?"

Da sauri DPO Yahaya ya gyara zancensa domin kuwa ya jima yana son Habibu ya shiga gonar da ta kusance shi. Irin gonar da idan Habibu ya sallami na sama dashi da kudi shi kuma zai nuna bacin ransa akan rashin goyon baya daga abokan aikinsa.

"Duk yadda akayi dubunsa ce zata cika. Yaya Salihi ka dawo gobe kawai in sha Allahu iwar haka yana cell."

Shawara suka zauna yi akan yadda zasu bullo masa a saka shi fiddo kudaden Uwani. DPO Yahaya ya dan muskutu gaban kujerarsa cikin muryar da babu cin fuska a tattare da ita ya ce,

"Amma don Allah garin yaya Maman Mubashir tayi wannan sakacin? A gaskiya ko babu addini a al'adance ma banga dalilin da zaisa mace ta riki wani namiji amini idan ba shakikinta ko miji ba. Duk da na san cewa muma mazan bamu cika kyautawa ba. Idan harkar kudi ta hadamu da mace sai muyi taking advantage din kyautatawarta mu danne mata kudi. To amma duk da haka wannan ba hujja bace da za ta dinga budewa wani shirgegen kato sirrin da mijinta bai sani ba."

Salihi sai ya yi murmushi. Kafin ya tashi ya ce masa zai dauki kwakkwaran mataki akanta. Sai dai yafi kowa sanin Uwaninsa. Duka abubuwan da tayi babu guda da zai yi mata uzuri akan shi. Bata kyauta ba iya rashin kyautawa. Duk da haka gidan da ta taso ya taka muhimmiyar rawa wurin shaping din rayuwarta. Bakin halinta na rowa ba komai bane illa nason da halin mahaifinta ya yi a jikinta da kuma tsoron kada a maimaita wata Innayo din da ita.

Domin ya sami cikakkiyar yarda tsakaninsa da ita da sauyin hali sai ya nuna mata cewa ba kowane namiji bane Alh. Rabi'u. Dukiyar matarsa ba tasa bace kuma nauyin dawainiyarta da ta yaransu a wuyansa yake shi namiji. A karshe yana son ta

bambance tsakanin kyautatawar da mata kan iya yiwa mazajensu domin lada da rainin wayon maza marasa tsoron Allah. Irin mazan dake sarayar da ayyukan da suka wajaba a garesu su barwa mace daga taimako. Sune suke tsorata mata da yawa su kasa taimakon mazajensu koda suna da halin yin hakan.

***

Kwalla fal idanun Innayo a lokacin da Honourable Habu yayi mata kyakkyawan albishir.

"Hasiyan ce dai da ciki ko?"

Kunyar da ya manta da ita a lokacin da ya iso gidan har ya fada mata da bakinsa ce ta kama shi. Ya dan dukar da kai yana murmushi. Ita ma murmushin ta mayar masa wanda ya koma dariyar farinciki.

"Fadi komai kan ka tsaye ai auta ce babu mai cewa mun yi rashin kunya."

Honourable dai sai dariya mai hade da kunya. Asibitin da Hasiyan take kwance ta tambaye shi sai ga Asabe a kansu kamar daga sama ta fado. Daga dakinta taji kamar suna ambaton Mariya domin 'ya' kawai taji da kuma asibiti. Bayan abin da ta gani dazu a firgice ta fito.

"Me ya sami Mariyan? Ina Munzalin?" Ta ce yayinda take waigawa hagu da dama tana dube dube.

Innayo tayi mamakin abin da ya tayar mata da hankali haka. Ba abin ta tambaya ba ta san tsaf za ta gwasaleta.

"Hasiya ce a asibiti."

"Au tooo...to Allah Ya sauwake" ta ce a sanyaye tana juyawa dakinta.

Innayo bata ma bi ta kanta ba ta shirya ita da su Salima zasu tafi asibitin. Dakinta ta koma inda ta baro Uwani tana ta kai gwauro da mari ita kadai.

"Na san cewa a karkashin wani kike nima ba zan so ki dinga yawo da aurenki ba. Amma ai ko sakon gaisuwa ga kanwarki kya bayar. Zumuncin da kike wulakantawa Uwani shi ne gatanki. Ba don kinsa kafa kin tattaka shi ba da bamu ga rana irin ta yau ba akan aurenki."

Kunyar rashin tunaninta taji da kanta.

"Kiyi hakuri Innayo. Ku gaisheta kafin na zo."

Murmushin takaici Innayo din tayi ta fita tana cewa "da girmanki baki san gatse ba. A yadda Hasiya ta dade tana neman haihuwa na zata kiran mijinki zaki yi ki nemi izinin zuwa dubota. Komai girman farincikin da zai gilma a gidan nan indai ba ke ya raba ba wato ba za kiyi murna ba..."

Har tayi waje Uwani tana jiyota. Abin ma sai ya sata murmushin da bata yi niyya ba. Autar Innayo da ciki kuma bata je dubiya ba. Ta san ba makawa yau sai ta kwana tana jin mitar mahaifiyarta. Sai dai kuma abin da yake damunta yafi karfin samun cikin Hasiya a yanzu dai. Hakuri ta sake bayarwa da sakon gaisuwar ta koma ciki. Suna fita ta fito ita ma ta shiga dakin Asabe. Daga bakin kofa ta tsaya cikin shiri don har mayafi ta yafa. Abin da ya kaita ta fada ba tare da kwana kwana ba.

"Gidan Munzali za ki kwatanta min ko ki rakani."

Da tsananin mamaki Asabe tayi mata duba irin na wanda ake tsammanin ya yi makuwa "gidan Munzali kuma?"

Uwani sai ta dauko waya ta mika hannu gareta don bata ga dalilin mamakin da Asabe ta nuna ba. Ta rasa gane me yasa kowa yake ganin kamar bata son zumunci. Waye cikinsu yake zumuncin da ita?

"Bani nambarsa idan kwatancen ba zai samo ba"

Asabe sai ta sabi mayafi. Yau din gani take kamar duniya tana hajijiya da ita. Ba kuma don abin da ta gani a tattare da Qibdiyya ba kadai. Harda maganganun Munzali. Tunaninta ya kasa hasko mata inda zantukansa suka dosa.

Da yake mai hali ba ya fasawa suna samun adaidaita sahu Asabe sai cewa tayi "amma dai ke za ki biya min ko? Tunda dai ke zan raka."

Uwani ta hade girar sama "Munzalin ba danki bane? To nima ba kudi gareni ba. In ba za ki biya ba ki kwatanta min."

Asabe tayi azamar gyara zama tana kallon idanun Uwani "Idan baki nuna min halinki ba ai bana ce ke din tsatson Alh. Rabi'u bace."

Direban da yaji irin maganganunsu sai ya tsaya cak a tsakar titi.

"Hajiyoyi ku sauka don Allah kafin mu isa mu soma rigima daku akan kudi."

"Muje zan biya" cewar Uwani tana hararar Asabe da gefen ido.

"Wai ma me zaki je yi a gidan Munzali?"

"Abin da yasa kika biyoni maimakon yi min kwatance ne zai kaini."

Asabe ta hangame baki "kema ya fada miki?"

"Labe nayi muku duk da dai hargaginki ne ya sani zuwa ba wai nayi niyya bane." Uwani ta bata amsa kai tsaye.

"Nice nake hargagin? Lallai Uwani baki da mutumci. Koda yake ki ka yiwa gyatumarki ma wace ni?" Cewar Asabe tana kara kulewa.

Uwani bata kulata ba. Hankalinta ya yi gaba cikin tunanin nawa zata caji Munzali idan ta duba 'yarsa. Ko babu komai yadda ake labarin arzikinsa da son da yakewa 'yar dole ya mata hasafi. Kila ma ya hada da toshiyar baki.

***

Banda 'ya'yan cikinta da jikoki babu wanda ya yi saura a bangaren Baaba Mari. Jama'ar gidan manya suna asibitin da Mal. Inuwa ya jagoranci kai Mal. Sa'adu. Sauran kuwa musamman mata suna bangarensu a tsorace. Labari yazo musu cewa Baaba Mari da kanta ta aika kiran Mal Sa'adu. Gashi daga shigarsa bai fito da kafarsa ba sai gadon asibiti.

A asibitin kuwa tunda Mal. Sa'adu ya dan farfado ya soma cewa a kai shi gida yana son ganin Baaba Mari.

Wannan abu ya harzuka Deluwa musamman taga ko sannun da take ta ce masa bai amsa ba.

"Jama'a ku kawo min dauki. Mari ta fito da maitarta fili ta lashe kurwar Malam."

'Yan koranta da na Mal. Sa'adu suka dinga jinjina kai alamun amincewa. Shi kuwa wanda ake yi dominsa ransa sai ya baci. Abu ne da bai taba zato zai ji a ransa ba sai gashi a yau duk kalmar batanci da za a fada akan matar kaninsa sai yaji tamkar an loda masa kaya ne a kansa. Tuntuni ya fahimci illolin da take son nuna masa game da bara. Sai ya zabi ya take gaskiya saboda bata kai matsayin da zai dauki shawararta ba. Kuma sauran yaransu masu zuwa ai kowa ya dawo lafiya. Gabansa

ya fadi da wani tunanin ya mamaye kwanyarsa. Shi ganau ne ba jiyau ba akan canjin da aka samu cikin 'ya'yansu da na makota.

Akwai uban da yake zuwa wurinsa yana yiwa dansa rubutu domin neman a raba shi da dauke dauke. Ya gallabi gidansu da makota babu damar mutum ya yi ajiya.

Wani kuma dan ya addabesu da haurawa matan aure cikin dare yana musu fyade.

Ga kwararren malamin tsibbu wanda matan aure suke tarawa arzikinsu akan mallakar miji da korar kishiya.

Suna da dan kwaya wanda har a kwata ana tsinto shi.

Akwai wanda ya koyo mugunta da tsantsar cin zali. Sau biyu yana zubarwa matarsa ciki da duka sannan ya karya mata cinya.

Wani ma dan damfara ya zama. Yana can Dubai ana damawa dashi

Wasu sun bata har yau babu su babu labarinsu.

A karshe akwai wadanda suka rasu sai dai a kawo gawa. Wani ma sai dai labari ya riski iyayensa bayan an binne shi.

Wadannan halaye hatta a makaratun boko na kwana ba baki bane saboda wahalar dake cikin tarbiyya. A can safe, rana, yamma da dare duka akwai ido akan yaran. Amma basu tsira ba. Idanun masu kular sun yiwa daliban kadan. Dalibai sama da arba'in a karkashin kulawar mutum daya na wani lokaci. Dole a sami masu kangarewa ba tare da sani ba. To ina ga makarantar allo wadda idon bai wuce na malami ba? Yaran kuma suna fita a duk lokutan cin abinci neman na kansu?

Duk da haka akwai wadanda suka yi dacen samun alkhairi daga zuwa karatu. 'DACE suka yi' Mal. Sa'adu ya tunatar da kansa. Irin dacen da wadanda suka fadawa halaka basu yi ba. Karatu ba zai taba tafiya babu tarbiyya ba. Tarbiyya kuwa tana samun kwakkwaran tubali ne a inda ake bayar da kulawa. Ita kuwa kulawa sai an jure an daure domin bayar da tarbiyar akwai wuya. Zamanin baya ido kadai d'a zai hada da mahaifiyarsa ya fahimci sakon dake cikinsa kuma ya yi aiki dashi. Yanzu kuwa sai ka zare idon shi ma ya bude maka nasa kirikiri yana dariya. Ka dake shi cikin sakan talatin ya manta ya sake maimaita laifin. Akwai wuya...ke uwa kina yi ma ya aka kare balle an kai dan nesa babu mai kwabarsa.

Mari ta ce ba za ta yafe masa ba.

Abbati ya zama dan luwadi...Wa Iyazu Billah.

Da me zai ji? Tsatson gidansu da yake alfahari da kyawunsa shi ne aka sami reshe guda ya lalace. Bayan sadaukar da rayuwarsa wurin ganin gidansu ya cigaba da amsa sunan gidan Malamai yanzu wannan masifa ta bullo. Zuciyarsa bata son karba amma kwakwalwarsa ta san gaskiya. Idan ma yaki neman gyara shi ne babban mai kwana ciki. Ba don ya so ba ya yiwa Deluwa magana akan kalamanta.

"Ba zan lamunci wannan shirmen ba Deluwa. Idan ba za ki iya kama bakinki daga barin aibata Mari ba ki wuce gida.

Kirji ta dafe ba shiri kamar tana gudun faduwarsa. Ta dube shi idanu a waje.

"Malam Mari ka ke karewa? Mari dai wadda muke raba dare muna kwashewa albarka ni da kai? Kaiiii..." Ta fada da karfi tana girgiza kai "Yasin da wata a kasa. Mari ta karawa bokanta kudi aiki ya ci."

Mal. Sa'adu da ya san shiru sosai yake bukata domin samun nutsuwar tunani da neman mafita tamke fuska ya yi. Bai bata damar roko ba ya ce lallai ta koma gida baya son zamanta a asibitin. Bata yi masa musu ba ta tafi gidan. Amma tana zuwa dakin Baaba Mari ta nufa tana danna ashariya.

***

Yamma tayi, gari ya soma duhun da dakuna suke bukatar haske. Lokacin da Asabe da Uwani suka yi sallama a falon gidan Munzali basa ganin kofofi da matattalar dake wurin. Ko ina dund'um an saki labulaye. Kwada sallama suka dinga yi da karfi tunda Maigadi ya tabbatar musu cewa ya shigo sannan ga motar da ya fita da ita a wurin parking. Uwani ta so shagala da kallon tsala tsalan motocin dake zube a wurin. Ga gidajen daga waje ma sun hadu. Tsarin fuskantar juna da suke yi dana Abbati ya sake burgeta.

Shigowar Kande ce ta kawo karshen sallamar tasu. Da yake ta san Asabe sai ta gaishesu da girmamawa.

"Alhamdulillahi kun zo Hajiya. Yanzu nake fakon idan aka yi Magriba Alh. Munzali bai fito ba zan taho gidan naki."

"Me ya faru kuma?" Cewar Asabe da saurinta.

Kande ta labarta musu yanayin da Munzali ya shigo gidan yana harhada hanya. Da ganinsa baya cikin nutsuwa ko kadan. Qibdiyya tana kafadarsa tayi bacci. Da ta nemi karbarta har wata tsawa ya daka mata. Dole taja baya ta zuba masa ido. Hawaye ne tabbas taga saukowarsu daga idanunsa. Sai dai kafin ta gama janyo tunanin da ya dace tayi, ya haye sama sai karar buga kofa taji.

"Ki hau ki kira min shi da Qibdiyyan" inji Uwani ga Asabe tana ajiye dan akwatin tafi da gidanka na kayan asibiti.

Hantar cikinta sai da ta dan kada don bata manta maganganunsa na dazu ba.

"Ban gane in hau ba? Don rashin tausayi tsofai-tsofai dani zaki sani hawan bene."

Uwani ta tabe baki. Abin kirki tazo yi amma halinta kam ya zanu akan dutse.

"Gidan danki ne fa kuma ni ban taba zuwa ba. Ke ya dace ki hau."

"Sai an magana ku dinga cewa ubanku daya. Da su Maimuna ne ai ba za ki ce yau kika fara..."

Sauran maganar makalewa tayi don tuni Uwani ta kusa kure benen.

Kankanin lokaci ya sadata da wani katafaren falo wanda yake cike da ababen more rayuwa. Kofofin dake cikinsa ta dinga kallo tana neman kofar dakinsa. Cikin sa a sai ta hango takalmin Qibdiyya a bakin kofar daya daga ciki. Duk yadda aka yi nan suke. Bata ji ko dar ba don dakakkiyar zuciya gareta ta karasa kofar dakin tana kwankwasawa gami da yin sallama.

Munzali yana zaune a gaban gadonsa inda ya shimfide Qibdiyya ya hada kai da gwiwa yaji sallamarta. Yayi matukar mamaki duk da ya san taji komai bayan haduwarsu ta dazu. Bai motsa daga inda yake ba kawai ya dago kai.

"Shigo."

BABI NA GOMA SHA BIYU.

Wata sallamar tayi ta kutsa kai cikin dakin da sanyinsa ya busa har kasusuwanta. A take taji kwarin gwiwarta ya dadu. Sai da ta shiga daga inda yake zaune ya danna remote kwayayen fitilu uku suka kama. Haske ya gauraye dakin da zaka rantse ba namiji ke gyara kayansa ba. Komai tsaf ga kamshi ga kyau.

"Ke da waye?" Ya tambayeta yayinda ta kai ido inda Qibdiyya take bacci.

"Asabe. Tana kasa."

Shiru suka yi na dan lokaci suna yiwa juna kallon kallo. Ita tana ganin wautarta na rashin kusantar kanin nata tun da dewa. Shi kuwa abubuwa da dama ne suka cunkushe kirjinsa. Zazzabi yake ji da matsanancin ciwon kai.

"Na san abin da ya kawoki Uwani zan kuma baki domin ki taimaki Qibdiyya. Sai dai abu daya ne ba zan miki ba..."

Idanunsu suka sarke da juna. Magana yake yi mata ba da wasa ba. Bata jin ma banda gaisuwa sun taba yin wata doguwar magana dashi banda yanzu. Idanun nasa sai suka zame mata tamkar masu wadanda ke huda sassan jikinta. Gabadaya sai ta tsargu ta kasa sakewa. Don ma tana da baki ne ta ce,

"Ban gane ka san me ya kawoni ba? Daga zuwa taimako sai ka soma fada min magana saboda raini."

Dan murmushi ya yi cikin son nuna burgarta bata je masa ko ina ba. Ya dora maganarsa ba tare da ya damu da bata amsar maganarta ba.

"Kamar yadda na ce zan biya ki dubata amma ko kwandala ba zan baki ba domin ki bar maganar nan a matsayin sirri."

"Me yasa?" Ta fara cewa tana zaro ido sai kuma tayi saurin gyara zancen "yaushe na ce maka idan baka biya ba zan tona maka asiri?"

Mikewa ya yi kansa na cigaba da sarawa ya matso da Qibdiyya bakin gadon yana cewa,

"Baki fi kowa so da damuwa dani ba Uwani amma sai gaki ke kadai a gidana a wannan lokacin. Ina Innayo ina su Zara? Me yasa baki fada musu kun fito tare ba?"

Hade rai tayi na borin kunya ta saka safar hannu.

"Saboda irin wannan abin ba abu bane da ake so ayi ta yamadidi dashi ba."

Wani dan murmushi ya yi mai sauti

"Qibdiyya dai 'yarki ce, tonon asirinta naki ne. Kuma magana dole zata fito idan aka tsinci tsinannen da ya yi mata wannan abin da rai ko babu."

Fita ya yi yaja kofar dakin ya barta da tunanin kalamansa. Taji zafin maganganun duk da gaskiya ce ziryan bai mata sharri ba.

Qibdiyyan ta tasa a hankali don kada yarinyar ta firgita idan taji ana tabata cikin bacci.

Cikin yan uwan mahaifinta Uwani tana sahun gaba na wadanda bata saba dasu ba kuma suke bata tsoro. A firgice take kallonta amma Uwani bata fahimta ba saboda sabgar yara ba tata bace.

A hankali dai take yi mata magana domin ta kwantar da hankalinta.

"Yi kwanciyarki dubaki zanyi."

Tana kai hannu zata cire mata pant, Qibdiyya ta runtse ido yadda ta yiwa Asabe.

"Kema hannu zaki saka min a nan? Idan an saka wannan safar ba zai min zafi ba?"

Hannuwan Uwani sai suka fara rawa ta kasa cire pant din. Wannan wadanne irin maganganu ne suke fita daga bakin karamar yarinya irin wannan?

Tana can tana tunani caraf idanun Qibdiyya akan alluran dake cikin first aid box din. Jikinta ya kama rawa ta soma kuka.

Munzali yana jin kukan ya bude kofar. Sai dai yaci karo da abinda yasa shi jin ina ma bai zo duniya ba. Qibdiyya ce take cewa,

"Don Allah kada kiyi min allura wallahi ba zan fadawa Daddy ba. Abin nan ne bana so ki tura min da karfi yana min ciwo kinji" kallon da taga tana yi mata ta kasa cewa uffan ne ya bata damar tashi zaune don ko kadan bata so ayi mata "Kwanta ni inyi miki. Nima na iya."

Tsigar jikinsa har tashi take yaji kansa kamar k'wari suna yawo. Da dan allinsa ya nunata yana daga murya ba tare da ya sani ba.

"Me kika iya? Me zaki yi? Qibidiyya waye ya koya miki wannan abin?"

Baiwar Allah a gigice ta tashi idanunta suna zubar da hawaye. Idan da abin da yafi komai daga mata hankali bai wuce shi ko Abbati su sani ba. Uncle Daddy alkawarin kisa ya yi musu. Zai yanka mata su irin yadda aka yi a bidiyon da ya nuna mata.

A zafafe Munzali ya sake cewa "nace waye ya koya miki? Da wa kuke yi? Innalillahi wa inna ilaihi raji'un." Ya rike kansa "Uwani kin ji abin da tace kuwa?"

Qibdiyya dai ba abin da take sai kuka. Haka ma Munzali wanda ya dubkule hannu yana dukan bango. Yatsunsa har kara suke amma bai daina ba. Uwani kanta ta kidime. Sai a lokacin taji wani girma ya sauko mata. Idan bata tari abin da yake faruwa ba da uban da 'yarsa duka zasu shiga wani hali. Hannunta ta kama ta zaunar da ita a kan cinyarta.

"Daina kuka Qibdiyya ki fada min waye yake saka miki hannu a cikin pant."

Cikin faduwar gaba Qibdiyya ta kalli Daddy dinta ta girgiza kai.

Wata irin tsawa ya yi mata wadda har Uwanin sai da taji cikinta ya kada. Kaiwa da kawowa kawai yake a dakin jikinsa na tsuma. So yake ya samu wani abu ya matse ko ya yi ta duka har sai kuzarinsa ya kare.

A lokacin azal ta fada kan wanda bai ji ba bai gani ba. Hakika Allah ba azzalumin Sarki bane. Sai dai kuma Yana nuna ishara ko aya akan wasu domin ya zama gargadi ga majibintansu.

"Uncle Lilu"

Amon muryarta ya fito lokaci guda da kiran sallan da Ladanin masallacin kusa dasu ya soma na Magariba.

Yawun bakinsa kafewa ya yi ya kasa hada harufan da zai kira sunan Lilu. Ga wani abu mai daci yana bin busasshen wuyansa yana saukar masa a ciki. Zuciyarsa kuwa tamkar farantin tangaran haka yaji tayi rugu rugu.

A karamar kwakwalwar Mariyatul Qibdiyya kuwa, tayi tunanin kama sunan Lilu tsira ne gareta da iyayenta. Shi yana da kirki ba zai yanka su ba. Uncle Daddy da yace yana ganinta duk inda take yanzu ba zai mata komai ba.

(Ba da niyya Munzali ya taka muhimmiyar rawa wurin janyowa Lilu laifin da ba nasa ba. Yarinya ce wadda aka tsorata tun lokacin da ake batawa rayuwa. Yanzu kuma an sake firgita ta da fada da tsawa. Wannan kadai ya isheta dalilin yin shiru ko ta kira sunan wani daban. Da wane mataki aka fi saurin samun bayyanar gaskiya a irin wannan yanayin da ba a fata? Rarrashi da laluma musamman ga kananun yara. Idan sun kama suna iyaye a bincika a sake bincikawa. Yara ma suna karya! Wani

domin kwatar kai, wani kuma domin maslahar da yake ganin canja gaskiyar zai kawo.)

***

Washegari bakwai a hanya ta yiwa iyalan Alh. Tahir. Ana sallame sallar Asuba suka shirya. Lilu da Mardiyya ma ko wanka basu yi ba saboda iyayen sun matsu su tafi. Awa biyu ta kaisu gida. Shi Alh. Tahir kai tsaye office ya wuce. Yana shiga ya shiga dube dube yana daga abubuwa. Wannan wayar da yake kiran 'yan matansa yake nema ido rufe. Fatansa kada ta fada hannun da asirinsa zai tono. Da ya gaji da neman sai ya kira direbansa da masinja.

Shi direban umarnin kai mota wanki ya bashi. Ya ce a cire duka kujerun a duba masa wayar. Masinja kuma ya kira masu shara a fitar da komai na cikin office din a duba masa. Amma fa koda ya bayar da wannan aikin yana da tabbaci dari bisa dari bai barta a office ba. Motar yafi zargi. Kawai dai ya yi amfani da karin maganar bahaushe da ake cewa idan kana neman rakuminka ka duba har cikin allura.

Dakin da suke meeting ya shiga ya zauna yana jin zuciyarsa tana wani irin bugu. Ya rasa me yake damunsa tun wayewar garin yau. Ransa a jagule yake ga fargabar da bai san dalilinta ba. Ya san dai yana matukar tsoron wayar nan ta fada hannun wani a cikin gidansa. Mutumcinsa ne zai zube wanwar. Matansa sun san komai amma ba zai so su gani kamar yadda suka ga sakon Yumna ba. Amma 'ya'yansa fa? Wanda Farha ta gani ya ishe shi jin kunya har ya mutu. Tunanin Yumna da ya yi sai ya sake kad'a shi wata duniyar. Rabonsa da ita tun ranar da wayarsa ta bata. Kamar sauran 'yan matansa ita ba bata da numbar kowane layi sai na wannan wayar. Yadda take babu hankalin nan yana tsoron kar ta zo gidan ta ce tana nemansa.

Wuni ya yi yana ta tufka da warwara har aka gama ayyukan da ya saka ba a ga wayar ba. Bai iya tabuka komai ba ya tafi gida.

*

Kurar da bata taka kara ta karya ba a dakinsa ya fara karkadewa kafin ya shiga wanka. Idan bai yi da kansa ba ya san Mami ba za ta bar Sauda ko Mardiyya suyi masa ba. Musamman da yake daga tafiya suka dawo za ta ce suma sun gaji.

Yana gama shiryawa ya dare gado zai yi ramuwar bacci sai ya bige da chatting. Hirar kwallon kafa ce suka kusa yin awa guda suna fafata musu shi da abokansa a group dinsu. Daga kwance sai da ya koma ya zauna. Can aka turo hoton jerin wasannin da suke magana a kai da sakamakon. Lilu bai san lokacin da ya yi ihun murna ba. Club dinsu ne suka yi nasara kamar yadda suka fada. Sun cinye musun. Yana cikin murnarsa Suhaib ya shigo sanye da wandon bacci da singileti. Da gani shi ma wanka ya sake yi zai kwanta.

"Ka fa hanani bacci da ihu."

Lilu ya daga hannuwa irin na masu saranda yana murmushi.

"Takawarka lafiya dan rigimar Mami yanzu nima zan kwanta."

Suhaib bashi da zabin da ya wuce yin murmushi.

"Kai kuma Dan-ta-kife din Mami ko?"

"Kada ka dora min sunan da ba halina ba."

Suhaib ya gyara tsayuwa gami da yin kwafa "ni rigimar halina ce kenan?"

"Banda rigima tun dazu me ya hanaka bacci sai yanzu daga yin ihuna za ka fito?"

Tsuke baki Suhaib ya yi ya juya yana murmushi. Me kuwa ya hana shi bacci sama da tunanin yarinyar da ya gani tare da makaniken nan? Haushinta ya kamata yaji a

ganinsa. Sai aka yi rashin sa a ta cike tunaninsa da wasu abubuwa da bai saba kai kansa garesu ba. Wai yau shi ne yake tunanin wace makarantar gaba da sakandire ce za ta fi kusa da gidansa (Alh. Tahir ya mallaka musu filaye shi da Lilu wadanda ake kan aikin ginawa) idan matarsa iyakarta sakandire kafin auren.

Dariya ya kama yiwa kansa na yadda aka yi daga haduwar rana daya ya san cewa iyakarta sakandire. Koda ya koma daki maimakon ya kwanta kamar yadda ya yi niyya sai ya zura jallabiya ya nufi bangaren Jiddo.

A dakin Lilu bayan fitar Suhaib da karewar musun nasu sai ya soma hamma. Gajiyar biki da ta tafiya tayi masa rubdugu lokaci guda. Mikewa ya yi ya nufi gaban socket din da yake saka chaji. A nan yaga chajarsa da bakuwar waya. Tsorata ya yi don bai ga ta inda za a ce wayar ta shigo dakinsa ta jona kanta ba. Yan uwansa kuma duka ya san babu mai irinta. Kamar ya tafi kiran Suhaib sai ya fasa. Yanzu kowa zai kara raina shi ace bai iya komai ba duk bakinsa. Ya daure zuciyarsa ya daga hannuwansa ya karanta musu Ayatul Kursiyyu ya tottofe.

"Kun dai san nan dakina ne amma duk da haka ban ji haushi don kun jona chaji da chajata ba" ya rage murya da salon rokon arziki "ina neman izini in cire in saka tawa ko rabin awa ne?"

'dillll'

Yana rufe bakinsa text ya shigo wayar. Hanjinsa gabadaya ya kanannade saboda tsoro ya koma kan gadonsa ya haye har kafafunsa.

"Daga magana sai ku turo min text? Indai chaji ne na hakura har abada." Ya zuro kafarsa yana kallon kofa gabansa na faduwa "don Allah zan fita inje dakin yayana. In je?"

'dillll'

Wani text din ya kuma shigowa. Dole ya fasa fita yana fadawa kansa cewa gargadi ne ake yi masa. Ya koma yana mika hannu yana janyewa duk a tsorace

"Bari in duba don kada ace nayi rashin kunya. Ni din banza in ja daku? Ku da ake cewa sai kun shekara dari kuke fara samartaka...."

'dillll'

"Naji. Naji!

Ya dauki wayar sai dai a kulle take. Abinka da fitinannen matashin zamani. Ya manta da tsoron da yake ji ya koma kokarin gano pattern din budeta. Bai sha wata wahala ba ya samu bayan yan dabaru. Abin da ya daure masa kai bai wuce ganin pattern din sak irin na Abbansu ba. Kai tsaye wurin messages ya shiga. Ya tarar da sakonni sun tasarma dari. Kuma wani abin al'ajabi na layin basu fi a kirga ba. Sauran kuwa harrufa ne wasu D, V, J, gasu nan dai. Na sama saman da suka yi alamar sune aka yi yanzu ya bude. Harafin dake jiki Y ne.

(Naji labarin tafiya kayi da tsofaffin matanka. Shi ne ka kasa daukar wayata saboda kana jin tsoronsu? Anyways an tabbatar min yau ka dawo. Na baka zuwa azahar idan baka kirani ba zan zo har gidan ai ba bakona bane. Aure ne dai ko ana so ko ba a so sai na amsa sunan matar Alh. Tahir)

"Abba?" Ya ambata a raunane, hawaye na zubo masa. Duk wani kuzarinsa ya kau sai zafin kirji.

Tarin tambayoyi ne a kansa na son sanin yadda aka kwana a ragaya. Neman amsa ya shiga yi ta hanyar bin text din yana maimaitawa. Bai samo amsar komai ba sama da haddace mummunan sakon. A kasan ransa kuma sai tunanin me zai fi dacewa ya yiwa wannan mai tsautsayin da ta iya shafawa idonta toka ta turo wannan sakon. Cikin sauri ya koma baya ya soma bin sauran harrufan da aka adana sunan mutane dasu ya bude nasu sakonnin. Sannan ne kuma jikinsa ya yi mugun sanyi. Hira ce tsakanin Abbansu da 'HARUFFA' daban daban ta rashin da'a. A haka ma ya kula amsoshin Abban basu da tsayi sosai. Wannan kuma dama ya yi ne domin tsira daga

forwarding chat ko screenshot da ake yi a whatsapp. Dena binsu ya yi ya koma saman wanda suka yi musaya da Y. Nata da yawa korafi ne akan rashin zuwansa da maganganun aure. Har tana cewa mahaifinta ya ce idan bai zo ba a satin zasu fasa bashi ita.

Ko kadan Lilu bai damu ba idan Abban aure zai yi. Salon hirar ce tafi daga masa hankali domin alamu sun nuna cewa ba a hira aka tsaya ba. Yaci karo da inda aka yi zancen hotel da guest house. Da kuma godiyar 'yan matan akan tarin kudaden da ya basu. Whatsapp yaso dubawa sai dai babu shi akan wayar.

Yana nan kansa ya rarrabu wurin fassara abubuwan da ya gani yaji shigowar wani sakon. Y din ce dai. Kamar dama jiranta yake yana shigowa ya bude.

(Kaga fa ina tunanin ciki ne ma dani. Zan yi test a gida idan positive ne zan turawa Farha hoton ta whatsapp. Sai a yiwa tsofaffin gwangwanye albishir sun kusa samun karuwa.)

Kuka Lilu yake tamkar yaron goye. Karshen sakon ma da kyar ya iya karantawa saboda cikar hawaye. Nambar ya kwashe ya zuba a wayarsa. Tunda ya kai nambobi shidan farko sunaye masu shigen nambar suka dinga raguwa. Yana saka ta bakwai sai ya rage suna daya.

YA YUMNA kamar yadda suke kiranta shi dasu Sauda a matsayinta na aminyar yayarsu.

Kin tsayawa ya yi sai da ya rubuce ta duka ya tabbatar da sunan da ya gani. Yana jin lokacin da zazzabi ya rufe shi hade da wani irin sanyin jiki. Bashi da hujjar karyatawa saboda harafin da ya gani a wayar Alh. Tahir ya kara bashi tabbaci.

"La haula wala quwwata illa billa. Abba? Ya Yumna?"

A gigice ya mike da ya tuna ma'anar sakon karshe. Indai Yumna ciki ne da ita kenan komai ma ya faru tsakaninsu. Zuciyarsa a take ta tashi saboda kyamar hakan da

yaji. Ya fada bandaki ya amayar da duk abin da ke cikinsa. Baki kawai ya kuskure bayan ya gama ya fita daga dakin.

*

Duk gidan Alh. Tahir babu wanda Jiddo ta tsana a tsukin kwanakin nan kamar Suhaib. Da can da baya shiga shirginta mantawa ma take dashi. Iyakarsu da juna idan zasu wuce kuma suna kusa taji sautin tsakinsa. Tsakin da tun aurenta da ubansa take ji kuma bai taba damunta ba. Ba kuma wani abu ne ya janyo yake yi mata shi ba sai kamasu da aka yi a daki wanda shi ma yaje wurin.

Abubuwan da suka biyo baya da auren nasu sun taimaka kwarai wurin dasa masa tsanarta. Sai gashi bayan shekaru sun shude ta sake bude kofar sabunta zarginta a zuciyarsa. Alal hakika bai yi wani mamaki ba lokacin da yaga tana shirin barin wurin dinner da makaniken nan. Sanannen abu ne cewa indai bawa ya kulla aminci da zina to ba makawa sai ta kawo masa ziyara watarana. Mahaifinsu yace yaji ya gani wurin sabon Allah. Dolensa kuwa ya girbi shukar da yayi ko ba dade ko ba jima. Shi dai adduarsa kullum bata wuce Allah Ya tsare masa mahaifiyarsa da kannensa.

Sallama hade da kwankwasa kofa ya yi da ya isa bangarenta. Mai'aikinta ce ta amsa ta bude masa. A hakimce kan two-seater yaganta tana waya. Ganinsa a tsakar falonta ya mugun firgitata. Lafiya ko rashinta basu taba kawo shi inda take ba. Yau da yazo ta san lallai akwai matsala. Wayar faduwa tayi daga hannunta ta kuma gyara zama ba shiri.

"Nambar makaniken nan zaki bani." Cewar Suhaib, fuska babu annuri.

Jiddo sai ta daburce duk saboda gudun tonon asiri. A haka ta cije ta harare shi.

"Rashin kunyarka ta isheni Suhaib. Idan ban ci darajar shekaruna ba ai ya kamata in ci na matsayina a gidan nan."

Surutunta bashi da gurbi a kwakwalwarsa balle yaci darajar neman ta maimaita domin ya fahimta.

"Zan samu ko in tafi?"

Rainin wayonsa ya sake bata haushi. Wato ma bai ji abin da tace ba bare ta san ran zai yi aiki dashi. Yatsina fuska tayi ita a dole bata san me yake nufi ba ta ce,

"Wane makaniken?"

Wannan karon Suhaib ne ya hango rainin wayonta. Sai da ya dage girarsa daya sama ya murmusa. Harsashi zai hada mata a wurin Alh. Tahir don ranar tada bom din bata zo ba. Wannan ba aikinsa bane. Lokaci da talalar Ubangiji ga bawan da ya dage akan aikin sabo zai cimmata wataran.

Wata irin murya ya yi amfani da ita sai a rantse sangartaccen da ne a gaban mahaifiyarsa yana zuba shagwaba.

"Don Allah ki bani Anti Jiddo."

Ita kanta da taji muryar sai da ta kara tsorata fiye da farkon zuwansa. Ta san dole akwai abin da yake nufi da haka. Ba dai ta zata maigidan ne da kansa ya shigo falon ba tare da ta kula ba sai yanzu.

Ran Alh. Tahir fari kal kamar takarda yau ga Suhaib a bangaren Jiddo. Yadda yake magana ya nuna masa sun jima da daidaitawa. Ya dinga zuba murmushi kamar sakarai har yana mantawa da halin da yake ciki.

"Wato kin saka danki a daki yana ta shagwaba aka rasa wanda zai amsa min sallama ko? Wai ma mene ne yake faruwa zan yi alkalanci."

Suhaib ya yi saurin bashi amsa kafin ta sami damar juya zancen.

"Nambar makanikenta na Kano nake so Abba shi ne taki bani wai sai na yarda gobe zan rakata shopping"

Wohohooo. Alh. Tahir da shi ma ba wani samun hira daga Suhaib din yake ba duk irin son da yake masa sai yaji kansa ya yi gingirin. Murmushi yaki yankewa a fuskarsa.

"To ai sai ka amince dan Jiddo"

'I reject it! Tuff, tuff' cewar Suhaib a zuci yana jin tsigar jikinsa na tashi saboda an kira shi dan Jiddo.

"Na amince. Don Allah ki bani"

Tsabar mamaki sai ta kasa cewa komai banda kai da take gyadawa kamar kadangaruwa taga manja. Sunan Danliti ta lalubo tunda Alh. Tahir ya musu karan tsaye yaki tafiya. Dama al'adarsa ce shiga bangaren kowa idan zai fita ko ya dawo.

Bayan Suhaib ya kwafe nambar ne Alh. Tahir yake tambayarsa me zai hada shi da makanike a Kano.

"Wani case ne babba ya taso tsakaninmu dashi."

Alh. Tahir ya dan bata fuska

"Ban gane ba? Wani abu ya yi maka?"

Suhaib ya yi hanyar kofa yana cewa "a'a, motar Anti Jiddo yaso lalatawa ba don Allah Ya kaini wurin da suke ba da wuri."

Sautin cikin Jiddo har kunnuwansu saboda tsoro. Suhaib kuwa ya fice yana jin Alh. Tahir na tambayarta me ya sami motar har aka nemo makanike shi bai sani ba. Rantse rantsenta kadai ya jiyo ya kara gaba don bashi da lokacin jin karairayin da zata yi.

*

Lilu kuma da ya fito bai zame ko ina ba sai bangarenta Mami Khadija. Ya yi zaton samunta ta kwanta ko shirin kwanciyar kamar kowa sai yaga sabanin haka. Laptop ce a gabanta ga tulin takardu ta soma barbazawa tana aiki. Gaban table din da aka yi mata musamman saboda aikinta yaje ya mika mata wayar.

"Ga wayar mijinki idan ya dawo ki bashi."

Tun shigowarsa take kallonsa amma furucinsa yasa ta koma yi masa firgitaccen kallo.

"Mijina? Mijina fa ka ce Lilu. Ko dai nice ban ji ba da kyau?" Ta furta a sanyaye.

Lilu ya cije lebe cikin bacin ran tuna abubuwan da ya gani.

"Mijinki maigidan nan nake nufi."

Laptop din ta tura gefe ta tashi tsaye tana dubansa.

"Ko agolanci nazo da kai gidan nan bana tunanin za ka iya budar baki ka kira wanda nake aure Mijina."

Duk shashancin Lilu bai taba zina ba. Mami Khadija ta dasa musu tsananin kyamar wannan laifin tun basu san kawunansu ba. Yafi kowa fitina a gidan amma akwai iyakokin da ko a mafarki bai hango kansa da ketaresu ba.

Kalaman Mamin murmushi suka saka shi.

"Mamina kinfi karfin haka a wajena. Wallahi indai mai mutumci wanda ya san darajar kansa data iyalinsa kika aura ni mai tayaki yi masa biyayya ne."

Da ya gama maganar ya dora wayar a kusa da tata ya fice da sauri. Zama a gabanta karyar masa da zuciya zai sake yi ya kaishi ga kuka. Tausayinta yake ji sai dai kuma jikinsa ya bashi ta jima da sani. A hanyar zuwa dakin ya dinga tuno irin nasihunta da fada da suna yara har kawo ga yanzu. Kusan komai yafi ta'allaka akan zina.

'Ba halinsa bane!' shi ne abin da Mami Khadija ta fara fadawa kanta a lokacin da taji kamar ta kwashe shi da mari. Kwalla ce ta taho mata saboda jikinta yana bata da wuya idan ba sirrin boye ne ya fito fili a wurinsa ba. Yadda Farha ta sani bayan Suhaib gashi yau shi ma ya sani. A ranta ta dinga tsarkake Mulkin Ubangijin da ya haramta zina. Hakika wannan kaba'ira tana zubar da mutumcin mai mutumci. Yau Lilu da bakinsa yake kiran mahaifinsa da wani suna ba Abba ba.

Kallon wayar tayi sau daya ta kawar da kanta. Alh. Tahir na shigowa bangarenta daga wurin Jiddo ta damka masa wayar daga bakin kofar da ta tare don kada ya shigo ciki.

"Lilu ne ya kawo"

Gumi a take ya tsatstsafo akan goshinsa.

"Ya ce wani abu ne?"

Mami Khadija ta kalle shi ido cikin ido ta ce "ya ce ga wayar mijina na bashi idan ya dawo"

Alh. Tahir ya karkata gefen fuskarshi gareta yana son tabbatar da abin da ta ce.

"Mijinki? Dani yake?"

Cikin ko in kula ta ce "a iya sani na ba."

Daga haka ta rufe kofarta ta barshi a wurin yana jinjina girman abin da yake samunsa a tsukin nan.

BABI NA GOMA SHA UKU.

Naji korafe korafe kai tsaye da ma na aike kala kala game da dorawa Lilu laifin da ba nasa ba. Na so kamewa daga bayar da amsa sai dai ku gani a rubuce. To amma wasu har ikirarin barin karatun suke. Jama'a idan kun barwa Batul labaranta ina ta kama? Sakon da nake fatan Allah Ya bani ikon isarwa bai je ko ina ba kenan. Ya zama dole na magantu.

Kafin na fara wanke kaina, ina so inyi amfani da wannan damar wurin yi muku godiya. Akwai gajiya matuka idan marubuci yana daukan dogon zango kafin ya yi post. Sai dai kamar kullum hakuri dai zan cigaba da baku. Ba da gangan bane. Yau da gobe ce wadda take nukurkusar daukacin al'ummar kasar duniya ba ma kasar nan ba. Allah Mabuwayi Ya kawo mana saukin lamura. Amin

To mu koma ga labarinmu. Kwanakin baya korafin akan yawan wahalhalun Innayo da rashin cin moriyar guminta ne suka yi yawa. Wasu har suna ganin kamar zan sagar musu da gwiwa wajen kulawa da amanar da Allah Ya bamu ta zuri'a. Ko daya ba nufina ba kenan. Labarin nan kacokan ban yi shi domin tsantsar nishadi ba. Wasu lamura nayi ta nazari a rayuwarmu shi yasa nake son yinsa ta yadda zaiyi kamanceceniya da zahirin rayuwa. Akwai Innayo bila'adadin a cikin al'ummarmu. Mace ta wahaltawa miji ta kuma wahaltawa 'ya'ya. Amma a karshe haka zata koma ga Allah da bakincikin dukkansu. Ta rayu a talauce ta mutu cikin talauci. To amma fa shafin rayuwarta ba zai kare a wurin Maqaginta ba muddin ta koma gareshi tana

mai gaskata kadaitar mulkinSa. Daga lokacin ne ma zata fara shan romon ladan ayyuka da hakurinta har zuwa tashin qiyama. Sai dai taji ance ta wuce Aljanna gidan dauwamamen farincki.

Game da Lilu kada mu manta su waye iyayensa. Uba mazinaci wanda har yanzu babu wata kwakkwarar nadama a tattare dashi. Shin idan zina bata dawo masa a inda zai yi masa ciwo ba kuna ganin zai san Annabi ya faku? Zai ji ciwon da iyayen 'ya'yan da ya mu'amalanta suka ji? Zai yi nadamar ayyukansa har ma ya tuba? Sanin tsohuwar sana'ar maneman 'ya'yansa ba ta da babban tasiri indai ba an riga an daura aure ba. A yanzu kam ba zai wuce ya soke auren ba ya cigaba da yawonsa. Wanda kuma duk ya yi zina da ahalin wani shi ma sai anyi da nasa.

A gefe guda kuma mahaifiya ga Lilu mace ce tagari. Uwa ce da ta amsa sunanta wurin tarbiyya da yawan yiwa 'ya'yanta addua. Ga Ubangijin da take mikawa lamuranta Mai ji ne ga kukan bayinSa. Al Hayyu, Al Qayyumu ba zai bata kunya ba.

Gamu ga Sarkin da baya saba alkawari. Mahaliccin da Adalci ya kasance cikin suffofinSa. Duk da cewa labari ne amma ina son tunatar damu uwaye karfin addua. Tabbas alkawarin Allah na dawowa mazinata da sharrinsu ta hanyar da zasu koka ba zai tashi ba. Sannan kuma adduar Uwa ta gari ga 'ya'yanta wannan kaifiyan ce.

Indai haka ne kuwa to lallai Alh. Tahir sai ya yi kuka akan sharrin da aka yiwa Lilu. Sannan Mami Khadija sai ta kara mika wuya ga Allah a yayinda Ya kubutar mata da danta daga dabaibayin da bai isa ya kwance ba.

Ya Rabbi ka karawa Annabinka daraja, Ka azurta shi da kololuwar daukaka. Amin.

***

Mami Khadija kiran Lilu tayi bayan ta rufe kofarta. A zatonta Alh. Tahir ya bar wurin ashe yana tsaye. Kafafunsa sun yi masa nauyi ya kasa dagasu. Lalacewarsa bata yi

kamarin da zai iya cigaba da jure juya baya daga tsatsonsa ba. Bazuwar zancen nan zuwa kunnuwan ragowar 'ya'yansa ba karamar barazana bane ga mutumcinsa a idanunsu. Shi kuwa zai iya komai domin kare wannan martabar. A tsarinsa miji ko mata kada ya fishi girman masauki a zuciyarsu. Yana son ya zama babban amininsu kamar yadda suka faro tun kuruciya. Wannan dalilin ne ma yasa Farha da Lilu suka ji ciwon laifin nasa fiye da yadda zasu misalta. Muryar Mami yaji cikin dakiyar da ya saba gani a tare da ita tana magana da Lilu.

"Ina ka tafi?"

Bai ji amsar ba sai abin da ta mayar masa. Yadda tayi magana babu alamun wasa ko wargi. Umarni ne take bayarwa domin ta kare dan nata.

"Yana daga cikin rahamomin Ubangiji garemu da Ya halatta mana yin abota. Lokuta da dama suna maye gurbi ko ma su fi family dinmu tsaya mana akan matsaloli. Sai dai kuma ba kowacce irin matsala ya kamata a fadawa aboki ba. Wani abin sirrinka ne har lahira. Idan yau kaje wurin abokai da damuwar nan har ka fada musu komai ka cuci kanka. Ba kai kadai ba hatta 'yan uwanka ka tozartasu a idon duniya. Saboda haka duk mummunan sirrinka da Allah bai tona ba kada ka zama mai fitar dashi. Zai zama tamkar ka cakawa kanka wuka ne da kanka. Shi mahaifi sutura ne ga zuri'arsa. Abu kadan idan ya faru wanda ya dauke uba daga muhallinsa a wurin 'ya'ya sai kaji ana kiransu 'ya'yan mace. Kuskure guda daya tak zasu aikata sai a kusa shekara ana goranta musu duk don babu uba kuma babu madadin uban. To ina ga kai da kanka ka tona halin naka? Abokanka karshenta suyi maka tayin kayan maye. A halin da kake ciki na san karba zaka yi"

Shiru suka yi na 'yan dakiku kafin Mami Khadija ta ambaci alkunyarsa wadda mutane suka bar kiransa da ita.

"Khalil?"

"Na'am" ya amsa da muryar da ta makale a makoshi saboda damuwa.

"Ina fata sunanka zai jagoranci hukuncin da za ka yanke domin ni kam bani da sauran abin cewa gareka. Banda iyayena dominku nake komai. Don Allah kada ku sa bayan kukan miji na dora da na 'ya'ya."

Lilu sai ya fashe da kuka. Mami Khadija ta dinga rarrashinsa da kalmomi masu dadi. Ba don gargadin da tayi masa ba tabbas idan yaje wurin abokan nasa sai ya farkewa mahaifinsa laya. A ganinsa hakan ba zai zama komai ga mutumin da bai iya daraja kansa ba. Ya manta bayan shi akwai 'yan uwansa. 'Yan uwan ma mata masu rauni. Gashi babu wadda tayi aure. Wane dan mutumcin ne zai so auren 'yar mutumin da aminiyar 'yarsa take ikirarin yayi mata ciki?

Da wannan tunanin ya sauyawa shawararsa akala. Alwala ya dauro ya sanya dogon wando da tsaftatacciyar jallabiya ya dauki littafi mai tsarki ya soma karantawa.

(Babu wani abu mai canja kaddarar bawa ko ya sassauta ta kamar addua. Duk takun da bawa zai yi domin kusanta kansa da Mahalicci, Sarkin da bashi da wa'adin zamani zai zo gareshi da fiye da wannan.)

***

Shi kuwa Alh. Tahir kamar kazar da kwai ya fashewa a ciki haka ya bar kofar dakin. Kamar da wasa haka ya shigo tariyo wasu kazaman mu'amala da ya yi da mata daban daban. Tunanin kuwa yayi sanadiyar radadi mai azaba a cikin zuciyarsa. Yana cike da tsoro matuka a wayi gari duka 'ya'yansa suna yi masa kallon fasiki. Wannan rana ya tabbata zata fi kowacce muni a gareshi. Ba zai jure kallon kyama irin wanda Suhaib da Farha suka bishi dashi ba daga dukkansu. Shi bai ma san soyayyarsu tayi masa irin wannan kamun ba sai yau. Har musu ya yi da zuciyarsa akan cewa yanzu son da fargabar kiyayyarsu ya ninku sau adadin da bai sani ba a ransa. Zazzabi ya soma ji tun kafin ya isa nasa bangaren. Tunani ya sha masa kai bai ga isowar Suhaib gabansa ba sai muryarsa wadda ta dawo dashi hayyacinsa yaji.

"Ina son zuwa Kano gobe in sha Allahu."

Alh. Tahir ya ware idanunsa sosai da son dawo da nutsuwarsa jikinsa. Bashi da lokacin zurfafa tambaya ko binciken me dan nasa zai je yi a Kano daga dawowarsu yau. Ya dai aminta dashi ya san ba shashanci ne zai kai shi ba. 'To ma idan shashancin ne ai a wurinka ya gada' wani sashe na zuciyarsa ya tuna masa.

Shi dai Suhaib yanayin sanyin da ya gani a wurin mahaifin nasa ya bashi mamaki. Domin Alh. Tahir mutum ne mai yin komai da kuzari. Sai ya sami kansa da kasa sharewa.

"Abba lafiya dai?"

Alh. Tahir yayi murmushin jindadi har hakoransa suka fito. Yau shi ne Suhaib yake nuna damuwa akan damuwarsa.

"Lafiya kalau. Kaina ke ciwo shi yasa ma na dawo da wuri. Anjima kazo in kara maka guzuri"

"Na gode. Kuma Allah Ya kara sauki" cewar Suhaib yana yin gaba.

Wurin Mami Khadija ya wuce don baya son sai dare yaje yace zai yi tafiya da safe.

Tunda taji sallamarsa bata yarda ya karaso dakin ya sameta a yanayin da take ciki ba. Fuska ta saki har ya shigo ya fada mata zancen tafiyar. Ba karamin dadi taji ba kuwa saboda ko kadan bata so ya fuskanci abin da ya faru. Tafiyar tasa tamkar rage karfin rikicin da take gudu ne. Dagula komai zai yi da fushinsa da zuciya.

"Allah Ya kiyaye hanya. Kwana nawa zaka yi?"

Suhaib wani irin kallo ya yi mata na rashin gamsuwa. Maminsa mai bin kwakkwafin yara normally cewa zata yi me zai je yi.

"Mami lafiya kuwa? Ko baki da lafiya?"

Fahimtar inda ya dagota da tayi yasa ta nemo murmushi ta dora akan fuskarta.

"Wai don kaga ban tambayeka komai game da tafiyar ba?"

Kai ya gyada kawai yana yi mata kallo na son gano inda baraka take idan akwai ta.

Murmushi ta sake yi sosai ta ce "jikina ne ya bani kamar surukata daga Kanon zata zo. Ko dai wurinta zaka je ko kuma idan ka tafi yau zaku hadu."

Suhaib dai bai san kujerar da Ayaah ta samu a zuciyarsa ba amma kalaman Mami sun saka shi jin kunya. Shi din ba ma'abocin harkar mata bane saboda tsoronsa na zama tamkar babansa. Faffadan murmushin kama kai ya shiga yi gami da susar keya.

Mami Khadija ta mike cike da farinciki tana dariyar da ta bayyana hakora.

"Hasashena ya zama gaskiya akwaita kenan. Alhamdulillahi. Na santa?"

"Nifa Mami ki ma daina wannan batu don ban girma ba."

Kallon ka-ma-rainani tayi masa tana cewa "to bari nayi addu'a ga wadda zaka je wurinta din. Allah Ya kawo mata santalelen miji wanda zai aureta nan ba da jim...."

Abin da yayi a lokacin har ya koma dakinsa yana mamakin kansa. Katse addu'ar Mami ya yi da saurinsa yana mai bata fuska.

"Ba amin ba."

Ta dage gira tana leken fuskarsa da yayi kicin kicin da ita.

"Koda kaine mijin?"

Shi ma sai sannan ya gano tasa katobarar. Gaggawar fita daga dakin nata ya yi cike da jin kunya yana cewa ba abin da take zato bane.

Sai da ta tabbatar ya fita ta iya sauke ajiyar zuciya. Farha ce kuma a ranta yanzu. Yarinyar tana da dauriya fiye da zato da tsammani. Da ta matsa mata da tambaya tabbas ta sanar da ita cewa har yanzu bata ji daga Abbati ba. Bai daga wayarta ba sannan kuma bai nemeta ba. Hankalinta taji ya tashi da tsoron kada zuwansa rayuwar Farha ya zama tamkar lasawa yaro zuma a baki. Da ace abin da ya saka shi komawa gida ya girmama bata jin mahaifiyarsa zata boye mata lokacin da suka yi waya. Tunanin ba zai fissheta komai ba shi yasa ta fita zuwa dakin 'yan matan.

*

(Allah Ya zama gatanka akan duk abin da baka da iko akansa)

Sakon sms da Farha ta turawa Abbati kenan taji an murda kofar dakinta. Mami Khadija ce ta shigo da sallama. Farha tayi saurin gyara zama daga kashingiden da tayi.

"Ya naga kowa ido biyu ne? Na zata zan sameku duk kun kwanta saboda sammakon da akayi."

Dan murmushi Farha tayi tana cewa kwanciyar zata yi yanzu. Mami sai ta sami wuri a bakin ta zauna.

"Farha" ta kirata a tausashe. Ba da baki Farhan ta amsa ba, sai dai ta tattaro hankalinta da nutsuwa ta mikawa mahaifiyarta. Mami Khadija ta cigaba da magana "kafin faruwar abin nan, ina nufin tafiyarsu gida babu shiri ranar da suke ganawa dasu Abbanku kun samu sabani ne?"

"A'a Mami" cewar Farha tana danne kwallarta. Kewa da damuwa akan rashin sanin halin da Abbati yake ciki sun yi mata yawa. Karfin hali da dauriyar tata sun kai makurarsu.

"Ki kwantar da hankalinki ki kuma yawaita addu'a. Ba komai da muke so bane alkhairi a garemu. Miji kuma babu matar da zata auri wanda ba nata ba" da dan sauri Farha ta dago ta dubeta tana son ta ce ita dai Abbatin kadai take so amma ta kasa. Mamin ma dai murmushi tayi "ke dai ki kasance mai mika wuya wurin karbar kaddara. Mijinki da yardar Allah wanda zaku kama hannun juna ne har aljanna. Bana miki fatan haduwa da abokin rayuwa wanda zaki so tatayyarku ta kare a duniya kadai."

Farha ta san da wa Mami take shi yasa ta dinga zubar da hawaye. Duniyar gabadaya sauki ne da ita amma mazauna cikinta suyi ta jajibowa kansu matsaloli ta hanyar sabon Allah.

A daren ranar Jiddo ta kira Danliti ta fada masa Suhaib ya karbi nambarsa a wurinta. Ta kara da cewa bata san manufarsa ba saboda haka tana mai gargadinsa da ya yi taka tsantsan. Ya kuwa yi mata alkawarin kiyayewa.

Sai dai kuma ta riga ta makaro. Tun bayan komawar Suhaib dakinsa ya kira shi. Sauya murya ya yi yadda ba zai saurin gano shi ba ya ce kwatancen garejinsu yake nema.

"Kwanaki mun zo tare da wani abokina daga Abuja har ka bashi nambarka. Na shigo gari ne mota take ta bani matsala. Idan zan sami gyaran da wuri ina son kawo maka ita gobe."

Kalmar Abuja kadai da Danliti yaji tasa shi bayar da cikakken kwatance harda wata nambar idan bai same shi a wannan ba. A gefe guda kuma maganar Jiddo ta sanya shi yiwa Ayaah mugun tanadi. Indai akwai wata alaka tsakaninta da Suhaib da wannan shirin nasa zai bakanta masa rai. Ita kuma ya zama ladan bata masa lokaci kamar bata san me ya kawo shi ba tun farko.

***

Duk wani taimako da Uwani zata iya bawa Qibdiyya tayi a lokacin wanda bashi da wani yawa. Mafi a'ala a kaita asibiti wurin kwakrarren likita domin a dubata yadda ya dace. Shawarar da ta bawa Munzali kenan bayan sun fito daga dakin.

Kai ya gyada mata ba tare da ya iya magana ba. Zazzabi yake ji yana bin lungu da sako na jikinsa kamar ana gasawa akan garwashi. Numfashi da iskar da yake fesarwa ta baki ta hanci duk zafine dasu. Daki ya nuna musu a kasa ya ce idan zasu kwana ne ga wuri nan idan sun idar da sallar magariba. In kuma zasu tafi ne shi ma ga kudin mota don ba zai iya tuki ba. Ficewa ya yi daga gidan bayan ya yi tasa sallar a daddafe yana taku kamar a iska saboda rashin nauyin jiki yaje kofar gidan Abbati. Shi kadai kawai yake son fadawa abin da yake faruwa domin ya dauki mataki. Don sai yanzu ya kara yarda cewa Abbatin ya fishi tunani. Duk inda ya laluba sai yaga kamar idan ya taba Lilu sai ya kashe shi. Ya san zafin fyade tunda Shazali ya yi masa a shekarun da suka fi na Qibdiyya ma. Ya san ciwon da rai ke rikewa a yayinda ya san cewa shi ne sanadiyar dulmiyar wani a aikin sabo. Wannan ya tilasta masa yin sanyin da yake ganin yanzu ba muhallinsa bane. Salamar da ya san Abbati zai cusawa ransa ko yaki ko yaso ya tattaro ya sanyawa zuciyarsa. Saboda idan bai nutsu ba yana da yakinin cewa sai ya yi abin da zai yi nadama a gaba. Gara ya nemi uban Qibdiyya ya nemi shawararsa kafin ya zartar da nasa hukuncin. Ya debi kusan mintuna goma yana sallama da kwankwansa kofa kafin Hanne ta bude masa. Yadda ta bude kofar da dankwali a hannu zai sanar da duk wanda ya ganta cewa daga bacci ta tashi. Yatsina fuska tayi da ta ganshi taja guntun tsaki. Murmushi mai ciwo ya yi mata. A ransa yake jin kinsa da take yi tuntuni ba zai rasa nasaba da kasancewarsa sanadiyar bata rayuwar mijinta ba.

"Don Allah kin yi waya da Abbati? Na neme shi na kasa samunsa."

"Rabona dashi tun ranar asabar da kuka fita tare" ta bashi amsa tana cika tana batsewa. Ganin bai ce mata uffan ba ya juya zai tafi sai ta ce "kayi ka gama munafurcinka na son saka shi ya min kishiya. Ta Allah ba taka ba."

Bai ko waiga ba balle ya kalleta. Yana ji ta buga kofa da karfinta kamar za ta balleta. Gida ya koma ya shige daki bayan sallama da su Uwani sun ce ba zasu kwana ba. Asabe ta so ya bata Qibdiyya su koma ya ki. Bayan tafiyarsu ya karbi abinci a wajen Kande ya bawa Qibdiyya. Yarinyar jikinta duk yayi sanyi ta kasa sakin jiki tayi wasa saboda yanayin da taga babanta. A jikinsa kawai ta sami wuri ta kwanta tayi lakwas.

Munzali ya dinga kallonta yana kara tsinewa Shazali. Ya kuma kara tsanar Alh. Rabi'u wanda sakacinsa ya zama masomin lalacewar tarbiyar gidansu. Duk abin da ya samesu da shi 'yan uwansa babansu ne sila. Sakarwa iyalansa mata ragamar gidansa da hadasu da nauyi da hakkokin da ba nasu ba shi ne matakin farko na tabarbarewar lamuransu. Tsatson Innayo sun dace da uwa ta gari amma halin uba ya zama jirwaye ga tarbiyar irinsu Uwani. Shi kuwa da 'yan uwansa da basu yi sa'ar uwa ba sai dukan ya zame musu biyu.

Waya ya dauka ya sake kiran Abbati duk da bai sa ran cewa za a amsa ba. Jikinsa yana bashi cewa Abbati yana cikin koshin lafiyar jiki. Sai dai bashi da tabbacin ta ruhi. Washegari litinin dama ya yi niyyar binsa idan shirun ya yi yawa. Ya tabbata sirrin boye ya riga ya fito fili. Wannan lokacin ne Abbati yafi bukatarsa. Su Baaba Mari zasu yafewa Abbati idan suka ji cewa shi ne ya fara saka shi a wannan hanyar zasu dauki laifin su dawo masa dashi.

*

A cikin halin ciwo Baaba Mari take sosai don sun sake komawa asibiti. 'Yan uwa da basu san me yake faruwa ba suna ta al'ajabin wannan abu. Ace mutum kamar Abbati ya kasa kai mahaifiyarsa babban asibiti a halin da take ciki. Tun ana kananun maganganu da safe har aka fara tararsa gaba da gaba ana fada masa zuwa yamma. Kannensa ma sai da suka nuna bacin ransu sosai. Ya rasa inda zai saka ransa yaji dadi. Ciwo yana cinta amma ta ce indai ba halal ya nemo ba ya barta ta mutu ta huta.

Wuraren Isha sai ga Mal. Inuwa ya shigo dakin kamar an koro shi. Kullin leda ya dauko daga aljihun 'yar sharar jikinsa ya mikawa Abbati.

"Ga wannan dubu talatin da hudu ne mu mayar da ita babban asibiti."

Da kyar Baaba Mari ta iya bude idanunta ta dube su. Mal. Inuwa yana ganin fasalin kallon mai kama da na tuhuma ya hau rantse rantse. Yanzu tsoron bacin ranta yake yi da gaske.

"Gonarmu da wajen gari na sayar. Da shike ba girma gareta ba shi yasa bata yi kudi sosai ba. Nan an warewa duka 'ya'yan Malam (yan uwansa da suka hada uba) kasonsu. Wannan ne nawa." Ya sake nuna ledar.

Da Abbati ya karba sai da yaji kamar bai taba rike rabi rabinsu ba a rayuwarsa. Kudi dai ya baya miliyan biyar baya a asusunsa na bankin da atm din yake jikinsa a yanzu haka. Da za a tara abin da ya tara da kadarorinsa shi ma ba zai ce ga adadin abin da za a samu ba. Sai dai duk wannan arziki tubalin toka ne. Kwakkwarar iska guda ta hure komai saboda haram dama bata da nauyi. Da zarar mutum ya dauki damarar rabuwa da ita indai da zuciya daya ne to tafi komai saukin saukewa.

Suna shirin tafiya don har an samu musu mota kwatsam sai ga Mal. Sa'idu a kofar dakin yana sallama. Kallon kallo aka soma tsakanin Abbati da kannensa. Dame kuma yazo?

Mal. Inuwa ne ya leka sai dai bai jima ba ya dawo yace Abbati yaje.

"Gani"

Leda sak irin ta hannun Mal. Inuwa ya mika masa. Da ace hankalin Abbati a kwance yake da yaga yadda tsufan kawun nasa ya sake bayyana. Ya zabge sosai a tashin hankalin kwana daya. Allah Ya ragewa aya zakinta akwai hannunsa dumu dumu a cikin rayuwar duka 'ya'yan gidan. Ba don haka ba da tuni ya lakabawa Baaba Mari laifin bata danta. Kila ma zuwa yanzu duka gidan da garin sun gama ji har an karar

da tofin Allah tsinen da za ayi masa. Da yake shi ne uban gayya mai daukar credit din cigaban duka 'ya'yan gidan dole ya karbi lalacewarsu ma. Ta Abbati dai ta fito fili, zuciyarsa kuma tana nan tana raya masa cewa ba shi kadai bane ya fada tarkon shaidan daga zuwa karatu.

"Gashi nan ka kara a kudin asibitin"

Karba kawai Abbati ya yi ya koma ciki ko daga kai ya kalle shi bai yi ba.

Haka suka fita ana ta juyayin wannan lamari na ciwon Baaba Mari da Mal. Sa'idu a cikin gidan. Deluwa tayi nacin har ta saduda aka son jin kwaf.

Habi da Abbati ne kadai masu tafiya tare da mahaifansu. Babban asibitin gwamnatin Dutse suka tafi. Cikin dare sosai suka isa garin. An kuma karbi Baaba Mari an fara bata taimakon da ya dace. Zuwa safiya jikinta ya soma daidaita sosai sai hamdala. Bayan azahar ne da Abbati ya tabbatar an sami kanta yadda yake bukata ya iya dauko wayarsa. Ashe ta shiga silent ba tare da saninsa ba. Missed calls ya gani rututu. Na Munzali sun fi na kowa yawa. Sai na wanda suka nada yake kular musu da ginin plaza. Plazar da sai dai idan gwamnati ta gaji da ganinta ta san yadda zata yi da ita tunda komai na samuwarta haram ne. Na Farha basu fi biyar ba. Ya san lallai ita din ba mai takurawa bace. Tunda ya tafi a irin wannan yanayin kuma bai nemeta ba ta tabbata abin ya girmama. Babu na Hanne ko daya. Dama ita bukata ke sanyata nemansa ko zai yi sati bata ganshi ba.

Wani irin yanayi na shaukin soyayyar da mai yinta ya san bata tafe da cikar buri ne ya shige shi. Abubuwan da ya yi ta gudu a baya game da rasata sun bayyana. Ko yana hauka baya jin zai iya sake komawa gareta. Arzikin da ya zame masa garkuwar neman aurenta ya kau. Yanzu bashi da maraba da almajirin kan hanya mai jiran sadaka. Messages din ta turo masa har sunfi kiran yawa. A kalla a rana ta turo uku. Nasihohi ne da maganganun kwantar da hankali. Zuciyarsa ta sake karaya. Ba don karfin addu'ar mahaifiya ba da jajircewarsa wurin son ya kyautata tuba da ya koma gareta. Zai kirata ya jaddada mata girman soyayyarta da alkawarin aure.

"Allah Ya baki wanda ya fini a wurinsa. Allah Ya cire min kaunarkiba don na daina sonki ba Ya Farha."

Adduar da ya yi kenan iya jin kunnuwansa sai dai Baaba Mari tana ganin motsin bakinsa.

Adadin kiran da Munzali ya yi masa ne ya dakatar dashi daga rufe wayar. Munzali ya san me ya kawo shi gida. Ya san abubuwa marasa dadi dole zasu faru. Ya kuma san cewa zai neme shi da zarar abubuwa sunyi sauki. Babu lafiya jikinsa ya bashi. Bai yi tunanin komai ba ya kira shi tare da fatan ya amsa da gaggawa.

Ringing din farko ma bai gama shiga ba Munzali ya dauki wayar da sauri. Hannunsa yana rawa ya kara wayar a kunnensa. Zazzabi yake mai zafi da matsanancin ciwon kai ya kasa tashi zaune ma balle ya nemi agajin kukunsu a kai shi asibiti ko a bashi magani.

Yadda numfashinsa yake fita da sauti da kuma canjin muryarsa kadai suka ganar da Abbati cewa bashi da lafiya.

"Munzali me ya sameka? Kana ina?"

"Qibdiyya aka yiwa .. "

Sallah Baaba Mari zata tayar daga zaune ba shiri ta katse kabbarar haramarta ta kira Abbati a fusace.

"Abbati. Bani wayar nan!" Ta kalli Habi wadda ta tsorata "bamu wuri". Da saurinta kuwa ta fice duk da tana son jin me ake boye musu.

Tashi Abbati ya yi yaje gabanta ya durkusa sannan ya bata wayar. A wurin ya cigaba da durkuso ita kuma ta kara wayar a kunnenta. Kafin tayi magana Munzali dama yaji kiran da ta yiwa Abbati saboda haka bai yi mamakin jin muryarta ba.

"Munzali..." Da fada taso kiransa domin ya san duk abin da zata fada ba wasa bane. Sai dai kuma yana amsawa taji tausayinsa ya tsirga mata.

Gaisheta ya yi da faduwar gaba "Baaba ina wuni?"

Bata amsa ba. Sai ma kai tsaye fada masa abin da yake gabanta.

"Don sonka da Allah da ManzonSa (SAW) babu kai babu Abbati indai da gaske tuban kuka saka a gaba."

Tunda Abbati yake bai taba yiwa Baaba Mari musu ba amma yanzu bai san lokacin da ya kira sunanta da karfi ba. Jikinsa ya kama rawa ya sanya hannuwa ya dafa cinyarta.

"Baaba don Allah kada kice haka. Nayi miki rantsuwa da sunayen Allah tsarkaka wallahi bama neman juna. Abotarmu ita kadai ce halattaciyar dangantakar dake tsakaninmu. Domin Allah muke yinta ba don..."

Fuskarta babu annuri ko miskala zarratin amma ga hawaye suna gudu akan nagartacciyar fuskarta. A lokacin da Abbati yake nasa maganganun tana jinsa da kunne daya shi ma Munzali nasa yake yi mata.

Magana yake cikin dakewar murya domin kuwa iya abin da ya rage masa kenan. Mutuwa yake yiwa kansa fata domin yana ganim idan har Allah Ya karbi tubansa to lallai can din zai fiye masa akan rayuwa ba tare da aminin kwarai ba. Ashe alkhairi na karshe da zai gifta a tsakaninsa da Abbati shi ne assasa masa tuban da bai hangowa nan kusa ba. Kamar wanda ake cakawa mashi a kahon zuci haka ya dinga ji a lokacin da yake yi mata magana.

"In sha Allahu zaki sameni mai biyayya a gareki Baaba. Babu ni banu Abbati. Zan tashi daga gidan da nake kafin ya dawo Kano."

"Shi ma ba zai dawo ba. Ku nesanta da juna sannan ku nesanta da dukiyar haram. Sannan ne zaku yi tuba da kyakkyawar zuciya. Wala Allah zaku samu rabauta a nan duniya da lahira."

Kuka ya fashe dashi ba tare da sanin cewa Abbati ma kukan yake mata ba.

"Ki yafeni Baaba. Don Allah kada ki kai karata wurin Allah akan Abbati. Ko naki hakkin na rage ina sa ran samun sauki ko yaya yake a wurin Mahaliccina."

Rufe ido tayi wasu hawayen suka sauko a guje masu zafi.

"Na yafe maka. Allah Ya yi muku albarka."

Abbati na jin haka sai ya ce "Baaba don Allah ki tambaye shi me ya sami Qibdiyyan"

Munazali yaji tambayar da yayi. Wani daci ne ya taso masa daga makogaro har wuya a sanda ya ce

"Fyade aka yi mata Baaba amma don Allah kada ki fada masa. Bata ji ba bata gani ba ta soma girbar shukata tun kafin ta fahimci duniyar kanta."

"Innalillahi wa inna ilaihi raji'un" Baaba Mari ta fada tana jin kamar ciwonta zai dawo. Masifun zamanin nan sun yi matukar yawa.

A gigice Abbati ya ce "mutuwa tayi?"

Da ta girgiza masa kai sai ya ce "Baaba ki bani don Allah ko sallama ne muyi dashi."

Tausayi ya bata ta mika masa wayar sai dai yana karawa a kunne yaji kit Munzali ya katse kiran. Kiransa ya yi amma taki shiga domin kuwa yana katsewar ya kasheta. Ya kuma lallaba ya kashe sauran ukun ma wadanda duka Abbati yana da lambobin.

Da Abbati ya gaji da gwada kiransa ya dubi Baaba Mari tamkar karamin yaro ya ce "kinga ya kashe wayoyinsa."

"Saboda yana son ka shiga sahun masu bin maganar iyayensu."

Bai iya cewa komai ba sai kifa kai da yayi akan cinyarta yana sheshekar kuka. Ita ma nata hawayen take yi saboda nauyin raba wannan abota. A bangaren Munzali kuwa shi ma kwanciya ya yi yana jin yadda hawaye suke gangarawa cikin kunnuwansa.

*

Gari ya waye yau ta kama litinin. A garin Kaduna Mardiyya da Sauda sun shirya sun tafi makaranta. A Kano ma Ayaah tana shirin tafiya tasu makarantar. Dukkaninsu suna aji shida ne a makarantar sakandire. Kwanaki kalilan suka rage su fara jarabawar NECO. Ayaah bata sami damar yin JAMB ba sabods rashin kudi amma su sunyi.

Kunun tsamiya Ayaah ta damawa Anti Hasiya kafin ta fita. Tana sanye da farin dogon wando da shudiyar rigar da ta kawo mata har gwiwa sun sha karin guga. Fitina irin ta dalibai rigar ta kamata tsam sai ka rasa yadda ma take iya numfashi.

A gaban Anti Hasiya ta durkusa da flask din kunu tana tambayarta ko ta zuba mata kafin ta tafi makaranta.

Yamutsa fuska Anti Hasiya tayi saboda rashin dadin baki. Jikinta gabadaya babu dadi ta rasa gane a wace duniyar take. Tunda aka sallamota ta kasa tabuka komai a cikin gidan. Daga amai sai kwanciya. Ita ce zazzabi ita ce ciwon kai. Honourable kansa ya zama kamar mai jinyar. Hasiya ita ce zuciyar gidansa. Matar rufin asiri ce wadda baya fatan ya shiga cikin sahun mazaje masu butulcewa a lokacin samu. Shi da yaransa duka rige rigen kyautata mata suke yi. Ga Abbas an sanya ranar aikinsa

nan da sati hudu. An hado shi da magunguna kuma ana ganin amfaninsu. Sai da ta gama yi mata fadan dinkin rigarta wanda bata san lokacin da aka tsuke shi ba da kashedin tana dawowa yau ta bayar a budeta sannan ta bata amsa.

"Kadan zaki zuba amma ki matsa min lemon tsami a ciki"

Ayaah ta fiddo ido waje ba shiri da taji abin da ta ce.

"Tsamiyar ta fito fa yadda kike so. Don Allah ki hakura ki sha a haka."

"In kin tafi ma Murja zata bani, gara ma ki saka min kawai."

Rabin wani dan karami Ayaah ta matse mata sannan ta dauke ledar lemon tsamin ta tura a jaka akan idon Anti Hasiya.

Ita kuwa ta marairaice mata saboda tsamin kadai ke taimaka mata ta sanya wani abu a cikinta.

Murja da ta zama raguwar karfi da yaji saboda tsabar tausayin halin da antinsu take ciki ta taso za ta duba jakar Ayaah ta dauki lemon tsamin. Ayaah ta galla mata harara tana kankame jakarta. Cikin fushi ta ce no

"Tunda ba ke za a haifawa kanin ko kanwar ba ai gara ki bata tasha ta haifo mai yamushasshiyar fata irin na Altine. Kin manta yadda muka dinga tsoron daukar dan saboda kamaninsa da tsofaffi?"

Murja ta ja tsaki "sai aka ce miki lemon tsami ne ya busar masa da fata?"

"Idan ma dai ba shi kadai bane wallahi kika bata bayan na tafi makaranta ban yaf..."

Anti Hasiya bata san lokacin da tayi murmushi ba.

"Ya isa Ayaah ba ma zan sha ba kada Allah Ya isan ta bini nima."

Duk sai suka yi dariya har Ummi da ke wankin wake. Bayan fitar Ayaah shiru Anti Hasiya tayi tana mai al'ajabin kudurar Ubangiji. Watanni biyu da suka wuce idan ance Ayaah zata sauko daga dokin da ta hau su zauna lafiya zata karyata. Sai gashi cikin lokaci kankani da ta dage da addua da kuma bin shawarwarin Salima komai ya sauya. Ko yanzu sai dai tayi ta hamdala ga Allah. Rayuwa kam tayi juyin alkhairi dasu. Zuwan Minister Abdulkarim ya kawo musu canji a rayuwa. Abbas ana sa masa rai da samun lafiya. Kan 'ya'yanta kuma a hade yanzu sannan uwa uba wannan gagarumar kyauta ta samun ciki.

Ayaah na adaidaita sahu wayarta ta dauki ruri. Lokuta da dama tafiyar kafa take yi kusan mintuna talatin a hanya zuwa da dawowa. Yanzu kuwa kudin mota na sati aka bata wannan satin. Mamakin mai kiranta da sanyin safiyar nan me ya kama ta. Cikin aljihun wandonta inda ta boye wayar ta zura hannu ta lalubota. Dama ta tafi da ita ne domin kawarta ta saka mata fim. Sunan Dani ta gani baro baro a jiki. Gabanta ya yi mummunar faduwa da ta tuna haduwarsu ta karshe. Amma abin da yafi tsaya mata a rai kuma ya sanyata tsorata bai wuce fuskar wannan saurayin da taji kannensa sun kira shi da Ya Suhaib ba. Ta shaida irin bacin ransa lokacin da Dani yake neman tabata. Tayi ta kokarin hana kanta tunanin abubuwan da suka faru ranar sai gashi wannan wayar ta dagula mata lissafi.

Wani kiran ne ya sake shigowa wancan na tsinkewa. Numfashi ta sauke da karfi sannan ta amsa. Cikin kwantacciyar muryar da ya saba hillatarta da ita ya yi magana. Sai dai wannan karon fushi ya nuna mata.

"Baby ni zaki kai gidan kakanninki ki wulakanta?"

Daburcewa tayi ta ce "wulakanci kuma Dani? Me nayi maka?"

"Au tambayata ma kike yi? Don na bude miki cikina kin san sirrin gidana shi ne kika kira yayanki yazo ya wulakantani. Me ya hanaki tsayuwa kiyi masa bayanin alakarmu banda kina min kallon dan iska?"

Gabadaya hankalin Ayaah sai ya tashi ta soma bashi hakuri. Ya dinga ja mata rai har sai da direban adaidaita sahun ya dan waiga ya kalleta saboda jin yadda take magiya.

A gadarance Danliti ya ce "Abu daya ne zai sa na hakura Baby. Zan zo makarantarku na daukeki anjima ki zo ki gaishe da Mummy"

Da murnar ganin rikicinsu yazo karshe Ayaah ta ce "ta dawo ne?"

"Ta dawo kuma na fada mata komai game dake. Tana son ganinki ne domin gobe ta yiwa kawunnai na magana. Wikent (weekend) dinnan sai su zo su ga Baba asa mana rana."

Dan jim Ayaah tayi kafin ta ce "yanzu makaranta zanje kuma gaskiya Anti Hasiya ba za ta yarda na bika ko ina ba."

"Matar da kika ce bata sonki."

Ita ta fada masa da bakinta amma da ya maimaita sai da taji mugun haushi. Yanzu kam uwa ta dauki Anti Hasiya kuma ba za ta yarda wani ya fadi maganar batanci akanta ba. Kwalla taji a idanunta ta daukesu da yatsanta. Danliti tuni ya gane zuciyarta a karye take. Hakuri kawai ya bata ya cigaba da dorata a keken bera.

"Ban san me nayi miki wanda ya dauke duk wata daraja da girmana da kike gani ba a baya. Ni dai alfarma nake nema ko daga makarantar ne ki zo muje taga zabina. In Allah Ya yarda nan da sati biyu ko ba ayi biki ba na tabbata an daura mana aure"

Sunan makarantar ta bashi tare da fada masa yadda zasu hadu idan an fito break karfe goma da minti arba'in da biyar.

Goma daidai Suhaib yana cikin wani gareji a unguwar Na'ibawa wanda ya dace da kwatancen da Danliti ya yi masa. Wani Dan bumburutu ya samu ya kai shi wurin tun daga gadar da zata sada bako da farkon garin Kano daga titin Zaria. Garejin nasu sananne ne saboda kusancinsa da babban titin fita gari. Matafiya da yawa suna tsayawa ko a dauko musu makanike daga nan. Bayan ya sallami yaron da ya kawo shi ya karasa wurin ma'aikatan da suka yi da'ira ana ta mayar da zance da wani Alhaji.

Sallama ya yi musu sannan ya ce "Don Allah Danliti nake nema."

Kusan mutum hudu a tare suka ce masa ya fita. Wani ne ya kara da cewa,

"Kaima wani abu ya hadaka dashi ne?"

"Eh" Suhaib ya ce kai tsaye ganin kowa ya zuba masa ido da alamun bacin rai.

Taron sai ya karkato ya hada dashi inda a take yaji rigimar da ake yi. Motar da ya gama gyarawa ya dauka ya sanar da abokinsa na garejin wai budurwarsa ce bata da lafiya a makaranta shi ne zai je ya kaita gida.

Gaban Suhaib ya yi muguwar faduwar da bai san ainihin dalilinta ba.

"Don Allah waye ya san inda zan same shi?" Ya kara da cewa "me yace sunan budurwar?"

Abokin masa da aka tsare yana bada amsa kamar shi ne Danlitin ya dan jinjina kai kafin ya ce "baby dai naji yana ta cewa. Amma kafin ya tafi ya kira wani abokinsa da suke yawan zuwa nan tare Rabilu ya ce masa wai yau zai rufe shafin Ayaah. Sai dai gaskiya ni ban san abin da yake nufi ba."

Kwatanta irin rudanin da Suhaib ya shiga ba zai misaltu ba. Su kansu mutanen wurin sun tsorata da yanayinsa. Musamman da ya ce,

"Ku san yadda zaku yi ku hadani dashi kafin ya cuci yarinyar mutane domin wallahi idan ya taba mutumcinta gabadayanku sai na daureku."

Hargaginsa bai basu damar binciken ko shi waye ba. Suturarsa da motar da yazo da ita sun ishesu amsa. Dan garejin nasu da bai taka kara ya karya ba basu ga mai kwarjinin ja da Suhaib din ba. Shi ma kuma mai motar da Danlitin ya dauka yabi bayan Suhaib ya ce kararsa zai yi. Saboda haka nan da nan wurin ya kacame ana tattauna yadda za a same shi tunda yaki daukar waya kafin ya ida nufi.

BABI NA SHA HUƊU.

***

Da sallamar da ya san babu mai amsawa ya murda hannun kofar dakin. Fitila a kunne take da alama cikin sauri aka manta ta. Ga kaya watse a ko'ina. Riguna ne da wanduna harda kwalaban turare na jiki da na kaya. Salihi ya yi ajiyar zuciya ransa duk babu dadi. Da kunnuwansa yaji Mubashir yana waya da abokinsa suna shirya yadda zasu fita party shadayan dare. Bai yi masa magana ba domin yana son tabbatarwa kansa Mubashir din zai je ko kuwa. Fitar da ya yi niyya ya fasa ya zauna a gidan ba tare da sanin dan nasa ba. Goma da rabi kuwa sai gashi ya fita daga gidan da sand'a a zatonsa babu kowa sai Ummule da ta dade da kwanciya.

Wata leda mai kyau Salihi ya gani a saman tebur din da Mubashir yake ajiye tarkacen makarantarsa. Ya dauka ya bude yaga sababbin takalma kala biyu da risit din sayayya. Abin da aka kashe na sayayyar ya girgiza shi. Bill ne na dubu casa'in da yan canji a sayayyar kaya. Shi dai bashi da kudin da zai iya bashi ya yi sayayya mai tsada haka. To a ina ya sami kudin?

A dakin yayi zaman jiransa har bacci ya kwashe. Goshin asuba ana tsaka da kiran sallah sai gashi ya shigo da sand'a. Rufe kofar yayi da sauri ya murda mukulli sannan ya kwantar da bayansa a jikinta yana ajiyar zuciyar tsira.

"Allah Ya soni Baba bai tashi ba"

"Ko kuma ni Ya soni da na kwana a dakinka ba."

Wani wawan juyi Mubashir ya yi a matukar razane yana kokarin murda mukullin kofar ya fita amma ya kasa. Ilahirin jikinsa babu inda baya ji yana rawa.

"Juyo ka dubeni Mubashir."

Maimakon ya juyo sai ya cigaba da kokarin fita har Salihin ya tadda shi inda ya juya masa baya. Hannunsa dake rike da mukullin ya kama ya rabasu da yatsun nasa. Sau daya ya murda su duka suka ji sautin budewar kofar. Mubashir dake faman gumi zuwa yanzu ya sake kama hannun kofa wannan karon. Shi fa burinsa ya bar gaban uban ko ta wane hali. Saboda shi da kansa ya san cewa bai taba yin laifi kwatankwacin wannan ba, shi yasa hankalinsa gabadaya ya tashi. Gani yake suna hada ido zai gano duk abubuwan da suka wakana a wurin party din.

"Irin wannan patin kuke kira till dawn ko?"

Shiru babu amsa daga Mubashir kuma har yanzu hannunsa yana jikin hannun kofar amma ya daina murdawa.

"Ban hanaka zuwa ba jiya bayan na gama jin shirinka da wani a waya."

Ras, ras, ras...haka gaban Mubashir ya cigaba da faduwa yana sauraron mahaifinsa a tsorace.

Salihi ya daure zuciyarsa iyakar dauriya saboda warin hayaki iri iri da yake ji a jikin Mubashir. Da wahala idan bai sha kayan maye ba ko tarkacen hayakin. Sassauta murya ya yi sai ka rantse kuka ne zai kwace masa a kowane lokaci.

"Tsakaninka da Allah Mubashir idan ka kwatanta abin da akayi a wurin da kaje da tarbiyar addini da ma maslahar zamantakewar dan Adam kana tunanin Annabin Rahama zai yi maraba da kai?"

Fada, mari, zagi, tsinuwa ko duka sune abubuwan da yasa rai dasu. Ko kadan bai yi zaton wadancan kalaman ba. Daga kai ya sami kansa da yi ya kalli babansa. Duk wani zafin kai na matasa sa'anninsa sai ya kufce masa. Rashin kunyar da aka koya masa koda zata baci irin yanzu yaji babu guda da zai iya. Allah SWT Yafi komai da kowa. Sunansa kadai da aka ambata gami da kwallar disappointment a idanun mahaifinsa sun dagula masa lissafi. Ba yadda ya iya dole ya girgiza kai a matsayin amsa ga tambayar da aka yi masa. Ta yaya ma zai yaudari kansa yace inda yaje bai sabawa musulunci ba?

Kogin tunanin da ya fada da mabambantan yanayin dake bayyana a fuskarsa kowace dakika sun sanyaya ran Salihi. Alamu ne na cewa tarkonsa ya kama kada. Da shirinsa ya shigo dakin Mubashir domin yana fata yau ta zama rana ta farko kuma ta karshe da irin wannan fadan zai shiga tsakaninsa da dansa. Wayarsa ya kunna har yanzu suna tsaye a bakin kofar ya kunno abin da yake so ya nuna masa. Bidiyo ne wanda ke nuni da jama'a suna jam'in sallah. Bayan kamar sakan goma anyi kabbarar dagowa daga sujjada amma wani matashi a sahun gaba bai tashi ba. Koda aka sallame aka duba ashe rai yayi halinsa. Mutane suka yi ta kabbara da ambaton Innalillahi.

Mubashir bai san lokacin da ya soma kuka wiwi ba yana cewa,

"Baba kaga fa ya rasu"

"Kamar haka ne ajali ke riskar kowane bawa a lokacin da bai yi zato ba. Da ace naka lokacin yayi a jiya karshenta da sai dai yanzu a kirani inda kaje party ace inzo in karbi gawa" tsigar jikin Mubashir ta tashi da tunanin hakan kawai.

Salihi kuwa dafa kafadarsa ya yi suna fuskantar juna.

"Abin tunani shi ne da ace kaine na cikin bidiyon nan da kila har nima na koma ga Allah ina bada labarin mutuwarka. Kai nayi imani 'yan bakinciki sai sun mutu saboda sun san cewa nayi babban rabo. Ranar lahira mune 'yan hura hanci saboda nayi

dacen samun dan da Allah Yake so har ya karbe shi a sujjada. Haka zaka karbi cetonmu ka kaimu aljanna idan ayyukan alkhairinmu sunyi karanci" Sai da ya ja numfashi sannan ya dora da "da kuma ace ka mutu a wurin patin haka zanyi ta boye fuska kada idon sani su ganni. Kuma ina mai imani da cewa zan dawo gida nayi ta gillawa mutane karya. Ba zan taba yarda a san a inda ajali ya riskeka ba. Kaga anyi biyu babu. Ka tafi a banza ka bar ubanka zai tafi a hofi tunda ya zama makaryaci"

Jikinsa Mubashir ya fada yana kuka duka jiki na bari. Salihi ya dinga bubbuga masa baya da rarrashi. Sai da ya kula nutsuwa ta zo masa sannan ya yi masa tambayar da ta zo masa a ba zata.

"A ina ka sami kudin da kayi waccan soyayyar? "

***

Bacci mara dadi Uwani tayi sakamakon abubuwan da suka faru a gidan Munzali jiya. Da suka dawo gida tare da Asabe tayi mamaki sosai da Innayo bata tambayeta daga ina suke ko dalilin fitarsu tare ba. Kalmar 'kema 'yarki ce' da Munzali ya yi amfani da ita lokacin da yake cewa ba zai roketa rufin asirin Qibdiyya ba tayi mata karan tsaye a wuya. Makomar rayuwar yarinyar a gaba ya sanyata cikin damuwa. Shikenan rayuwarta ta baci tun yanzu? Sai kuma nata 'ya'yan da basu wani dameta ba suka fado mata. Anya ta ma san wani abu cikin rayuwarsu sama da dan abin da ba a rasawa? Irin abin da kowa ma zai sani muddin ya zauna dasu. Ita dai a matsayinta na uwa ba za ta dorar da komai ba. Babbar 'yarta Amira ta tuna. Yarinyar da har almajiri take sawa yi mata tsarki lokacin da take karama saboda bata son tashi daga kemis dinta. Sai ta bawa almajirinta mukullin gidanta ya tafi ya gyaro mata jiki su dawo. Kudi ne kawai a gabanta sannan bata son mai aiki mace don kada ta dauke hankalin mijinta. Ta biyun kuma Anisa a lokacin tata kuruciyar wani kanin Salihi da yake karatu ta sakarwa ragamarta. Sai da Salihin ya yi mata tatas lokacin da ya farga. Idan ma da mugun nufi kila har anyi an gama. Yaran basa kaiwa shekara biyar take barinsu su fara wanka. Saboda ita ce Uwani ina kika fito neman kudi, ina zaki neman kudi. Mubashir ne ma ya dan samu kulawa a matsayinsa na dan fari kafin ta gaji ta watsar. Duk wannan tunanin sai ya kare a inda take ganin cewa ai kudi take nema musu.

'Kudin da baki iya kashe musu' zuciyarta ta tuna mata.

'Kudin da suke neman salwanta a banza?'

Kamar an tsikareta haka ta tashi firgigit ta janyo wayarta. Nambar Habibu ta dannawa kira ta kara a kunne. Ta shiga har ta katse bai dauka ba. Ta cigaba da gwadawa missed calls sun kai goma zai gani amma duka shiru. Lokaci ta kalla sai taji bari tayi masa uzuri kila bai tashi ba. Nan kuma ta canja akalar kiran ga Salihi. Kiran yaje gareshi lokacin da Mubashir cikin kuka ya fada masa da kudin wa yayi sayayya. Sam bata yi la'akari da cewa yanzu ake sallar asuba ba. Kudadenta kadai take tunani.

Yana amsa kiran Uwani ta hau fada kamar ta ari ba. Bakinta yana kumfa saboda tsabar bala'i amma ko jan numfashi ta gaza yi.

"Wallahi Salihi ka fadawa matarka ta dawo min da kudadena da sarkoki. Ba yau muke tare da kai ba na san baka taba daukar min komai ba idan baka dashi. Ka fada mata ta dawo dasu idan ba haka ba police station zan kai maganar nan su kwatar min hakkina"

Ba speaker Salihi ya saka ba amma yadda Uwani take daga murya babu abin da Mubashir bai ji ba. Jikinsa sai ya sake yin sanyi. Kunyar mahaifinsa ta sake lullube shi. Hannu yasa ya karbi wayar ya kara a kunnensa.

"Umma ni na dauki kudin da sarka sai dai abin da ya rage babu yawa."

Yana gama magana ya mikawa Salihi wayar ya shige bandaki. To shi ma dai Salihin bai ce komai ba ya katse kiran ya fita yin alwala.

Uwani tafi minti biyar a zaune da waya a hannu. Ta san waye Salihi. Ta san abin da zai yi da wanda ba zai yi ba. Sanya Mubashir karbar laifin da ba nasa ba baya cikin abin da zata taba yarda zai yi. Idan ta kure zai iya karbar laifin amma ba dai yace wani ya karba ba.

'Mubashir?' ta dinga maimaita sunan a zuciyarta kamar yau ta fara ji.

"Kai! Ina! Sata?"

"Idan kin gama surutan ki tashi kiyi alwala ko ki rufe mana baki muyi sallah a nutse"

Juyawa tayi taga Innayo akan abin sallah. Bata san lokacin da ta shigo ba. Da azamarta ta tashi amma ta kasa fita yin alwalar. Kanta ya dauki mugun caji ne yana daf da bugawa. Yadda zuciyarta take zafi ko duka aka yi mata da itacen darbejiya ba za ta ji wannan radadin ba. Ayi maka gagarumar sata kuma ka gane dan cikinka ne ya aikata? Kamar sakarya haka ta dan tsaya galala da ta tuna yace abin da ya rage saura kadan. Tuntuni satar bata wani dameta ba saboda tasa ran Ummule ce. Ko ana tsiya tsiya sai ta fito da kudin domin kararta zata yi. A kwato mata kudinta sannan a nunawa Salihi kuskuren tunanin zai iya mata kishiya ya kwana lafiya. Jikinta, zuciyarta, ruhin dake rike da ranta da ma tunaninta a take suka koma na kankanuwar yarinyar dake tsananin bukatar mahaifiyarta. Ji tayi kamar an mata tsirara duk sanyin duniya ita yake duka. Uwa ce kadai zata fahimceta ta suturta ta. Aikin da take takama dashi karshenta sun rabu kenan, kudin da ya rage dan cikinta ya sace. Kudin Hajji kuma wani sashe na zuciyarta mai dan hankali ya dage akan ta nemi Habibu komai rintsi. Zargin da mijinta yake masa ya sanyata wasiwasi. A zatonta a dake ta soma magana, bata san tun a kalmar farko komai nata ya ruguje ba.

"Kiji wani abin mamaki Innayo. Sata aka yi min ta kudade masu yawa da 'yan sarkokina wai amma Mubashir yace shi ne. Ni kuwa me nayi masa da zai min sata irin wannan? Na wahala sosai ina hada kudin nan" sai hawaye sharrrr kamar famfo.

"Allah Ya kyauta. Matsa zan tayar da sallah."

Uwani ta girgiza kai ta dafa kafadun Innayo "baki gane ba Innayo. Ba labari nake baki ba ya faru ne a gaske. Kudin nan dashi nasa ran biyan KNUPDA su sakar min gidana. Bani da komai duk na kashe a gini da biyan Hajji. Wurin aikin ma sun dakatar dani saboda mugunta irin ta masu kudi."

Salima da Zara duk sun ji maganganun Uwani. Salima sai ta kasa hakuri ta shiga dakin. Da Innayo suka hada ido saboda ta juyawa Uwani baya tana share tata

kwallar. Kwalla ce ba ta tausayin Uwani ba kadai harda ta kara ganin girman Allah. Soyayyar 'ya'yanta bata hanata hango cewa abin da ya sami Uwani harma da matsar bakinta ta tonawa kanta asiri duk yana cikin sakayyar Allah ba. Irin wannan lokacin take ta jiye mata. Halin rayuwa ya juyo wanda zaisa ta dawo gareta ba domin Allah ba.

Kai Salima ta girgiza mata don ta daina hawayen sannan ta da daga hannuwanta sama tana dariyar takaici.

"Allah Ya jikan Hasiya ba don ta mutu ba. Ta ce Allah Ya hadaki da babun da kike yawan kira watarana. Yau gashi kun gamu har ta fara saka ki kuka. To kadan ma kika gani wallahi" tayi kwafa da karfi "Baki ga komai ba. Uwa? Ke har kina tunanin kin ci bulus kenan akan hawayen Inn.."

"Salima ya isa!" Innayo ta fada tana riko hannunta.

Hannun ta janye ta cigaba da tsayuwa a gaban Uwani.

"Ki barni in sauke mata kafin Hasiya taji banyi komai ba tayi min Allah Ya isa."

"Nace ya isa haka. Idan kuma kema shaidanun ne dake shi yasa ku ke neman hanani yin sallar asuba to Bisimillah"

Bayan tafiyar Salima har Innayo ta idar da sallah Uwani tana tsaye. Da gaske kanta ya rikice har bata iya gane mai yake faruwa a kusa da ita. Zuciyarta ta kasa rabe mata tsakanin sace kudin da wanda ya sata wanne yafi dimauta hankalinta. Kai a takaice ma duk wani labari mara dadi da ta samu game da dukiyarta sai yanzu ya yi zaman dirshan a kwanyarta kamar wadda ta farka daga magagin bacci.

*

Da Innayo ta idar da sallah ta zauna tana addu'o'inta amma hankalinta yana kan Uwani. Abin da take gani shimfide akan fuskarta yafi karfin damuwa sai dai a kira shi tashin hankali. Tausayinta ne ya tsirga mata. Sai kuma kamar wadda aka girgiza tayi kokarin kawar da tausayi daga zuciyarta. Uwani ce fa! 'Yar cikinta wadda ta wahaltawa amma ta dinga wulakanta ta. Kalmar wulakanci ita ta dace da duk abubuwan da ta dinga yi mata a baya. Ta tuna mugun ciwon hakorin da idan ya tashi sai ta kusa fitsari a jikinta. Amma Uwani ta rufe ido tace bata da kudi. Kuma taki kaita ganin likita don kada a alakantasu da juna. Duk wata soyayya da uwa zata yiwa da itama tana yiwa Uwani, amma hakan ba zai sa zuciyarta ta kankare mikin da ta bar mata ba. Ba za ta taba yi mata baki ba amma ta san cewa lokaci zai musu alkalanci. Tana so Uwani ta rarrabe tsakanin zare da abawa, me yiwuwa hakan zai sa tayi hankalin da ta jima tana yi mata fata. Da wannan ta mike domin tunaninta ya karkata zuwa ga autarta magamin kukanta. Hasiyatu mai zuciyar zinare. Hasiya takwarar Asiya matar da ta gagari shaidancin Fir'auna. Jarumar matar da ta zama majinginar Annabin Allah Musa AS. Ita Innayo taga ranar sanyawa yaro sunan magabatan kwarai. Ta kasance cikin farinciki domin kuwa da kyawun hali da addu'a gashi matsalolin gidan Hasiyan sun kau. Suna cikin ganiyar samun rufin asiri, ana saka rai da samun lafiyar Abbas, gashi zuciyar Ayaah ta karkato daga hudubar shaidan. Sannan uwa uba ga rabo Allah zai basu na zuri'a.

"Salima idan kin sallami 'yan makarantar (yan matan 'ya'yanta) nan ki zo ki tayani yiwa kanwarki dambu."

Zara sai tayi saurin tashi ta goya 'yarta "Kawo in yi mata Innayo."

"Yi zamanki kada ki kwasar mata sanyi sanyin safiyar nan"

Kwance goyon tayi ta kwantar da ita a kusa da Salima.

"Gata nan bari inje in taya Innayo aiki"

Bata jira cewarsu ba ta fice. Tana isa rumfar da suke amfani da ita a matsayin madafi ta dinga share kwallar dake bin idanuwanta. Ita Zara me zata ce da duniya banda NAGODE. Ta koyar da ita darasi mai wuyar fassara. Mijin da take takama dashi har take wulakanta mahaifiyarta dominsa ya juya mata baya. A zahiri ya nuna mata har yanzu yana sonta. Amma ko kusa yaki sab'awa mahaifiyarsa akanta. Yaki kawo mata 'ya'yanta sannan yaki sanyawa jaririyarta suna. Innayo ce ta tsaya mata

har tayi masa magana akan haka. Wayarsu ta karshe da ita bayan ta gama sauraron bayaninsa abu daya ta fadawa Zaran wanda ya sakata zubar da kwalla.

"Biyayya yake yiwa mahaifiyarsa wadda komai rashin dadinta gareni da tawa 'yar dole muyi hakuri. Ita Uwa ta wuce tunanin duk mai tunani. Allah ne kadai Ya san fadi tashin da tayi dashi kafin ya kai yanzu. Idan na ce ya sab'a mata dominki ina ganin ban yi musu adalci ba. Ki mikawa Allah lamuranki ki zuba ido ki ga yadda Ubangiji Yake shigarwa bayinSa fadan da yafi karfinsu"

Da yammacin ranar Innayo tayi sadakar kosai tayi tawassuli dashi akan nemawa Zara zabin alkhairi.

Kukan da tayi a ranar ko digo bashi da nasaba da halin da take ciki da mijinta. Hawayen na nadama ne da dana-sani. Sai kuma tsantsar godiya ga Allah da Ya ara musu rayuwa ita da Innayo din. Dole ne tayi amfani da wannan damar ta daidaita da mahaifiyarta.

Bata ji isowar Innayo ba sai muryarta da taji tana cewa "kin tuna lokacin da ake cewa kin fi kowa iya girki a gidan nan? To kiyi mata farfesu da naman kazar can na firij, ni kuma zanyi dambun. Duk na wanda tafi ci to mai shi tafi iya girki sai a daina cika mana baki."

Zara ta juyo da murmushi mai hade da hawaye. Innayo din ma da guntuwar kwallarta domin kuwa ta dan jima tana kallonta.

Abin da ba kasafai mutanen da suke yi ba Zara tayi a lokacin. Rungume Innayo tayi tana cigaba da kukanta. A haka take magana da dusashshiyar muryar da ta cakude da kuka.

"Don Allah Innayo ki ce kin yafe min. Ba wai don na koma gidansu Maryam ba. Sai don kawai wannan kullutun hakkin naki da na daukarwa kaina ya sauka daga kirjina"

Ta dago kai tana mai nuni da kirjinta.

"Na sani sarai cewa ban kyauta ba amma kaina na yiwa ba ke ba. Don Allah ki yafe min."

Innayo ta dan tura baki duk ta rikice da kunya "to cikani don Allah kada a ganmu"

"Sai kin ce kin yafe"

"Zara zan ci kaniyarki fa. Cikani nace"

Zara ta cikata tana dariya kasa kasa.

"Baki ce komai ba."

Innayo ta numfasa tana kallonta tana girgiza kai tare da murmushi.

"Indai nice ki sani cewa hatta waccan yayar taku mai rangwamen tunani na dade da yafe mata. Babban burina dama bai wuce ku fahimci kuskurenku ba. Wallahi Zara ba kudinku nake so ba. Ku din da na haifa a halin maraici ba uwa ba uba ku nake so."

Kwalla ta sake taruwa a idon Zara. Innayo kuwa sai tayi gaba ta fara tattaro abubuwan da take bukata na girki. Yau dai gidan Hasiyan zata je da kanta ba aike ba.

Da suka gama Maimuna ce ta daukar mata kwandon da aka zuzzuba abincin. Kiranta tayi a waya tace ta nemi izinin mijinta yau sai gidan Hasiya. Zara da Saliman sun so zuwa ta hana. A cewarta bata son yawo kawai don suna gida. Wuraren shabiyu suka fita.

***

Awa guda da fitar Ayaah, Hasiya ta kula da 'yar pos dinta a inda ta durkusa ta zuba mata kunu. Dauka tayi ta bude taga 'yan kudaden da basu kai dari uku ba a ciki. Ta san ba za su wuce kudin motarta bane ta manta a gida. Idan kuwa haka ne in ba a kai mata ba karshenta ta dawo a kafa ko ta kare da rance. Wannan ma bai dameta ba sai da taga takardar da Ayaah ta nannade kudin WAEC dinta a ciki dubu sha biyar. Daren jiya Honorable ya bata saboda yau din ne rana ta karshe da zasu biya. Duk da tana jin jiri haka ta daddafa bango ta tashi tana kiran Murja da Ummita.

"Don Allah wata cikinku ta zo tabi Ayaah makaranta da pos dinta da ta manta."

Murja ta ce yanzu suka yi waya da wata mata zata zo kitso. Ummita na jin haka ta san ita ce mai zuwa. Hanzarin shiga wanka tayi ta fito ta shirya da sauri. Bata son lokacin break ya yi taje ta wahala wurin neman Ayaah cikin dalibai. Idan ta isa da wuri ajinsu kadai zata nema.

Ta gama shiri ta fito Honourable ya bata kudin adaidaita suka ji sallama. Direban Minister ne wato Abdulkarim. A soro suka hadu da Honourable Habu ya mika masa wani envelop.

"Oga ya ce jiya likitan Abbas ya turo masa. Gwaje gwaje ne da ake son ku sake kai shi ayi yau dinnan. Idan sakamakon ya fito zasu gane aikin da za ayi dole sai an bude kan ko kuwa irin wanda ake soka na'ura ne tayi. Ya ce kuje kai tsaye ya biya kudin."

Honourable Habu ya ma rasa irin na'u'im godiyar da zai yi. Shi kuwa direba fadi yake ai bai ga komai ba cikin dimbin alkhairin wannan bawan Allah.

Direban na fita Ummita ta fito. Riga da siket ne a jikinta na atampa. Ta yane kanta da mayafin pashmina wanda ya sha jiki ba laifi. Sai dai a wanke yake ya kuma sha guga.

Ta hango mota a farkon layinsu ikayar inda mota ke tsayuwa amma bata yi mata kallo biyu ba ma. Kanta a kasa tana tafe hankalinta yana kan cimma titi da wuri ta sami abin hawa. Bayanta gefenta taji ana horn sai ta kara rabewa kusa da kwatar

dake gefe, a zatonta ko ta tsaya akan hanyar motar ne. Sake horn aka yi ta kuma matsawa. Da aka yi na uku sai ta juya baya cike da tsiwa. Direban na bude kofa ta ce,

"Malam ko kwatar kake so na fada ne sannan ka sami hanyar wucewa?"

Ganin dan dattijon da ta gaisar dazu tare da mahaifinta sai kunya ta kama ta. Kasa tayi ta rissina mayafinta ya rufe mata gefen fuska ta sake gaishe shi tare da bashi hakuri. Murmushi ya yi don ko da ya dameta da horn din sai da Maigidansa ya ce kada ya firgita 'yar mutane.

"Shigo a rage miki hanya"

Girgiza kai tayi da sauri "Baba zai yi fada. Na gode"

Abdulkarim yaji abin da tace sai yaji ta burge shi. Idan bai yi kuskure ba ita ce Ummi babbar diyar Honourable. Bude bayan ya yi ya fito da kafarsa daya ya tsaya.

"Zo muje a fara sauke ki ina sauri ne."

Yawu ta hadiya da kyar da taga mai maganar. Sake yin kasa tayi zata gaishe shi ya ce,

"Shigo motar sai mu gaisa"

Ummita ta daburce "Allah Baba da Anti Hasiya sun hana"

Abdulkarim sai ya dauki waya ya kira Honourable Habu. Yana tsaye bai mayar da jikinsa ciki ba har wayar ta shiga. Gaisawa suka yi sannan ya kada baki ya ce,

"Tare muke da Mal. Amadu amma sai nace kada ya fada muka ina mota saboda bana son ka fito da safe haka. To yanzu mun hadu da Ummi nace ta shigo mu kaita inda zata je amma taki. A takaice dai neman izini na kira"

Honourable ya dan ji nauyi domin harga Allah baya son take dokarsa. Sai dai kuma yana kyautata zato ga Ministan. Ba wai kuma don sakar masa bakin aljihu da yayi yanzu ba.

Tuntuni bai taba saninsa da mugun hali ba. Duk da dadewarsu basu hadu ba, baya jin zai kira shi domin neman izinin cutar masa da 'ya.

Dariya ya yi ya ce "Tana karkashin ikonka babu ruwana."

Kallonta Abdulkarim ya yi tana kallon kasa ya ce "to sai ki bar kirgen kasar kizo mu tafi ya bayar da izini"

Ummita ta dan tsuke baki tana mamakin salon yadda ya yi mata magana kamar yaji haushin kin shigarta.

Daya barin ta zagaya zata shiga amma ga mamakinta sai taga kofar baya a bude. Direban ta kalla galala tana ware idanuwanta ta dan rage murya ta nuna kofar a tsorace.

"Wai nima bayan zan shiga?"

"Baki yarda da azkar dinki na safe ba kenan, ko baki yi bane kike wannan tsoro?"

Mamakin wannan Minista yana neman zauta ta. Shi da yake abokin babanta ya akayi yake yi mata magana kamar ta yiwa tsaranta laifi? Kuma ma da wane kunnen yaji abin da ta fada a hankali.

Dan murguden bakin da tayi duk akan idon Abdulkarim din. Dariyarsa ya gimtse don kuwa da gayya yake yi mata magana a haka. Baya son ta shigo a darare kamar tana tare da uba. Bashi da masaniyar ko anyi mata miji amma haka nan yake jin wani kwarin gwiwar tunkararta. Idan da mijin a hannu sai ya hakura. Bai san lokacin da dariya dai ta subuce masa bane a yayin da ya hangota ta kai hannu baki tayi tofi. Ba kunya tabi jikinta ta shafe ta kuma tofawa motar sannan ta shiga da kafar dama gami da Bisimilla da dan karfi. Har ta shiga yana dariya.

Mal. Amadu ma sai da ya dara. Ta zauna a dofane tana kallonsu. Dariyar masu kudi ma daban take, babu sauti mai karfi ko hargagi ta ayyana a ranta. Tambayar da ya yi mata ce ta maidota hankalinta

"Wai me da me kika karanta kika tofa mana ne?"

"Su Au'zu bi kalimatillahi...." Sai tayi azamar dora hannunta akan labbanta "ba daku nake ba. Tunawa nayi ban yi ba kafin na fito"

Hannu ya mika mata yana murmushi "to sai ki bani abin sadaka ladan yi miki tuni ko. Don da farko na zata mu kike tofewa don kada mu gudu dake."

Mayafi ta janyo abin da ya lura ko dabi'arta ne ta rufe rabin fuska tana dan murmushi.

"Wai ya sunanki ne?" Ya tambayeta saboda yana son sake jin muryarta.

"Ummita"

"Ummi-ta? Tawa kenan ko ta mutane da yawa?"

Hanjin cikinta taji ya yi wani juyin waina a tanda ta manta da kunya ta kalle shi cikin ido. Ba shiri ta sauke nata ta dukar da kai kamar mai shirin kwanciya akan cinyarta.

Basu sake magana ba sai kwatancen da take yi har suka isa makarantar. Ga mamakinta dana Mal. Amadu sai suka ji Abdulkarim yace a jirata.

Ta kusa minti ashirin a cikin makarantar kafin ta fito a guje tayi bakin titi. Shaf ta manta da wanda ya kawota kuma yake jiranta. Hannu bibbiyu tasa tana tsayar da adaidaita sahu. Abdulkarim na ganin yanayinta harda hawaye kwance a fuskarta ya fito da sauri.

"Ummita"

Ganinsa yasa kukan nata ya karu. Ta dawo da baya suka hadu domin shi din ma nufota ya yi. Kafin ma ya tambayeta ta fada masa abin da ke faruwa.

"Ba a ga Ayaah ba. Wai ta kusa awa biyu da fita fitsari har yanzu bata dawo ba. Kuma ga jakarta a ajin. Anje duka bandakunan da lab da ko ina bata nan" shirun sakan biyar tayi wani tunani yazo mata "ko dai aljanun bandakin sun dauketa?"

"Bama mutane ba aljanu Ummita?" Abdulkarim ya tambayeta yana kada kai don kada ta saka shi dariya a halin da ake ciki "Muje bandakin mu duba. Allah Yasa dai kin iya rukiyya sai na tsaya daga bayanki ko?"

Duk da tashin hankalin da suke ciki bai hanata fassara shi a ranta ba. 'Mutumin nan ba dai bakar magana ba'. Ita da kanta kuma ta hango wautarta ta ce,

"Ko masu satar mutane" ta dan tafa hannu irin na ta canka daidai "ai fa an ga kana zuwa gidanmu shi kenan za a fara kawo mana hari."

Abdulkarim bai ma san lokacin da ya ya balla mata harara ba.

"Ji mun yarinya. Ni kuma zaki dorawa laifin?"

"To ai ..."

Kai ya girgiza kawai ya ce ta zo su koma cikin makarantar. Suna tafe zuwa ofishin Principal ta daga waya zata kira gida ya hanata. Idan sun san aihinin me yake faruwa sai su fada. A haka hankula ne zasu tashi babu sanin madafa.

A ofishin Principal din banda ita akwai malamai biyar ana ta mayar da zance. Kowa ya shiga rudani har wasu suna cewa a tashi yaran kowa ya tafi kada a hada dasu. Yana shiga mutum uku suka gane ko waye. Da radar da bata buya ba suka sanar da ragowar. Nan da nan kuwa aka dinga raba idanu tsakaninsa da Ummita wadda ke biye dashi sau da kafa. Kallon ne ya tunzura shi kafin ma ya tambayi ya ake ciki ya fara da bayanin da ya baiwa Ummita dasu kansu mamaki.

"Wannan 'yar tsohon Ubangidana ce. Mun dade da rabuwa sai kwanakin nan Allah Ya sake hadamu. Yanzu ma daga gidansa nake kuma da izininsa muka taho nan."

Principal sai ta hau borin kunya "ranka ya dade me ya kawo wannan bayanin?"

Ya dage kafadu sannan ya ce "zuciya abar banza ce wani zubin. Yanzun nan sai ta shiga yiwa mutum sake sake ta sanya shi zargi a gurbin da bai dace ba."

Kowa kuma sai ya shiga gyara tsayuwa ana gyaran murya. Bai kulasu ba ya tambayi ba'asin sanda aka farga da batan Ayaah.

Bayanin da aka yiwa Ummita aka sake yi masa. Ya gyara zama tamkar a ofishinsa ya nuna wani Malami.

"Kirawo min Maigadinku"

"Su uku ne"

"Duka su biyoka sai ku saka wasu malamai a wurin saboda kada yaran su fice"

Masu gadi duk sun tsumu kowa ya rantse bai ga fitar wani bako ba ko na dalibar da ake magana a kai. Guda cikinsu yafi kowa dagewa aka rantsuwarsa. Gashi a shekaru alamu sun nuna ya girmi wadancan sosai. Yadda ya gabatar da kansa ya sanya Abdulkarim dora masa ayar tambaya. Dalilinsa kenan ma na daga waya yace zai kira Kwamishinan 'yan sanda domin a zo ayi bincike.

Hakuri aka soma bashi ya rufe ido yana fada akan sakacinsu da amanar 'ya'yan mutane.

"Idan sun zo zasu tafi da masu gadin a kullesu na a kalla sati koda an ganta kuwa. Wannan ai sakaci ne da rashin sanin aiki."

Dan dattijon maigadin yana jin haka ya soma muzurai. Rashin fara'a da ya gani ko digo a fuskar bakon nasu ta tsorata shi. Haka kawai da iyalinsa azo a kulle shi yana zaman zaman sa. Hularsa ya cire ya dan firfita fuskarsa wadda ta soma tsatatsafo da gumi sannan ya rankwafo a gaban Minista.

"Yallabai ai ba ayi haka ba. Yarinya dai babu wanda ya saceta. Duba min nan..." Ya zaro wata kodaddiyar naira dari biyu "ka gani wani matsiyacin Alhaji ne yazo da katuwar mota ya dauketa. Wannan abar ya iya bani don na barta ta tafi da alkawarin zata dawo kafin a tashi."

Dan ofishin Principal a take ya karade da sallallamin malamai mata da fadan malamai maza. Dattijo kamar a cinye shi danye. Principal ta ce barin aikinsa yazo domin bata san tun yaushe ake haka ba.

"Wallahi Hajiya yanzu ma tsautsayi ne. Wata yayi nisa nayi haka ne da tunanin zan dan samu na cefane. Ni yarinyar ko wayewa da fuskarta ma banyi ba sosai."

Ummita dai sai kuka kawai take yayinda Abdulkarim ya ce ba zai tafi ba har sai 'yan sanda sun zo.

***

Goshi Suhaib ya dinga murzawa ya rasa wane irin tunane ya kamata yayi. Ta ina zai fara nemanta? Baya son Munzali duk da ya san 'yar yayarsa ce amma yana gudun halin da zasu shiga kafin a ganta.

"Idan ta bishi kanta ta yiwa" ya furta a zafafe. Sai dai kuma can kasan zuciyarsa ya san cewa ba zai taba iya kawar da kai ba. Haka kawai yana zamansa yarinyar tayi masa karan tsaye a rayuwa. Banda mahaifiyarsa da kanne babu wata mace da ya taba damuwa da shirginta sai wannan yarinyar mai idanu a tsaye.

Mota ya shiga ya zauna ya bar abokan aikin Danliti da mayar da zance. Kusan minti goma ya yi kansa na kan sitiyari yana tunanin mafita kafin dabara tazo masa. Waya ya dauka ya kira nambar Ayaah yana ta addu'ar ta dauka.

***

Kokarin danne tsoro Ayaah take yi amma ya bayyana karara. Ta fara nadamar biyo shi tun kafin su bar layin makarantarsu amma ta rasa bakin cewa ya tsaya ta sauka. Banda ragon azanci ta yaya ma zata je gaishe da suruka da kayan makaranta? Idan matar mai hankali ce tana ganinta karshenta tayi mata fada.

"Wai ina zamu je ne naga muna yin bayan gari."

"Walalamb'e" Danliti ya bata amsa kai tsaye.

"Walame?" Ayaah ta tambaye shi da sauri don tana jin kamar bata ji me yace bane da kyau.

Danliti ya sake maimaitawa wannan karon harda dariyarsa.

"Kada ki damu Baby. Yanzu zaki gani da idanunki."

Tun daga Hotoro ta daina gane ina suke tafiya. Ta dai ga wani roundabout daga nan suka yi hagu gefen wani gidan mai. Jikinta ya yi sanyi kalau kamar mara lafiya. Gashi yau gabadaya tsoronsa ma take ji. Suna zuwa kofar gidan zata gudu kawai. Don kada ya gane ta kakalo murmushin dole. Ana haka 'yar wayarta ta soma vibrating. Bata san nambar ba amma da sauri ta dauka. Don ta san yanzu da wuya idan ba a fara nemanta ba.

Danliti bai damu da wayar da zata amsa ba saboda ya gama yanke hukuncin cewa ko me zai faru yau sai ya kusanceta. Ikon a hannunsa yake kamar yadda ya fadawa kansa.

Da sallama ta dauki wayar, muryarta tana dan rawa.

Suhaib yana jin yanayinta wani abu ya taso masa a kokon rai.

"Ayaah kina tare da Danliti? Zaki iya magana sosai?"

"Eh amma ba zan iya ba" ta amsa masa tana kokarin kin kallon inda Danliti yake.

"Kin gane ni ko?"

"Eh"

"Good, ki saurareni da kyau kuma kada kiyi abin da zai gano ki. Mutumin da ya daukeki wallahi makanike ne yanzu ma ina garejinsu. Mutumin banza ne. Ya fadawa abokin aikinsa zai zo daukarki ya kaiki inda zai..." Sai ya kasa karasawa.

Ayaah ta sake tsorata sosai jikinta ya soma rawa. Yawu ta hadiya da kyar a hankali ta ce "ba na fada miki mumminsa zai kaini na gaisar ba? Yanzu muna hanyar gidansu ne. Kar ki bari a gane bana aji kinji"

Ba karamin burgeshi yaji tayi ba. Ga tsoron yana iya rarrabewa cikin zancenta amma a haka ta fada masa abin da ya dace ya sani.

"Na fahimta. Ki kokarta ki turo min address din inda kuke ta sms saboda kada ya gane."

"In sha Allahu. Ni dai ki dauko min jakata ki jirani a bakin gate ko an tashi."

Danliti ya dan kalleta ya murmusa yana kiran "Baby na kenan! Ki gama wayar nan ki fada min kalaman da zasu sanyaya min rai"

"Kiji min dan iska..."

Saboda yanayin da take ciki murmushi kadai ta iya yi amma duk da haka Suhaib yaji sautinsa. Shi kuwa gogan ya zata dashi take.

"Dariya ma na baki?" Suhaib ya ce yana shan kunu

"A'a. Don Allah ni dai kiyi sauri. Zan turo miki nambar registration din tawa ki cike min form din."

Kafin ya ajiye wayar ya sami kansa da cewa "Ki kula da mutumcinki Ayaah. Kada ki yarda ya taba min jikinki."

Shi da ya fada ya yi mamakin karfin halinsa sai dai kuma yanzu ba lokacin hakan bane. Haduwar kwana daya ce amma zuciyarsa taki bashi hadin kan yakiceta daga tunaninsa.

Ita ma a nata bangaren wani irin nauyi kalamansa suka yi mata. Haka nan ta cije ta sake yanko karya ta fadawa Danliti bayan ta kashe wayar.

"Wai nambarmu ta NECO ake bukata daga ofishin Principal. Shi ne kawata ta kira don kada a neme ni."

Mutumin da ko sakandiren bai gama ba sam bai fahimci karyar ba. Hankalinsa bai bashi yasa ido akan abin da take rubutawa ba. Iya abin da ta gane a hanyar da suka bi da sunan unguwar da ya fada wanda bata ma rike daidai ba ta rubuta.

Suhaib ya koma wurin sauran makaniken ya karanta musu text dinta.

"Da mamaki dai amma wannan kwatancen ya dace da hanyar gidansa. A can unguwar Walalamb'e yake da zama"

"Muje ka nuna min"

Mutum uku ne suka shiga motar. Harda shugabansu cikon na hudu. Rayukansu duka sun baci akan abin da yake yi. Ga daukar abin hawan masu kawo gyara sannan kuma ya dauki mace yana shirin bata mata rayuwa.

*

Bangaren inda suka nufa wawakeken filin unguwa ne da gidaje tsilli-tsilli basu matse juna ba. Gidajen wurin kaf babu bene ma a iya ganinta. Duk sunfi kama da gidajen gargajiya. A takaice dai unguwa ce ta masu karamin karfi sosai. Cikin Ayaah ya sake kullewa da mugun tsoro a lokacin da faka motar a kofar wani dan tsakon gida.

"Ina ne nan?" Ta dan dake ta tambaye shi.

"Gidan mai ban ruwan fulawa a gidan Mummy. Kiyi hakuri zan shiga in duba shi ne yanzu na fito"

Tunda dai bai kirata ba sai taji dama dama a ranta. Fita ya yi ya rufeta a cikin motar ya shige gidansa da sauri. Mukullin dakin Rabilu abokinsa da ya bashi aro tun jiya ya manta a aljihu yazo dauka. Sun yi da Rabilun can dakinsa dake kusa da unguwarsu Ayaah zai kaita. Kuma idan shi Danliti ya gama biyan bukatarsa da ita shi ma mai dakin zai yi.

Kafin ya fito ta sake turawa Suhaib wani sakon.

(Ya kulleni a mota wai wani wurin zamu je ba inda na turo maka ba. Don Allah kayi sauri wallahi tsoro nake ji.)

(Ki kula da duk inda kuke bi ki sake turo min. Please take care of yourself.)

Amsar ta karanta ta gyada kai kamar yana kallonta.

A ciki kuma matar Danliti da murna ta tashi tana yi masa maraba ya doka wani uban tsaki da ya saka ta ja da baya. Naira dari biyu irin wadda ya bawa maigadin makarantarsu Ayaah ya jefa mata a wulakance.

"Gashi nan na san abin da kike yiwa kenan. Ke dai a baki kudi ku ci abinci da 'ya'yanki."

Hawaye taji ya taho mata tayi saurin tarewa da hannunta. Kudin ta duka ta dauka ta ce,

"An gode. Allah amfana"

Tsaki ya sake yi mata ya shige daki yana neman wandon da ya cire jiya. Ita kuma mayafinta ta zara a kan igiya. Ta goya karamar ta rike hannun mai wayon ta fice tana ce masa zata karbo kayan miya.

"Na ajiye mota a waje ta mutane. Kada ki kuskura kije kusa da ita. Ke dawo idan na tafi sai ki fita."

Sarai ta ji abin da yace amma tayi biris ta fita soro ta leka. Abin da tayi tsammani ta samu. Yarinya ce mai fuskar kamala a cikin motar. Takaicin halinsa ya turnuketa. Babu wani bakon abu a halayyarsa da bata sani ba. Bakon abin da shi bai sani ba tare da ita shi ne a yau ta gama hadiyar bakincikinsa in Allah Ya so. Komawa tayi cikin gidan suka yi kicibis a bakin kofa. Rai a bala'in bace ya dinga yi mata masifa.

"Me yasa kika fita? Da kika fitan me yasa kika dawo?"

Hakuri tayi ta bashi tana cewa taji kamar ya kirata ne. Sai da ya gama fadan ya koma dakin yana cilli da kaya.

"Me kake nema ne in tayaka?"

"Mukullin dakin Rabilu nake nema wanda na bari a cikin wando"

Kai ta jinjina tana tunanin wato can zai je da yarinyar. Dauko mukullin da ta gani da tana ninke wandon tayi ta mika masa. Haka ya warce shi a hannunta ya fita da gargadin ta jira sai ya tafi.

*

Sakon da Ayaah ta turawa Suhaib ya riske shi ne suna kurkusa da unguwarsu Danliti. Tun fitowarsu har yanzu bai fasa ambaton Allah cikin addu'a da fatan nasara

ba. Da ya gama tura mata amsa ya sanar da abokan tafiyar tasa abin da ta ce. Guda a cikinsu sai ya ce su karasa gidan nasa. Kila suyi sa'ar samunsa ko su tambayi matarsa ina yake.

"Muna ma iya cewa ta kira shi ta ce anzo nemansa akan motar da ya dauka da 'yan sanda. Na san da wuya idan bai tsorata ba"

Shawararsa ta sami karbuwa suka karasa. Da yake Allah Maji roko ne sai gashi sun sami fiye da abin da suka saka rai.

Wanda ya bada shawarar ne ya yi sallama a kofar gidan. Ta fito da yaranta da 'yar ghana must-go wadda ta zubawa kaya. Ta ganinsa ta dan saki fuska suka gaisa. Ba tare da bata lokaci ba ya ce,

"Idan kin san inda Danliti yake ki fada min don Allah. Daga gyaran mota ya dauko motar wani mutum. Yanzu haka yace 'yan sanda zai kawo mana."

Sauke jakarta tayi daga dakalin kofar gidan tana cewa "ba zan fada ba don laifin nasa ya kara yawa a dukkan dakikar da 'yan sandan suka wahala nemansa. Sannan idan kun hadu ka fada masa ya aiko min da takardata."

A rikice ya ce "kiyi hakuri ki taimaka mana"

Su Suhaib suka firfito ta dubesu ta kau da kai.

Suhaib din ne ya tako gabanta ya dubeta a mutumce ya ce "don Allah ki taimakeni kada ya keta haddin 'yar mutane. Har makaranta ya bita ya daukota yana shirin bata mata rayuwa."

Da sauri ta dago kai tana mai tono yarinyar da ta gani.

"Bari na shiga adaidaita sahu ku biyoni in kaiku inda nake tunanin zai kaita"

Suhaib ya ce na gaban ya koma baya ita da yaranta su zauna. Su da suke makanikai basu fitar da warin jiki irin nata da na yaran ba. A haka kuma ba karamin kokari take ba. Duk albashin Danliti a cin banza da hofi sai yan mata yake karewa. Sabulun wanka da wanki sai tayi kamar ta ari baki. Ruwa ma iya na girki kadai yake saya mata. A haka take cancanawa suyi wanka bayan kwana bibbiyu ko uku. Ga zafin gari da ake fama.

Kai kawai Suhaib ya dinga kadawa cikin takaicin wai wannan matar aurece. Mace da ake son a mutunta amma ita ce nata mijin har yake da guts din zuwa kofar gidansa da yarinyar da zai nema ta gani. Kodayake ba kansa farau ba da ya tuna nasa uban. Neman tsari ya dinga yi akan fadawa wannan kaba'ira ta zina har suka kai kofar dakin Rabilu. Ya kuwa laluba aljihunsa ya bawa yaran dubu goma ya ce ga kudin mota. Bata cuci kanta ba ta karba tana ta godiya.

***

Da kuka Ummita ta shiga gida duk da irin gargadin da Abdulkarim ya yi mata akan tayarwa iyayenta hankali. Kasa daurewa tayi tana shiga ta fada kan Innayo tana kuka. Hasiya ta saki cokalin dambun da take ci ta tashi da sauri tana tambayarta me ya faru.

Maimuna da Innayo basu dade da shigowa gidan ba. Kuma hirar dadewar Ummita da rashin samunta a waya ake yi sai gata ta fado.

"Ki yi min magana Ummita me ya same ki?" Hasiya ta sake tambayarta tana hawaye tun kafin taji me ya faru.

"Anti an sace Ayaah. Har makaranta wani yazo ya bawa maigadinsu kudi ya tafi da ita"

Hankalinsu ashe bai tashi da kukan Ummita ba sai yanzu da tayi magana. Kan kace meye wannan gidan ya rude da kukan mata. Murja, Hasiya, Ummita da Maimuna babu mai rarrashin wani. Innayo ce tayi ta maza ta daure tana basu hakuri. Suna kukan suka ji sallamar Honourable da yaron da ya taya shi rike Abbas suka je aka yi test. Kukansu ya saka shi shigowa tun kafin su amsa. A nan yaji labari mara dadi. Gidan ya sake cika da Larai (mahaifiyar A'i) dasu Hasina kannenta. Sun zo duba Abbas ne saboda Honourable ya fada musu za ayi masa aiki. Wannan ya sake dagula lamarin domin fada ne kuma yaso kacamewa.

Larai tana kuka ta ce "Hasiya naji labarin kina da ciki ai. Wato kafin ki haifa zaki fara daidaita 'ya'yan marigayiya saboda kina tunanin samun gado tunda maigidan ya soma farfadowa."

Hasiya bata iya cewa komai ba da yayyenta suka hada baki ana ta fada mata maganganu. Innayo ta hana Maimuna da ma Murja da Ummita din mayar da martani. Batan Ayaah ne a gabansu ba zantuka marasa amfani a gaban suruki ba. Maigidan kansa kasa tsawatarwa ya yi saboda yawunsu da kuma damuwar da yake ciki. Tunda ya ce suyi shiru suka ki sai kawai ya fita zai tafi makarantar. 'Yar nutsuwar da ya samu ma ta biyo bayan kiransa da Abdulkarim ya yi suka shigo gidan tare. Shi ya fada masa case na hannun 'yan sanda ana bincike. Ko sau daya babu wanda ya yi tunanin kiran wayarta saboda gargadi da jan kunnen da Hasiya take mata akan zuwa da ita makaranta. Duk sun zata wayar tana gida saboda haka babu amfanin kiran.

***

"Shigo mana Baby" Danliti ya ce da Ayaah bayan ya zura mukulli ya bude dakin shagon Rabilu.

Rainin wayon nasa ne ya bata mamaki ta ce "ban gane in shiga ba? Ya zaka ce min zan je gaishe da mahaifiyarka ka kawoni nan?"

Hagu da dama ya dan waiga bai ga idon kowa a kansu ba kawai ya fizgota cikin dakin ya rufe kofa. Budar bakinta zata yi ihu ta rufe sakamakon tozali da hoton tsohon saurayinta Rabeel (Rabilun Danliti).

Cikin kidima ta ce "Dani dama ka san Rabeel?"

Danliti ya kwashe da wata irin dariya harda tafa hannuwa kamar biri a hannun mai wasa dashi.

"Idan ya shigo anjima zai yi miki bayanin da zaki gamsu. Ni nan cire hijabi zaki yi mu farantawa juna rai."

Kallonsa tayi taji dukkan wata tsana ta duniya ta tattara a kansa. Ga haushin rashin hankalinta da ta bari ya yi wasa da tunaninta.

"Ashe abin da aka fada min gaskiya ne duk da dama bana tunanin mai fadar zai yi min karya."

Danliti bai wani damu da maganarta ba ya kama kayan aron jikinsa ya soma cirewa. Ayaah ta juya ta fara dukan kofa da ihu taji ya daka mata tsawa.

"Juyo nan ki gani"

Ta juya a fusace ai kuwa tayi tozali da kakkaifar wukar da yake nuna mata. Shi ma cikin fada ya ce,

"Ki kama bakinki ko idan na gama wallahi in kashe ki in kashe banza."

Durkusawa tayi a wurin ta fashe da kuka "me nayi maka da ka zabi cutar dani?"

Kishingida ya yi akan katifar daga shi sai singileti da gajeren wando masu dan banzan datti yana wasa da tsinin wukar ya zuba mata idanu. Sau daya ta kalle shi

taji amai ya taso mata. Wani uban gashi ne a hammatarsa wanda da gani har kitso zai yi.

"Bana son munafunci bayan na san kema kina so. Banda gulma me zai sa ki biyoni wai zaki gaishe da Mummy? Ni Innata tana kauyenmu."

"Naji na cuci kaina don Allah kayi hakuri ka barni na tafi"

Danliti ya sake yin dariya "dama ai ba kwana na dauko ki kiyi mana ba. Za dai mu gwangwaje a jikinki ne kawai mu kaiki gidan tsohonki." Kula ya yi kamar tana danne amai ya dinga dariya "wai nan kyamata kike ji? Tabdi. Yarinya wannan jikin yau zai kafa miki tambarin da har ki mutu ba zai goge ba"

"Allah Ya fika" ta ce cikin kuka tana tofar da yawu."

"Ke dai anyi azzaluma. Kina ta kada jiki a gabana amma kin kasa karasowa ki bani kasona? Ki taso kafin na farde kayanki da wukar nan"

Duk wata magiyarta bata yi tasiri ba. Gashi babu halin buga waya. Karshe kayanta ya umarceta da ta cire ta zo ta same shi akan katifar. Da taki ya taso ya kamata ya tsarge hijabin ya wurgar dashi. Ayaah ta fashe da wani irin marayan kuka mai ban tausayi. Duk wata hudubar Anti Hasiya ta dinga dawo mata. Matsatsiyar rigarta ya gani yana karewa surar jikinta kallo harda lasar labba. Ta sake dukawa tana bashi hakuri ya dagota ta mike ya dalla mata mari saboda ransa ya kai makura sannan hakurinsa ya kare.

"Ni ban daukoki domin na gwada miki karfi ba. Soyayya mai zafi nake son mu shayar da juna amma kin tsaya kina neman yi min taurin kai. Wallahi idan kika bari na saka miki karfi yau ko uwar da ta haifeki ba za ta ganeki."

Hankadeta gefe ya yi ya koma ya kwanta rigingine da wukarsa a gefe ya dauko tecno dinsa ya kunna wata mahaukaciyar waka ya kure sautin.

"To maza ki cire kayan ki zo muyi rawa."

Ayaah taga cin mutumcin da tozarcin nasa sun wuce tunaninta. Yadda zata samu ta karbi wukar hannunsa ma dabara ta kare mata. Bata daddara ba kawai ta juya tayi masa ba zata wurin dukan kofar dakin da hannuwa biyu, iyakar karfinta. Danliti ya taso a guje bayan ya jefar da wukar zai kamota. Iskancin nasa na matsorata ne domin kuwa yana tsoron 'yan layin su farga a dauki mataki. Sun saba kawo yan matan da suka amince ne ba jjc irinta ba.

*

Ayaah na wannan bugun Suhaib na gama mikawa matar Danliti kudi. Kusan a tare shi da tawagar makanikai da ita suka kalli kofar. Baiwar Allah sai ta kada danta tabar wurin. Duk lalacewa bata son yaron yaga ubansa a yanayin da ta tabbatar zai shiga na muzanci nan da dan lokaci.

Jikin Suhaib na tsuma ya karasa jikin kofar suna biye dashi ya soma bugawa iyakar karfinsa.

Danliti da Ayaah suka kalli kofar a tare. Dankwalinta da gashinta ya hada ya yiwa mugun riko dama yana shirin fizga yadda zata ji zafi aka yi bugun.

"Waye?" Ya tambaya muryarsa ta fito kamar ta kyanwa don ya tsorata.

Ogansa ya yiwa Suhaib alamar ya yi shiru sannan shi ya yi magana da kaushin murya.

"Mutumin banza bude ka bani mukullin mutane don tare muke da 'yan sanda"

Yawu ya hadiya ba shiri " 'yan sanda kuma?"

Sake buga kofar Suhaib ya yi da karfi Danliti yaji kamar ya saki fitsari a wurin. Yana can hankalinsa a rabe da tunani bai farga ba Ayaah ta dauki wukar da ya yar sai kawai gani ya yi ta nuna shi da ita.

"Ko ka bude kofar nan wallahi ko na burma maka wukar nan a cikinka"

Shi ya jiyota, na waje ma kowa yaji abin da ta ce.

Jikin kofar Suhaib ya raba da sauri ya ce "Ayaah?" da taushin murya.

Kuka ta fashe dashi tsabar farinciki "na'am?"

"Kada kiyi abin da zamu yi regretting kinji ko?"

Kai ta gyada tana wani kukan ta dubi Danliti "ka bude ni"

Gaba kura baya sayaki. Wukar hannunta bata dame shi kamar jin muryar shegen yaron nan ba. Idan bai bude ba ma zasu balle kofar ne ayi masa abin da aka ga dama. Saboda haka babu yadda ya iya haka ya zura mukullin ya murda kofar.

Mukullin yana yin karar ta bude kafin ma ya zare sakatar da ya saka ta sama yaji sun yi baya tare da kofar. Wawan bugu Suhaib yayi mata da kafa sai da ya jijjigeta gabadaya ta balle. Ayaah na ganin hasken waje bata yi wata wata ba ta danna kai a guje sai ji tayi sun yi karo da mutum har suna shirin faduwa. Dole ya saka hannuwa ya tarota. Tsigar jikinta da nasa suka tashi lokaci guda da suka hada ido cikin ido karo na farko tun haduwarsu.

Da sauri Suhaib ya sanya hannu ya rabata da jikinsa. Kallo guda ya sake yi mata ya runtse idanu. Rigarta ko kadan bata dace da ganin idanunsa ba balle na wasu. Bai yi tunanin komai ba ya shiga balle maballan shirt din jikinsa. Rigar dogon hannu ne da

ita. Cireta ya yi ya rage farar T-shirt din jikinsa. Ayaah bata ankara ba taji ya dora mata rigar ta gaban kirjinta.

"Rufe jikinki ki jirani a waje" ya ce ba tare da ya kalleta ba. Da sauri ta fice kuwa ta koma gefe tana share hawaye.

Kansa tsaye ya fada cikin kazamin dakin mai warin kazantar kaya da ta fasikancin da aka jima ana yi a cikinsa. Da kafa ya doke kofar daga kan Danliti yasa kafarsa dake cikin hadadden cover shoe ya danne tsakiyar kafafun Danlitin.

Razanannen ihun da Danliti ya yi sai da yaje kunnuwan makotan shagon. Mutane suka firfito ana kallon ikon Allah. Ayaah kanta durkushewa tayi ta cusa yatsunta a cikin kunne. Tsinuwa da zagi kala kala daga bakin jama'a ana fadin yadda suka mayar da dakin dandalin yan mata.

Suhaib kuwa bai ragawa Danliti ba don ko kadan bai yi niyar cire kafarsa nan kusa ba. Ogan makanikan ne ma ya ji tsoro yaje ya riko shi.

"Yallabai ka yi hakuri ka bari a hadashi da hukuma kada ka dauki mataki a hannunka."

Kamar ba zai dauke kafar ba sai ya cire. Sauran mazan kamar su ya yiwa suka dinga sauke ajiyar zuciya. Suhaib ya shammacesu ya sake daga kafar kawai kuma buga masa. Ihun Danliti har yafi na dazu don suma ne kawai bai yi ba saboda azaba.

Biyu cikin makanikan suka leka waje wurin Ayaah.

"Ki zo ki yi masa magana kada yayi kisa"

A hanzarce ta tashi ta koma kofar dakin. Ta san sunan shi tunda kannensa sun fada taji. Amma bata san ita me ya dace ta kira shi ba. Wasu hawayen ta goge ta sami kanta da cewa,

"Yaya"

Suhaib ya juyo ransa a matukar bace

"Ban ce ki fita ba?"

"Ka zo ka kaini gidanmu don Allah"

Yadda tayi maganar da sanyin murya ya taba shi sosai. Cije lebensa ya yi don bai so barin Danliti haka ba ya biyo bayanta. Haka ya tasata a gaba har bakin motarsa don baya son kowa yaga bayanta. Da kansa ya bude motar har ta shiga sannan ya rufe ya zagaya barin direba ya zauna. Yana tuki yana kula da hawayen da take gogewa lokaci-lokaci da rigarsa mai kamshi. Sai da suka bullo titi ya yi mata magana.

"Ina zamu bi?"

"Dama"

Shiru ya sake mamaye motar na 'yan dakiku sannan ya ce,

"Ba kya jin magana ko? Abin da ya faru shekaranjiya bai isheki ba sai da ki ka biyo shi"?

Da jajayen idanunta da suka rine saboda kuka Ayaah ta dube shi.

"Kayi hakuri don Allah."

"Ya tabaki?" Ya tambayeta idanunsa na kallon titi.

Ta girgiza kai tana wani kukan. Ba don sun zo ba da yanzu tana can ya gama da ita.

"Dago kanki ki dinga yi min kwatance"

Umarninsa tabi ta dinga kwatanta masa har suka shiga layinsu. Nan ta tarar da motar 'yan sanda har biyu a kan layin.

"Kinga abin da kika janyo a gidan ko?"

"Ai ba zan kara ba"

Suhaib ya taka burki ba shiri ya kalleta "tunanin karawa dama kike yi?"

"A'a" ta amsa masa da sauri.

Da ya tsaya tare suka fito daga motar. Shi da ita duka kunyar suturar jikinsu ta kamasu.

"Kinga abin da kika ja mana ko?"

Kunkuni yake don bai san da yaya ma zai shiga gidansu ba. Tsayuwa ya yi a hanya yace ta karasa. Tayi narai narai da idanu za ta yi kuka.

"Don Allah kazo kayi musu bayani. Yau ina jin Baba sai ya yi min duka."

"Banda abinki Ayaah, ance miki bana so a dake ki ne?"

Baki ta bude amma bata iya cewa komai ba ta rufe. Ta zata ba zai karasa din ba sai gashi ya cigaba da bin bayanta har kofar gidan. A tsorace ta saka kafa sai ta dawo da baya. Gabanta ke faduwa bata san abin da iyayenta zasu yi mata ba.

"It will be okay. Ki shiga"

"Wallahi zuciyata kamar za ta fito ta baki."

Tausayi ta bawa Suhaib sosai. Bai san tun yaushe take ta kuka ba yau ga wani ta fara na tsoro. Rab'awa ya yi ta gefenta ya shiga kofar farkon sosai.

"Assalam alaikum wa rahmatullah."

Murya tafi biyar da ta amsa. Amma a ciki Ayaah ta bambance ta babanta da Anti Hasiya.

BABI NA SHA BIYAR.

***

Abbati ya zagaye gidansa yafi a kirga. Babu wani lungu da sako da bai leka ba bayan fitowarsa daga wurin Baaba Mari. Akwai wuraren da rabonsa da taka kafarsa tun ana ginin. Wasu irin tunane tunane suka dinga zarya a cikin kansa. Son muhallin nasa ya darsu a zuciyarsa irin wanda bai taba ji ba. Sai idanu sun zaga sosai a cikin garin nasu ma za a sami gida makamancin nasa. Lallai shi yasa ake cewa idan an ga matashi da kudi bayan bashi da kwakkwarar sana'a ya kamata a bincike shi.

To wai ma ya aka yi bai taba jin korafi ko da wasa game da tarin arzikinsa da wadak'ar da yake da kudi ba a garin? Ko ana tsegungumi a bayan idonsa ne bai sani ba? Yau daya da ya yiwa gidan kallon tsanaki sai ya fahimci yawan titsiyen da Baaba Mari take yi masa akan wurin aiki. Wajibi ne uwa ta matsu da son jin silar rayuwa irin tasa.

Ga gida ga motoci ga kudi kamar bai san ciwonsu ba. Samarin garin da dama idan sun kawo kawunansu ko iyayensu sun musu jagora akan ya saka su a hanyar sana'arsa sai da ya cikasu da kudi. Ana karbe kudin zaka ga mutum ya ja gefe an koma kasuwanci ko a cinyesu a banza. Ya gode Allah da ya kasance ba shi da

alhakin sanya d'an kowa a layinsu. Da yanzu bai san yadda zai yi da lodin zunubai ba. Ga nasa da yake fatan samun gafara ga na wasu da babu lallai su so tuba.

Kan kasaitacciyar kujerar kushin din dakin da aka yi domin kwanciya ya tafi ya kwanta rigingine. Tunani bai barshi ba har ya luluka yana tuna masa yadda aka yi suka kawo zuwa yanzu. Yayinda Munzali ya zama mukullin bude masa wannan duniyar, shi Abbati, shi ne ya fara mayar musu da ita sana'a a lokacin da Munzali ya kwanta ciwo. Shi ne ya nemi Shazali wanda ya kaishi wurin wani babban mutum.

Tunanin komai da kowa ya yakice ya sanya kansa a faifan zuciyarsa yana tuhuma. Shin yana wannan dabiar ne a matsayin sana'a ko matsayin namijin da yake jindadi mu'amala da jinsinsa? Amsarsa ita ce zabi na biyu.

Hakika ya yi mugun sabo da wannan dabi'a wadda ta sanya har yanzu sha'awar mu'amalar ta kan taso masa. A kalla kusan bayan kwana bibbiyu ko uku ya kan sami kansa a mugun yanayin son wannan abu. Yana jin wahala har ma ya kai ga siyan magani don wani zubin ko bacci kasawa yake. Haka kuma take a wurin Munzali shi ne ma dalilinsa na biya musu makudan kudade domin samun lafiya. M

Matsalar irin wannan zinar ya wuce mutum ya tashi watarana kawai yace ya tuba. Ita jiki take bi tana yi masa illah. Idan bukatarta ta taso mutum dole ya nemi hanyar biyanta ko ya wahala. Allah ne shaidarsu amma rabonsu da neman juna tun gabanin ciwon Munzalin. Shamaki ne Allah Ya saka musu sannan Ya maye musu zukata da tsaftatacciyar kaunar juna domin lokaci irin wannan.

Duk wannan abu zuciyarsa bata fasa fada masa cewa shi din har yanzu namiji bane. Soyayya dai ta zuciya da zuciya Farha yake yiwa. Tunaninta kadai sai da yasa tsigar jikinsa ta tashi. Yana sonta da dukkan abin da zuciya za ta iya bawa wanda take kauna. Burinsa na duniya akan mace ahi ne ya mallaketa a matsayin matar aure. A wayi gari wasu yara suna kiransa Baba suna kiranta Mama.

Duk mazan da yake mu'amala dasu kallon maza yake yi musu. Mata kuma suna nan a mata. Bai taba sanya kansa a ajin 'yan daudu ko wadanda suke karyar cewa da son jinsinsu aka haifesu ba. Shi lafiyayyen namiji ne wanda ya mayar da kusantar maza 'yan uwansa sana'a. Idan babu namiji zai rayu sarai da mace sai dai kawai illar wancan abu zai dinga damunsa kafin Allah Ya yaye masa jarabar.

Infact yana daga cikin dalilansa na cigaba da zama da Hanne duk irin rashin dadin zamansu kuwa. Tuntuni auren ya wuce na umarnin Mal. Sa'idu, domin kuwa a irin kudinsa da ya saketa idan har da mai ce masa don me ba zai wuce Baaba Mari da Gwaggo Jummai mahaifiyarta ba. Sauran kowa so yake ya zo ya auri tasa 'yar. Abin

da ya hada auren nasu ma tuni an manta dashi. Shi da ita suna zaune ne kawai saboda auren rai gareshi. Babu soyayya, babu shakuwa sannan babu damuwa. Gara ma shi yana bata kulawa domin sauke nauyin hakki. Ita kuwa tsakaninta dashi bai wuce kudi idan har ta neme shi. Ga misali yanzu rabonsa da gida tun asabar daga zuwa daurin aure. Amma har yau ko flashing bata yi masa ba.

A kasalance ya tashi ya shiga hada kayansa na sakawa a wasu manyan akwatuna. Ya zabi aikin ne domin rage radadin rashin Munzali da Qibdiyya. Sai dai ko kusa bai sami abin da yake so ba. Komai ya taba indai nasa ne to Munzali ma yana da irinsa sak. Haka ya gama loda kaya masu muguwar tsada a jakunkuna da akwatuna ya jeresu a gefe. Sai da ya gama da nasa ya soma tunanin ta ina zai fara sabuwar rayuwa? Duk abin da ya mallaka da kudin zina mafi muni ne don haka dole su rabu.

To yanzu me zai ce da duniya? Yaya mutane zasu kalle shi? Da ya dauki aniyar sauya rayuwarsa sai ya ga ashe abu ne mai matukar wahala. Ashe rayuwar da ya bari lokacin yana dan shekara goma sha biyu sai bayan shekaru ashirin da hudu zai cigaba da ita. Abbati almajiri ne zai taso ya dora rayuwarsa daga inda Abbatin Munzali ya yi masa katsalandan. Abin da wuya....da matukar wuya.

Shaidan ya shiga kai kawo wurin nuna masa tarin kalubalen da zai fuskanta da zarar ya sanya kafarsa a waje. Ya shawarta zuwa ya baiwa Baaba Mari hakuri akan ta barshi da iya abin da ya tara yafi a kirga amma ya fasa. Dukiyar ta haram ce. Indai ba yana so daga shi har mata da 'ya'yan da yake fatan haifa a gaba su zama cikin wadanda Allah ba zai ji kukansu ba dole ya hakura. Shaidan din yana nan amma so da addu'ar uwa sun yi matukar tasiri a zuciyarda da gaske Allah take fuskanta. Faduwa ya yi cikin sujjada domin neman karfin zuciya daga Sarkin dake jujjuya zukatan bayi.

"Ya Rabbi kada Ka barmu. Idan Ka barmu munyi asara. Allah Ka haska min hanyar da zata bulle dani kamar yadda nake fatan Ka haskawa Munzali. Duk wani abin da zai lullube mana zuciya daga barin yi maka da'a Ya Allah Ka nesantamu dashi. Ya Allah Ka jagoranci sabuwar rayuwarmu kada Ka kunyata tubanmu a duniya da lahira. Ya Allah Ka rufe sirrinmu kada Ka bari mu tozarta a idon duniya."

Adduarsa kenan. Kuma ya yita cikin kuka da kankantar da kai hade da yakinin ganin kudurar Ubangiji akan lamarinsu. Abin da Allah Ya hukunta ba zai wuce bawanSa ba. Abin bukata bai wuce tsayuwa akan imani da kyautatawa Allah zato ba.

Yana tashi sai ga wayar Baaba Mari. Sarkin da baya bacci Ya juya zuciyarta. Hakika tun bayan fitarsa da abin da Munzali ya ce ya sami takwararta sai ta rasa sukuni. Hukuncinta na rabasu tun farko domin su jidadin tuba yana nan. A matsayinta na uwa dole ne tayi duk wani abu da ta san cewa zai taimakawa danta ya tuba. Tabbas d'a na kowa ne to amma fa game da naka Allah zai fara tambayarka ranar lahira kafin na wani. Sannan yana daga cikin sharudan tuba da aka koyar da ita a Islamiyya, bawa ya nesanci wurin da yake aikata wani sab'o, ko ya canja abokai ko abin da zai kusanta shi da hakan a yayin tuba. Shin ta so kanta kenan don tana nemawarwa danta tsira daga azabar wuta? Kwalla mai zafi ta silalo mata ta share. Zuciyarta a kuntace take. Lallai ita Mari tafi uwar da 'yarta take yawon karuwanci shiga tashin hankali. Luwadi? Luwadin da Allah Yasa aka kife al'ummar Annabi guda a sanadinta amma ace dan da tayi rainon cikinsa ta haifa kuma ta shayar ita ce sana'arsa?

Kaico! 'ya'yan mutane da suke cikin wannan mummunar rayuwa ba zasu kirgu ba. Wadanda suka shigeta a matsayin sana'a ko hanyar jindadi a sanadiyar almajiranci sun ninka masu shiga a gaban iyayensu. Babu dalili komai dadin bakin mutum da za a fada mata wanda zai sa ta taba goyon bayan a cigaba da tura yara almajiranci. (Wannan gaba zaman fayyace halin da almajirai suke ciki zai iya cinye ragowar labarin namu. Na dai yi imanin cewa mun sani ko mun saba jin labarai marasa dadi akan yaran da suka tsinci kansu a nesa da iyaye da sunan neman karatu. Fatanmu Allah Yasa masu ruwa da tsaki su kawo gyaran da ya dace game da rayuwar al'ummar nan a kowane fanni.)

Munzali! Matsayin Munzali ta tuno a wurin Abbati ba rawar da ya taka a rayuwarsa ba. Lokuta babu adadi Abbati zai turo mata katin waya ko da tana dashi ya ce don Allah ta kira Munzali.

"Ki yi hira dashi Baaba irin ta uwa da danta. Ki dinga yi masa fada kina bashi shawara. Yana bukatar hakan."

Tun tana kiran bayan Abbati ya saka ta har ta koma yi a karan kanta. A duk lokacin da ta kira sai ta kara jin kaunarsa a zuciyarta. Yaro ne mai saukin kai ga wanda ya fahimce shi. Mutum ne shi wanda yake fama da k'ishin (thirst) uwa a rayuwarsa. A hirarrakinsu yana bude mata sirrinsa da damuwa akan gidansu. A dalilin haka ta yi yunkurin hada zumunci da Asabe amma abin bai yi nisa ba.

Lokacin 'ya'yan nasu basu yi kudi kamar yanzu ba. Asabe ta dinga yi mata lakabi da Uwar Almajiri. Ko a waya suke gaisawa da wannan sunan take kiranta. Da aka yi

masa haihuwa ya sanyawa diyarsa Mariyatul Qibdiyya kuwa kiranta tayi ta ci mata mutumci. Bata fadawa kowa ba har Abbati amma ta janye jikinta. Sai dai abin da ya sami takwararta ya mata karan tsaye. Fyade ta furta kazamar kalmar a raunane. Tufka da warwara basu barta ba sai dai tunaninta ya tsaya wuri guda. A takaice raba Abbati da Munzali ba zai zama mafita ba. Hadasu da nuna musu hanya a tare shi ne jigo.

(Wato 'yan uwa na fa sha korafi akan dalilin sanya Baaba Mari ta umarci Abbati da rabuwa da Munzali. Da yawa basu san manufar yin haka ba. Na so nuna muku hukuncin farko da iyaye kan zartarwa yaransu ne a duk lokacin da aka sami bullowar mummunan hali. Za ka sami uwar abokin barawo da son raba danta da barawon harma tana ikirarin zai bata mata d'a. Sau tari bata ma san cewa nata shi ne ya bata na wani ba. Illar rabawar musamman ga masu wayo shi ne su dinga haduwa a bayan idon uwa.

Idan da zata zurfafa tunani sai ta gano matakin farko shi ne ta kokarta wurin taimakawa duka yaran da suka yi tarayya a barna. Ita da iyayensu su hada kai su gyara. A inda aka kasa samun haka sai guda daya ta gwada. Sai taga hakan ya kasa zama maslaha sannan ta canja tsari. Idan zamansu tare da fadan da nasihu yaki aiki sai a shigo da shawarar rabuwarsu. Wannan shi ne abin da naso nunawa da hukuncin farkon. Wallahu Ta'ala A'alam)

"Zo ina son ganinka"

Da sauri ya mike domin ya zata jikin ne. Ya sameta a zaune a dakinta ita kadai. Ta nuna masa wurin zama da hannu.

"Abbati na baka amanar kanka da ta Munzali. Na yarje muku zamewa juna jagora a kokarinku na inganta tuba. Na amince ku hada kai ku nemi taimakon Allah akan umarnin da na baku na rabuwa da duk wata dukiyar haram. Wallahi Abbati albarka ba za ta bi ku ba alhali kuna ci kuna sha da kudin zina. Rayuwarku za ta tafi akan tsarin da zai haskaka zukatanku ne a lokacin da ku ke cikin halalinku komai kankantarsa. Ita haram banda tarin zunubi harda kuncin zuciya take sakawa."

Ko kusa bai zata abin da zata fada masa ba kenan. A bazata mafi girma kalamanta suka dirar masa. Hawaye ya cika idanunsa har ya zubo a lokacin da ya matsa ya kama hannunta ya rike cikin nasa.

"Allahu Akbar. Allahu Akbar. Baaba kin sani cewa ban taba kokwonta akan Sarautar Allah ba amma yau na kara imani. Na roki Allah kuma hakika Ya taba zuciyarki. Na gode. Mun gode"

Hancinta ta ja ta hanyar shaka alamun kukanta bai kare ba ta murmusa.

"Allah Ya karawa Annabinmu SAW daraja."

"Amin"

"Ka bar duk abin da kake yi ka tafi Kano domin Munzali yana bukatarka. Ni shaida ce ba don matsalar da ta taso ba da tuni ya biyoka."

Abbati yaji gabansa ya fadi "akan Qibdiyya da ya ambata ne?"

Baaba Mari ta gyada kai.

"Fyade aka yi mata"

"La haula wala quwwata..." Abbati ya ce a yayinda ya yi wata irin mikewa cikin mummunan tashin hankali.

"Ka nutsu domin a yanzu kai ne kwakwalwar tunaninsa. Idan kaima ka makance babu lallai ku iya daukar matakin da ya dace. Ka tafi Allah Ya tsare."

Cikin minti goma sha biyar har ya isa tasha. Wurin mutum uku ya biya domin motar tayi saurin tashi.

****

Ana amsa sallamar Suhaib Ayaah ma sai tayi cikin muryarta da ta dusashe saboda kukan da tayi. Ba a amsa ba. Sai dai cikin abin da bai fi sakan biyar ba ilahirin jama'ar dake cikin gidan

Honourable a wannan lokaci suka tsaya a bakin kofa. Sunan Ayaah kawai ake kira ana kukan murna da hamdala. Jikin Hasiya ta fada tana kuka sosai. Kukanta ya tayar musu da hankali. Farincikin da suke yi na ganinta ya koma alhinin jin daga ina take da kuma abin da ya sami suturar jikinta.

Honourable kurawa Suhaib ido ya yi yana neman fassara yanayin da ya gansu a ciki. Matashi mai jini a jika sanye da 'yar singiletin da ta bi jiki da damatsansa. Ga 'yarsa ta suturta jikinta da rigar da ya yi imanin ta matashin ce. Me yake faruwa? Gabansa ya shiga faduwa yana fatan ba abin da yake tunani bane.

"Ya kamata mu zauna aji me yake tafe da yaron nan ko?"

Larai ce tayi magana tana janyo Ayaah daga jikin Hasiya ta rungume. Gani take ta fi kowa damuwa da son jikokin nata na wurin marigayiya A'i.

Ita dai Ayaah hawaye kawai take yi tare da yayyenta Ummita da Murja har suka shiga cikin dan falon da ba zai dauki mutanen gidan ba. Basu san me ya sami kanwar tasu ba amma hankalinsu a tashe kamar na kowa. Mazan duka suna waje. Honourable wayar Abdulkarim ya kira ya fada masa dawowar Ayaah tare da tsawaita godiya akan taimakonsu da ya yi.

Zamansu Ayaah ke da wuya sai ga Anti Hasiya da kwanukan abinci. Murja ce ta karbi tray din ta ajiye a kasa ita kuma ta koma kusa da Ayaah ta zauna. Tana zaman Ayaah ta dora kanta a cinyarta ta cigaba da kuka. Kasa daurewa tayi ta biye mata suna yi tare har sai da Innayo tayi magana.

"Kun bar mutum a waje kin zo kin sakata a gaba da kuka maimakon ki rarrasheta."

Larai ta hararetа saboda so take ace ita ce mai rarrashin. Bata son duk wani abu da zai nuna Innayo ko Hasiya sun fi ta sanin me ya kamata akan jikokin. Sai cewa tayi,

"Wani irin rarrashi a wannan yanayin da ake ciki? Ai ki barta tayi kuka ko zata sami sa'ida."

A tsakar gidan kuma Honourable ne ya ce da Suhaib idan babu damuwa ya zauna zasu yi magana. Bai yi mamakin jin hakan ba shi yasa ya zauna akan tabarmar dake shimfide a wurin. Honourable ya shiga falon ya ce don Allah su fito waje amma yana son a dan jira zuwan Abdulkarim. A ganinsa yadda ya kokarta masa yau dinnan ya kashe duk lalurar gabansa ya dace shi ma ya san me ya faru. Ita dai Ayaah ji tayi kamar wata igiya ta kwance daga wuyanta zuwa kafafu. Yawun bakinta duk ya kafe ta rasa na jika lebenta ma. Rawar jiki kawai take yi saboda firgici. Da Salima ta kula da yanayinta sai ta yiwa Honourable magana cikin hikima. Mutumin da yake a tsorace bai dace idanu su yi masa yawa ba a irin wannan lokacin. Tana gudun tayi musu karya saboda rashin sakewa. Shi yasa taga gara ace mahaifinta ne kawai da Hasiya.

"Inaga duk abin da za a tattauna gara ayi a nan. A kira saurayin da ya kawota ya shigo ciki sai mu baku wuri."

Larai da 'ya'yanta sun so kin tashi sai dai Salima bata barsu ba. Musamman ma dai 'yan uwan nasu. Ai kuwa ta hau fada akan cewa a madadin uwa tafi kowa cancanta da zaman jin bayanin Ayaah da bakonta.

"Don Allah mu koma dakin yaran nan tunda ya dan fi yin ciki. Sai kuyi shawarar a can ko don bakon da bamu san ko waye ba."

Honourable ne da kansa ya yi magana saboda ya san halin Larai. Jan zance zata yi, gashi shi kuma a matse yake yaji bayani.

Da suka fito Hasiya ta nunawa Suhaib kofar falon ta ce ya shiga suna zuwa. Suna zuwa Honourable ya ce da Hasiya, Innayo da Larai zasu zauna da yaran. Sai Abdulkarim idan ya iso. Daga jin haka Larai tayi gaba tana mitar ai 'ya'yan cikinta ya kamata ya kira ba Innayo ba. Babu wanda ya ce mata komai a cikinsu. Suna zuwa bakin kofar Abdulkarim ya yi sallama ya shigo gidan suka rankaya ciki tare.

*

Suhaib ya shiga ya sami Ayaah tana faman goge hawaye da rigar jikinta-rigarsa! Haka nan yaji hakan ya zo masa a matsayin kusanci da ita. Kasa yi mata magana ya yi bayan sallamar da ya yi sai kallon yadda ta take kuka.

A nata bangaren kuma ganinsa yasa taji wani kwarin gwiwa fiye da farkon shigowarta. Wasu hawayen ta goge ta dago kai ta dube shi.

"Don Allah ka rufa min asiri kada ka fadawa su Baba abin da ya faru. Ban san me zasu yi min ba."

Kwayar idanunta wadanda suka yi jazur gami da kankancewa Suhaib ya kalla ya dan yi murmushi.

"Kada ki firgitani yadda kika firgita kanki mana. Nace ki kwantar da hankalinki komai zai daidaita in sha Allahu"

Amsarsa bata bata nutsuwar da take nema ba domin ba abin da take muradi ya fada ba. Jikinta duk ya yi sanyi ta marairaice fuska.

"Kenan fada musu gaskiya zaka yi?"

"Banda gaskiya babu wani abu da zai fitar dake. Me zamu ce a matsayin dalilin da ya hadamu har na kawoki gida? Banga wani abu da zamu fada wanda zai gamsar damu kanmu ba balle su."

Bata hakura ba ta ce "Iyayena zasu ji kamar naci amanarsu. Don Allah..."

A tausashe ya ce "I will be here Ayaah. Zan yi musu bayani yadda zasu gamsu in sha Allahu."

Abubuwa taji suna shiga zuciyarta daga sautin kalaman har zuwa sakon da suke tafe dashi. Hankalinta ya dan kwanta amma tsoron bai barta ba. Turo baki tayi ganin magiyarta taki tasiri cikin kunkuni ta ce,

"Ni wallahi na zata ma sona kake shi yasa ka taimaka min."

Tun bayan zuwansa Kano a yau sai yanzu Suhaib ya yi dariya. Dariya mara karfin amo amma mai nuni da har cikin zuciya mai yinta yana cikin nishadi.

"Wato kin zata sonki nake?"

Ayaah ta murguda baki da kumburarrun idanunta ta ce

"Dariya ma na baka?"

"Ai dole nayi dariya."

Ance wai mai hali baya fasawa. To Ayaah ma bata manta tsiwarta ba tunda Danliti bai sami damar koya mata hankali ba. Juya idanu taso yi amma nauyinsu ya hanasu bata hadin kai. Sai ma zafi da suka yi wanda yasa ta runtsesu da sauri. Duk da haka bata hakura ba sai da ta ce,

"Ko a nan gaba kaji kana sona kada ma ka fada don ba zan baka hadin kai ba."

"Zamu gani" ya ce yana cigaba da murmushi.

Kofar da aka taba ta danyi kara ce ta kawo karshen maganar tasu. Honourable ne a gaba sai Minista, matan suna biye dasu.

An zazzauna kowa ya fuskanci Ayaah wadda ta rakube a jikin Anti Hasiya. Honourable ne ya soma magana cikin nutsuwar da ya arawa kansa ta dole.

"Kun san zaman me muke yi a nan? Ku dubi girman Allah ku fada mana gaskiyar abin da ya faru."

Ayaah baki sai ya soma rawa. Dauriyar da taso yi ta kasa sai kuka. Wannan yasa Suhaib ya karbi ragamar jawabin daga inda ya sani.

"Suna na Suhaib Tahir kuma a Kaduna nake da zama. Kanwata Mardiyya ita ce Alh. Munzali yake nema..."

Innayo ta gyada kai saboda tun dazu take yi masa kallon sani. Ya cigaba da fada musu ranar da ya fara ganin Danliti a wurin dinner. Sai ya sakaya ya ce matar dan uwansa ce ba matar babansa ba. Irin abubuwan da ya gani da maganganun da Danlitin ya yiwa Jiddo da Ayaah duk ya fada. Akan haka ne hankalinsa bai kwanta ba har ya karbi nambarsa a wurin Jiddo da zuwansa Kano. Dama duka abubuwan da suka biyo baya har ya sami damar kubutar da ita da taimakon Allah.

La haula wala quwwata illa billah. Suhaib yana bayani Anti Hasiya da Larai suna kuka. Innayo ma ba a barta a baya ba domin tabbas ba don tsarewar Ubangiji ba da yanzu suna kukan bakinciki. Honourable kuwa sunkuyar da kansa ya yi kasa. Shi kadai ya san halin da zuciyarsa take ciki. Sam ya kasa magana sai Abdulkarim ne ya dauki matsayin uban. Godiya ya fara yiwa Suhaib sannan ya koma kan Ayaah.

"Saura ke"

"Don Allah ku yi hakuri" ta fara cewa Larai ta daka mata tsawa.

"Za kiyi bayani ko sai na saba miki? Mutuniyar banza mutuniyar hofi."

Idanunta a kasa ta fadi abin da ya kamata ta fada. Tana magana hannunta yana cikin na Hasiya wadda ta rike domin bata kwarin gwiwa. Labarin bai yi mata dadi ba amma kuma bata so tsoro ya hanasu gane bakin zaren.

Kunyar duniya yau Ayaah ta gama sha. Da bakinta take maimaita yadda abubuwa suka kasance a gaban iyayenta da Suhaib. Ko ba a fada ba ita da kanta ta dinga ganin wautarta na yarda da zantukansa baro baro.

Honourable ya dago kai a fusace bayan ta gama magana.

"Taso ki zo nan?"

Suhaib ya kula da bacin ransa sosai. Shi ma zuciyarsa a cunkushe take da takaici amma bai bar tausayinta ba. Yana jin kiran da mahaifinta ya yi mata sai ya mike tsam. Hukunci ya zama wajibi sannan shi din bashi da hurumin hanawa.

"Bari na baku wuri"

Bai jira yaji abin da zasu ce ba ya fita daga falon. Haka Ayaah ta rarrafa gaban babanta ta kama kafafunsa tana kuka. Hakan bai hana shi tureta ba ya daga hannu zai mareta Abdulkarim ya hana.

"Bata kyauta ba amma don Allah kayi hakuri. Mace kamar wannan ta wuce ladabtarwa da duka"

"Inji wa?" Cewar Larai tana face majina "yau ba don yaron can dan albarka ba da yanzu muna cizon yatsa"

"Duk da haka dukan bashi da amfani. Kamata ya yi mu godewa Allah da Ya tsare mutumcinta"

"Sai kuma ayi mata me bayan addu'ar? In kyaleta gobe ma ta bi wani katon banzan?" Honourable ya tambaya cikin fushi.

Kafafunsa Ayaah ta sake dafawa ta ce "Don Allah kayi hakuri Baba ka yafe min. Wallahi ba zan kara ba."

Girgiza kai ya yi da disappointment karara a fuskarsa "kin bani mamaki Ayaah. Kamarki ace kin iya hada baki da namiji ya zo makaranta ya daukeki. To ma wa ya san tun yaushe hakan take faruwa?"

A gigice ta dora hannu a baki tana rantsuwa "wallahi yau ne kadai."

"Kina tunanin zan yarda ne?"

Bata fuska Larai tayi "ban gane ba Habu, me kake son cewa? Tun dazu nake ta bata laifi tunda na san bata kyauta ba. Amma ba zan zuba ido ka jefeta da kazafi ba." Ta juya bangaren Anti Hasiya "dama na fada da sa hannunki akan abin da Ayaah tayi. Banda haka wace uwa ce zata kasa gane irin wadannan abubuwan? Da ace kina kula da marayun nan ai da kin fahimci abin da take yi tun kafin ya yi nisa. Ki bari ki haihu din kafin ki wargaza rayuwar 'ya'yan gidan."

"Maganganu irin wadannan basu dace da gab'ar da muke kai ba Larai." Innayo ta furta cikin lumana. Na farko Honourable Habu suruki ne sannan ga bakonsa. Bai dace magana irin wannan ma ta raso a yanayin da ake ciki ba. Sannan ta gaji da daure zuciyarta kan kalaman Larai akan Hasiya. Tana tsoron kada a kai ta bango ta rama duk su taru su bawa kansu kunya.

Mayar da kallonta tayi ga Ayaah ta ce "ina ji a jikina abin da ya faru yau ya isheki darasi da ishara akan rayuwar da kika so jefa kanki a baya. Ki kiyayi maimaituwar yau din a rayuwarki domin duk ranar da namiji a sami galaba a kanki walau da son

ranki ko babu indai babu aure a tsakaninku ya cuceki har abada. Wani tsautsayin kirawo shi ake yi da sakaci. Allah Ya kiyaye gaba."

Amin suka amsa su duka har Larai din. Abdulkarim ya yi murmushi a ransa yana kara yabawa da tsatson da Hasiya ta fito wanda ya yi tasiri akan 'ya'yan Honourable. Dolensa ma ya zage damtse akan Ummita don bai ga wadda ta dace ya nema da gaske ba kamar ita.

Innayo sallama ta yi musu ta ce zata tafi. Honourable sai ya ce yana son su zama shaida akan hukuncin da zai yankewa Ayaah. Jin batunsa Anti Hasiya da Ayaan suka dinga bashi hakuri. Suna cike da tsoron abin da zai ce. Sun san shi mutum ne mai hakuri da kawaici amma bashi da dadi idan ya kai bango. Ummita da Murja yasa Ayaah ta fita ta kirawo masa. Babu bata lokaci sai gasu duka a tare kowacce ciki ya duri ruwa. Fadan baban nasu bashi da dadi ko kadan.

"Ku zama shaida" ya ce dasu Innayo, "ban yarda Ayaah ta sake fita in ba tare da wani daga cikin gidan nan ba. Makaranta ma in sha Allahu ta bar zuwa sai ranakun jarabawa. Shi ma da kaina zan dinga rakata na daukota. Sannan in sha Allahu sati daya da gama jarabawar Ayaah zan aurar dasu. Duk wadda bata da manemi zan samar mata kafin lokacin. Ke kuma..." Ya nuna Murja "ki fadawa Mahiru tunda dama ni suke jira. Ku tashi ku tafi."

Murja ta mike. Ayaah da Ummita suka kasa kwakkwaran motsi. Maganar abin da bai fi wata uku ake ba. Kuma basu da maneman a hannu. Anti Hasiya ma maganar dirar mikiya tayi mata. Ayaah kam tayi laifi mai girma sai dai ko kusa ba za ta yarda ya yiwa yaran nan auren dole ba. Ita da nata mahaifin ya yi mata, Allah ne kawai Ya dubi zukatansu ita da mahaifiyarta Ya daidaita zaman. Sai ya kasance Honourable din ya zarce duka tunaninsu a fagen kyautatawa sabanin sanin da suke tunanin sun yi masa lokacin yana auren A'i.

"Ku tashi mu tafi" ta ce da 'ya'yan nata ganin hatta Ummita ita ma kukan take. Suka bi bayanta kuwa suna tafe kamar kwai ya fashe musu a ciki.

Da fitarsu Honourable ya bawa kowa mamaki da ya yi 'yar dariya. Innayo ma da Abdulkarim sai da suka murmusa. Ita nata ya dace da na Honourable. Fushi ne suke gani muraran Hasiya tana yi na sanya mata yara a tsaka mai wuya. Shi kuwa

Abdulkarim na farincikin fahimtar cewa Ummita bata da kowa a hannu yake. Lallai zai ci karensa babu babbaka. Tunda babu wani yaro a hannu da zai masa shigar sauri ya hure mata kunne.

Dakin da suka baro su Maimuna suka shiga, Ummita da Ayaah suna kuka babar tasu ma tana yi. Maimuna ta gaji da rarrashinsu ta koma fada.

"Tunda baku san hakuri ba sai kuyi ta yi. Amma ki sa Ayaah ta cire rigar d'an mutane ta mika masa"

Sai a lokacin ta tuna da rigar. Da sauri ta shiga balle maballan ta cire ta mikawa Murja.

"Don Allah ki kai masa"

Anti Hasiya ta kai mata duka ta kauce

"Amma baki da kirki Ayaah. Mutum ya yi miki irin wannan taimakon amma godiya ta kasa shiga tsakaninku. Tashi maza ki kai masa da kanki."

Hijab ta dora ta fita tana jiyo muryar Larai tana bada labarin abin da ya faru. Duk inda take tunanin ganinsa kama daga tsakar gidan, soro da kofar gida. Bata manta da gargadin babanta ba saboda haka bata yarda ta fita ba. Ciki ta dawo da niyar daukar wayarta ta kira shi sai ta kula da takalminsa a kofar falon. Kenan Baba ne ya sake kiransa ta ambata a zuciyarta. Kamar wadda tayi magana da karfi sai ji tayi Babanta ya kwala mata kira.

Da hanzari ta shiga don yanzu bata kaunar abin da zai bata masa rai.

"Dama rigarsa zan ce ki kawo ashe ma kin dauko."

Abdulkarim sai cewa yayi "muje waje in ganka kafin na wuce Honourable."

Hon. Habu ya dan yi turus sai da ya sake maimaitawa ya mike. Suna fita Abdulkarim din ya ce da Suhaib idan ya fito zasu yi sallah don har biyu da rabi.

Rigar ta mika masa bayan sun fita ta furta kalmar godiya a hankali.

"Ya naga duk kin yi laushi ne? Ko hukuncin da Baba ya ce min ya yanke ne bai yi miki ba?"

Dago rinannun idanunta tayj da sauri ta ce "yanzu sai da ya fada maka zai min auren dole?"

"A'a" ya ce yana mai girgiza kansa "cewa ya yi kawai za ki daina fita har zuwa school sai kina da paper" ya kare da dan murmushi.

"Auren dolen ka ke yiwa dariya ko hanani fita?"

"Kina da rigima" Suhaib ya furta da wani irin yanayi sannan ya tashi tsaye "ni zan wuce. Sai in ce sai mun zo biki ko?"

Shiru tayi bata kula shi ba don ta kula yana jindadin zolayarta.

"Au ba za ki amsa ba?"

"Kana farinciki da auren dolen da za ayi min ya za ayi na amsa?"

Sai da ya je bakin kofa sannan ya juyo ya kalleta cikin ido ya ce "dazun nan ki ka yi warning dina da cewa ko ina sonki kada na fada domin ba za ki yarda ba. Ba don

haka ba da na sake introducing kaina a wurinsa a matsayin...." Ya lumshe ido ya budesu a gajiye "idan kin bani matsayin da ya dace na sake gabatar da kaina a wurinsa ki kirani kafin lokaci ya kure mana. Take care."

Har ya fita su Ummita suka shigo bata sani ba don ba karamin kashe mata jiki da zuciya kalamansa suka yi ba.

Sallah ya tsaya suka yi sannan ya ce zai tafi. Ba yadda Honourable bai yi dashi ba akan ya zauna yaci abinci yace ya koshi. Da fitarsa bai zame ko ina ba sai garejin su Danliti. Ogansu ne ya kira shi yana shiga mota zai bar unguwarsu Ayaah.

"Mal. Suhaib muna kara godiya akan taimakon da kayi mana. Dalilin kiran naka kuwa yanzu ba wani abu bane illa wayarsa da nake son baka kafin 'yan sanda su nema."

"Waya kuma?" Suhaib ya furta yana yamutsa fuska saboda son sanin dalili.

Mutumin ya ce "Kwarai kuwa. 'Yan sandan da suka zo basu kula da ita ba sai wani cikin yarana ne ya dauko. Yanzu suka budeta har sun cire lock din ma. A garin bibiyar hirarrakinsa na chatting muka ci karo da hirarsa da wata mata suna kuma yawan ambaton sunanka. Matar har tana cewa idan ka zo Kano ya sake maka kamanni da duka. Shi ne nace gara dai ka zo ka gani kada ya cuci wata"

'Alhamdulillah' Suhaib ya ce yana mai fadada murmushin fuskarsa domin wannan batu ba karamin taimako zai yi masa ba. Shaida ce guda da zai samu ya nunawa Abbansu akan Jiddo. In anyi sa'a yaga cewa matarsa ma tana yin yadda yake ko kusa da kila ya canja hali. Da wannan tunanin ya wuce garejin.

Kafin ya karasa kafarsa ta dama ta soma wani irin tsukku kamar ana cakarta da allura. Da kyar ya iya karasawa sai dai yana fitowa ya kasa takata da kyau. Ogansu Danliti yana ganin yanayin tafiyarsa ya ce,

"Dama na san a rina. Wannan duka da ka yiwa kofar dakin nan da wuya idan baka bugu ba ko targade. Don da karaya ce da wuri zaka fara jin ciwon."

Wasa-wasa Suhaib kasa jan motar ya yi. Shi da ya yi niyar komawa Kaduna a lokacin sai gashi wani aka samu ya mayar dashi gidan kawunsu inda aka yi zaman biki. Abinci ma kasa ci yayi dole suka tafi wani asibitin kashi na kudi. Har x-ray aka yi masa saboda kafar ta fara kumbura ta wurin idon sawu. Dunduniyar kuma tana ciwo. Babu karaya yadda suke tsammani sai tsabar buguwa. Irin leg brace dinnan aka daura masa bayan an yi mata gashi sannan suka koma gida. Matan gidan suna can suna kiran Mami Khadija su sanar da ita shi kuwa ya kira Lilu ya ce ya taho washegari su koma tare.

***

Zara taga ikon Allah zamansu da Uwani bayan fitar su Innayo. Surutai take yi ita kadai kamar wadda ta sami tabin hankali. Kalma ko daya ba za ta iya cewa ta gane ba amma ga bakinta nan yana ta motsi da sauri-sauri. Abin tsoro ya soma bata ta tashi daga dakin ta koma falo. Kafin ta zauna Uwani ta fito tana mai cigaba da maganganunta. Babu zato taji ta ce mata,

"Kiyayyar da kuke min har ta kai a rasa mai tambayata damuwata Zara?"

"Idan na tambaya za ki fada min ne?"

Uwani na jin haka ta dawo kusa da ita ta zauna. Da gaske neman wanda zata saukewa damuwarta take. Innayo din da ta zata har abada ba za ta taba juya mata baya ba yau gashi tana magana taki sauraronta da kyau. Kanta ta dinga dunguri da yatsanta manuni.

"Zara ina ji wadansu notina suna kwancewa a kwakwalwata wallahi. Daf nake da zarewa idan Habibu bai dauki wayata ba"

"Habibu kuma ko Salihi?"

Uwani ta maimaita sunan da karfi "Habibu nace. Ai ce miki nayi kaina zai kwance ba wai ya kwance din ba"

Mikewa Zara tayi "me yayi zafi za ki sauke min fadanki. A kira Habibu lafiya"

Da sauri Uwani ta riko hannunta ta dawo ta zauna. Bata boye mata komai ba cikin matsalolin da suka fuskantota a dan kankanin lokaci.

"Idan na rasa komai wallahi zuciyata za ta iya bugawa. Zara gabadaya rayuwata fa akan yadda zan gujewa rayuwa irin ta Innayo na yita. Sai yanzu bayan na gama shan wahalar har ina hango soma cin arzikin sai komai ya rushe? Meye marabata da Innayo yanzu? Karatun da aikin duka babu riba."

Kwalla ce ta taru a idon Zara saboda ita kanta ta hango tsagwaron rashin hankali a zantukan Uwani.

"Ko kadan baki yi kuskure ba don kin yi fatan gujewa irin rayuwar Innayo. Babu wani mai hankali da zai so bayan ya tashi a wahale ya cigaba da rayuwa a haka. To amma kuskurenmu daya ne ni da ke. Mun so gujewa rayuwar ne mu kadai ba tare da tunanin wadda tayi sanadiyar rabamu da ita ba. Da gumin wa muka rayu? Wa ya ciyar dake? Waye ya kai ki makaranta? Wa ya aurar dake? Addu'ar waye ya zame miki garkuwa tsahon rayuwarki? Sai ace kuma da kika sami dadi ita ce mutum ta farko da kike gudu tamkar ita ta zabawa kanta kuncin da take ciki. Ke din wayonki ne yasa ki ka sami duka nasarorin da kike tinkaho dasu? Idan wayonki ne to ki sake tsallake wannan ramin dake gabanki. Ni dai na dawo daga rakiyar shaidanin da ya taba min zuciya. Uwata ita ce madubin rayuwata. Ranar da kika gane haka kuma ki ka roketa gafara shi ne lokacin da zaki fara ganin haske."

Tun zuwanta gidan ta kula da yadda Zara take neman shiri da Innayo. A zatonta abin na ganin ido ne kadai. Sai gashi taji daga bakinta. Wannan yasa tayi wata irin dariya. So take ta san waye mara hankali tsakanin ita da kanwar ta ta.

"Da bambanci sosai tsakanin matsalata da taki. Baki san juya kudi ba sai dai a dauka a baki. Shi yasa da miji ya juya miki baya ki ka yi saurin laushi a hannun

Innayo tunda arzikinta kike ci. Ni kuwa gumina ne. Nafi karfin tozarcin da namiji wallahi."

"Hakka!" Cewar Zara da gatsali.

"Don kin ganni a gida ki ke min magana haka? Hala baki ji na fada miki ina da gidan kaina ba?"

"Kan ki kuma ake ji"

Zara dama ba kyalle bace. Da ta fuskanci Uwani bata da niyyar bin hanyar da take nuna mata sai taji gara a bar maganar kafin su fara fada. Tashi tayi ta fito falo. Uwani sai ta biyota rai a bace.

"Ni kike cewa kaina ake ji saboda ga 'yar macukule ko? Har kina da bakin fadawa wani magana ma ke da kike goyon 'ya mara suna?"

"Wai in tambayeki Uwani. Anya kin taba zama kin karewa Innayo kallo kuwa? Kin ma santa kuwa? Sani na wace ce ita a matsayin 'yar Adam ba na matsayinta na uwa a gareki ba." Shiru Uwani tayi tana sauraron zancen da Zara ta dauko.

"Innayo bata sami gatan uwa da uba ba a dalilin maraici amma mu ta zame mana uwa da uba harda kari. Mu tara ta aurar Uwani. Mata tara wata na bin wata. Ta sadaukar da lafiyarta da jindadinta domin rayuwarmu ta inganta. Amma cikinmu banda Hasiya waye take jindadi a jikinsa? Salima da Maimuna suna kyautata mata amma ai har yau guminta suke ci. Su Hasina dama tun zamanin marigayiya Allah Ya jikanta suka juya mata baya. Me tayi mana da zafi Uwani? Saboda ta auri ubanmu ta haifemu shi ne laifi? Ko don ta jure wahalar gidansa domin ta zauna damu don kada rayuwarmu ta tagayyara? Kiyi tunani idan har kina da rabon jindadin duniya da lahira. Innayo jininta ne kadai bata zubar domin mu ci, mu sha kuma mu sami ilimi ba. Tun karfe hudu take tashi amma babu ita babu sake kwanciya sai wuraren shadaya ko shabiyun dare. Hannunta kullum a ruwa, ido a gaban murhu. Haba Uwani? Kamar baki rike ciki kin yi nakuda ba? UWA, UWACE komai lalacewarta. Balle kyautar Allah irin Innayo."

Bata kara tofa komai ba bayan haka ta shige daki saboda kukan da yaci karfinta. Uwani kuwa zama tayi dabas akan kujera duka jikinta babu kwari. Ta kwashi kusan minti ashirin tana juyayin maganganun Zara kafin wani irin bacci ya dauketa. Tabbas sau tari mutum yana ganin abin dake zuciyarsa ne a cikin bacci. A yadda take a zaunen ko gyara zama bata yi ba baccin nata ya dauketa zuwa duniyar mafarki mai ban tsoro. A cikin baccin take fatan Allah Ya kawo mai tashinta saboda firgicin da ba za ta ce ga abin da ya kawo mata shi ba.

*

"Shazali ya maganarmu ne? Ranar laraba muka yi da Alh. Tahir gashi har yau litinin baka ce min komai ba"

Gefen titi Shazali ya gangara da motarsa domin maganar da zai yi da Comared tana bukatar nutsuwarsa sosai.

"Ranka ya dade akwai shirin da nake yi ne. Hatsaniya ta shiga tsakanina da mutumin da nake son kawo masa ne, saboda haka sai na lallaba shi a hankali."

Tsaki Comared ya ja ya kuma kama yi nasa fada harda zagi.

"Ka tabbata yaron ya zo domin idan aka sami akasi raina da naka duk sai sun baci"

Hakuri Shazali ya bashi a ransa yana ta tufka da warwarar yadda zai yi ya sami kan Abbati cikin lumana. Aikin Comared din da ya yi masa bayani ya wuce biyawa Alhajin da zai zo bukata kadai. Aiki ne na sihiri wanda Alh. Tahir ya zata za ayi ne domin toshiyar baki (Yumna). Bai san cewa Comared tasa tukunyar yake son gyarawa ba. Sharri yake son kulla masa ya watsa hotunansa ta yadda zai rasa duk wata kwangilar dake hannunsa. Sai a bawa Comared don dama irin sana'arsu daya. Lokaci guda Alh. Tahir din ya yi musu zarra, sunansa kadai ake ji. Abotar sai ta koma murmushin gaban ido da gulmar bayan ido, batare da saninsa ba.

To shi ma Shazali burinsa ya yi amfani da wannan damar ya tozarta Abbati. Duk da cewa a gaskiyar lamari yafi jin haushin Munzali saboda yafi baki. To amma wulakantar Abbati sai tafi ta Munzali ciwo kamar yadda ya yi hasashen tonon asirinsu. Abbati dan dangi ne. Munzali kuwa da danginsa da babu duk daya a tunaninsa. Sannan son da Munzali yake yiwa Abbati zai sa yaji ciwon abin sosai. Dama ce ya samu da zai nuna musu shi din ba kanwar lasa bane. A matsayinsa na silar arzikinsu bai kamata su juya masa baya ba. Sai da suke ganiyar samun kudi kamar hauka sannan zasu ce wai sun tuba. Ko waye ya fada musu cewa shi baya son samun rahama bai sani ba. Lokacin tubansu idan ya zo ba sai kowa ya fada musu ba. Tsufansu ya ishesu sanin cewa ya kamata a koma ga Allah. Su gina masallatai su dinga bayar da sadaka. A haka zasu koma lahira kamar jarirai. (Babu bawan da Allah Ya yiwa alkawarin jinkirta masa rayuwa zuwa wani wa'adi. Lokaci yana zuwa ne ko da tsufa ko babu. Ko an tuba ko ba a tuba ba sai an tafi. Ya Rabbi Ka yafe mana zunubanmu na zahiri da badini. Amin)

Da waccan magana ya katse kiran Comared ya shiga laluben layin Abbati. Cikin sa'a kuwa ta shiga sai fatan a dauka. Abbati na ganin sunansa a jikin wayarsa ya ja tsaki ya mayar da ita aljihu. Sun kusa Jogana motar tasu ta soma hayaki suka tsaya. Abin duniya ya taru ya yi masa yawa domin ya kasa samun mota mai tsayuwa ta dauke shi. Ga yamma ta kawo kai. A gefe guda kuma ya kasa samun Munzali. Hanne da yake tunanin zata hadasu ita ma wayarta a kashe. Daga baya ne ya yi tunanin kiran Kukunsu. Cikin sa'a kuwa ya sameta. Shazali da bai hakura da nemansa ba ya dinga jin wayar tana shiga number busy.

Kalmar lafiya kalau kadai Abbati ya iya cewa ga dukkan tarin kalaman gaisuwa da kukun yake jefa masa. Jin zai fara tambayarsa mutanen gida ya yi saurin katse shi.

"Don Allah hadani da Munzali"

Kuku ya dubi hanyar bene ya ce "yau ko sau daya bai fito ba. Sannan yaki barin Qibdiyya ma ta sauko. Abincinsu ma ni ban sani ba ko sun ci don ya kulle kofarsa"

Dunkule hannu Abbati ya yi ya daddaki goshinsa cikin rashin sanin abin yi. Can dai ya ce masa yana zuwa ya kashe wayarsa. Hannunsa yana rawa ga gumin tashin hankali ya shiga scrolling din sunaye a wayarsa. So yake ya gani ko zai yi dacen samun nambar 'yan uwan Munzali amma babu ko daya. Tsoronsa kada ya dauki

mummunan mataki musamman da Kukun yace yana tare da Qibdiyya. Kiran kukun ya sake yi da wata shawara ta zo ransa.

"Ka san gidan iyayen Munzali ko?"

"Na sani ranka ya dade"

"Ka je gidan ka nemi mahaifiyarsa Asabe ka fada mata. Ita zata san me ya kamata ayi kafin na iso. Ka tabbatar ita ka samu"

A kofar gidan Alh. Rabi'u kukun ya tsayar da mashin dinsa ya sauka ya dinga kwada sallama.

A cikin gidan Asabe tana kuryar dakinta abin duniya ya yi mata yawa. Zantukan Munzali basu da ma'anar da zata iya cewa ga dalilin da yasa yake rokon Qibdiyya gafara don an mata fyade. Ta so tahowa ma da ita a jiya a hana. Yau kuma yaki daukar wayarta. Daga baya ita ma bata samunsa. Ga sunan yaron da Qibdiyya ta ambata ma ya kwanta mata don bata taba jinsa ba. Shawara tayi tafi dari akan ta kira su Ummakati ta fada musu ko tayi shiru. She was never a Mom to all of them. Ta dai san wahalar daukar ciki da nakuda. Ta kuma dan san wahalar raino musamman kafin yaro ya fara zama. Daga nan kuma sai abin da hali ya yi. Allah Mai rayawa Shi ya raya mata zuri'arta cikin mugun sakaci da rashin sanin ciwon kai.

Da Innayo ce tabbas ta san da tuni ta lalubo abin da ya dace har ma ta aiwatar. Yinin ranar bata tsinana komai ba sai kullawa da kwancewa. Ga ranar da duk girman d'a yake bukatar mahaifiyarsa. Gata da rai da lafiya amma bata san me ya kamata ta yiwa Munzali ba.

*

Tashin da Uwani tayi daga firgitaccen baccinta yana da alaka da karfin sallamar Kuku. A razane ta tashi tayi hanyar kofa da sauri. Zara ta kalleta ta girgiza kai. Ita ma sallamar ce ta fito da ita.

Kallon ina-na-sanka Uwani ta dinga yiwa masa. Shi bai ma ganeta ba sai Asabe da ya tambayeta.

Juyawa tayi kamar ta koma daki sai dai ta karasa ta fadawa Asaben. Tare suka dawo bakin kofar. A gabanta ya fada mata halin da Munzali yake ciki. Cikin tsantsar rudani kuwa Asabe ta soma kuka. Ita kuma Uwani wani case ta tuna a asibitinsu inda uba ya kusa kashe 'yarsa saboda bakincikin an mata fyade a kauye. Ya ce gara ta mutu akan duniya taji wannan labari. Ba tare da tunanin komai ba sama da ran kaninta da 'yarsa ta koma daki da gudu. Mayafin dake jikin Zara wanda ta lulluba zata fito tun zuwan Kuku ta warware ta yafa. Ta ruga daki ta dauko jakarta mai dauke da kayan aikin gaggawa ta fito.

"Ki fadawa Innayo na tafi gidan Munzali"

Zara ta bita da sauri "gidan Munzali kuma? Me ya faru?"

Uwani bata ce komai ba ta fita. Asabe har lokacin tana tsaye tana koke koke bata iya cewa komai ba ga kuku. Isowar Uwani ce ma ta ankarar da its cewa ya kamata tayi wani abu.

"Malam muje don ba gane gidan zanyi ba"

Kuku ya dan ja baya "ke ce Asaben?"

Rai a bace da ganin yana bata mata lokaci ta ce "ni yayar Munzali ce. Ka wuce mu tafi"

Asabe sai ta gyada masa kai ta koma ciki da zummar dauko mayafi. Kafin ta fito sun bar wurin. Duk da tsoro irin na Uwani haka ta hau mashin din tana salati har suka isa.

BABI NA SHA SHIDA.

Karfe goma na safe Habibu ya shigo cikin ministry da wata 'yar jaka a hannunsa. Kayan sawarsa ne da abubuwan bukata na kurkusa ya hada a ciki. Zaman Kano ba nasa bane ya sani tun ranar da Salihi ya titsiye shi. Babu shakka bayani ya kai kunnen Uwani. Sanin da ya yi mata na son kudi ba na yau bane. Abu mafi karanci da zata yi masa shi ne ta hada shi da 'yan sanda. Shi yasa zai yiwa tufkar hanci ya gudu. Ba kudinta ne kadai ya jike a hannunsa ba, harda na wasu da dama. Da ace kudaden suna da albarka a hannun macuci kuma maha'inci irinsa da tuni ya zama wani. Shekara da shekaru da 'yan dabaru yake kwatar kudi a hannun mutane ya danne. Haduwarsa da Uwani da amincinsu ne yasa ya rage rarakar aljihun wasu. Bai taba shan wahala ko ta anini ba wurin tatsarta. Ita take kawowa tana bashi, shi kuma yana gina kansa.

'Algungumi, an dai fadi ba nauyi' ya ambaci maigidanta Salihi dashi a lokaci guda yana jan tsaki. Duk shi ne ya bata komai da ya far masa kamar ita ta aiko shi. Tunda ya san gaban kansa yake yi gara ya gaggauta guduwa kauyensu har kura ta lafa. Manyansa a harkar magudi ba za su bari ya rasa aikinsa ba. Yanzu ma daya daga cikinsu ne ya ce ya biyo ya karbi rabonsa na wasu kudade da suka yi kashe mu raba da hakkin talakawa.

Hagu da damansa ya waiga don yana ji kamar ana kallonsa sai dai bai ga bakuwar fuska ba. Hakan yasa shi sakin jiki ya shiga office din mutumin. Yana rufo kofa wani masinja ya kira wayar DPO Yahaya kai tsaye ya sanar dashi shigowar Habibun.

"Ka san yadda zaka yi ka rike min shi idan kaga zai tafi har mu iso."

"Yallabai kada ku dade domin da jaka na ganshi"

"In sha Allahu ba za mu wuce minti ashirin zuwa talatin ba."

Masinja ya cika aiki kuwa. A matsayinsa me da ma'aikacin da aka fi gani tare da Habibu, DPO Yahaya yasa aka kai shi station. Bayan guntuwar tsoratarwa suka gano da gaske bashi da hannu wajen ha'incin Habibu. Ya dai san yana yi kuma kamar yadda ya dinga yi musu rantsuwa yana yawan yi masa fada. Alakar tasu ba wata mai zurfi bace sama da yawan musayar yawu game da bambancin ra'ayin siyasa.

"Muna so ka bamu hadin kai ka taimaki abokinka ya daina cutar mutane" abin da DPO din ya fada masa kenan da ya bashi lambar wayarsa.

Bai fi minti bakwai ya rage a lokacin da Masinja yake tsammanin isowar 'yan sandan ba sai ga Habibu ya fito yana fara'a. Masinja ya karaso suka gaisa ya soma jansa da hira.

Idanun Habibu akan gate yana daddaga wuya ya zaro dari biyar "sauri nake ga wannan ka sha ruwa"

"Yi hakuri ka saurareni Habibu. Matsala ce ta taso a unguwarmu."

"Ka ganni nan? Garin zan bari yau dinnan. Ka nemi gidan Dagaci ko Mai unguwa ku kashe matsalar"

Masinja bai hakura ba ya bi bayansa ya rage murya kamar sirri zasu yi.

"Na san kana dan taba harkar nan. Ka taimakeni ko wani abu ne sai na biya."

Saurin takun Habibu sai ya ragu. Masinja kuwa ya gimtse dariyarsa da yaji me yace.

"Wace irin matsala ce? Yadda na dauke ka dan uwa kaima ka san ba zan iya dauke kai akan matsalarka ba"

Masinja ya kirkiro labari ya shiga zuba masa. Wai fili ya sayar ba tare da sanin mai shi ba miliyan biyar. An gama biyan kudi amma balli na neman tashi. Shi ne yake neman mafita.

Hannu Habibu ya dora akan kafadar Masinja yana murmushin mugunta.

"Ina kudin yake yanzu? Allah Yasa baka kaisu banki ba"

A madadin amsar Masinja da yake jira sai jiniyar 'yan sanda ta ziyarci kunnuwansa. Saboda tsabar kaduwa, hannun nasa da ya dora a kafadarsa ya kasa saukewa. Jikinsa ya yi sanyi kalau amma haka ya daure domin a zatonsa motar wucewa tazo yi ta unguwar. Dif ya daina jin karar har ya samu damar sauke numfashi. A ransa yake tunawa kansa cewa mijin Uwani a yadda take fada masa yafi kama da marasa wayo. Ita kuma tunda bata san ainihin me ya mata ba da wuya tayi kararsa. Wayar da tayi masa da asubar ranar dama ita ta kara saka masa son guduwa sai kura ta lafa. Yana can yana zancen zuci sai ji ya yi an damki hannuwansa. Ya zabura ya kalli masu rike shi yaga duka kayan gida ne a jikinsu. Wannan kuwa dabarar DPO Yahaya ce domin kada Habibu ya farga ya yi tunanin gudu.

"Lafiya? Ku su waye? Satar mutane kuma da safiyar Allah a gaban jama'a?"

Daya daga cikinsu ya dauko ID card ya nuna masa "mal. Habibu, ana tuhumarka da satar kudin Uwani Rabi'u ta hanyar yaudara"

"Bangane ba!" Da ya fada a tsorace ta nuna cewa ya gane tsaf.

"Idan mun station za ayi maka cikakken bayani. Muna neman hadin kanka ko mu tafi da kai ta karfin tsiya"

Mutanen da suka fara tsayuwa kallo ya kalla sai kawai ya hakura yabi su. Bai san da sa hannun Masinja ba tunda gefe yaja ya tsaya.

Ana tafiya da Habibu station DPO din ya sanar da Salihi. Shi ne ya bukaci ya zo da Uwani domin jin ta bakinta. A lokacin ya tafi gidansu daukarta sai yaci karo da ita a bayan mashin din Kukun su Munzali. Hawa mashin ba dabi'arta bace. Ganin da ya mata ya tayar masa da hankali. Ko dai fitar da tayi ta son zuciyarta ce ko kuma ta emergency ce na abin da ya shafi wani. Zuciyarsa sai tafi karkata da tunanin farko tunda ya santa da son kai. Babu bata lokaci yabi bayansu har gate din gidan Munzali. Akan idonsa ta dira da sauri don saura kiris ta fadi ta tura karamar kofar

jikin gate ta shiga da gudu gudu. Shi ma sai ya kashe motarsa ya bi kukun da sauri ganin an bude masa gate zai shiga da mashin din.

"Me yake faruwa ne a nan? Ni ne mijin matar da ta shiga yanzu Uwani."

Kuku ya ce "Alh. Munzali ne babu lafiya"

***

A cikin dakin Munzali kuwa a kwance yake yana rawar sanyi. Zazzabi yayi masa mummunan kamu. Har ta kai yana jin kamar ana kwankwatsa masa kasusuwa. Ciwon kai kuwa bai san daga wane bangare yafi sukarsa ba. Tunani barkatai sun addabi zuciyarsa. Mafi girma a ciki bai wuce jin tsoron ko tubansa ne bai karbu ba. Da tubansa ya karbu da babu wanda ya isa ya ketawa Qibdiyya haddi.

"Da tubana ya karbu da Allah Ya tsare min ke ko bana raye" ya furta a kasan makoshi yana shafa kan Qibdiyya.

Sake nanike mahaifinta tayi ta ce "Daddy har yanzu Papa bai zo ba"

Kwalla ta taho masa ya yi saurin riketa saboda kallon kurillar da take yi masa.

"Zai zo. Watarana zai zo...in Allah Ya yarda" saboda bai dade da gama wayar da ta kara masa ciwo da Baaba Mari ba.

"Daddy..."

Wata tambayar ce ya riga ya sani. Tun safe take faman damunsa. Da yace ta fita saboda ciwon kansa sai ta kulle kofar da mukulli maimakon ta bude bisa kuskure. Shi kuma azabar ciwon kai ya hana shi tashi.

"Kaina ciwo yake don Allah kiyi shiru"

Can gefe ta koma ta dauki biskit da juice wanda ya zame mata abinci tun safiyar yau din ta cigaba da ci. Wasa-wasa sai ga Munzali yana zubar da hawaye saboda ciwo. Komai ya jagule har yana tunanin rayuwarsa ce ta zo karewa. Sai dai yana tsoron tafiyar ba tare da sanin ko akwai nakasu a tubansa ba. Duk masu kwankwasa masa kofa ana kiransa yana ji amma ya kasa daga koda hannunsa ne. Ita kuma Qibdiyya bacci ne ma ya dauketa. A wannan halin Uwani ta iso gidan. Da sassarfa ta hau saman tana buga kofa amma shiru. Ana haka Salihi ya shigo Kuku yana yi masa jagora. Kiran da bugun da take yi ne ya kai hankalinsu gareta. Salihi yabi bayanta da sauri. Shi da Kuku suka hadu suna bugun kofa amma ko gezau taki motsi.

"Qibdiyya"

Munzali ya tabota da muryarsa da ta dashe bata fita sosai.

Gyara kwanciya tayi abinta ta juya masa baya. Ya sake kai hannu ya tabata idanunsa na fitar da kwallar azabar ciwon kai. Da kyar ya samu ta farka tana zuba masa magagi.

"Jeki ki bude kofa"

Zuwa tayi ta kama mukullin tana ta murda shi ba daidai ba. Hamdalar Uwani da Asabe da bata jima da isowa ba ta tsaya a dalilin rashin buduwar kofar. Salihi ne ya yi dabarar cewa a miko mukullin ta kasa.

"Na kasa cirewa" ita ce amsar Qibdiyya saboda ta kasa murda shi ya koma yadda zai fita. Sai da suka kwashe kusan minti goma sha biyar ana kwatanta mata yadda zata yi tana kasawa.

"Ina babanki?" Asabe ta tambayeta a firgice.

"Yana kwance. Kuma kuka yake yi"

Innalillahi wa inna ilaihi raji'un. A zaton Asabe ya ma mutu. Cigaba da juya mukullin Qibdiyya tayi har ta gaji. Ta cire hannu kenan Munzali ya taso da bin bango ya bude kofar. A tare Uwani da Asabe suka tura kofar ya fado gabadayansa akan Uwani saboda ita ce a gaba.

"Munzali? Munzali tashi. Na shiga uku na lalace. Ku taimakeni"

Zantukan Asabe kenan tana faman jijjiga shi bayan Salihi ya daga shi daga jikin Uwani. Da ta tashi jakarta ta dauko a kofar dakin ta soma auna shi. Jininsa ya hau ta yadda ita kanta ta tsorata sosai.

"Asibiti zamu kai shi"

Ta ce da Salihi tana mikewa tsaye. Ko tunanin daga ina yake ma bata yi ba. Shi da kukun dai suka saka shi a motarsa. Asabe, Uwani da Qibdiyya kuma suka shige bayan mota.

Hayaniyar fitarsu ce ta taso Hanne har ta leka ta taga. Akan idonta aka sanya Munzali a mota. Jiki na rawa ta sami abin fadi ta dauko wayarta ta kira Abbati. Rabonta dashi tun yana shirin tafiya daurin auren kanin Mami Khadija. Tunda akwai kudi a hannunta bata ga dalilin kiransa ba. Shi ne mai kokarin kiran duk inda yake koda sau daya ne a rana saboda hakki. Neman kudi kadai ke sanyata kiransa. Yau da yake gulma ce sai bata ji kyashin kiran ba. Yana dauka ta saki baki ko tauna magana babu.

"Yanzu naga an dauko Munzali an saka shi a mota kamar matacce"

Razanar da yayi zai rantse ko tonuwae asirinsa bata sa yaji makamanciyarta ba.

"Me kika ce?" Ya tambayeta da muryar da take fita kamar ba tasa ba.

Sai kuma ta dan yi jim da ta hango wautarta "bani da tabbas fa"

Kashe wayarsa ya yi ya sake kiran Kuku. A nan yaji cikakken bayani. Tashin hankalinsa ba zai misaltu ba. Allah Yasa lokacin suna Jogana. Daga nan tafiyar bata da yawa sosai za a shigo garin Kano.

Bayan minti arba'in Abbati ya shiga wani babban asibitin kudi wanda suke zuwa tare da iyalansu shi da Munzali. Sai dai ya daki gurbi domin kuwa ba nan aka kai shi ba.

*

Bangaren A & E na asibitin Sir Sunusi Salihi ya nufa. Sai lokacin Uwani ta farga da ina suke. Kaddara za a kira shafewar tunaninta a game da hukuncin da CMD ya yanke mata har aka shigo. Ta dade da gane hanyar nan din Salihi ya dauko tun a baya amma tunanin an dakatar da ita daga aiki bai zo ba sai yanzu. Da ta fito daga motar sai taji kafafunta tamkar ba za su iya daukar nauyin jikinta ba. Shi kuwa Salihi tunda bai san halin da take ciki ba sai cewa yayi,

"Shiga kiyi musu magana mana a zo a dauke shi. Idan ke ki ka shiga na san ba za a bata mana lokaci ba"

Sati biyu da suka gabata da ita ce ta shiga tana da yakinin cewa a lalace mutum biyar su biyo bayanta. Idan kuwa aka san cewa kaninta ne to Allah kadai Ya san irin kulawar da zai samu. Sai gashi a dalilin son zuciyarta yau ta zo amma tana kunyar shiga. Labari ya risketa daga masu kiranta jajen gaske da na karya cewa kowa ya san an dakatar da ita.

Matron Uwani Rabi'u sananniya ce a asbitin sosai. Akwai kwazon aiki da shige shige. Ga masifa kamar da Alh. Rabi'u aka gina asibitin. Shi yasa ta tara makiya da yawa masu son ganinta a kasa. To yau ga ranar. Taimakon wadanda take nunawa dagawa ne zai sa kaninta ya sami kulawar da ta dace.

"Matron Uwani me kike yi a nan?"

Da sauri ta juya suka hada ido da wata Matron din. Kallo daya ta yiwa Munzali ta dubi matar.

"Wallahi kani na ne babu lafiya. Yana bukatar emergency care."

"Ai kuwa nan dai cike yake da jama'a saboda an kawo masu accident."

"Innalillahi. To don Allah Matron ki taimaka min don yanayinsa ba zai yiwu mu fita dashi ba"

"Sai dai ki fara kulawa dashi kafin likita ya zo"

Har ta fara murmushi ta sake tunawa da suspension dinta. Amma haka ta daure tabi bayanta tana cewa su shigo dashi. Da gaske wurin a cike yake. Wheelchair (kujerar guragu) wani sub-staff (karamin ma'aikaci) ya kawo za a dora shi sai yaja baya da ya hada ido da Uwani tana kokarin sokawa Munzali allura a hannu inda za a kara masa ruwa.

"Matron? Ko ba Matron Uwani bace?" Ya furta da karfi har aka fara kallonsu.

"Nice. Don Allah yi sauri ka kawo ya zauna"

Mutumin ya dakata yana yi mata kallon biyu-ahu

"In baki kiyi aiki aji dadin korata?" Ya kara daga murya ya kira Matron din da ta shigo da ita wurin yana cewa " da alama dai baki san an dakatar da matar nan har na tsahon wata shida ba ko? To wallahi babu ruwana don dokar daga sama aka aiko da ita.

Uwani ta kalli Munzali ko tsayuwa ya kasa yi. Yana tsakiyar Salihi da Asabe ne sun rirrike shi yana neman faduwa. Harbawa zuciyarta ta kama yi ta dubi mutumin rai a bace.

"Wannan ba patient din kowa bane nawa ne. Kanina ne wallahi. Don Allah ka bani kujerar a zaunar dashi"

"In na baki Allah Ya tsinan..." Ya tabe baki "ko doka bata hau kanki ba Matron wallahi yau dai sai dai wani ya taimaka miki. An fada miki na manta tarin rashin mutumcin da kika yiwa matar kanina a labour room ne? Ga kuruciya gashi haihuwar fari ce amma kika dinga yi mata tsawa kamar wata baiwar da kika saya da arha."

Daga bandakin bangaren emergency din wata dattijuwa mai aikin shara da wanke bandakuna ta fito. Duk zancen da ake yi taji kuma ta kara da nata.

"Ashe ba ni kadai matar nan ta yiwa diban albarka ba. Nifa matar makocin dana aka kawo sai a baranda ta haihu. Kememe Matron Uwanin nan ta dage sai an biya kudin gado wai na gwamnati sun kare saura na kudi. Yaron wajena yazo muka tafi nace mata nima nan nake aiki sai cewa tayi wai tayi ragin dari biyu albarkacina. Su biya dubu tara da dari takwas."

"Uwani Rabi'u ake fada muku. Matar da ta kasa biyawa uwar da ta haifeta kudin ganin likitan hakori? Nan asibitin suka zo babarta ko bude baki ta kasa amma Uwani ta ce bata da kudi. Kai ranar naga rashin mutumci ajin karshe. Wallahi sai da na godewa Allah da bai bani haihuwa ba. Da haihuwar dan da ba zai ji kanka ba gara kayi ta shafa fatiha."

Uwani ta juya suka hada ido da daya daga cikin nurses din bangarensu na haihuwa. An kirata ne saboda cikin masu hatsarin harda mai ciki.

Muzanta da tozarci irin wanda ko a labari bata taba ji ba ne suka saukar mata. Idanu sun fi a kirga a kanta. Ciki harda na Salihi da Asabe. Ga maganganun 'yan kallo harda majinyata ana zundenta tana ji. Jikinta a take ya yi sanyi kalau kamar an jefata a ruwa. Gumi ne kawai yake karyo mata sakamakon zafin da take ji yana bin jikinta. Ta kuma kasa yin motsi don ji take kamar an zare mata laka. Kai ta sunkuyar kasa ta dunkule 'yar robar daure hannun wanda za a sakawa allurar karin ruwa a hannunta da karfi. A hankali ganinta ya ragu a dalilin kwallar da ta cika idanun. Hannu taji a kan na damanta an riketa ana jijjigawa.

"Mu fita mu nemi private hospital (asibitin kudi)"

Da kyar ta iya daga ido ta kalli Salihi sai ta mayar da kanta ga Munzali. Idanunsa ne suke yin luuu yana shirin suma. Ganin haka bata san lokacin da ta dauko wayarta ta duba nambar Barr. Umma Jibril. Ringing hudu ta amsa kiran.

"Matron Uwani?" Ta ambata cike da mamaki.

Yawu Uwani ta hadiya mai daci. Bata manta da haushin matar da take ji ba da yadda ta rufta ta a gidanta da sunan dinki za ta yi mata. Bacin ranta ba wai don tana tantamar rashin gaskiyarta bane. Ta san ita din mai laifi ce sosai. To amma yadda aka bi aka kunyata ta duk da ba a gaban mutane bane ya tsaya mata a rai. Ga matsalolin daban daban da suka kunno mata kai lokaci guda. Amma hakan bai hanata jin cewa Barr. Umma ita kadai ce hope dinta ba a yanzu. Muddin ta tsaya girman kai ta ce su tafi wani asibitin Munzali zai iya shiga mawuyacin hali fiye da yanzu.

Barr. Umma sai ta ce "Ko ba Uwani bace?" Da taji shirun ya yi yawa.

"Nice" ta amsa da sanyin murya tana kallon kaninta. Kanin da ba wani abu na zumunci da zata ce ya taba giftawa tsakaninsu tun kuruciya. Sai gashi a yau tana jin damuwarsa ta danne tata. Ga ciwo ga maganganunsa da bata gane ba sannan ga babbar lamari game da 'yarsa....'yarmu ta gyara a zuci.

"Hajiya don Allah ina rokonki da ki taimaka ko na yinin yau ne kisa CMD ya janye dokar suspension dina"

Karaya da nadamar da ba a son bayyanawa Barr. Umma take ji daga muryar Uwani. Da yake ba halinta bane sai ta kasa jan zancen ta hanyar nuna mata dama rana irin yau sai ta zo dole.

"Me yake faruwa?"

"Kanina ne muka kawo gashi babu wanda zai iya duba shi a emergency saboda yawan patients. Ki taimaka min don Allah."

Yau wai ita Uwani ce take magana da roko har tana jin taruwar kwalla a idanunta. Ina zuwa taji Barr. Umma ta ce. Ba a yi minti goma ba aka kira babban likitan dake emergency din. Da kansa ya zo inda Uwani take kai gwauro da mari ya mika mata dan akwatin awon bp.

"Ki daukar min duk wani relevant detail ki fara kara masa ruwa kafin na gama da wadanda suke kan layi."

Murmushin da yafi kama da dariya gami da fitowar kwalla duka suka sauko mata a lokaci daya. Asabe tana ta hamdali yayi da Salihi ya karbe wheelchair din da sub-staff din nan yaki basu da farko ya zaunar da Munzali. Ita kuma ta kama hannunsa ta dauki bp. Sakamakon da ta gani ya tsorata ta sosai. Lokuta kalilan ta taba ganin wadanda jininsu ya hau haka a bangaren haihuwa. Zafin zazzabin shi ma ya haura ka'idar da aka saba. Da taimakon Salihi ta samu ta saka masa ruwa shi kuma ya rike ledar saboda stand din ma babu a kusa. Tayi masa allurai da duk wani agajin da ya dace da halin da yake ciki.

Bayan ta gama iya nata ta ruga duk infa likitan nan ya saka kafa tana biye. Bata so ya manta da dan uwanta akan layi. Da ya ce a miko wani abu sai tayi azamar yi duk don idan yazo kansu ya kyautata. Asabe tana tsaye rike da hannun Qibdiyya amma idanunta suna biye da duk takun Uwani. Sanda kwalla ta silalo mata ita kanta bata sani ba.

"Innayo bata yi asarar haihuwa ba" ta fada da raunanniyar murya.

Salihi ya gyada kai a inda yake tsaye yana kulawa da Munzali wanda bacci ya fara daukarsa. Uwani baudaddiyar mace ce. Shi kan shi bai taba zaton akwai ranar da zai ga tambarin mahaifiyarta a tattare da ita ba. Indai mara kirki wanda ya amsa sunansa mutum yake nema to lallai in yazo kan Uwani ba zai matsa ba. Zai ce ya sami abin da yake nema ne kai tsaye. Inama Innayo tana kusa ta ganewa idanunta.

***

"Mami zani Kano gobe in sha Allah"

Wayar da aka yi mata daga Kanon ta fasa amsawa ta kalli Lilu da sauri.

"Wani abin ne ya faru?"

"Ya Suhaib ne ya buge a kafa ba zai iya tuki ba"

"Kada ka boye min komai Lilu" ta furta cike da tsoro.

Murmushi ya yi kawai ya kira Suhaib a wayarsa ya bata. Da kansa ya fada iya abin da zai iya. Kofar daki ya daka ya bugu a kafar. Hankalinta ya dan kwanta amma ta san Suhaib da dauriya akan abin da yake ganin zai janyo mata damuwa. Ga Lilu kuma shi ma bata jin yana cikin nutsuwar jan mota shi kadai har Kano.

"Zan bika amma ka san ni ina son sammako"

Dage gira ya yi harda 'yar dariya "dan farin kuma Mami? Ai na zata za ki daure har ya iso gida"

" Fita ka bani wuri" ta ce ita ma tana dariyar.

Fitarsa keda wuya ta kira Alh. Tahir ta fada masa abin da ya sami Suhaib. Izinin tafiya ya yi mata. Ya kara da cewa shi ma jibi abu mai mahimmanci zai kai shi Kanon. Su jira shi sai su dawo tare.

Da ta ajiye wayar kwakwalwarta aikin tunani ta shiga. Lamarin 'ya'yanta yana matukar damunta. Kowa da irin tasa damuwar. Yanzu da tace tana son zuwa Kano bata ce ga dalilinta ba. Indai buguwa ce tabbas abu ne da zata iya jiran a dawo mata da Suhaib din gida. To amma zuciyarta ta gaza sukuni. Kanon dai take son zuwa.

BABI NA SHA BAKWAI.

Su Innayo basu san wainar da ake toyawa a gidan ba sai da suka dawo ita da Salima. Tambayar inda Uwani ta shiga ta yiwa Zara ta fada mata duk yadda suka yi har fitarta.

"Ban san me yake faruwa ba amma tana fita Asabe ma ta fita"

Dama da tunanin halin da ta bar Uwanin a gida ta wuni. Wannan labari sam bai mata dadi ba. Duban 'ya'yan nata tayi ta ce daya daga cikinsu ta kira mata Uwanin a waya. Salima ce ta kira da aka amsa ta mika mata.

"Ban hana ki fita ba Uwani?"

Fita tayi daga dakin da aka kwantar da Munzali don kada ta tashe shi daga bacci. Kofar ma a hankali ta rufeta sannan ta ce,

"Muna asibiti da Munzali an kwantar dashi"

"Me ya same shi?"

"Bayanin ba zai yiwu ta waya ba Innayo"

Muryarta babu wannan gadarar da ta saba da nuna isa. Kamar ma da sigar rarrashi Innayo take jin amsoshin Uwani. Da taji a wane asibiti suke sallar magariba kawai tayi ta sake tashi. Sai da Salima tayi da gaske wurin hanata fita bata ci komai ba. A lokacin ne ta fadawa Zara abin da ya faru da Ayaah. Suka gama jajantawa sannan suka fita zasu tafi asibitin. Wannan karon dai Zara sam taki yarda su barta a gida. Ciwon dan uwansu da zai kai Uwani asibiti ko biyanta zai yi ba abin rainawa bane. Innayo ta girgiza kai kawai don bata ga alamun zata ji maganarta ba suka tafi.

Basu wani sha wahala ba suka iso dakin da Uwani ta kwatanta musu. Mamakin ganin Salihi a wurin ne ya kama Innayo. Ya gaisheta da fara'arsa sannan ya bata kujerar da yake zaune.

Sai da ta zauna sannan ta kalli inda Asabe take tayi lakwas. Ta kira kannin Munzali namijin mai suna Bature akan yazo ya kwana amma kememe yaki. Uzuri mara tushe ya dinga bata. Dama rabonta da ta sanya shi a ido an tasarma sati. Da dai rabon kudi yake ba zai yi fashin zuwa. Ummakati kuma mijinta yace dare ya yi za su zo gobe, duk da lokacin da aka fada mata shida bata karasa ba. A gidanta autarsu mace ta tare saboda kwadayi. Gashi mijin Ummakati yana mata kulle. Sai abin ya shafi kanwar da ya kula tana yawo. 'Ya'yan Innayo mata wadanda kullum take aibatawa tare da yi musu kallon rashin galihu sune a tare da ita.

"Asabe ya mai jikin?"

"Da sauki, gashi ya sami bacci."

Dakin sai ya yi shiru tunda hirar kirki dai bata taba hada duka mazaunan cikinsa a lokaci guda ba. Uwani waya take yi da wata mai shara tana bata sautun irin abincin da za a siyo da adadin mutanen dakin. Jin haka Innayo ta ce,

"Mu kam a koshe muke"

"Sai a tafi dashi gida. Guda bakwai za ki karbo kinji" ta karkare wayar tana duban Qibdiyya wadda ke faman matse kafa.

"Kina jin fitsari ne?" Ta tambayeta. Da ka ta amsa don ta matsu sosai.

Tashi tayi domin ta kai ta sai Asabe ta riga. Dakin ya zame mata kamar akurki. Kwarjinin Innayo da zuri'arta yasa ta kara jin kanta kamar wata 'yar kora. Suna fitowa taji ance,

"Barka da dare Asabe"

Sakin fuska tayi da ganin fuskar da ta sani.

"Barkanmu dai dannan. Shiga ciki ga dakin da aka kwantar dashi."

Qibdiyya da ya gani tare da ita ya jefa tunaninsa a mizanin aune-aunen hanya mafi saukin bullewa. Babu bata lokaci kuwa ya cafki damar da ta zo gareshi da gaggawa.

"Ina zaki je ne?"

Hagu da damanta ta dinga kalla ta ce "wallahi inda zan sami piya wata (pure water) nake nema wai fitsari Qibdiyya take ji"

Dan waro idanu yayi "babu bandaki a ciki ne?"

"Ka san bangaren maza ne bai yiwuwa na shiga"

"Haka ne. To bari na dauko miki a mota"

Ya dan soma tafiya kenan ya tsaya.

"Qibdiyya zo muje ki rakani"

Wai aka ce tsaytsayi baya wuce ranarsa sannan mai halo baya fasawa. Asabe ta manta da halin da Qibdiyya take ciki har ta iya bari wani namijin ya tafi da ita mota. Sai da suka fara tafiya kawai taji kamar an sharara mata mari ta dawo hankalinta. Da gudu tabi hanyar da taga sun yi sai dai har ta isa wurin motocin babu shi babu alamunsa. Kin yarda da tunanin dauke mata jika tayi ta koma ta tsaya a inda ya barta tana jiransu.

Bata jima ba kuwa su Innayo suka fito. Uwani ce karshen fitowa tana yiwa Nos din da ta rakosu godiya. A ka'ida tun shida ya kamata 'yan dubiya su fita. Amma ganin dan uwanta ne shi ne aka barsu.

"Ina Qibdiyyan?" Zara ta tambayi Asabe tana gyarawa Salima goyon jinjirarta.

"Ina fitowa naga wani abokin Munzali. Shi ne ya ce zai dauko piya wata a motarsa"

"Abbati ne?"

Innayo ce tayi tambayar. Kafin ma ta karasa Asabe ta girgiza kai.

"Sunansa Shazali. Su kan dan zo gaisheni tare dashi jifa-jifa"

Sai suka tsaya aka koma shawarar zuwa a dauko kukunsu Munzali ya zo ya kwana dashi. Minti shabiyar, talatin, talatin da biyar...a daidai mintuna talatin da bakwai da tafiyar Shazali da Qibdiyya sai ga Abbati ya fado gabansu kamar an jeho shi.

"Ina Qibdiyya?"

*

Awa daya da rabi kafin zuwan Shazali asibiti gidansu Abbati ya fara zuwa. Rashin samun kowannensu a waya ya kawo shi gidan babu shiri. Kwana daya ya rage a lokacin da Comared ya bashi gashi ya kasa samun su. Yana zuwa maigida ya sanar da shi an kai Munzali asibiti. Hankalinsa kuwa ya tashi domin ya tabbata idan Munzali yana asibiti ba makawa Abbati ma yana can. Kenan ba shi da abin da zai tilasta musu zuwa don ko yafi kuda naci bai ga dalilin da zai raba Abbati da asibiti idan Munzali yana kwance. Wautar saurin tonawa Abbatin asiri da ya yi a wurin Baaba Mari ya gani. Ganin abubuwa suna neman rikice masa sai ya tambayi wani asibiti ne. Idan ya yi sa a suka fada tarkonsa na tsoron watsuwar sirrinsu a duniya kila ko Abbatin shi kadai ya je.

Kuku ne ya kira Uwani domin ya karbi nambarta kafin su tafi bisa umarnin Abbati. A wurinta ya sami kwatancen da ya yi masa. Babu bata lokaci ya nufi asibitin cikin gaggawa. Sai da ya kusa shiga ya dinga kiran Abbati amma ba a dauka. Ya san za a rina saboda abubuwan da suka shiga tsakaninsu. Bai damu ba ya shiga da niyyar yi musu barazana. Da shigarsa kuma ya hadu da Asabe shi ne ya canja shawara ya gudu da Qibdiyya. Sai da ya yi tafiyar minti goma sha biyar ya tabbatar ya yi nisa da asibitin sosai sannan ya turawa Abbati message.

(Idan kana son sake ganin Qibdiyya ka zo ka same ni a Guest house din Comared gobe.)

*

Kiran Shazali a wayar Abbati yafi goma amma yana sane yaki dauka. To me ya rage a tsakaninsu ma da zai sa shi yawan kiransa? Kunnuwan da yafi tsoron su ji irin gurbatacciyar sana'arsa sun riga sun ji. A tunaninsa babu wata sauran barazana da Shazali zai zo da ita wadda tafi tashin hankalin da ya gani a cikin 'yan kwanakin nan. Shi yasa yaki dauka domin alkawari ne sun bar shi har abada. Ba don son sanin halin da Munzali yake ciki ba ma da tuni ya kashe wayar tasa. Suna shigowa gari ya

sami adaidaita sahun da zai kai shi gida. A gurguje ya shiga ciki ya fada bangarensa da sallama.

Hanne ya gani tayi daidai a falo tana kallo. Sanye take da kayan bacci wadanda bashi da masaniya yau ta saka su ko tun na jiya ne. Kai ta dago ta ce masa sannu da zuwa ta cigaba da kallonta. A yau sai bai ga laifinta ba. Mutum irinsa ta yaya ma zai yi zaton cewa komai na rayuwarsa zai zo da sauki? In zai yi mata adalci ma a ganinsa ita din abar tausayi ce. Yana dai sauke hakkokinta dake wuyansa amma daga nan babu wata shakuwa ko soyayya. Laifina ne ya ce a hankali yayinda a zahiri ya tambayeta ya gida.

"Lafiya lau" ita ce amsar da ta bashi ta mayar da kai ga tv.

Bai tsaya a wurin ba ya karasa sama. Mukullin mota kawai ya dauko ya dawo ya ce mata zai tafi asibiti wurin Munzali.

"A dawo lafiya"

Daga nan bata kara cewa komai ba ta kuma mayar da hankalinta ga talabijin.

Zamansa ke da wuya a mota Shazali ya sake kira. Da yaga sunan tsaki ya yi. Sai kuma ya kula da shigowar text da sunan Shazalin. Budewa ya yi yana mamakin bakin naci irin na wannan mutumi.

Maigadi gani ya yi motar ta yo kansa gadan-gadan. Ihunsa ya dawo da Abbati hayyacinsa. Bai san ya saki hand break ba sai a lokacin. Cikin sauri ya tsayar da motar sannan ya leka da kansa ta taga.

"Bude min gate da sauri"

"Yallabai kamar bai dace kayi tuki a yanayin..."

"Na ce ka bude min!" Ya fada da tsawa. Gumi kawai yake yi yana kiran Shazali wanda a lokacin banda kyakyata dariya babu abin da yake yi.

"Shege ashe yana da hannun daukar waya"

Kafin yaje nasa gidan Abbati ya kira sau ashirin da 'yan kai. Ya tura text yafi goma. Shazali dai dariya kawai yake yi kamar mahaukaci. Ba gidansa da su Abbati suka sani ya nufa ba. Wani dan karamin gida yaje a wata unguwa da bata gama cika ba. Kafin ya fita daga motar ya turawa Abbati sako ya kuma kashe wayarsa a take.

(Aiki ne ya samu wanda yinsa ne kadai zai fanshi 'yarku. Idan kuma ka ki to ka kwana da sanin cewa ni Shazali zan sayar da ita ga duk wanda yake da bukata.)

A motar ma ya kulle wayar da Abbati yake da layin ya dauki sauran biyun ya watsa a aljihu. Ya fito ya zagaya inda Qibdiyya take bacci ya dagota yaga ta jike sharkaf da fitsari. Sau biyu kafin tayi baccin tana sake tuna masa fitsari take ji. Daga baya ta soma kukan kiran Paapa da Daddy da Asabe har bacci ya dauketa. Tsaki ya dinga yi da kananun zage-zage. Baya son harkar yara ko kadan. Ba don kada ta mutu a motar ba da a ciki zai kulleta ta kwana.

Haka nan ya sabata a kafada ya yi amfani da nasa mukullin ya bude gidan. Wani yaro matashi da bai fi shekara goma sha shida zuwa sha bakwai ba ya fito sanye da gajeren wando da fara'arsa zai tarbe shi. Ganin yarinya a hannunsa yaja tunga ya tsaya.

"Zo ka karbeta mana" Shazali ya ce dashi da dan fada-fada.

Yaro ya noke kafada harda buga kafa.

"Wallahi ba zan karbeta ba sai na tabbatar ba 'yarka bace"

Shazali ya yi dariyar jindadi ya mika hannu guda ya rungumo yaron a jikinsa yana bubbuga masa baya.

"Da mace da buhun siminti duk abu daya ne a wurina. Basu taba burgeni ba balle a kai ga sha'awa..." Ya kashewa yaron ido.

A falo ya kwantar da Qibdiyya suka shige daki shi da yaron suna dariya.

(Mai karatu wannan yaron dan wata makarantar kwana ne ta maza. Shazali ya jima kwarai da daina mu'amala da idon sani. Ya kuma fi son yaran da suke ganiyar tasawa. Bisa shawarar wani abokinsa a irin wannan harkar suke zuwa makarantun kwana suna biyan masu gadi ko malamai sai a fito musu da yara. Wani zubin washegari yake mayar dasu da sassafe. Wasu ma basa kwana. Amma wannan yaron tun haduwarsu gabanin hutun makaranta ya kasa rabuwa dashi. Dubu hamsin ya biya ya dauko shi ranar da aka koma hutu wato lahadi. Yana so ya kai wata lahadin sannan ya mayar dashi. A cewarsa ya yi kewar yaron.)

*

Wani irin ciwon kai ne ya kama Abbati yayinda ya fahimci da gaske Shazali ya dauke Qibdiyya. Ga Asabe a gefe ta soma kuka tunda taga halin da ya shiga ta san babu lafiya.

"Shi yaron ba abokinku bane?"

Amsar da zai bayar yafi kowa sanin cewa karya ce. Sai dai karyar ita ce cigaban rufin asirinsu. Yana bayar da amsa yana mai Allah wadai da sana'a ko dabi'ar da muninta zai sa mutum ya dinga karya da gangan.

"Abokinmu ne a baya. Rigimar kasuwanci ce ta hadomu. Ya cinye mana kudi ya kuma ki yarda mu hadu balle ya yi mana gamsashen bayani game da kudin. Shi ne muka yi masa barazana da zuwa kotu. Saboda yana so mu janye karar da zamu kai shi ne ya dauketa."

"Amma anyi lalataccen yaro. Na rasa gane inda duniyar nan take dosa damu" cewar Innayo ita ma tana share kwallar tausayin dauke 'yar karamar yarinya.

Salihi ya dafa kafadar Abbati ya ce "Zama bai kama mu ba. Muje a kai raport ofishin 'yan sanda"

A razane ya dubi Salihi. Shigowar 'yan sanda cikin lamarin nan a yanzu ba komai bane zai faru illa allura da za ta tono garma.

"Ya ce gobe naje na same shi tare da takarda mai sa hannu cewa mun yafe masa kudin. Idan ba haka ba zai sayar da ita. Ka bari naje tukunna mu gani. Idan ya saba alkawari sai mu nemi 'yan sandan. Yanzu ya kashe waya ne kawai saboda ya tayar mana da hankali sannan ba gidansa ya tafi ba."

Zukatansu ba duka suka yi na'am da shawarar Abbati ba. Sai dai kuma sun san cewa a yanzu ko masu satar mutane suna gaggauta cutar dasu ne idan suka fuskanci hukuma za ta damkesu.

Da wannan aka samu suka bar maganar haka. Abbati ya fadawa Uwani shi ne zai kwana da Munzali. Ya kuma jaddada musu mahimmancin iame bakunansu daga zancen abin da ya faru. In ya nemeta ace masa tana wurin Asabe. Hankalin kowa sai ya kwanta suka tafi gida ana tararrabin me zai faru washegari.

A gaban gadon Munzali ya tsaya yana kare masa kallo. Ya zabge sosai kamar ba shi ba. Gashi dai bacci yake yi amma ana iya ganin yadda fuskarsa ta tattare kamar wanda ya fada tunani mai zurfi saboda damuwa. Tausayinsa ya sake kama shi da ya tuna abin da aka yi mata da dauketa da Shazali ya yi. Iska mai zafi ya fesar ya fita daga dakin ya koma mota. Ya dauko abin sallah sannan ya sayi ruwa ya dauro alwala ya koma. Tashin hankali ya hana shi jin yunwa. Da ya idar da sallar dorawa ya yi da nafilfili cikin kankantar da kai da cikakken tawali'u. Addu'oinsa basu da yawa sosai. Istigfari ce yake ta yi domin neman gafarar Ubangiji gare shi da amininsa. Idan sun samu rabauta ya yi imani komai zai zo da sauki. Asirinsu zai rufu, iyayensu zasu yafe musu. Sannan Allah zai tsare Qibdiyya a duk inda take. Yayi nisa cikin ibadarsa yaji muryar Munzali tana fitowa a hankali.

"Ka yafe min ko zan sami sassaucin kunar dake raina."

Dago kai ya yi suka hada ido. Abin da ya gani a idanun Munzali ya bashi tsoro. Irin yanayin nan ne da zaka ga mutum bashi da maraba da mutum-mutumi. Total hopelessness and helplessness. Mikewa ya yi ya ja kujerar gaban gadon nasa ya zauna suna kallon juna. Munzali ya zauna ya jingina bayansa da bango.

"Ni kake cewa in yafe maka Munzali?"

Murmushin karfin hali ya yi da yaga kamar ran Abbati ya sosu ya ce

"To ko sai na durkusa?"

"Ka ajiye wasanka muyi magana. Me zaisa ka ce na yafe maka bayan ni da kai muka yi laifin kuma Allah Ya kamata mu roka gafara?"

Kodaddun idanun Munzali sai suka ciko da kwalla. Yana so ya yi magana ba tare da ya nuna karayarsa ba amma ya kasa.

"Ina ta rokon Allah gafara kamar yadda ka ce amma zuciyata tana raya min tubana ba zai karbu ba. Ga nauyin zunubina ga na lalata maka taka rayuwar daga zuwa karatu."

Rai a bace Abbati ya ce "dakata haka"

Girgiza masa kai Munzali ya yi yana murmushi wanda ya koma kuka kafin ya kai karshen maganarsa

"ka barni na karasa magana. Laifinmu yana da girma. Abin da aka kifar da al'umma guda a dalilinsa. Shi ne nayi silar fadawarka gare shi har muka mayar dashi sana'a. Wallahi zuciyata har kokonto ta soma akan amintarmu. Shin Abbati amincin Allah da Annabi ne tsakaninmu ko kuwa kazamar soyayya nake yi maka? So nake a shafe babina a doron kasa domin ban san waye ni ba. Da wannan nauyin kana tunanin

har ina da darajar dukawa gaban Allah in roki gafara? Baka ganin tun yanzu na soma ganin bala'i? Qibdiyya me ta sani a duniyar da har ..."

Abbati ma kwalla ya soma fitarwa yana ta girgiza masa kai don ya yi shiru.

"Ka daina irin wadannan maganganun Munzali kada kayi sabo."

"Sabawa Allah ai na riga nayi. Gashi yanzu ina jin kaina kamar mafi kaskanci a cikin halittun Sa. Idan na tuna kwanciyar kabari sai naji na karaya fiye da tunaninka. Abin da ya sami Qibdiyya bai min ciwo kamar tsoron mutuwata. Me zan ce da Allah?"

Wani irin kuka Munzali ya fashe dashi wanda ya janyo makotan gadonsa a dakin suka fara kallonsu. Abbati ya gama sauraron dukkan zantukansa sannan ya kama hannunsa na dama ya rike.

"Na rantse maka da wanda rayuwarmu take hannunsa gafarar Allah ta ninninka azabarSa. Sannan wadannan tunanin na banza da suke damunka ba komai bane illa wasiwasin shaidan. Idan ka bari rayuwarka ta kare a haka to tabbas zaka mutu cikin nadama..."

Munzali ya galla masa harara ya ce "a dinga tauna harshe idan za ayi nasiha don likita ya ce jinina ya mugun hawa"

Shi ma Abbatin hararsa ya yi yana jin kamar ya mangare shi ya ce,

"Gara ka tsorata kada kayi min sanadin rashin samun wuri a karkashin inuwar al'arshi"

Munzali sai ya yi kasake yana sauraronsa. Wannan ya bashi damar yi masa bayani gamsashshe.

"Tsahon lokacin da muke tare cikin sabon Allah kai shaida ne ina yawan karatu. Karatun ne ya taimaka min wurin kara fahimtar munin abin da tuntuni muka san haramun ne. Shi yasa na damu da son mu tuba. Amma kafin na cigaba da magana zan yi maka tambaya guda daya. Kana jin da bamu tuba ba za ka iya yin mu'amala dani Munzali?"

Wata irin zabura ya yi ya ce "A'uzubillah minash shaidanir rajim"

Abbati ya ce "to Shaidan sai a nemi wani gaulan wannan dai ya tsira"

Dole Munzali ya yi dariya. Abbati ya yi murmushi ya dora da cewa "Masha Allah. Abotarmu ta Allah ce ba ta shaidanci ba. Da ace zukatanmu suna marmarin haka a tsakaninmu to ina mai tabbatar maka tubanmu ba zai cika ba sai mun nesanta da juna kamar yadda Baaba ta fara bamu shawara domin samun nutsuwar zuciya"

Munzali ya hau ambaton "Alhamdulillah" da yaji wannan bayani mara wahala.

"Abu na biyu kuma mafi mahimmanci shi ne ka daina raina rahamar Allah. Ta yaya ma za ka dinga tunanin ba zai yafe maka ba bayan ya yi alkawarin gafara ga bawa idan ya tuba. Inda na karanta fa cewa aka yi zunubi ko ya kai kumfar kogi Allah zai yafe idan aka tuba."

Cikin rauni Munzali ya sake cewa "Amma gafarar ba sai ga wanda yaso ba? Idan bana ciki fa? Alfarmar wa zana hau a cikin mutane wanda zanci albarkacinsa har a yafe min?"

Abbati ya dauke duk wani burbushin fara'a a fuskarsa ya ce "in ka sake magana wallahi sai na bata maka rai. Ta yaya ina fada maka girman Allah kana dawo da hannun agogo baya? Tudun da za ka ci ya wuce na kasancewarka daya daga cikin halittun Allah? Ko kana tunanin akwai wanda Allah zai yafewa zunubai a dalilin aikin wani ahalinsa alhalin shi bai mika wuya da gaskiya ba? Tsarki ya tabbata ga Sarkin da yake yafewa bayi a kan kowane zunubi indai sun tuba. Munzali da za ka tuba yau gobe ka komawa zunubi ka sake tuba zai yafe maka (hakan ba yana nufin bawa ya

yi ta wasa da damar tuba bisa izgilanci da tunanin gobe ma za a yafe masa ba. Idan mutuwa ta wafce mutum a cikin halin sabo kafin ya tuba shikenan!). Kai..."

Ya tabo kafadar Munzali domin ya sami cikakken hankalinsa a tare dashi "akwai wani sahabi kuma surikin Annabi SAW mai suna Abu Sufyan. Ko ka san irin taskun da suka sanya musulmi kuwa? Yana cikin jagororin yakin musulunci na farko wato Badar. Matarsa kuma a yaki na biyu (Uhud) ta hayi wani ya kashe mata kawun Manzon Allah SAW. Kawunsa fa wanda yake matukar so. Sunansa Hamza. Kuma bayan an kashe shi aka ciro mata hantarsa ta tauna. Sannan ta lalata gawar ta hanyar yayyanka sassan jikinsa. Da Allah baya yafe laifuka da bai basu damar karbar musulunci ba duk su ukun."

Zaro idanu Munzali ya yi "sun musulunta?"

Abbati ya gyada kai "da Abu Sufyan din, da matarsa (Hind bint Utbah) da wanda ya yi kisan (Wahshi ibn Harb) na dai manta sunayensu. Amma wallahi duk sun shiga inuwar musulunci kafin su bar duniya. Sahabbai ma suka zama tunda sun rayu da Annabi SAW. Duk sahabi daya kuwa darajarsa ta ketare tamu akan kowane aikin ibada."

"Allahu Akbar" cewar Munzali da wani irin shaukin fahimtar addininsa.

"Dalla can. Sau nawa ina kawo mana littafin tarihi kana kin karantawa sai aukin danna waya?"

"To ai dai na daina. Ni islamiyya ma zan shiga wallahi."

"Zamu shiga dai. Kaga irin wannan kambana girman zunubin da jin kamar baka da rabo ba komai bane illa aikin shaidan. So yake mu dauwama a zunubi. Idan muka tashi tuba kuma ya nuna mana kamar laifinmu yafi karfin a yafe mana. Kaga imani sai ya sami rauni. Muje lahira ..."

"A tutar babu" Munzali ya karasa masa.

Maimakon su kwanta sai suka koma tattauna abubuwan da suka danganci laifi da tuba. A nan ne Abbati ya sake fayyace masa kowane bawa da aikinsa zai dogara ba kusancinsa da waliyyi ko asharari ba. Ya bashi misali da tarayyar Fir'auna da Asiya Allah Ya kara yarda da ita. Ga Annabi Nuhu AS da Annabi Lud' AS da matansu wadanda Qur'ani ya tabbatar mana cewa 'yan wuta ne.

"Duk da haka amma fa musulmi masu imani suna cin darajar juna indai kowannensu ya yarda Allah da zuciya daya. Misali wanda dansa ya mutu kafin shekarun balaga indai yayi hakuri akwai sa ran dan zai cece shi (ina kara mika ta'aziyya ga Ummu Sadiq da Ummu Abdurrahman na Sparkling, Sanah Matazu Fikra da Halima Siyama H2H da duk wadanda suka rasa 'ya'ya. Allah Yasa rashin da muka yi masu ceto ne a garemu) , ko idan kana da d'a hafizin al-Qur'ani zai daga darajarka a aljannah. Sannan Allah zai bawa wasu ceto ranar lahira"

Bakin Munzali a bude har Abbati ya gama magana sannan ya ce "to wai ni ina ina ka tara wannan ilimin? Wallahi ganinka nake kamar wani shaihin malami."

Dariya babu shiri ta kama Abbati ya ce masa "Allah Ya shiryeka. Babu bashin salloli akan ka ko?"

"Akwai wallahi" ya amsa yana mai jin kunyar kansa.

Da taimakon Abbatin ya shiga bandaki ya yi alwala. A zaune ya gabatar da sallolinsa ya jima yana neman gafarar Allah. Sa'annan ya hada da godiya da Ya hada shi da Abbati. Lallai a cikin abota akwai riba idan an dace. Kuma masu cewa zama da madaukin kanwa yana kawo farin kai basu yi kuskure ba. Halin da ya tsinci rayuwarsa ya yi jirwaye a rayuwar Abbati. Yanzu kuma an zo wakafin da halin rayuwar Abbatin zai wanke musu duka jirwayen.

Karatu ne ya kawo Abbati Kano kuma cikin kudurar Allah Ya samu ya yi. Babbar illar da ya samu ita ce ta rashin idon mafadi da rashin kulawar iyaye a shekarun da ake bukatarsu. Allah Ya hada shi da mutum mai saukin kai da tausayi irin Munzali. Da ace Munzali ya tashi da kulawar iyaye tabbas da an yi bawa mai yawan kyautatawa na kasa dashi. A cikin halin kuruciya da rashin ilimin da iyaye suka barshi ya iya

janyo almajiri jikinsa. Ya nuna masa sana'ar da yake yi domin yaci abinci. Sannan bai taba yi masa hassada ko kyashi ba. Wannan rayuwar bata hana Abbati cigaba da karatunsa ba wanda zamu iya alakanta shi da yawan addu'ar da mahaifiyarsa take yi masa da nasiha. Shi ne yaja hannun Munzali zuwa makarantar yaki da jahilci. A gefe guda yana ta bibiyar duk wani littafin da ya danganci addini wanda zai iya karantawa. Zuciyarsa bata nutsu da sana'arsu ba sai dai kuma a lokacin bashi da karsashin son su barta ko don kudin da suke samu. Munzali bai taso da akidar karatu daga wurin uwa da uba ba shi yasa baya ma mararin karanta irin litattafan Abbati. Ashe zasu yi musu rana. Ashe abotar irin wadda ake fatan ta kai ma'abotanta karkashin inuwar al'arshi ce.

Da ya shafa addu'arsa bacci Abbati ya tilasta masa yi. Yana son jin bayani game da fyaden da aka yiwa Qibdiyya sai dai dan saukin da Munzali ya samu yana bukatar a tattala shi. Tambayar damuwa za ta dawo masa da ita. Haka ya hakura sai dai har gari ya waye bai rintsa ba. Yana ta faman tufka da warwara akan yadda ya kamata ya fuskanci Shazali.

***

Alh. Rabi'u ya dawo gida daga wurin da suke buga karta da abokansa shadaya da rabi na dare. Innayo dama ba kwana gareta ba. Babbar rigarsa ya cire ya nufi bangaren Asabe. Kudi yake so a wurin Munzali ya kasa samunsa a waya. Ba za a rasa wani abu a hannun Asabe ba ko yaya ne. Shi ne ya taho da dan kunshin tsirensa ya kai mata. Ko kallo ledar bata isheta ba har ya ajiye. Rashin kulawarta ya bashi mamaki domin ko mage bata fita jin kamshin nama ba. Ledar ya kama ya shiga kwancewa yana 'yar dariya.

"Hala mura kike baki ji yadda kamshin tsiren nan ya cika dakinki ba. Nace wai ina Munzali ne kwana biyu"

A hautsine ta kalle shi da jajayen idanunta tana kada kai.

"Ga mayya ba. Ai dole in juyo tunda maigida ya kawo nama"

Ledar ya dire ya kare mata kallo a tsorace sannan ya ce "wani abin Innayo tayi miki?"

Asabe bata amsa ba sai ma juya masa baya da tayi. Da ya san yadda zuciyarta take a jagule da ya fita ya bar mata dakin. Shi kuma a wautarsa sai ya zata da gaske Innayo din ce.

"Ai kuwa yau daga ita har wadancan zaurawan da ta tara a dakinta ba za su kwana lafiya ba."

Hanyar fita yabi Asabe ta tashi tayi saurin dakatar dashi da taji ya fara kiran sunan Innayo.

"Dakata min Malam don wannan hargagin naka ba zai burgeni ba. Innayo kuma da kake magana da taron zaurawan dakinta a yini guda sun yi min abin da baka taba yi min ba a iya tsayin shekarun aurenmu. Duk wanda ya damu da naka ba don abin hannu ba shi ne cikakken masoyi."

Kirjinsa ya shiga nunawa cike da kokonto yana cewa "dani kike Asabe?"

Dama can zuciyarta tana wuya. Wannan borin kunyar nasa sai ya kara tunzurata. Da yatsa ta nuna shi tamkar dan cikinta.

"Da kai nake Rabi'u. Da kai nake sako tumaki ballo jakai."

Tas ya dauke fuskarta da wawan mari yana huci.

"Ni kike zagi a cikin gidana?"

Ita kuwa rike kumatu tayi tana kuka ta ce,

"An zageka din. Wannan ginin kuma billahillazi ba gida bane. Gida ai inda miji da mata suke tattalin 'ya'yansu ne. Nan kuwa bashi da maraba da bariki gidan ka zo na zo. Gara ma Innayo tana yiwa 'ya'yanta. Amma da yake jini baya karya ai bata fara jindadinsu ba sai da duniya ta koya musu hankali. Sun so gadon bakin hali a jikinka ba don Allah Ya tarfawa garinsu nono ba."

"Wai Asabe ko kin fara shaye shaye ne?"

"Zancen kake so kuma zan yi maka shi filla-filla. Munzali yana kwance a gadon asibiti. Jiya ya yi min wasu zantuka da na kasa fahimtarsu amma sun yi matukar razana ni. Sannan wani dan iska ya yiwa Mariya fyade kuma an saceta ma amma duk halin da muke ciki babu wanda yaji a ransa wai ya kamata a sanar da kai. Saboda me?" ta sake nuna shi da dan allinta "saboda kai da babu sammakal. Amfaninka daya a gidan nan shi ne ka yiwa mace ciki ta haihu..."

Tunda suka fara rigimarsu Innayo, Salima, Zara da Uwani suka yi shiru suna sauraronsu. Kalmar Asabe ta karshe ta janyowa Zara da Salima harma da Innayo muguwar kunya. Su biyun suka tashi suka shige daki da dimbin mamakin fyaden Qibdiyya. Uwani kuwa ko gezau ta cigaba da zama tana kallon yadda Innayo ta takura. Kofar dakin da su Salima suka shiga tabi da ido ta ce,

"Ai ba karya tayi ba duk suka wani watse don munafunci."

Innayo ta kada kai ta ce "Uwani kenan"

Ta kuwa yi kicin kicin da fuska "to banda sunansa da muke karawa a gaban namu akwai wata riba ne?"

Kafin ta dauko abin da zai karasa kunyata ta sai ta tambayeta ko tana da masaniya game da abin da Asabe ta ce ya sami Qibdiyya.

Nan da nan fuskarta ta canja kuwa. Al'amarin da ya faru tun zuwanta gidan na farko ta labartawa Innayo. Bayan ta gama gani tayi Innayo din tayi ajiyar zuciya amma bata ce komai ba.

"Kin san wani abu ne akan abin da ya same shi?"

Da hanzarinta ta girgiza kai "ko kusa. Kawai dai ina rokon Allah da Ya kawo mana komai cikin sauki ne"

Uwani bata gamsu ba ta ce "amma na fada miki cewa ya dinga yi ta yafe masa wai laifinsa ne"

"Duk iyayen da suke kaunar 'ya'yansu suna dorawa kansu laifi ne idan wani abu mara dadi ya faru dasu." Ita ce amsar da Innayo ta bata. A fuska kuwa kana iya gane zancen ya tayar mata da hankali fiye da yadda take son nunawa.

Mikewa Uwani tayi ta dan bata rai "da yake ba su Hasiya bane sai nema kike ki katse 'yar hirar da na samu kina yi dani." Tayi hanyar daki "Bari naje na mike bayana yau na sha tsayuwar aikin lada. Allah Yayi mana albarka."

Innayo bata san lokacin da ta tuntsire da dariya ba. Uwani tayi kasake tana kallonta. Abin sai ya taba mata zuciya fiye da zatonta. Ji tayi kamar an tsikareta a kahon zuci. Bata san tayi kewar fara'ar mahaifiyarta ba sai yau. Yaushe rabon da taga ko murmushi ne daga Innayo akanta?

Bayan ta gama dariyar ta ce "Allah Ya bada lada Yayi albarka".

Kafin Uwani ta sami damar magana ta tashi ta shige bandaki. A ciki ta share wata kwalla ta bata ma san ta taru a idanunta ba sai yanzu. Da a wuri mai tsarki take tabbas babu abin da zai hanata sujjadar godiya ga Allah. Bayan shekaru masu yawa ace wai ita ce take hango yunwar mahaifiya a idanun Uwani. 'Yar da tasa kafa ta take duk wani kusanci dake tsakanin uwa da 'yarta. Uwanin da take nuna mata kyama kirikiri saboda ta sami abin duniya. Kaico! Duniya abar banza. Dan adam ya

yi ta daga kafada yana nuna izza a doron kasa. Lokaci guda Allah Yana nuna masa iko sai ya yi lakwas. Tana son furtawa Uwani kalmar yafiya sai dai tana tsoron kada a koma gidan jiya idan duniyarta ta sake zukar iskar wadata.

Wanka tayi amma har ta fito tunanin rayuwa bai barta ba. Munzali da Qibdiyya ne a ranta fiye da komai. Bata son fadawa kowa ne amma ta dade da dora alamar zargi akan sa. Yaron da bai yi boko ko islamiyya ba sai yawo cikin unguwa ace lokaci guda ya yi kazamin kudi. Tabbas da dan cikinta ne da ta jima da kwankwasarsa akan sana'arsa. Shi kuwa yanayin gidansu yasa ta kame bakinta. Tun da ta taba magana Asabe ta ce ta saka masa ido ta janye jikinta. Banda Allah Ya taimaka da kansa ya sake waiwayo ahalinsa da yanzu haka zai shiga halin nan shi kadai. Dalili mai karfi ne zai sa ya ambaci fyaden Qibdiyya a matsayin laifinsa. Kamar Baaba Mari sai gashi ita ma tana tunanin ko sata yake yi.

BABI NA SHA TAKWAS.

A gidan Innayo ita da 'ya'yanta sun yi sammakon tashi domin hada abincin asibiti. Gabadayansu 'yan dakin babu wadda tayi baccin kirki saboda batan Qibdiyya. Duk sun matsu da son ganin an dawo da ita lafiya a yau kamar yadda Abbati ya sanar dasu. Asabe da Alh. Rabi'u kuwa tun rigimar da ta barke tsakaninsu da daddare babu wanda ya kara jin duriyarsu.

~Gidan Mami Khadija kuwa ita da Lilu tare da Farha ne a mota suke shirin tafiya Kano. Sai da gari ya waye su Sauda na shirin tafiya makaranta sannan Mami ta ce da Farha ta shirya. Basu da niyar kwana sai dai ita tafiya ta Allah ce. Shi yasa suka dauki kaya na kwana dai-dai koda bukatar hakan zata taso.

~Baaba Mari ta tashi da karfin jiki a yau har taji zama ba nata bane alhalin Abbati da Munzali suna cikin wannan yanayi. Bata ma da labarin dauke Qibdiyya amma taji zancen kwanciyar Munzalin a asibiti. Garin Allah na wayewa ta nemi izinin Mal. Inuwa. Da ya so hanata saboda yanayin jiki sai ta dage ba za ta iya zama ba. Muryar Munzali a lokacin da ya fada mata abin da aka yiwa takwararta da ma rokon gafararta da yayi suna ranta. Tare suka shirya domin lokacin sakar mata ragamar 'ya'ya ita kadai ya riga ya wuce. Makauniyar biyayyar da yake yiwa Mal. Sa'idu bata yi masa rana ba. To kuma sai Mal. Sa'idun ma ya ce zai je. Haka aka fito dashi ba yadda yake ya zauna a gaba da yar sandarsa.

*****

Damuwa ce karara a fuskar Zakiyya lokacin da ta tashi daga bacci. Irin baccin nan rabi da rabi wanda kusan duk abin da ake yi a kusa da mutum zai ji tayi. Ba komai ya haddasa mata wannan rashin kwanciyar hankali ba sai rashin dawo da Qibdiyya da Munzali ya yi. Indai ba lokacin hutu ba a ka'ida bata wuce lahadi idan tana wurinsa. Hutun da ya wuce da bai zauna a gari sosai ba da kansa ya maidota kafin a koma makaranta. Sai kuma daukarta da Abbati ya yi ranar Juma'a. Tunda kowa ya san litinin za a koma makarantu ta zata zai yi aiki da hankali. Daren lahadi tunda aka yi isha take kiransa shiru baya dauka. Litinin ma haka. Yau gashi talata. Me yake nufi?

Tana can duniyar tunani bata ji shigowar Ummansu ba sai da ta kai mata duka a kafada.

"Raba kanki da yawan tunani tun da kananun shekaru ba alkhairi bane" ta sami wuri kusa da ita akan gadon ta zauna sannan ta cigaba da magana "wai akan rashin dawowar Qibdiyya ne kika kasa baccin safen naki na jaraba?"

Kwabe fuskarta tayi ta ce "Umma daga cewa zata kwana biyu sai in ji shiru sannan yaki daukar waya?"

Maganar haushi ta bawa Umman ta ce "tunda dawa ta tafi ai dole ki tada hankali."

A sanyaye Zakiyya ta ce "ba haka bane. Kinsan makarantarsu da tsauri. Yanzu sai kiji ana cewa za a maye gurbinta da wani dalibin idan bata dawo ba."

"Na dauka don Allah kika damu da ita ashe don tijarar makarantarsu ne. To Allah Ya kyauta. Kin bi kin sakwarkwace daga haihuwa daya. Babu wani kulawa sai aukin hada lanci bus (lunch box) a kai yarinya makaranta." Ta mike tana tabe haki "Sai ki sake kiransa ko ita Yaya Asaben don ni dai babu wanda zan nema."

"Umma na sakwarkwace fa kika ce?" Zakiyya ta ce a shagwabe.

Da fada Umman ta karanto mata abin da yake damunta wanda a karshe ta kai ta daga murya sosai.

"Yo sakwarkwacewa mana. Da kina da kula sosai akan abubuwa amma yanzu idan kika fara danna waya da kyar kike tashi sallah. Kin bari ta namaye miki rayuwa baki da katabus kan lamuran rayuwarki. Yarinya daya ba don ina gidan ba ni ban san yaya zaki yi da ita ba. Maganar gaskiya ko yau Munzali ya yi aure ya bukaci 'yarsa wallahi ko ba kya so sai na bashi. Kulawar da take samu in taje hutu ta ninka taki kuma kema kin sani. Shi ne zaki wani dami mutane don ta kara kwanaki don wawanci? Mtsewww"

Fadan Umman bai karawa Zakiyya komai ba face sake shiga rudani. Tabbas tafi kowa sanin yadda taja baya wurin kula da 'yarta. Mafarkinta na jiya ya sake dagula mata lissafi. Ganin Qibdiyya tayi a yanayi mara dadi har tana neman taimakonta. Anya idan ta cigaba da zama ba za ta amsa sunan sakarai bayan wawiya da Ummanta ta kirata a cikin fada ba? Da wannan tunanin ta mike a gurguje tayi wanka ta shirya.

"Sai ina kuma?" Cewar Umma ba tare da ta sakar mata fuska ba.

"Gidan zanje in daukota"

"Yanzu ba za ki bari ya dawo da ita don kansa ba?"

"Umma gara inje dai. Daddy zai kaini"

Cikin minti goma sha biyar Daddy da Zakiyya suka dauki hanyar gidan Munzali.

***

Alh. Sadisu Nakano rikakken dan bangar siyasa ne wanda ya iya takunsa a wajen iyayen gidansa. Da abin da ya dinga tarawa a jikinsu ya hada jarin da ake yi masa kasuwanci kala kala. Duk fadin Kano babu wanda zai ce bai taba jin sunansa ko labarinsa ba. Yana da baki kamar reza. Idan ya sako mutum a gaba to kashinsa ya bushe. Idan yana yi da kai kuma da wuya ka fadi takara ma. Da karfin cin tuwo ya mayar da kansa uban 'yan siyasa da 'yan jagaliyarsu a Kano. Mutum ne shi wanda baya yafiya, komai daren dadewa sai ya fanshe idan aka yi masa laifi. An alakanta shi da muggan laifuka iri iri wadanda suka hada da safarar hodar ibilis da yankan kai saboda kudinsa da k'aurin suna. Gashi bashi da tsoro ko digo. Kai har cewa aka yi ya taba sawa an dauko masa gwamna cikin dare ya yanka masa warning akan wani kuduri da ya sabawa aikinsa. Jita jita mara dadi kullum cikinta yake. Wata gaskiya ce wata kuma ana kara gishiri. Duniyarsa dai tana garawa yadda yake so ta kowane fanni illa lamarin zuri'a. Dansa daya mai suna Abdul. Yana ji dashi kamar rai. Matansa hudu amma ta biyun ce ta haife shi. Sai dai wani abu na ban mamaki shi ne duk irin kishin gidan gabadaya matan suna kaunar Abdul. Kowacce tana kokarin faranta masa ko don gyara fadarta a zuciyar maigida.

Saboda yanayi na sa ido daga abokan hamayya a dalilin karatowar zab'e da rashin tsaro Alh. Sadisu ya dauke Abdul daga makarantar da yake ya mayar dashi zuwa wata 'yar kadaran kadahan ta kwana. Masu matsayi irin nasa a jam'iyun gaba suna neman sako shi a gaba ta hanyar dansa. Duk wata yana bayar da kudi mai tsoka domin a kula masa da gudan jininsa. Burinsa ya kai shi waje da zarar ya gama sakandire.

A makarantar aka sami wadansu fitinannu suka koyawa Abdul mummunar dabi'ar luwadi. A nan ne kuma malamai marasa tsoron Allah da hadin bakin maigadi suke sana'ar tura kyawawan samari masu wannan hali wurin shaidanun mutane a waje. A takaice dai, Abdul Sadisu wanda aka boyewa inkiyar Nakano yana gidan Shazali!

A washegarin da Qibdiyya ta kwana a gidan shashancin Shazali ta tashi ne da kuka. Ta waiga hagu da dama bata gane inda take ba ga sanyi sanyin safiya sai ta fara kiran iyayenta.

A lokacin Abdul ya fito daga wanka kenan. Falon ya fito ya sameta a bakin kofa tana bubbugawa da karfinta. Sai ta bashi tausayi. Ya san ba huruminsa bane yin bincike akan duk wani abu da ya shafi personal rayuwar Shazali. Duk da haka sai yaji ba zai iya dauke kai daga yarinya karama irin wannan ba. Me ya hadata da Shazali har ya kawota gidansa?

Nufota ya yi da dan murmushi ya ce "Zo, ya sunanki?"

Ai tana juyawa da ta ganshi da tawul a kugu sai ta firgice fiye da ganin kanta a bakon wuri. Uncle Daddy ne ya fado mata a rai taji tsoron ko shi ma abin nan yake shirin yi mata. Da yaga yadda ta tsorata sai ya yi nufin tuntubar Shazali domin a bata koda shayi ne tasha. Yana kawo kai yaji wayar da shi kanshi ta kada masa ciki har ya kasa motsi.

*

Comared yana kwance tsakanin 'yan mata biyu yaji kiran Shazali. Rabonsa da gidansa yau kwana uku. Ya sanar da matansa ya tafi Lagos aikin sati daya. Basu san yana garin a guest house din da kalilan ne suka san da wanzuwarsa. Muryarsa a shake kamar basamuden kwad'o ya ce,

"Shazali ya ake ciki?"

"Comared an samu sai dai ina rokon idan da hali yazo ayi yau dinnan kawai. Da kyar na sami kan mutum daya daga cikinsu don sai da na hada da dauke musu yarinya"

"Dauke 'ya kuma Shazali? Nifa bana son abin da zai je ya dawo gareni."

Shazali ya yi dariya ya ce "kada ka damu. Akwai tamu dasu ne. Yarinyar ce kadai tikitin samun hadin kansu. Da azahar zamu zo."

Comared ya shafa kurcin cikinsa yana dariyar shakiyanci.

"Idan bai sami zuwa ba ni ka kawo min yarinyar na dana mana."

"Comared bata fi shekara shida ba fa"

"Irinsu sunfi...kai dai kawai nayi shiru. Ni dai ina so"

"An gama. Zan kawota indai bai zo ba. Amma sai dai daga wurinka a san inda za ayi da ita don babu hannuna kuma."

Jikin Abdul ya yi mugun sanyi da ya fuskanci girman abin da ke gaban Qibdiyya. Kafafu babu kwari ya koma da baya da sauri ba tare da ya shiga dakin ba. Bai san tun tsayuwarsa Shazali ya ankare dashi ba. Da ya fito ya kusa dariya ganin Abdul ya firgice a kokarinsa na son basarwa, shi a dole bai ji komai ba. Duk yadda yake son yaron dole ne ya dauki mataki a kansa tunda har ya san gidansa. Da niyarsa yace masa tsintota yayi kawai a bar maganar a haka.

***

Bayan Alh. Tahir ya gama waya da Comared bashi da zabin da ya wuce bin hanyar Kano a yau dinnan. Bayani daya aka yi masa shi ne cewa yau da yamma mutumin da zai zo suyi abin zai yi tafiya zuwa wata kasa. Shi kuma Comared a cewarsa wai shi kadai ya sani wanda zai rike musu sirri a kankanin lokaci. Sannan tunda shi din bai saba ba dole aka nemo masa kwararre. Har zuciyarsa yake kyamar wannan abu to amma idan ya tuna da kalaman mahaifiyarsa akan auren Yumna sai yaji wani irin kwarin gwiwa. Ko ta wane hali sai ya kifar da maganar aurenta sannan yaci mata mutumci akan wulakanta shi da tayi a gaban 'ya'yansa. Allah wadaran bariki. Banda haka me zai sa yarinyar da take durkusawa har kasa ta gaishe shi ta koma abokiyar sa'in'sarsa? Har ta kai yana fada tana fada. Yau da ta halali ya nemi aurenta komai son da yake mata ya san dole ta bashi girmansa na mijinta kuma sa'an uban da ya haifeta.

Suna hanya da direbansa ya kira Mami Khadija ya fada mata aikin da zai yi a Kano ya dawo yau. Zai fara zuwa duba Suhaib da sun shigo gari sannan ya wuce. Tana jiran ya fara ajiye wayar bayan tayi musu fatan sauka lafiya su duka sai taji ya fara cigiyar 'ya'yansa.

"Bani su mu gaisa" ya tambaya da dan jin nauyi.

"Lilu yana tuki, Farha kuma tayi bacci" ta kashe wayarta bata jira taji me zai ce ba.

Su biyun duka sai suka juya bayan motar inda take zaune ita kadai suna kallonta. Ta dauke kai abinta ta lumshe idanu tana 'yan tunane tunanen da suka zame mata jiki. Idanunsu da ta dinga ji jifa-jifa yasa tayi dan murmushi ta bude nata a kansu. Ba shiri suka mayar da kallonsu gaba lokaci guda.

"Lilu rami kake son tura mu ne kake kallon baya haka?"

Kai ya shafo da 'yar dariya "wane ni in kai Ya Farha rami saurayinta yasa a kulleni?"

"Dama ka gama raina ni shi yasa ka rasa amsar fada sai wannan" cewar Farha tana kai masa duka shi kuma yana karewa.

"Bana son ganganci ana tuki."

Nutsuwa suka yi na dan lokaci kafin Lilu ya soma magana.

"Wai Mami musulunci ya wajabtawa mata zama da miji mai bin mata ne?"

Gaban Farha ya fadi da tsoron kada Mami ta zata ita ta sanar dashi abinda ta sani. Ta kalle shi ta kalli Mamin a fakaice. To shi ma din bakinsa ya rufe da hannu saboda shirmen da yake tunanin ya yi na maganar a gaban Farha.

Yadda suka koma kallon kallo suna tuhumar juna da ido sai kawai Mami Khadija ta ce "don Allah ku rike sirrin nan kada ya kai kunnuwan Sauda da Mardiyya. A kalla ko su biyu ne a samu su dore da yiwa mahaifinku kallon nagartaccen uba."

"Ya Suhaib ya sani?"

Farha ce tayi tambayar sai dai kafin ma taji amsar Mami ta fahimci ya sani din. Biri yayi kama da mutum. Tsahon lokaci suna mamakin rashin shakuwar babansu da babban wansu duk yadda Abban yake da jan yara a jiki. Abin ya dade yana damunsu. Ashe ba a banza ruwa ya yi tsami ba.

Tunda Mami Khadija ta rufe ido bata kara cewa dasu uffan ba. A tunaninsu tayi bacci ne shi yasa suka fadawa juna abin da suka sani. Farha harda kwalla. Tana jinsu suna ta maganar mutum mafi soyuwa a garesu a 'yan kwanakin baya da sigar kyama da bakinciki. Me yafi wannan tashin hankali da ciwo a wurin uwa? Ashe zaman da iyaye suka tursasata ake yi masa kallon rufin asirin miji fanko ne? Da ta bar gidan sun yi nesa dashi da matukar wuya su san halinsa. Ko sun sani ba zai musu ciwo kamar yanzu ba da suke rayuwa tare suna yi masa kallon nutsatstse. Da karshenta yana nan da darajarsa ta uba.

Duk lalacewarsa mijinta ne shi dai uban 'ya'yanta. Babu yadda za ayi uwa tayi maraba da raini ko tsana ta gifta tsakanin mijinta da 'ya'yansu. Uwaye da dama sun sadaukar da manyan burikansu domin 'ya'yansu su tashi a happy home. Ayi ta jure mugun halin miji domin kada gurbin mahaifi ya sami tawaya a rayuwar yara. Ita dai sadaukarwar bata yi mata rana ba. Amsa sunan matar fasiki mai gadara da sab'on Allah ba hakuri bane....!

(Ya Rabbi kada Ka jarabcemu ko mazaje/matayenmu da alfasha. Wadanda Ka hada da fasikai Ya Allah Ka basu ikon daukar matakin da zaka yi farinciki dasu rana gobe kiyama. Amin)

Hukunci ta yanke a take a zuciyarta. Wannan karon babu gudu babu ja da baya.

***

Karfe bakwai Abbati ya gama kimtsa dan abin da ba a rasa ba mallakinsu a dakin asibitin. Munzali ya kafe kai da fata ba zai kuma kwana ba. Jinyarsa ta ruhi ce ba gangar jiki ba. Idan zai sami nutsuwa a zuciyarsa babu abin da zai hana lafiyarsa dawowa.

Sai shadaya da kwata da likitoci suka zo round aka sallamesu. Tare suka tafi gida da Innayo, Salima da Uwani. Sai kuma Salihi wanda shi ma da wuri ya iso saboda kwana da suka yi da fargabar halin da Qibdiyya take ciki. Asabe bata zo ba suna gida ita da Zara saboda Abbati yace ta zauna a gida a matsayin tana kula da Qibdiyya.

Da suka fito zasu tafi ya kasance inda Abbati ya ajiye motarsa da tazara da inda Salihi ya aje tasa. Abbati sai ya ce su Innayo su shigo motarsu. Idan gida zasu koma zai kai su. Baya suka fara shiga sai ga Salihi ya zo bangaren da Uwani take ya yi mata magana.

"Muje ina son magana dake."

Tsuke baki tayi sai da Innayo ta leka tayi mata kallon da ya sanyata bin sa babu shiri. Munzali yana fama da kansa amma hakan bai hana shi yin dariya ba.

"Wai ni Uwani yaji tayi ne kamar wata karamar yarinya?"

"Kaima ka fada Munzali. Sai kun taru kun sauke mata Al-Qur'ani izzu sittin ina jin."

Dariya aka sake yi yayinda Abbati ya tayar da motar suka wuce gidansu kai tsaye. Munzali ya tambaye shi me zai hana su fara sauke su Innayo maimakon yaje Rijiyar zaki sannan ya koma Dala. Motar sai tayi dif na takaitaccen wa'adi kowa yana tunanin amsar da ba za ta fallasa abin da suke kokarin boyewa ba. Abbatin ne ya amsa masa da cewa zai taho da Asabe dasu Ummakati tunda basu sami zuwa asibitin yau ba. Cike da farincikin hangen nesan amininsa Munzali ya yarda da amsar har ma ya murmusa.

Da isarsu gidan bayan maigadi ya bude gate suka ga mota a ajiye a kusa da bangaren Munzali. Su Innayo basu shiga cikin gidan ba amma Abbati ya bi bayan Munzali har cikin falo. Zaune a ciki kuwa ba kowa bane illa Daddy da Zakiyya suna gaisawa da Kande mai kula da Qibdiyya. An janyo centre table gabansu inda Kuku ya ajiye musu kayan motsa baki.

Daddy yana shan juice sai wani gadara da fizgar kai yake irin na matasa masu zafin kai ko gaishe da maigidan bai yi ba. Abbati kuwa gabansa ne ya buga sosai har sai da ya dafa kujera yana mai fargabar ko Shazali ya nemi Zakiyya ne.

Munzali bai bi ta kan Daddy ba don sam baya son girman kan yaron. Amsa gaisuwar Zakiyya ya yi tayi masa sannu da jiki tunda taji labarin rashin lafiyarsa a wurin masu aikin gidan.

"Amma dai bana jin dubani kika zo yi ko?" Ya tambayeta bayan ya zauna.

Abbati ya cigaba da tsayuwa a bayan kujera yana jiran jin amsarta. Maganar da Zakiyyan tayi masa maimakon amsa tambayar Munzali kusan kara tsorata shi tayi.

"Abbati ina kwana? Ya wajen Hanne?"

Bakinsa yana sarkewa ya ce "lafiya kalau"

Dan dukar da kai tayi saboda jin kunyar rashin hakurinta da zargin wani abu ta ce "dama naga har an koma makaranta ne baka dawo da Qibdiyya ba"

Nasa gaban ne ya fadi yanzu. Ya kalli Abbati a fakaice ya daure ya daidaita fuskarsa don kada ta gane da matsala. (Fyaden da yake tunanin Lilu ya yi mata)

"Saboda yanayin jikina Asabe ta dauketa..."

Daddy ya katse masa magana da sigar izgilanci yana tabe baki.

"Asaben ce za ta wani iya kula da ita?"

Duk wanda yake falon harda Zakiyya yaji rashin dacewar furucinsa da sigar da aka furta shi. Munzali yaji bacin rai sosai akan hakan. Ko hauka take baya jin ya dace dan kanwarta ya yi magana irin haka a kanta. Cikin fushi ya nunawa Daddy kofa yana fada.

"Malam get out! Idan bata ci darajar komai ba a wurinka ai taci ta zama silar mallakar motar da kake karade garin nan da ita. Bayan kuma ka san na saya ne don ka dinga kai min 'ya makaranta. Ko an fada maka ban san irin yawo da gangancin da kake da ita wanda ni ke biyan kudin gyara ba? Duk kuma a cikin alfarmar Asabe da tasa ni auren yayarka?"

Kafadarsa Abbati ya dafo "ya isa haka ba lafiya gareka ba"

"Don Allah kayi hakuri" cewar Zakiyya a tsorace da fadan nasa.

"Ya fita kawai za a kawota da weekend. Sai ki fadawa makarantar zata yi fashin sati daya."

Rashin kunya Daddy yaso yi musu sai dai dukkaninsu sun yi masa kwarjini. Yanayin jikinsu ma ba daya ba. Ya san uwa da ubansa zai ci la'ada waje idan ya kara magana. A hanyarsa ta fita ne dai ya yi magana da kunkuni ya ce,

"A jikin 'yarka zan fashe"

Kalaman sun sami nasarar shiga kunnuwan Abbati. Matsalolin gabansa basu hana shi juyayin maganar a zuciyarsa ba a hanyarsa ta kai su Innayo gida. Dukanta zai yi?

*

Bakin Uwani bushewa yayi har ta rasa yawun hadiya da Salihi ya ajiye motarsa a jikin katangar police station ya ce ta fito. Hannunta yana rawa ta murda hannun kofar ta fita ta fara bin bayansa. A daidai gate din da zasu shiga kafafunta suka yi mata nauyi saboda tsabar tsoro. Jiki a mace ta coje a wurin don ji take kamar ta kwasa da gudu. Muryarta ta fito kamar mai shirin kuka ta nuna kirjinta da rawar jiki.

"Karata kayi? To me nayi maka? In kana so na dawo gidanka ai ka san umarni kadai zaka bani ba sai ka hadani da hukuma ba."

Kiris ya rage ya kwashe da dariyar kalamai da yanayin fuskarta. Kuma don karfin hali so take ta nuna masa cewa bata ji komai ba.

"DPO ne yake son ganinki"

Habar mayafinta kamar yaji me aka ce ta sabule ta rasa yadda zata gyara shi tsabar firgici. Da kansa ya saita mata mayafin a kafada yadda zai zauna ya ce "muje"

Suna tafiya mayafin ya kara cirewa ta dube shi idanunta suna shirin zubar da kwalla.

"Da ka fada min inda zamu zo ai da na saka hijabi. Ko babu komai zan shiga da mutumcina" a fusace ta wurga gefen mayafin kafadarta tare da cewa "in zaka zauna ka zauna ko in cireka kowa ya huta"

"Ina ruwan mayafi za a huce a kansa"

Allah ne Ya taimake shi yana gaba da ita da tuni ta ga dariyar da yake dannewa. Maganar da ya yi ce ma ta kara kular da ita.

Yawancin 'yan sandan da suka tarar a wurin counter sun gaishe shi da girmamawa saboda DPO Yahaya ya fada musu cewa surikinsa ne tun zuwansa na farko. Uwani bata sami sukuni ba sai da suka shiga cikin ofishin DPO din taji yana gaisheta tare da kiran Salihi da yaya.

"Bari nasa a kawo shi" cewar DPO bayan sun gama gaisawar.

Ba a jima ba kuwa sai ga wani dan sanda ya taso keyar Habibu wanda alamu sun nuna anyi lugude da jikinsa. Yana ganinta ya sunkuyar da kai don ya sha gargadi akan ko hada ido ya sake yi da ita sai an masa fin dukan yanzu. Ita kuwa mamaki ne sosai ya kama ta.

DPO Yahaya ne ya yi magana domin warware mata me yake faruwa.

"Kin san wannan mutumin?"

"Eh" ta amsa da baki tare da gyada kai.

"Good. Kamar nawa ne kudinki da yake hannunsa?"

Tunda ta fahimci ba tuhumarta aka zo yi ba sai ta hau lissafi. Akwai kudin kujerar Hajji, kudin sallamar agent, kudin hotel din da za a kama mata a Makka da Madina (bata san cewa duk a cikin kudin da ta bayar ake cire na kujera dana masauki ba), kudin fili, kudin masu gini ma ta hannunsa suke bi, kudin sallamar dillalai....

Lissafi ya dinga tafiya a yayinda ta cigaba da fadin nawa ta bawa Habibu. Da aka tambaye shi bai musa ba.

"Sai kayi musu bayani game da komai kamar yadda kayi mana."

Kai ya dukar ba don kunya ba sai tsoron hukuma. Da farko babu batun dukansa a lissafinsu. Sai da ya yi kokarin sayesu da kudi domin a kashe maganar. Sannan ne suka nuna masa cewa akwai bambanci tsakanin 'yan sanda da muna 'ya'yan sanda.

"Kudin Hajji babu su gabadaya nayi amfani dasu, filin da kika yi gini kuma ku biyar na sayarwa wurin. Ban san waye ainihin mai wurin ba ma. Sannan..."

Gajiya tayi da jin bayanin nasa mai neman sanya mata hawan jini ta ce "ya isa! Ya isheni haka. Allah zai saka min."

Ta dubi DPO Yahaya ta dan rissina kai tayi masa godiya sannan ta tashi ko bangaren Salihi bata kalla ba. Da sauro ya tashi ya bi bayanta.

Daga kafa kawai take tana saukewa ba tare da sanin ina ta nufa ba. A zuci take kukan bakinciki. Tanadin da ta soma tun ranar da ta fara daukar albashi ya rugurguje. Darasin da ta kasa tsayuwa ta koya yau duniya ta fahimtar da ita a cikin 'yan tsirarun dakiku. 'Duk gudun mutum ba zai wuce kafafunsa ba'. Babu wani bawa da ya isa ya tsallake kaddararsa. Talauci da babu take gudu kuma gashi sun zo sun risketa. Kai ta girgiza ta gyarawa kanta da cewa taje ta riskesu dai. Aikin da take takama dashi bata san makomarta ba akan shi. Kudi kuwa yanzu da matukar wahala ta fito da dubu hamsin indai ba motarta za ta sayar ba. A karshe dai mutum biyun da take ta kokarin ta wuce a rayuwa su ne dai suka rage wadanda zata koma garesu. Uwa da Miji.

"Shigo mota mu tafi."

Gefenta ta kalla inda Salihi yake binta da mota ta kawar da kai. Ransa ya baci ya daga mata murya.

"Meye haka kike yi ne kamar wata mara tawakkali? Ki zo mu tafi nace."

Ba musu ta zagaya ta shiga. Suna tafiya tana goge hawayen da yake ta yi mata zarya a kumatu. Sai da ya saita motar yadda za ta iya shiga gida sannan ya yi mata magana. Muryarsa ba da karfi ta fito ba kamar dazu amma tana iya gane zancen nasa ba da wasa yake so ta dauke shi ba.

"Ke ba Innayo bace. Bana jin har abada za ki taba zama ita. Mutane masu irin zuciyar mahaifiyarki kalilan ne"

Daga kai tayi ta dube shi sai taji a karon farko bayan wasu shekaru wai tana jin nauyinsa. Salihi ya yi mata kwarjinin da ko zamanin samartaka bata jin ta taba jin haka a kansa. A dole ta mayar da kanta kasa ta cigaba da sauraron shi.

"Ni ba mahaifinki bane. Ban taba aibata miki uba a gabanki ko bayan ido ba amma na san halinsa gaba da baya. Ta yiwu bisa kuskure na taba yin wani abu da yasa kika ji kamar tarihin iyayenki zai maimaita kansa a naki gidan auren..."

"A'a" ita ce amsarta da sauri.

Dan murmushi ya yi ya nuna mata kofar gidansu.

"Ki je ki roki gafarar Innayo gwargwadon girman laifukanki. Idan kin tabbata ta yafe miki ki kirani zan zo na daukeki mu koma gida"

Kama kofar tayi za ta fita ta dawo ta kuma zama cikin rashin kuzari.

"Za ta yafe min kuwa?"

Dariya ta bashi ya ce "zan iya rantsewa ko yanzu ma ta yafe tun kafin ki roka. Ai ba ita bace abin ji ba, ni ne."

"Au, baka yafe min ba?"

"Kin rokeni ne?"

Fuskarsa a sake take. Hakan ne ya bata damar yin murmushi ita ma. Jikinta a sake kamar burodin da ya tsumu cikin ruwan shayi ta bude motar ta shiga gida.

***

Tunanin Abbati akan manufar kalaman Daddy ya katse a lokacin da Innayo ta soma labarta masa abin da ya sami Ayaah da suka isa gida. Rokonsa tayi da su sake yiwa Suhaib da iyayensa godiya. Ta sanar dashi cewa Munzali bai sani ba. Kuma taki fada masa ne saboda halin da suka riske shi a ciki a asibiti. Amma don Allah tana so kada Abbati ya manta wurin yi musu godiya. Hakan zai sa suji cewa lallai sun ji dadin abin da dansu ya yi musu. Ya soma mamakin inda suka san juna sai ta fada masa zuwansu duba Qibdiyya harda babarsu. Murmushi mai ciwo ya sami kansa da yi. Halin Mami da 'ya'yanta na karrama mutane abin yabawa ne. Zai so ace ya hada zuri'a da wadannan kamilallun mutane. Ina ma kaddara bata riga fata ba? Da ace shi ma mai tsafta ne kamarsu da zai yi duk abin da ya dace domin samun amincewarsu wurin bashi 'ya.

Yana ajiye su ya kira Shazali ya nemi ya bashi adireshin inda zasu hadu.

"Da azahar nace maka zamu hadu ba yanzu ba" yace da shi a gadarance.

"Allah Ya kaimu azahar din."

Danne zuciyarsa ya yi wurin bayar da waccan amsa. Baya son ya nuna tsantsar damuwa da tashin hankalinsa a zahiri. Abu ne mai sauki Shazali ya yi amfani da wannan damar ya wulakanta shi. Gashi bashi da juriyar wulakanci. Karshe idan abin ya kare da rikici sune zasu kwana a ciki tunda Qibdiyya tana hannunsa.

Maganganunsu da Innayo ya tuno yaji ya kamata ya kira kamar yadda ta bukata. Akalla ko godiya ne ya yi.

***

Cije lebe Mami Khadija tayi a yayinda ta gama sauraron bayanin Suhaib game da Danliti. Wayarsa da ya karbo ya mika mata bayan ya budo mata chats dinsa da Jiddo.

"Mami" ya ambaci sunanta a tausashe saboda yadda ya fuskanci abin data gani ya tabata.

Sakin fuska tayi ta kai hannu kan bandejin da aka nade masa kafa.

"Allah Ya baka lafiya Suhaib. I am proud of you. Ka tseratar da mutumcin wata kaima in sha Allahu babu mai taba mutumcinka dana 'yan uwanka ."

Kawar da zancen take son yi sai dai ko kadan bai yi niyyar barin maganar haka ba.

"Mami jiya kusan kwana nayi ina neman fatawar da ta tilasta miki zama da ...."

Bata bari ya gama magana ba ta dakatar dashi da hannu a lokaci guda tana mikewa.

"Zanyi abin da ya dace Suhaib. Abin da ya kamata nayi tun da dadewa." Ta karashe maganar a hankali tana fita daga dakin.

Da taimakon Allah ta isa dakin da aka saukesu ita da Farha.

BABI NA SHA TARA.

Suhaib ya kamata ya kira amma gangar jiki da ruhi suka ki bawa Abbati hadin kai. Haka yatsansa ya dinga jujjuyawa akan sunan Farha yana tuhumar zuciyarsa da rashin jin magana har ya kai ga kira bai ankara ba. Cikin sauri ya kai hannu zai katse kiran sai dannawar tasa tayi daidai da sallamar muradin rayuwarsa. Zuciyarsa wani irin dokawa tayi sai da ya dafe kirjinsa. Ba yadda ya iya dole yayi saurin bin kiran da wani.

Sake dauka Farha tayi cikin macewar jiki da faduwar gaba. Sallamar da ta kuma yi ta riski kunnen Abbati da sautin karaya da tsoro. A take yaji tausayi da soyayyarta sun taso masa. Baya bukatar tuni yana sane da cewa shi mai laifi ne. Cikin kankanin lokaci ya sanya mata rai da soyayya harma da tunanin rayuwa a karkashin inuwa guda. Sai kuma ya soke mafarkin da ta fara ba tare da ya bata gamsashen bayani ba. Barinta cikin rashin sanin tudun dafawa ba karamin cutarwa bane. Bai tashi sanin hakan ba sai yanzu.

Ajiyar zuciya suka sauke a tare wanda sautin ya shiga kunnuwan junansu. Hakan ya sanyasu yin murmushi a lokaci guda.

Farha ce ta fara yin magana da cewa "nayi sallama baka amsa ba"

Tunanin Qibdiyya ne kadai ya hana shi nuna mata zahirin halin da zuciyarsa ta shiga sakamakon jin muryarta kadai.

"Kiyi hakuri. Wa alaikum salam. Kina lafiya?"

"Alhamdulillah. Kai fa?"

"Nima Alhamdulillah"

Shiru suka dan sake yi sannan ya yi ta maza ya ce "Ya Farha muna cikin wani yanayi ne yanzu dake tsananin bukatar addu'a. Don Allah ina neman alfarma ko sau daya ne ki roka mana sauki a wurin Allah."

Tausayi taji ya bata. Ta matsu taji mene ne ya yiwa kyakkyawar alakar da suka fara ginawa shamaki har tazara irin wannan ta wanzu a tsakaninsu.

"In sha Allahu zan yi"

"Baki tambayeni ko meye ba?" Ya ce da dan murmushin karfin hali.

"Na san idan ya kamata naji ba za ka boye ba"

Allah Sarki zuciya. Kalaman Farha kara nutsar da ita suka yi cikin zuciyar Abbati. A kullum yana kara yabawa da irin tarbiya da tsaftar tsatson da ta fito. Kafin ya manta ainihin dalilin kiran nasa ya ce ta yiwa Mami godiya akan taimakon da Suhaib ya yiwa Ayaah kafin su zo Kaduna suyi da kansu. Tunanin sake ganinsa nan kusa yasa ta fada masa cewa suna Kano ga kuma halin da Suhaib din yake ciki.

"Kuna gidan da muka zo biki?"

"Eh"

"Zan zo koda ni kadai ne saboda Munzali ma yau ya fito daga asibiti idan baku koma ba zuwa gobe ko jibi. Don Allah kada ki manta da adduar."

Zai katse wayar kenan yaji ta ce "baka bani abin sadaka ba. Naji ance ku Kanawa ko me zaku yi sai an biyaku"

Dariya ce ta kama shi ya ce "dadin abin kauyenmu a Jigawa yake nima bakon Kano ne"

Da murmushi Farha ta ce "Ai shikenan tunda ka fara rowa"

Da kyar ya iya sallama da ita suka ajiye wayar kowannensu yana jin matsananciyar kewar dan uwansa.

Daga nan zagaye ya dinga yi a titi domin zaman wuri daya ninka masa damuwa yake yi. Wani masallaci ya tsaya a gefen titi da aka kira azahar ya yi sallarsa tare da

fatan samun nasara daga wurin Maikowa da komai. Akwai mutane da dama da zai iya kira su wulakanta masa rayuwar Shazali ba tare da ya daga hannu ba. Ya san manyan da zasu yi komai domin farincikinsa. Amma ko kusa ba zai nemi kowa ba. Domin kofar da yake son rufewa ce zata sake budewa. Shi yasa ya zabi kai kukansa inda ba a barin mutum ya dawo empty handed. Kamar jiransa Shazali yake yi kuwa sai ga waya. Sanar dashi adireshin inda zai je yayi da dariyar mugunta. Wannan yasa ya figi motar a guje da fargabar me ya sami 'yarsu.

***

Minti arba'in kafin Shazali ya kira Abbati ya amsa wayar wani kusan gwamnati wanda yake yiwa kawalcin 'yan mata. Da yake zancen nasu ya hada da yadda zasu koma biyan malaman makarantun kwana kamar yadda suke yi a ta maza ana basu dalibai sai ya fita daga gidan. Hirar sirri ce baya so ko Abdul ya san me yake ciki. Mukullan mota ya dauka ya ce masa zai je siyo wani abu ya dawo. Minti goma da fitarsa kuwa Abdul ya kamo hannun Qibdiyya yace ta zo ya kaita wurin mamanta.

Bata yi musun binsa ba don ta soma galabaita. Sam taki cin abinci sannan ga rashin iyaye ko wani idon sani. Abdul gani ya yi tana jan kafafu ya sunkuceta ya goya. Durowar da ya taba gani Shazali ya ajiye mukulli ya duba yaci sa'ar ganin mukullai daban daban a ciki. Lokutan baya bai taba tunanin dauka ba duk da idan Shazali zai fita yana rufe shi a ciki.

Wurin kala shida ya soka a jikin kofar saboda kusan duka girmansu daya kafin ya yi sa'ar jin ta bude. Ajiyar zuciya ya saki gami da sake ruko kafafun Qibdiyya a cikin hannuwansa. Yana sako kafa a waje yaji kamar an dauke masa kansa sakamakon hada kan da bango da Shazali ya yi. A kofar gida ya zauna yana wayarsa. Duk gwajin mukullan da Abdul yake yana ji. Haka ya shigo gidan a harzuke ya banka kofar ta rufe da karfi kafin ya hankada shi. Da kyar Abdul ya iya tsayuwa akan kafarsa don gudun kada ya kifa da baya ya danne Qibdiyya. Bayan ya sauketa kafafunsa ta rike ta buya a bayansa tana kuka. Shi kuwa kunnen bangaren da ya hadu da bangon yaji ya dauke dif sai wata kararrawa ce take bugawa kamar an kada tara a firamare.

"Har kayi tsaurin idon shiga lamarina Abdul? Waye ubanka a garin nan da kake jin ko kasheka nayi za a tada magana ma?"

Abdul babu amsa sai kunnensa da yake ta bubbugawa ko jinsa zai dawo daidai.

Kafadunsa Shazali ya rirrike ya shiga jijjiga shi yana masifa. Abu biyu ke damunsa. Na farko ya san duk kaunar da yake yiwa Abdul ya rasa shi kenan domin ba zai kuma kawo shi gidan nan ba. Na biyu kuwa wani mutum ya wuce ta kofar gidan a daidai lokacin da Abdul din ya tura kofar gidan. Babu tantama ya san cewa an ganshi. Bayan kuma ba a taba jin duriyar kowa a gidan ba.

Da kansa da ya gaji ya sake shi ya nuna shi da yatsa. Har lokacin dai bai dawo daidai ba. Kana ganin kwayar idanunsa zaka gane a cikin dimuwa yake.

"Ka jawowa kanka bala'i don na fuskanci akwai ganganci idan na mayar da kai makarantarku. Ka jirani in kai yarinyar nan wurin ubanta na dawo."

Cikin gidan ya wuce ya tafi dakinsa ya barsu a dan sararin tsakar gidan. Kukan Qibdiyya tuni ya dauke sai ajiyar zuciya saboda tsorata da tayi. A gabanta Abdul ya durkushe ya fiddo wata 'yar karamar waya kirar samsung mai torchlight. A makaranta ma ba a san yana da ita ba. Bai taba kiran kowa ba sai Shazali da suke musayar text messsage. Shi ma kuma bai san yazo gidan da ita ba. Gefen siket din Qibdiyya ya samu ya saka ta ya yi mata nadi biyu. Siket din sai ya dage sama amma ba za a gane da wayar ba saboda dan fadin rigarta.

"Ki boye wayar nan in kin hadu da babanki ki ce ya kira babana."

Da ka ta amsa tana rike dashi har Shazali ya dawo. Hannunta ya fincika ya fita da ita a ransa yana tunanin ko wa zai hadu dashi cikin makota ba zai damu ba domin yana dawowa zai fita da Abdul ya bar gidan gabadaya.

Fitarsu ke da wuya Abdul ya fadi a tsakar gidan. Jini kuma ya dinga silalowa daga cikin kunnen da ya bugi bango ta bangarensa.

***

Duk wata addua da Abbati ya sani ya karanta ta a hanyarsa ta zuwa gidan shakatawar Comared. Manyan motoci ya gani har biyar a harabar gidan. Da yake gidan gona ne mai dan karen girma. A kusa da ta Shazali ya ajiye tasa ya fito ya kira shi a waya. Maimakon ya dauka sai ya fito ya yi masa jagora zuwa ciki. Karfin zuciya ne ya hana shi far masa da duka tun a lokacin saboda bai san me zai sami Qibdiyya ba idan haka ta faru.

A cikin gidan kuwa Alh. Tahir ne zaune a wani daki wanda kofarsa take cikin falon suna magana da Comared.

"Har yanzu babu wani canji dole sai da namijin?" Ya sake maimaita tambayar da bai san sau nawa ya yiwa Comared ba.

Fuska ya kyabe kamar mai jin tausayinsa har zuci ya ce "ko dazu sai da na sake kiransa har nace ko ni zan iya yi maka aikin yace a'a"

"Allah Sarki mutumina. A hakan ma nagode sosai. Na san kai mai taimaka min ne har inda karfinka ya kare."

Comared ya tashi daga bakin gado ya ce "so nake ka kwantar da hankalinka. Yaron kwararre ne ya san me yake yi. Kafin ka farga anyi an gama"

Suna ciki suka jiyo sallamar Abbati domin dai shi Shazali bata gabansa. Hasali ma hankalinsa yana wurin Abdul. So yake ya koma gida ya yiwa yaron rashin mutumci kafin ya watsar dashi a titi.

Falon wayam babu kowa sai kayan ciye ciye da karar tv data AC. Qibdiyya Abbati ya nema da ido babu ita babu dalilinta. Cikin zafin nama da gajiya da danne bacin ransa ya riko Shazali ya tsayar dashi a gabansa. Da kakkausar muryar da shi kansa bai san bacin rai zai taba bashi irinta ba ya ce,

"Shazali ina Qibdiyya?"

To shi ma Shazalin bai san dakin da Comared da Alh. Tahir suke yana kusa dasu ba, shi yasa ya bashi amsa babu kwana-kwana. Dariyar mugunta ya fara da ita kafin ya ce,

"Tana nan kalau ko farcenta ban taba ba. Nan da awa guda idan kaso zaka tafi da 'yarka gida. Bukatarmu kawai kabi umarnin da aka baka"

Murya kasa-kasa Alh. Tahir ya tambayi Comared me yake faruwa. Ganin babu wata mafita sannan ya san a cikin matsi abokin nasa yake shi ne ya yi masa takaitaccen bayani. Bai kai ga yin magana ba suka ji Abbati ya daka wata irin tsawa. Su biyun duka jikinsu ya amsa duk da ba dasu yake ba. Barin ma Comared wanda tun isowarsu gidan yasa aka bata maganin bacci. Tana dakinsa na sama yana jiran Abbati da Alh. Tahir su shiga daki shi ma yaje ya afka mata.

"Shazali! Ka fito min da Qibdiyya idan ba haka...."

Cike da dakiyar 'yan barikin da suka yi nisa Shazali ya katse shi da cewa "in ba haka ba sai me Abbati? Kana da abin da zaka iya ne? Duk wani k'usan gwamnati ko maikudin da kake takama dashi ta dalilin wa ka sanshi?"

"Ana takama da Allah waye yake ta mutane? Wawa irinka ne zai dogara da halitta mai kayyadajjen wa'adi bayan akwai Maihalittar da bashi da karshe. Da nace maka ni da Munzali mun tuba ba da wasa nake ba."

"Aikin banza. Wane d'an son zuciyar ne ya ce muku Allah zai karbi irin wannan tuban naku? Shekararku nawa a wannan rayuwar? Kudi da duk wani connection dinku a kasar nan ba jikinku bane sanadinsa? Sai yanzu kuna tunanin kun gama tara abin da kuke so zaku wani ce kun tuba? Malam in zaka sha giya kasha ta duba. Allah Gafurur Rahim ne kowa ya san wannan. Kawai ku cigaba da gashi suya sai ranar sallah. Idan mutuwa tazo ka gaggauta istinginfari me yiwuwa a dace."

Karkada kai Abbati ya yi da murmushin takaici. A matsayinsa na bawa mai tarin zunubi kuma mai neman rahama ya yi imanin cewa shi din ba kowa bane. Amma duk da haka bakinciki mara misaltuwa ya danne zuciyarsa saboda maganar Shazali. Tsanarsa ta kara ruruwa a zuciyarsa saboda kalaman izgilancin da yaji daga bakinsa. Nasa imanin da tawakkalin kuma suka karu domin ya yarda cewa lallai shiriya ta Allah ce. Su da suka tuba ba wayo ko dabararsu bane. Cike da kosawa ya ce,

"Don Allah Shazali ka fito min da ita mu tafi. Bana son wannan case din ya kaimu gaban police."

Sama Shazali ya nuna masa yana yi masa kallon wulakanci

"To ni waye yace maka ina tsoron police? Kaga Abbati ka amince kayi abin nan ka zo ka tafi don nima uzuri ne a gabana. Mutumin nan ya riga ya saba sakarwa mata kudi kamar hauka. Wannan harkar ma don bako ne shi a cikinta shi yasa na nemo ka. "

"Babu ruwana da sanin ko shi waye. Da Allah fa nake hadaka akan ka bani 'yata mu tafi. Mece ce ribarka idan na koma wannan kazamar rayuwar?"

"Riba? Eh to ina da riba gaskiya. Zan jidadi na rabaku da tuban da kuke ikirari wanda yasa kuke yi min kallon dan wuta. Munafunci ne tuban naku tunda sai da aljihunku ya yi nauyi da haram zaku ce wai kun komawa Allah. Indai ina numfashi sai kun koma ruwa."

Murmushi Abbati ya yi mai ciwo. Bin Shazali ta laluma ba zai kara masa komai ba sai bacin rai. Idanuwansa ya daga yana kallon fanka wanda a zahiri zuciyarsa ce take fuskantar Mak'aginta.

"Ya Allah idan tubana dominKa ne, kuma niyyata ta barin dukkan abin da na mallaka ta haramtacciyar hanya dominKa ce ina rokonKa da ka tsare Qibdiyya. Kasa su fito da ita da kansu. Ya Allah kada Ka bawa Makiyanka dama a kaina da abokina. Kada Ka basu ikon sake mayar damu kazamar rayuwar da ka haramtawa bayinKa."

Kafada Shazali ya kada irin na ka yiwa kanka ya ce "Tunda baka da rabon arzikin nan to ka zauna ka jira Qibdiyya. Tana can ubangidana yana morar jikinta. Na san zamu sami fiye da abin da ya kamata a biyaka"

A guje Abbati ya tashi ya yi hanyar benen jikinsa yana rawa ga gumin da ya wanke shi a take. Ko rabin benen bai kai ba Shazali ya finciko shi ya fado. Akan hannunsa daya ya fada kuma yaji karar da ya yi amma hakan bai hana shi mikewa da zafin nama ba ya bangaje Shazali ya sake nufar benen.

"Qibdiyya! Qibdiyya!!"

Da Shazali ya sake riko shi rufe masa baki ya so yi saboda gudun kada Comared yaji hayaniyar. Idan ya rasa kudin wahalarsa ta kawo Abbati gidan nan ba karamin abu zai yi masa ba domin huce haushi.

Hannun da ya kai da nufin toshe masa baki Abbati ya damko ya sami sa'ar janyo shi ya kifar dashi a kasa. Bai dakata ba saboda tsananin bacin rai da kunar zuciya ya haye kansa ya shiga kai masa duka ko ta ina a fuska da lafiyayyen hannunsa. Cikin kankanin lokaci baki da hanci suka soma fitar da jini.

Duk kokarin Shazali da son ture shi ya kasa. Ihun neman ceton da yake yi da kyar yake fita saboda wahala.

Tun farkon maganganunsu Alh. Tahir yaji jikinsa yayi sanyi da Comared ya fada masa wanda aka kawo yayi ikirarin tuba. Kuma hakan ne ma ya zama dalilinsu na dauke 'yar amininsa wadda bata da maraba da matsayin 'yar cikinsa. Zai iya yin komai dominta. Sai kuma kwatsam yaji ya ce Munzali. Sannan ya kara da ambaton tuba da zantuka masu taba zuciya. Irin zantukan da ya saba jinsu da kalamai masu tasiri fiye da na Abbati daga matarsa. Amma a yau ne kadai ya fara shiga hankalinsa. Harbawar zuciya da gudun jininsa a cikin jijiyoyi ya dadu. Ya san suna Munzali da Abbati da kuma kasancewar Munzali uba ga wata yarinya da bai rike sunanta ba. Matasan samarin dake shirin zama surukansa. Idan ya fita Abbatin da ya kasance saurayin Farha na farko zai gani?

Bai san yadda aka yi ba ya iso kofar dakin zai murda Comared ya kama hannunsa.

"Alhaji kada ka fita don na fuskanci dan iskan yaron nan zai iya bamu matsala. Idan yaga fuskarka bai mana aiki ba tabbas zai iya tona mana asiri. Kuma yadda zuciyarsa take a kusan nan mu kanmu bamu san me zai mana ba. Ka jira in kira security."

Fizge hannunsa ya yi ko amsa bai iya bawa Comared ba ya fita. A halin da ya sami Shazali da Abbati bai san lokacin da ya kwalawa Abbati kira ba bayan ya gama razana da ganin da gaske shi din ne.

"Abbati sake shi kada kayi kisa"

Bai san waye ya yi magana ba amma wuyan Shazali da yake neman shakewa yana maganganu a zauce don duk tunaninsa da gaske ana can ana cin zarafin Qibdiyya ya saki farat daya. Idanunsa hawaye suke fitarwa ya tashi a firgice da tsanar aika-aikan da yaso yi ba don an dakatar dashi ba. Da kakkausar murya ya nuna Shazalin dake kwance sannan ya juya ga mutane biyun da suke tsaye a hagunsa.

"Kai ne mutum na farko da ya fara sakamu cikin wannan masifa Shazali. Kuma har yanzu ka kasa hakura ka barmu mu koma ga Allah. Idan wani abu ya sami Qibdiyya wallahi zaku ga rashin ...."

Bai sami damar karasa maganar ba a sakamakon ido hudu da suka yi da Alh. Tahir. Idanuwansa ne kadai suka kara girma a yayinda wani kololon abu mai daci ya taso daga cikinsa ya tsaya masa a wuya. Cikinsa ya kulle tamau har sai da shiga da fitar iska cikin hancinsa suka soma wahalar dashi. Kafafunsa da yake umarta da su zaga dakunan gidan su nemo Qibdiyya sannan ya fita kuwa suka ki motsawa.

'Zina 'yar aike ce. Duk inda ka turata zata dawo ta isar maka da sako. Bana yi mana fata domin dawowarta gidan nan ba zai taba zama alkhairi ba. Sai dai ina so ka sani koda tayi batan kai da sannu wata rana za a sami mai nuna mata hanya. A lokacin

ko bata tuna cikakken sakon ba saboda shudewar lokaci, sallamarta kadai zata hargitsa tunaninmu. Na barka lafiya!'

Ga Alh. Tahir kuwa, wannan sakon na Mami Khadija wanda ta tura masa tun washegarin ranar da Yumna ta fallasa komai ga Farha ne ya dawo masa tar. Ko batan wasali bai yi ba wurin tunano kalmomin daki-daki tamkar yanzu yake karanta su. Hantar cikinsa ta buga a tsorace da ya yiwa sakon fahimtar da ta dace dashi. Tun kafin ya bincika yaji ko akwai wanzuwar haramtacciyar alaka tsakanin su Abbati da 'ya'yansa ya gama shiga tashin hankali. Sanin cewa sun taba yin luwadi duk da a yanzu kunnuwansa sun jiye masa nadama da tubansu kadai ba karamin bala'i ya jefa zuciyarsa ba. Ko shi da zina ta gama bin jinin jikinsa ba karamin kyama yake yiwa wannan nau'in nata ba. Haka ya dinga jin kamar ana sassara adda a sassan jikinsa. Bai san wanne daga cikin masifun da suke gabansa ya kamata ya fara yiwa kukan bakinciki ba. Ganin Abbati a wannan gida da sanin waye shi ko kuwa ganin da Abbati ya yi masa da sanin nasa sirrin?

Kallon kallo da suka tsaya yiwa juna ne ya bawa Comared damar tayar da Shazali ya zaunar dashi akan kujera. Da yaga kallon yaki karewa ne ya dubesu da mamaki sosai.

"Alh. Tahir ko kun san juna ne?"

Yawu yaso hadiya domin bayar da amsa amma ya laluba yaji babu danshi a bakin nasa. Kansa yaso kadawa shi ma yaji ya yi masa nauyi. Comared kawai sai ya ce,

"Shi ne yaron da aka dauko 'yarsu ai domin ya amince da aikinka." Yana gama magana ya juya ga Abbati "wannan haukan da kayi a gidan nan baka ci bulus ba wallahi. Idan kana takama da zafin kai ka tarar da ubangidansa. Sai na daureka igiya tayi rara."

A sanyaye Alh. Tahir ya daga kai ya kalli dakunan dake sama ya ce "Comared a wane daki yarinyar take?"

Wani irin duba Comared din ya yi masa sai dai bai iya yin musu ba ya nuna masa kofar da hannu.

Abbati ya kalla fuskokinsu duka babu digon nutsuwa.

"Daukota ka zo ku tafi"

"A'a Alh. Tahir, bangane ba. Ya zaka sallamesu batare da shawarta ta ba?"

"Nawa ne zai fanshi uba da 'yar Comared? Nawa zan baku ku kyalesu har abada?"

Sakin Shazali Comared ya yi ya taso har gaban Alh. Tahir cike da dumbin mamaki.

"Alhaji ka san shi din da gaske?"

"Da ne a wurina. Iyaka abin da zan iya fada maka kenan"

Kai Comared ya kada alamun ya amince Abbati ya hau saman. A gurguje kuwa ya haye ya bude dakin da aka rufe ta waje amma key na jikin kofar. A tsakiyar gadon ya sameta ta dukunkune jiki tana bacci. Kwalla mai zafi ta zubo masa a lokacin da ya rankwafa ya daukota. Jikinta zafi rau da zazzabi. Yana dorata a kafadarsa yaji dumin zafin yana nasar nasa jikin. Ba shiri ya dagota ya dorata akan kafar damansa da ya dora a bakin gadon.

"Qibdiyya. Bude idonki Papa ne"

Da kyar ta bude idon saboda gajiya, yunwa da kuma aikin maganin baccin da Comared ya dura mata. Yadda kanta yake kifewa da kansa kamar 'yar maye ya sake daga masa hankali. Jikinta yabi da hannu daya ya mammatsa domin son ya farkar da ita. A nan ne kuma yaji ya tabo wani abu mai dan tauri a kugunta A razane ya dan daga rigarta ya ciro shi daga cikin siket dinta. Bakinsa da kyar ya iya hada tambayar wayar waye gareta. Cikin yanayin rashin kuzarin da take ta ce masa,

"Cewa ya yi na baka"

Aljihunsa ya tura wayar ya mayar da ita kafadarsa ya sauka. Idan ta dawo daidai zai tambayeta waye ya bata. Da ya sauko babu wanda ya kalla haka ya fita daga falon. Sai da ya isa bakin motar har ya kwantar da Qibdiyya a baya sannan yaji an ambaci sunansa da murya mai rauni sosai. Gabansa ya yanke ya fadi domin bai san da wane ido zasu kalli juna ba balle har su yi bayanin fidda kai.

***

Minti goma sha biyar da isar Alh. Sadisu Nakano makarantarsu Abdul ta hargitse kamar ana cin kasuwa. Tun daga Principal har Masinja babu wanda bai shiga sahun zagaye makarantar ba ana neman Abdul. Principal din yafi kowa rikicewa don sai yau ya san akwai dan Alh. Sadisun a makarantar.

Tun lokacin da yasa aka kawo shi makarantar dama ya bukaci a boye ko dan waye. Kudin da yake turowa domin kulawa dashi kuwa bai bambanta da wanda wasu iyayen kan yi ba sai ta adadi. Malamin ajinsu wanda kudin ke biyowa ta hannunsa yana isar da sako tare da yin tasa bushashar son rai.

Daya daga cikin masu gadi ne ya ruga ya sanar da Principal bakon da suka yi tun kafin su shigo ciki. Principal din ya tashi da sauri ya shiga kankanta ofishinsa domin yana da labarin zuwan bazata da Alh. Sadisu ya kan yi makarantu. A zatonsa yau sallarsa ce ta kama don yasa rai da samun wani abu mai nauyi daga babban bako. Bai tashi shiga tashin hankali ba sai bayan sun gaisa Alh. Sadisu ya bukaci a kira masa dansa. Dan aike wato Masinjansa ya dawo da mummunan labari cewa wai washegarin dawowarsu makaranta ya koma gida bashi da lafiya. Daga nan aka soma diramar!

Tashi Alh. Sadisu yayi tsaye cikin fushi da kaduwa ya hankada teburin Principal din dake gabansa. Ji kake kiyyyy, ya tafi ya daki bango. Abubuwan da suke kai wadanda suka yi zaman dakin kishiyar da ba a shiri da ita suka rufto kasa.

"Bana son zancen banza da hofi. Yaron wajena nake nema Abdul. SS2 B yake. Sunan form master dinsu Sir Balarabe. Hostel dinsu kuma Sardauna House. Ya ce min a kwanar da gadonsa yake akwai Victor da Faisal"

Jinjina kai Masinjan da Principal suka yi na mamakin yadda ya rike komai da ya shafi dansa. Direbansa da PA da suka zo tare basu dauki hakan komai ba. Saurin rike abubuwa suna daga cikin manyan jarinsa da suka kawo shi inda yake yanzu.

"Ranka ya dade zauna bari naje ajinsu da kaina na kirawo shi. Ina jin sakon ne bai fahinta da kyau ba."

Principal dai bai sami damar dawowa ba sakamakon matsalar da ya tarar. Lokacin ba a tashi daga aji ba. Yana zuwa Monita da sauran 'yan aji suka tabbatar masa da cewa kamar yadda aka bukaci su dawo asabar saboda damina ana bukatar gyara makaranta, Abdul ya dawo amma ba a wayi garin lahadi dashi ba.

"Me yasa ban san labarin nan ba sai yau?" Cewar Principal yana gumi tare da tsare malamar dake ajin tana koyarwa a lokacin.

"Ranka ya dade Mal. Balarabe ya kamata ka tambaya. Nima ban san komai ba"

Tare da Monitan ajin da Assistant dinsa ya tafi staffroom din malamai maza. Yana shiga ya kira sunan Mal. Balarabe sai dai nan take aka sanar dashi baya nan shi da wasu malamai biyu abokansa.

"Bangane ba? Ina ya tafi ana cikin wannan yanayin?"

Wani malami ne ya bashi amsa da cewa "babu yadda za ayi ya zauna alhalin duka makaranta ta dauka cewa dan Alh. Sadisu ya bata."

"To shi ya batar dashi da zai gudu?" Ya tambaya a fusace.

Malaman dai basu ce komai ba tunda basu san me yake faruwa ba. Haka ya koma ofishinsa da yaran nan biyu cike da fargabar yadda zai fara yiwa Alh. Sadisu bayani. A inda ya barshi tsaye ya dawo ya same shi yana kai gauro da mari. Yana ganinsa kuwa ya ce ina Abdul.

"Yallabai ka zauna kaji daga bakin yaran nan. Daga nan sai mu san abin yi."

Rainin wayo Alh. Sadisu ya dauki zancen Principal din. Sai dai kuma ance idan rakuminka ya bata ka duba har cikin hudar allura. Bisa wannan dalilin ya saurari Monitan wanda ya maimaita sak abin da ya fadawa Principal.

"Yanzu kai baka ji kunyar cewa na tsaya jin wannan wasan yaran ba? Cewa zaka yi makarantarka babu tsaro har ana shigowa a sace 'ya'yan mutane. To wallahi banda dana. Kai, ina tsammanin baka gane ni ba ko? Suna na Alh. Sadisu Nakano kuma ko uban mutum ne yake mulkin kasar nan bai isa ya hanani koya masa hankali ba." Ya nuna kofa da hannu "kaje ka nemo maigadin da ya kwana ranar asabar din. Da malamin ajinsu duk inda yake..ku hadu ku nemo min dana"

Da Principal da mataimakansa biyu tare da malaman da suka yi cirko-cirko a kofar ofishin kowa hankalinsa ya tashi. Alh. Sadisu ma dauriya kawai yake domin zuciyarsa tuni ta fara karanto masa sunayen abokan hamayyarsa wadanda zasu iya dauke masa da a matsayin fansa ko garkuwa.

"Sir?"

Kowa juyowa yayi don jin wa dalibin dake matsayin mataimakin monita yake kira. Kai tsaye Principal din nasu yake duba ya ce,

"Ina jin fa ba bata ya yi ba. Tun kafin hutu yawanci da daddare ranar juma'a Sir Balarabe yana zuwa kiran wasu a hostel. Yawancinsu da safe suke dawowa. Wasu kuma sai lahadi..." Ya kalli monitan "ba shi ne muke cewa ko lesson ake musu banda mu ba?"

Da ace kunnuwa suna jin gaibu yau da ofishin Principal dinnan ya cika da bugun zukata. Duk wani mai hankali a cikin wurin tunaninsa ya karkata daidai da na uban yaron da ake nema. Wannan kuwa ba bakon abu bane tunda akan ji labarai makamantan haka a makarantun kwana.

Cijewa Alh. Sadisu ya yi ya daure ya tambayi yaron ko mutum nawa ne suka bar makaranta rana daya da Abdul. Babu musu kuwa ya lissafo masa su biyar.

"Amma sauran hudun duka ranar lahadi suka dawo da daddare. Shi kadai ne Sir Balarabe ya ce gida ya koma"

Cikin karaji da gigita Alh. Sadisu ya ce "A nemo min Balaraben da masu gadi"

"Sir Balarabe ya fita"

"Mal. Bawa maigadi baya nan"

"Malaman dake abota da Sir Balarabe ma basa nan"

Wadannan ne amsoshin da suka biyo bayan umarnin da Alh. Sadisu ya bayar. Da aka gama fada dariya ya kwashe da ita. Wata irin dariya mai dauke da bakinciki da bacin rai gami da tsoro. Kamar yadda ya fara ta kuma a bazata haka yayi dif ya daina lokaci guda. Kallo mai ban tsoro yabi mutanen da suke gabansa sannan ya daga waya ya kara a kunne.

"Ku fara aikinku"

Cikin kankanin lokaci gabadaya makarantar ta kasance a zagaye da 'yan sanda. Wasu suka shigo aka fara yiwa duk mai ruwa da tsaki tambayoyi. Ya kira su ne tun kafin Principal din ya dawo daga binciko masa me ya faru.

Ma'aikatan jarida kama daga na gidajen rediyo zuwa tv suma suka soma dafifi. Alh. Sadisu ya tsaya a kofar ofishin Principal da na'u'rorin daukar magana kala kala a saitin bakinsa ya ce,

"Ba roko nake ba shawara ce. Na bada awa biyu kacal a dawo min da dana inda aka dauke shi."

***

Ayaah, Murja da Ummita ne suka tashi daga gaban mahaifinsu da Abdulkarim bayan sun gaishe shi. Kafin su fita ya sake jajantawa Ayaah abin da ya faru jiya tare da shawara gareta da 'yan uwanta akan tsare mutumci saboda gurbacewar zamani. Bayan sun koma wurin Anti Hasiya aikin gabansu suka cigaba. Ayaah kuwa kusa da antinta ta koma ta kwanta ta rufe ido.

"Dalla can tashi, ai kin san yau kece da wanke-wanken safe"

Baki Ayaah ta turo ta tashi rai a bace za ta soma gunaguni Anti Hasiya ta ce ta koma ta kwanta.

"Haba Murja! Yanzu har kin manta abin da ya sameta jiya kike kira mata wanke-wanke? Duka duka yaushe garin ma ya waye?"

Murja da Ummita suka dubi juna suka bushe da dariya. Karfe goma shadaya harda minti bakwai. Shi ne Antinsu take cewa yaushe gari ya waye. Sannan bata tashi ba Ayaah da Murja suka yi fada kamar zasu ari baki a kofar bandaki. Ita kuma tana tasowa ta cigaba da lallabata.

Labarin fadan suka bata ta koma yiwa Ayaah kallon tuhuma. Amma da yake ba a cinyeta da baki sai da ta magantu.

"Dauriya ce fa kawai nake Anti amma har yanzu ban dawo daidai ba. Kuma bana son ki shiga damuwa shi yasa nayi kokarin dawowa daidai."

"Yanzu tsiwa ce daidai dinki Ayaah? Allah nagode Maka" cewar Anti Hasiya tana dariya.

Raharsu suka cigaba da yi cike da so da kaunar juna. Anti Hasiya ta dubesu daya bayan daya ta sake mika godiyarta ga Allah. Irin wannan zaman na ahali daya kuma da zuciya daya tayi ta buri. Sai gashi lokaci guda Allah Ya amsa addu'o'i'nta. Kan yaranta ya hadu sannan ita ma ta sami rabon da zata kira nata. Uwa uba an Abbas yana shirin samun lafiya da yardar Allah.

*

"Ina ta sa ran jin ka tambayeni me yasa na nacewa gidanka naji shiru"

Abdulkarim ne ya yiwa Honourable tambayar bayan sun gama gaisawa sannan ya fada masa daren yau ake bukatar kwantar da Abbas a asibiti. Washegari ake sa ran yi masa aikin da safe. Likitan da zai jagoranci aikin ya iso Kano.

Da yake Honourable ya fishi kwarewa a sakin magana sai cewa ya yi "Wata kake so cikin 'yan matan gidana ko?"

Yadda ya yi maganar kai tsaye ya bawa Abdulkarim mamaki domin bai yi maganar da kowa ba sai zuciyarsa. Zaro idanun da ya yi ba tare da ya ce komai ba yasa Honourable bude baki.

"Don Allah wai da gaske kake?"

Kwarjini Honourable ya yi masa fiye da kullum amma ya san ranar wanka ba a boyon cibi. Tunda dai Ummita ba za ta aurar da kanta ba dole ne ya fadawa mahaifinta.

"Da gaske nake"

Honourable ya gyara zama yana dariyar kunya da takurar da yake gani a tattare da Abdulkarim.

"Murja dai an kawo kudinta. Ya rage Ayaah da Ummita"

Abdulkarim ya dan tura hularsa baya kadan ya ce "Umminmu din nake so. Allah Yasa wani bai rigani ba. Kuma don Allah kada ka sako zancen shekaru wallahi da sauran tafiya kafin nayi hamsin ma."

Dariya sosai ta kama Honourable. Farincikinsa ba zai misaltu ba. Wato da gaske bayan kowane tsanani akwai sauki. Sai dai wani hanzari ba gudu ba...

" Abdulkarim anya baka yiwa Ummita nisa ba. Ba batun shekara nake maka ba. Ina nufin a zamantakewa ta wayewar rayuwa da arziki. Ina jin tsoron kada ku sami rashin daidaito a dalilin ..."

Dakatar dashi Abdulkarim ya yi ya nuna masa rashin jindadin furucinsa.

"Ka sanni kafin na zama wannan Abdulkarim din. Duk abin da na samu a sakamakon kusanci da kai ne a lokacin da nima ban dace da kusantar mutum irinka ba. Amincewarka nazo nema domin na nemi soyayyarta. Ba zan so ayi mata fin karfi ba saboda wani abu da na samu na takaitaccen lokaci"

Fuskar Honourable dai babu komai cikinta sai annuri. Tashi ya yi ya ce masa idan sun gama shiri anjima zasu tafi asibitin zai kira shi.

Abdulkarim sai ya shiga rudani ya ce "maganar Umminmu din fa?"

Wata dariyar Honourable ya sake yi

"Naga dai yanzu ba lokacin tadi bane da rana tsaka amma dai bari na turota kwashe kwanuka."

Kunya ce ta kama Abdulkarim amma abinka da manya sai ya fuske. Ba jimawa kuwa yaji sallamarta a kofar falon. Da ya amsa ya yi zaton zata shigo amma shiru har kusan minti biyu. Ga alamun tsayuwarta a bayan labule yana gani amma taki motsi. Babu mamaki babanta ya fada mata yadda suka yi. Banda haka me zai hanata shigowa don yana ciki?

"Nifa dan gata ne a gidan nan. Idan baki shigo da kafafunki ba ko Ayaah na kira zasu hadu da Murja su daukoki a ka"

Ja da baya tayi cike da tararrabin me ya kamata tayi. Bayan kusan sakan talatin ta matso jikin labulen ta damke shi da hannu ba tare da ta bude ba ta ce,

"Ni wallahi kunya nake ji"

Murmushi ya sami kansa da yi ya taso ya dawo bakin kofar ya tsaya ta yadda suke iya ganin shatin juna. Ummita bata ma san ya iso wurin ba sai da taji amsarsa a kurkusa.

"Banda abinki idan baki ji kunyata ba ai sai ki sa na fara kokwonton zabina"

A wautarta ji tayi amsar tasa bata cika ba.

"Ni kadai ce mai jin kunyar?"

"A iya sanina dai mata sun fi son namiji mai karancin kunya akansu."

"Wai naga kamar 'ya nake a wajenka"

"Wai idan kin dauka kallon 'ya nake yi miki ki ajiye."

Hannu kawai Ummita ta kai ta rufe bakinta saboda murmushin da ta kasa daina yi. Gabadaya nauyinsa take ji sannan tana mamakin yadda ya sake abinsa ya ma manta ita wace ce. Duk da cewa ba yau ta fara sanin soyayya ba, wannan tazo mata da salo mai girman da yafi karfin shekaru da tunaninta.

Zurfafa da tayi a tunani ya bashi damar kallon irin tsayuwar da tayi. A jikin kofar ta dan jinkina sai gefen labulen da ta rike amma taki budewa. Kusa da inda hannunta yake ya kama bata lura ba sai ganin fuskarsa tayi ta bayyana a gabanta. Ja tayi da baya zata gudu ya girgiza kai wanda yanayin fuskarsa da tayi mata kwarjini ta hanata kin bin umarninsa.

"Gajiya nayi da hirar bayan labulen kamar wani mara gaskiya"

"To ka koma zan shigo na zauna"

"Na yafe. Zan dawo anjima idan za a kai Abbas asibiti."

"To Allah Ya kaimu." Ta furta da azama tana son tafiya.

"Dawo Aminatu ban sallameki ba tukunna."

Dagowa tayi a hankali da niyar kallonsa ta kasa. Ya san mamakin sunanta da ya fada take yi. Shima ya yi mamakin rashin mantawa. Kodayake bai taba manta duk abin da ya shafi Honourable ba.

"Nace ba, wai nayi miki kuwa?"

"Innalillahi ..." Furta tare da rufe fuska tana dariya kasa-kasa.

"Ya kike ja min Innalillahi? Nayi?"

Dariyar dai ta cigaba da yi cike da kunya ya ce "in dauki wannan kunyar a matsayin amincewarki kenan?"

Da ka ta amsa masa.

"Nagode Ummi-ta. In sha Allahu ba zan baki kunya ba daga ranar da zama ya hadamu a inuwar aure."

Kafin ta daga kafa har ya fito. Kunya bata barta tayi masa sallama ba.

BABI NA ASHIRIN.

***

Kan Abbati a kasa ya kasance har Alh. Tahir ya isko shi a bakin motar. A bakinsa wani irin daci yake ji mai naci domin duk yadda ya kai ga hadiyar yawu yaki wucewa. Halin da ya tsinci kansa baki ba zai taba iya fada ko ya kwatanta ba. Zuciyarsa ce kawai take harbawa fiye da ka'ida. Bai ga wata maraba tsakanin sanin sirrinsa da Alh. Tahir ya yi ba da Farha. Tunda uba ya sani, me zai hana 'yar ta sani? So ya yi su rabu asirinsa a rufe. Gara ta dinga tuna shi a matsayin mayaudari akan fasiki...fasikin ma kuma manemin maza.

Firgici da tashin hankalinsa ko kusa basu kai rabin abin da Alh. Tahir yake ji a dukkan gabbansa ba. Ko tafiyar da yake ba zai iya cewa ga da yadda aka yi yake

iya daga kafa ba. Ya dai dawo hayyacinsa da yaga bai fi taku biyar ya rage tsakaninsu ba.

"Abbati..."

A tunanin Abbati maganar da Alh. Tahir zai yi masa ba za ta wuce tuhuma akan 'ya'yansa ba. Saboda haka bai bari ya kai karshen abin da zai fada ba ya ce,

"Babu abin da ya taba mutumcin su Farha a a hannunmu. Ban kuma kawo kaina da niyyar aurenta ba kamar yadda yake a wurin Munzali sai da muka tuba" ya ciji lebensa na kasa wanda yake nuni da karayarsa yayinda ya cigaba da cewa "mun yi nadama, mun tuba har muna shirin barinsu kafin duniya taji a dalilin barazanar da Shazali yake yi mana...amma ban san me yasa Allah Yasa asirinmu ya tono ba a irin wannan yanayi."

"Asirina ne ya tono ba naku ba Abbati. Ni Allah Ya gwadawa IkonSa ba kai ba."

Da sauri ya daga kai ya dubi Alh. Tahir. Shi ma din Abbatin yake kallo. Idanunsa sun cicciko da kwallar da ya manta rabonsa da yinta. Haka ya cigaba da magana jikinsa yana mutuwa da kowacce kalma. A jikin motar ya jingina saboda babu sauran karfi a tare dashi. Ya daure dai ya fada masa cewa maganin bacci ne aka shakawa Qibdiyya saboda haka ya kwantar da hankalinsa zata dawo daidai nan da awa daya ko kasa da haka kamar yadda Comared ya fada masa. Yana ganin yadda Abbati ya shafa fuskarta cike da kulawa. A ganinsa wannan ita ce soyayyar iyaye da 'ya'ya ta gaskiya ba wadda yake ikirarin yiwa nasa ba. Zantukan da suka biyo baya kuwa ya yi su ba a cikakken hankalinsa ba.

"Ban taba tuba ba. Shekara da shekaru Khadija tana kuka tana hakuri dani. Sai yanzu ne ma wani dan dalili yasa ni nadama. Bukatar kawar da wannan dalilin ce ta kawo wannan lokaci. Kafin zuwanka ina tunanin akwai lokaci a gaba da zan sami damar yin hakan in tsufa ya kamani. Ashe lokacin zai biyoni yau? Suhaib ya sani! Farha ta sani!! Lilu ma ya sani!!! Amma hawayen 'ya'yana dana mahaifiyarsu bai sa naji lokacin tubana ya yi ba. Ba don abubuwan da suka faru ba a ciki da yanzu kila na amince anyi..." Karshen maganar nauyi ya yiwa bakinsa dole ya datse zancen.

Kamar saukar guduma maganganun suka dinga shigar Abbati. Farha ta san mahaifinta yana zina? Ko shi ne musabbabin ganin canjin da ya yi a gareta kwanakin baya da Alh. Tahir ya dawo gida suna wurin?

"Ban taba mu'amala da maza ba. Na yau din ma dalili ne" kamar an matsi bakinsa ya fadawa Abbati abin da yasa ya zo Kano yau da kuma dalilin nadamarsa. Wato sanin da Farha tayi cewa yana neman aminiyarta wanda da ace aurenta yake nema kadai ma da sauki.

"Mayafin da ya lullube soyayyar da 'ya'yana suke yi min naso yayewa. Na tabbatar fasa auren Yumna zai iya dawo min da martabata a idanunsu. Ashe Yumna ba ita ce matsalata ba. Ni ne matsalar kaina. Wallahi Abbati ina jin kamar na bude ido naji an shafeni baki daya."

Shi dai Abbati kasa cewa uffan yayi saboda shi ma din mai laifi ne. A nutse dai ya saurari dukkan maganganun Alh. Tahir wanda ya sake dauka a matsayin izina. Babban mutum, mai kudi, iyali, da kima a idanun al'umma ya tasa shi a gaba yana ta sumbatu. Ashe idan basu tuba ba nan gaba suna da rabon ganin rana makamanciyar wannan ko ma wadda ta fita muni.

Duk wata daraja da kimarsa shi da kansa yake jin sun gudu sun bar shi a dalilin haduwarsa da Abbati a gidan nan. Zuciyarsa har lokacin bata huta da kakkarfan harbin da take yi masa a kirji ba. Wace irin masifa ce tafi wannan? Ya aka yi bai ji girman laifinsa ba a lokacin da 'ya'yan cikinsa suka san sirrinsa sai yanzu a gaban mutumin da bai riga ya zama surukinsa ba? Kalmar surukin da ya ayyana a ransa ita ta sanya shi yin wani tunani. Babu bata lokaci kuwa domin tabbatarwa ya nuna saitin jerin wasu motoci guda hudu ya ce,

"Don Allah taimaka ka miko min wayata a cikin mota in kira likitana"

Durkushewa ya fara yi wanda hakan yasa Abbati yin saurin zuwa wurin motocin ba tare da ya tambayi wacce bace cikin hudun. Da d'ai-d'ai ya dinga bin tagogin motocin yana lekawa ko zai hango wayar amma bai samu ba. Ya taba hannun babu wadda ta bude. Ya dawo da sauri ya tambaye shi ,

"Wacce ce a ciki? Duka a rufe suke."

Maimakon ya bashi amsa sai yaji ya ce "Zina bata yarda taci bashi bata biya ba komai daren dadewa. Naji dadi da kunnuwana suka jiye min kalaman tuba daga gareka wanda yanzu na tabbatar baka fadesu domin ka san ina ciki ba."

Yana gama magana cikin gidan ya koma. Abbati ya sake taba jikin Qibdiyya sau daya bayan ya shiga mota ya zauna sannan ya tayar ya tafi.

***

Wani irin ihu Zakiyya tayi da Abbati ya shigo da Qibdiyya cikin falon Munzali tamkar bata da rai. Ya manta ta zo gidan da bai shigo kai tsaye ba. Munzalin ma hankalinsa ba karamin tashi ya yi ba da yaga hannuwanta suna kadawa su kadai.

"Me ya sameta kuma? Tare da Asaben ka daukosu? Ko ita kadai ta biyoka bayan ka ajiye su Innayo?"

Akan doguwar kujerar da Zakiyya ta tashi ya kwantar da ita.

"Maganin bacci aka shaka mata. Nan da. .."ya dubi agogon hannunsa "minti talatin idan bata tashi bane zamu nemi likita"

"Ka kara sakani a duhu. Me yake faruwa ne?" Cewar Munzali yana tattaba jikin Qibdiyya.

"Zakiyya bamu wuri don Allah"

Gyara zama tayi abinta a kusa da Qibdiyya tare da rike mata hannu.

"Gara ma ka fadi ko ma mene ne don babu inda zani alhali akan 'yata zaka yi magana."

"Zaki tashi ko sai na mugun bata miki rai"

Tsawar Munzali ta tsorata ta amma bai kai yadda zata iya bin umarninsa ba. Zai sake magana Abbati ya ce,

"Zakiyya ki dauketa ku je sama ki yi mata wanka. Nayi miki alkawari zaki ji duk wani abu da ya kamata idan na gama magana dashi."

Ba haka taso ba sai dai kuma a yau din Abbati ya yi mata kwarjinin da bata taba gani a tare dashi ba. Tashi tayi da Qibdiyya a kafadarta sai Munzali ya zo ya karbeta. Dakinsa ya kaisu ya fito ya rufe kofar. Da sauri ya dawo ya zauna a gaban Abbati. Shi kuma sai ya kama hannunsa suka fito waje ya bude mota suka shiga. Tafiyar kimanin minti goma suka yi wadda ta dan nesantasu da gida sannan Abbati ya tsaya.

"Ina so ka saurareni da kyau Munzali."

"Don Allah ka daina ja min rai haka. Wallahi kiris nake jira zuciyata ta buga kawai. Me ya faru?"

Tiryan tiryan Abbati ya shiga labarta masa abin da ya faru a daren jiya da yana kwance a asibiti har zuwa yanzu. Kai ya rike wanda yake azabtar dashi da bala'in ciwo da yaji karfin halin Shazali na daukar musu 'ya. Ga kuma bacin ran son tilasta Abbati ya koma ruwa. Murfin motar ya kama ya ji ta a rufe.

"Bude min Abbati. Ina jin nine ajalin Shazali." Ya furta a fusace idanunsa sun kankance sun kara yin jazur.

"Munzali ka daina magana irin wannan" Abbati ya ce dashi a tausashe.

Kallon takaici Munzali ya bishi da shi yana taune labbansa.

"Wacce iri ya kamata in yi? Fatan alkhairi zan masa ko me? Da ka amince fa? Da shegen ubangidan nasa ya taba Qibdiyya fa? Da me zan ji? Da me zan ji??" Karshen maganar muryarsa karyewa tayi sakamakon hawayen da ya soma bin fuskarsa.

"Idan kana irin wannan abin bana jin zan sami kwarin gwiwar karasa maka labarin nan."

Idanunsa fayau kamar fanko ya dubi Abbati ya ce "ina jin ka. Har akwai wani mummunan labari da zai kara tayar min da hankali makamancin wannan?"

Abbati bai bar komai ba game da haduwarsu da Alh. Tahir da kuma abin da Innayo ta fada masa na Ayaah da Suhaib. Sai ga Munzali ya kasa cewa komai sama da bude baki da rufe shi. Mamaki da kaduwarsa suka ninku dari bisa dari da ya fada masa abin da Innayo ta ce Suhaib ya yi na taimakon Ayaah. Da kuma wayarsa da Farha.

"Tabbas akwai kudurin Allah a cikin haduwarmu da iyalin nan. Ka duba kaga alakarmu da 'ya'yan gidan, da haduwata da babansu wanda ba don shi ba kila da Allah kadai Ya san halin da zamu shiga yau. Sannan ga taimakon tsare mutumcin Ayaah da ...

Yana cikin magana kawai yaga Munzali ya zura hannu ta gabansa ya bude lock. Hakan ya bashi damar bude bangarensa ya fita da sauri ya zagaya ya bude shi.

"Fito in tuka"

"Ina zamu je?"

"Don Allah ka fito. Wannan labarin ya bude min tunanina akan abubuwa da dama"

A zaton Abbati tunanin Munzali ya tafi daidai da nasa akan ganin akwai abin da Allah Ya yi nufi da Ya hadasu da mutanen nan. Bai san cewa a nasa lissafin ya kara gaskata cewa lallai Lilu ne ya bata masa 'ya ba.

***

Anti Hasiya da kanta ta hada kayan Abbas dana Honourable na tafiya asibiti. Ranakun farkon aikin ne zai dinga kwana. Daga nan kuma sai dan mai bin A'i ya cigaba da kwana. Larai ce ta dage bata yarda ya nemo mai kwana da jikanta ba a cikin danginsa. Mutanen da basu iya taimaka musu da hatsi ba a lokacin da komai ya jagule masa. Ita ma Anti Hasiya tayi na'am da shawarar. Ta san yaron ba zai kuskura ya yi wasa da lafiyar dan uwansa ba ko don gudun fadan kakarsa. Sun gama ta kira Innayo ta fada mata karfe nawa duka zasu rankaya asibitin. Ba za su dawo gida ba a cewarta sai an fito dashi.

"Inji waye ya ce ba za ku dawo gida ba? Ke fa na lura ganin kanki kike yi daidai da kowa" Honourable ya ce yana mai daure mata fuska da wasa bayan ta gama wayar. Tuni ta gano korafin nasa bai rasa nasaba da cikinta ba.

"Don Allah kada ka koroni gida wallahi fargaba ba za ta barni ba"

Illolin zaman asibiti da yanzun nan ya tattarasu a kansa saboda rashin son ta wahala ya shiga jero mata. Daga karshe ya hada da rarrashi.

"Hasiya bana son mu yi sakaci da taki lafiyar. Allah bai hana ni 'ya'ya ba kuma nagode Masa akan wannan ni'ima. Hakan bai hana ni kwadayin son ganin irin da zaki haifa min ba."

Murmushi ta bige da yi don ta riga ta san cewa ya gama cin wannan yakin. Da lokacin tafiya asibitin ya yi baki dayansu suka tafi aka rufe gida. Larai ma iyalanta a asibitin suka riskesu.

***

Ba karamin dadi Suhaib yaji ba da zuwan su Mami. Abin da bai saba yi mata ba ma ya dinga yi lokacin, wato raki da shagwaba. Damuwa da kulawar da take nuna masa ne bai gaji da gani ba. Ko yaya ya motsa kafar sai ya ce wash. Ita kuwa jiki na rawa ta dinga ambaton sannu, ko ta ce a koma asibiti. Mayafi ta yafa ta riga kowa mikewa tana cewa gara dai a je ayi x-ray a kafar. Matan gidan dasu Farha suka taru suna yi mata dariya da suka fahimci yana yi ne da gangan.

"Ki yi zamanki Mami tsokanarki kawai yake yi." Cewar Farha bayan kowa ya fita daga dakin an bar uwa da 'ya'yanta.

Kan Suhaib ta shafa cike da kulawa ta ce "idan ma karyar ciwo yake babu ruwanku. In yana so yau har goyo zamu yi."

Lilu da Farha basu san lokacin da suka sake kwashewa da dariya ba. Suhaib kuwa pillow ya dauka ya kare fuskarsa yana cewa,

"Haba Mami a gaban yara ki ke kiramin goyo don su raina ni?"

Daure fuska tayi cikin wasa ta ce "Kai ba a gaban yaran ka ke ta wash-wash ba saboda samun wuri?"

'Yan uwansa ya kalla suna ta dariya ya wulla pillow din saitinsu "Da daya daga cikinsu ne ba za ki ce suna yi don samun wuri ba"

Sai da suka gama zolayarsa ita da Farha da Lilu sannan ta dawo gefen gadon ta zauna. A ranta take kara jin cewa tabbas haihuwa kyautace daga falalar Ubangiji. Duk tarin bacin ran da babansu yake haddasa mata da ta kebe da yaranta sai ta manta da wanzuwarsa. Murmushi ta sakar masa tare da mika masa wayarsa.

"Saki ranka ka kira wadda tayi nasarar canja min kai daga sarkin zafin kai zuwa wannan Suhaib din dake gabana."

"Ummmmm"

Lilu da Farha suka fitar da sautin shakiyanci a tare. Mami babu bata lokaci ta nuna musu kofa tana shan kunu. Ficewa suka yi ana jiyo dariyarsu. Sai da suka rufo kofar sannan ta ce,

"Ayaah ce ko?"

Kallon rashin fahimta Suhaib ya yi mata ya amsa da cewa "tayi me?"

"Ta taba zuciyarka har kake yi min abin da ban taba gani ba tun tasowarka."

Kai ya shiga sosawa irin na marasa gaskiya "nifa babu komai a tsakaninmu"

"Sai ka dage ka gina abu a tsakanin naku kafin wani ya riga ka."

"Kai Mami..." Suhaib ya furta a kunyace yana kawar da kai. Da kafarsa kalau take ma da ficewa zai yi daga dakin a guje.

Zuciyarta tamkar an zuba ruwan sanyi ta dube shi ba tare da alamun wasa ba.

"Suhaib ka cinye kuruciyarka wurin dauke damuwata da kulawa da 'yan uwanka. Shi yasa ba ka san wasa ba balle yadda ake yinsa. You were too serious. Yau gashi Allah Ya amshi addu'ata. Da kan ka kake kirkiro wasa a tsakaninmu ba tare da ka san kana yi ba. Na san ba zai wuce haduwarka da niece din Munzali ba. Kana sonta ko?"

"Mami sa'ar su Sauda ce fa. Yanzu

take shirin gama secondary school"

"And so?"

Kada kai ya yi yana dariya ya ce "wannan hirar tayi min nauyi Mami a canja wata"

"An canja Suhaib. Ai ni yarinyar nan ta gama min komai. Allah dai Ya rabaka da sharrin late-comer. Idan ka tsaya wasa labari zai sha bamban."

"Allah ma Ya kiyaye"

Sai da maganar ta fito ya kama bakinsa. Karo na biyu kenan da ya fadi kalmar nan garera akan Ayaah. Tare suka yi murmushin farinciki. Mami ta sake dubansa, shi ma sai ya nutsu da ya gane magana take son su yi. Wayarta ta mika masa daidai sakon da ta turawa Abbansa. Ya karanta sau daya ya ajiye wayar a sanyaye ya ambaci sunanta

"Mami?"

"Na taba yunkurin neman sakin har sau biyu amma iyaye suka hana ni. Sai dai wannan karon kamar yadda na tura masa text dinnan to in sha Allahu babu gudu babu ja da baya."

"Su Yakumbo zasu amince?"

"Da Allah kadai na dogara. Shi ne Ya haramta zama tsakaninmu. Allah ne shaidata ban taba kusantar kowa a waje ba. Na killace kaina da taimakonSa. Kuma nayi imanin zai taimakeni akan kudirina."

Hannunta kawai ya rike yana jin wani irin nauyi a zuciyarsa. Ba don rabon haihuwarsu ba da wannan baiwar Allah bata zauna ta kwashi bakinciki irin wannan ba.

"Na rasa kalmar da zan yi amfani da ita domin kwantar miki da hankali Mami"

"Kayi mana addu'a ni da ku Allah Yasa hakan alkhairi ne a garemu baki daya. Zaman da ake ta cewa nayi domin ku bai amfana komai ba sai tonon silili. Farha da Lilu na fada maka sun san komai. Da ace na tafi tun kuna yara da har yanzu kuna ganin mutumcin Abbanku. Akwai ciwo a dan da zai san mahaifinsa yana yawo a waje. Har gara mata akan dan cikinka."

Kwalla ce ta zubo mata Suhaib ya soma bata hakuri. Lokacin kuma Farha ta bude kofar saboda ta manta wayarta. Halin da ta riskesu ya daga mata hankali. Da sauri ta shigo tana kukan da ta riga ta gane musabbabinsa.

Wayar Danliti dake gefensa Suhaib ya budo ya mikawa Mami.

"Kinga sakayyar Allah. Ki daina damun kanki. Gara mu tafi kafin muma wata rana dattin ya shafemu."

Da ta karanta irin kazaman chats din Danliti da Jiddo bata san lokacin da ta kankame Suhaib da Farha ba.

"Kada ku kusanci zina. Wallahi a cikinta akwai tozarci da kaskanci. Ko da raina ko babu don Allah kada ku yarda shaidan yaci galaba akanku. Ba zan yafewa duk wanda ya aikata ta ba cikinku."

Suna cikin wannan yanayin Prof. Zuwaira aminiyar Mami Khadija ta kirata. Sai a kira na uku bayan ta saita kanta ta iya daukar wayar.

"Dr. Khadija kun iso?"

"Eh, a nan shadaya tayi mana."

"Kin ganni mun gama shiri zan bar Kanon yanzu ni kuma. Kwatanta min gidan sai na biyo na duba d'ana kafin mu wuce"

Cikin yaran gidan Mami ta samu aka turawa Prof. Zuwaira text na kwatancen gidan. A falo suka hadu da kowa ana taba hira. Suhaib kuwa zamansa ya yi a daki ya dauki wayarsa yana jujjuyawa. Muryar Ayaah yake son ji tana tsiwar nan. Har zai kira ya tuna ta ce babansu ya karbe mata waya. Komai tsaya masa ya yi da tunaninta. Anya zai iya barin Kano bai ganta ba?

Waya Mami ta cigaba da yi da Prof. Zuwaira inda take kara yi mata kwatance saboda sun kasa gane layin. Ta nemi Lilu domin ya fita hanya bata gan shi ba. Sauran yaran cikin gidan duka mata ne.

"Gidan shi ne mai bakin gate a close din. Bari na fito waje kila ku hango ni"

Tashi tayi ana cewa ta bari a tura wata cikin yan matan ta ce babu komai. Da wayar a kunnenta ta taho bakin gate din suna waya da Prof. Zuwaira. Zuwan Lilu ne ya taimaka wurin saukaka musu. Location dinsu ya turawa Prof. Zuwaira ta whatsapp din Mami. Ba jimawa kuwa sai ga kiranta ta ce layi daban suka shiga amma yanzu zasu juyo. Tare suka tsaya jiran isowarsu a bakin gate ta ciki yana ta tsokanarta wai zamani ya canja waye yake zaman cewa a bi hagu a karkata dama.

***

Saboda mugun gudun da Munzali yake saura kadan ya wuce gidan Kawunsu Suhaib sannan ya farga. Da sauri ya taka wani wawan burki sai da taya tayi kara sannan

shi da Abbati suka yo gaba kamar an hankado su. Cikin fushi kuwa Abbati ya hau shi da fada.

"Lafiyarka kuwa Munzali? Wane irin tukin ganganci ne kake yi?"

"Kira Farha ka ce mata ta turo Lilu ya zo ya shiga damu."

Abbati ya kalle shi a tsanake ya adana bacin ransa domin son fahimtar inda matsalar take.

"Me yake faruwa? Don zamu zo duba Suhaib sai mu fito a haka? Jallabiya ce fa a jikinka. Kalli yadda Shazali ya yi min da riga." Ya nuna masa kayansa da suka dukunkune kamar sun fito daga rami.

Ficewa Munzali ya yi daga motar idanunsa a rufe da bacin rai ya nufi gate din gidan ko kallonsa bai yi ba. Yana fita Abbati ma ya fito. Yana ganin ya daga hannu har ya buga gate din sau daya yayi saurin riko masa hannuwa.

"Munzali meye haka wai?"

"Sake ni Abbati. Ka sakeni in kamo dan iskan yaron nan..."

Gaban Mami Khadija yankewa yayi ya fadi ta damki hannun Lilu a tsorace.

"Muryoyin nan ba na Munzali da Abbati bane?"

Kafin ya iya cewa komai Abbati ya sake yin magana. Ransa a bace yake matuka don duka kafadun Munzali ya riko ya juyo dashi suka fuskanci juna. Zuciya ta tunzura shi ya daga murya yana fada.

"Wane yaro? Sai tambayarka me yake faruwa nake ka ki kayi magana. Me muke yi a kofar gidan nan?"

"Lilu zan kashe."

"Me???" Abbati ya sake shi babu shiri yana yi masa kallon mara hankali.

"Yadda bai iya tausayawa Qibdiyya ba nima..."

Da sauri Abbati ya dora hannunsa ya toshe bakin Munzali sannan ya ce,

"Shi ne? Qibdiyya ce ta fada maka?"

Munzali ya gyada kai hawaye yana zubo masa.

Mamaki ya kama Abbati ya ce "A yaushe? Duka duka sau nawa suka taba haduwa? Kaga zo mu koma gida..."

Zuciya da bata da kashi. A take ta Munzali ta shiga kuncin ganin kokonto a fuskar Abbati. Bai san lokacin da ya fuzge hannunsa daga gareshi ba ya ja baya.

"Nufinka karya nake yi?"

Sassauta murya Abbati ya sake yi saboda ko kadan baya so wani yaji sirrinsu. Da lallashi ya ce,

"Ba haka nake nufi ba Munzali. Wannan maganar tana da girma. Ka zo mu tafi mu fara yin shawara a gida."

Zuciyar Munzali ta kara zuwa wuya. Wace irin shawara kuma zasu yi a gida bayan gasu a kofar gidan da zasu sami Lilu? A tunaninsa jin sunan wanda ya bata Qibdiyya sai ya batawa Abbati rai fiye dashi. Me Abbati yake nufi da nuna sanya akan lalurar 'yarsu? Sai yanzu ma ya tuna cewa tun zuwan Abbati jiya ko sau daya bai tambaye shi waye ya keta mata haddi ba. Wani hawayen ne ya zubo daga idanunsa da suka rine kamar garwashi ya yiwa Abbati kallon takaici. Kallo irin wanda bai taba tsammanin zai gifta tsakaninsu ba.

"Sanin waye ubansu da kayi a yau dinnan bai isheka hujjar yarda da maganata ba? Ko soyayyar da kake yiwa Farha ce tasa kake kokarin kare kaninta ko kuwa don baka san zafin haihu.."

Tsayuwar gaggawa ce ta kama numfashin Abbati da bugawar zuciyarsa. Jikinsa ya hau bari saboda tsananin bacin ran sanin abin da Munzali yake shirin fada. Gumi ne kawai yake zubo masa kamar ruwa ga wani uban sanyi da yake ratsa kasusuwansa. Bai barshi ya karasa maganar ba ya dakatar dashi cikin zafin rai.

"KAR KA SOMA WALLAHI! Kada ka kuskura kayi min gorin haihuwar Qibdiyya don bacin ran da zamu shiga sai ya ninka wanda muke ciki a yanzu"

Munzali kasa motsawa ya yi ko kadan sai idanu da ya kafe Abbati dasu.

Shi kuwa Abbati jikinsa sai karkarwa yake kamar wanda zazzabi ya yiwa mummunan kamu. Bai haifa ba ya sani. Qibdiyya ba jininsa bace wannan ma ya sani. Fargabar da ya shiga ba komai ya janyota ba sai tsoron kada wannan masifar ta zama silar watsewar alakarsu da dan uwansa don ya wuce amini. Zai iya daukar komai banda gorin haihuwarta. Domin da zarar ya fito daga bakin mahaifinta kai tsaye zuwa gare shi, ya tabbata babu sauran zama a tsakaninsu. Munzali ba zai taba yi masa furuci irin wannan a halin rashin sani. Idan ya yi to tabbas daga zuciyarsa ne. Cikin sanyin gwiwa ya juya ya fara nufar motar.

"Ina za ka?"

Munzali ya fada da wata irin murya tamkar ba tasa ba. Yawun bakinsa ma daci yake yi masa saboda masifar halin da yake ciki.

"Ka same ni a gida idan ka aiwatar da abin da zuciyarka ta raya maka."

Yana rufe baki wani adaidaita sahu ya tsaya a gabansa wanda Munzali bai kula da lokacin da ya daga masa hannu domin ya karaso ba. A guje kuwa ya bi bayansa yana kwala kiran Abbati. Da suka ki tsayawa ya durkushe a wajen ya dauki hannu ya dinga dukan goshinsa da cikin tafin. Idan bai yi a hankali ba yana jin yana daf da zarewa. Banda haka me ya kai shi furta wandannan kalamai ga Abbati?

*

Gudun jinin Mami Khadija ya ninku, bugun zuciyarta ya zarce ka'ida. Tashin hankalin da ta shiga ya zarce tunani balle a fade shi. Duk wata kalma da ta fito daga bakin Abbati da Munzali ta sami damar shiga kunnuwansu ita da Lilu. Ma'anar zantukan nasu ya fita dalla-dalla basa bukatar karin bayani.

Daga gabar da suka fahimci inda maganganun suka dosa Lilu ya saki wayarsa a fusace ya nufi gate din. Kunnuwansa sun kurmance, haka nan idanunsa sun makance. Abu daya kawai yake hangowa shi ne hannuwansa a wuyan Munzali a yayinda zai tuhume shi dalilinsa na yi masa sharri.

"Me kake shirin yi? Ina za ka?" Mami ta tambaye shi a firgice lokaci guda ta riko hannun shi domin hana shi bude gate. Sa'arsu daya maigadin ya zaga bayan gidan zai cirowa matar gidan zogale.

Muryarsa tamkar ba tashi ba saboda tashin hankali ya dube ta da mamakin tambayar da tayi masa.

"Baki ji me ya ce ba? Ki barni in je..."

"Kada ka fita" ta furta tana girgiza masa kai.

Shi ma kan ya girgiza kuma sai lokacin hawaye ya sauko masa ya ce "idan ki ka hana ni fita zuciyata za ta iya bugawa Mami. Wallahi baki san yadda nake ji ba. Zan iya mutuwa...Mami ni ba Abbanmu bane. Ba zan taba yarda ko da wasa wani ya jefeni da irin abin da ya dade yana sanyaki kuka akan Abba ba. Kina ji fa akan sanin halinsa aka dogara da cewa ni nayi."

Daga nan bai kuma sauraronta ba ya fita da sauri. Cikin sa'a yana fita ya sami Munzali ya shiga mota kenan har ya tayar. Ba tare da bata lokaci ba kuwa ya zagaya daya barin ya bude.

Kallo daya Munzali wanda idanunsa suka yi masa nauyi saboda tsabar zubar hawayen da suke ya yi masa ya kashe motar. Mamakin karfin halinsa ya ma hana shi cewa komai. Sai Lilu ne da kansa ya ce,

"Ka kaini gidanka. Ka kaini gaban Qibdiyya in ji yadda aka yi na yi mata fyade."

"Kada ka sake ambaton sunanta. Kuma ka fice min daga mota don ban san me zan maka ba."

Wata irin dariya Lilu ya yi yace "kaga nayi kama da matsoraci ne?"

Domin samun damar wanke kansa a gaban Abbati ya fizgi motar a guje. Tashin motar ya faru akan idon Farha, Mami Khadija da Suhaib wanda ya fito yana jan kafa. Sai Prof Zuwaira da suka iso lokacin. Jama'ar gidan da suka biyosu bayan shigar Mami tana kiran Farha duka sun shiga tashin hankali. Da ta bawa Farhan mukullin mota akan su bi bayansu sai da matar kawun nasu ta ce ga direba ko ma mene ne gara wani ya kai su.

"Kiyi hakuri Anti. Idan Allah Yasa wutar ta mutu da kaina zan baki labari. Ki ara min yau ta zama sirrin gidana don Allah." Ta juya ta bawa Prof. Zuwaira hakuri da alkawarin zasu yi magana a waya in Allah Ya yarda.

Dole kowa ya hakura. Suna kallo Mami ta taimakawa Suhaib suka shiga baya, Farha taja mota da gudu. Kafin ta karasa kan titi ta kira Abbati bisa umarnin Mami. Da yake shima suna tsaye a junction ba a basu hannu ba shi yasa yaji kiran. Ganin sunan Farha ya bashi tsoro ko Munzali ya yi wani abu. Yana amsawa yaji muryar Mami.

"Kwatanta min gidanku"

"Lafiya kuwa Mami?" Ya ce a razane.

" Munzali ya tafi da Lilu."

"Innalillahi wa inna ilaihi raji'un. Kuna ina yanzu? Bari na juyo. Ko dan gari ne zai kawo ku?"

"Mu kadai ne"

Inda suke kawai ya bukaci sani ya ce su jira shi a nan. Tsayuwar minti goma sha biyar suka yi domin ya hadu da goslow a hanyar dawowa. Kafin isowarsa ne Mami ta sami damar sanar dasu Suhaib abin da suka ji ita da Lilu. Hankulansu duk a tashe har Abbati ya iso. Yana zuwa bangaren direba ya nufa ya bude kofar. Farha tayi masa wani irin kallo wanda ko kusa bai bata masa rai ba.

"Ki bashi wuri ya tuka" taji muryar Mami a kunnuwanta.

Ba don ta so ba ta fita ta koma daya barin. Abbati ya dinga tukin 'yan Kano saboda tsoron abin da zai iya faruwa a gidan kafin su isa.

BABI NA SHIRIN DA ƊAYA.

***

Fitar su Munzali ba jimawa su Mal. Inuwa suka iso. Maigadi ya bisu har bangaren Abbati yana yi musu maraba bayan ya rufe gate din. Bai gane Mal. Inuwa da Mal. Sa'idu ba. Amma Habu ba bakonsa bane tunda yana yawan zuwa gidan. Sannan ya hadu da Baaba Mari sau biyu. A wurinsa suka ji cewa Abbati da Munzali basa gida amma Hanne tana nan. Da murnarsa ya dinga kwada sallama a kofar gidan tare da bubbuga dan hannun kwankwasa kofa da yake daga wajen.

Hanne tana tsakar cin abinci taji bugu. Tsaki ta jejjera sun kai goma sannan ta mike ta ajiye plate din da ta gama shakarewa da abinci.

"Waye ne?" Ta ce bayan sautin wani tsakin nata ya karade kunnuwan su Baaba Mari.

A gajiye suke su duka musamman ita da Mal. Sa'idu saboda yanayi na rashin lafiya.

"Iyayenki ne" Mal. Sa'idu ya furta da fada.

Faduwar da gabanta ya yi a lokacin ba na wasa bane. A iya saninta idan ka cire tafiyarsu Hajji bata taba ganin kawun nasu a Kano ba. Mantawa tayi da hannu ta fara cin abinci ta damki hannun kofar ta bude. Da d'ai-d'ai ta bisu da ido har suka shiga suka zazzauna. Habu ne kawai bai biyo su ciki ba ya tsaya suna sake gaisawa da maigadin. Hanne ta rufo kofar ta durkusa ta gaishesu. Babu yabo babu fallasa suka amsa. Na iyaye mazan bai dameta ba sai na Baaba Mari. Tunda suke bata taba ganin ta canja mata fuska daga faram-faram ba. Shi yasa taji gabanta ya soma faduwa ta fara tunane tunane barkatai.

Gauron numfashi da Mal. Sa'idu ya sauke da kyar na ciwon jiki ne yasa ta mayar da hankali gareshi a k'agauce.

"Ina yayan naki"

"Ya fita"

Mal. Inuwa ya ce "ya yi miki bayani akan abin da yake faruwa?"

Kafadarta ta daga da fari alamun ko-in-kula, sai kuma taga rashin dacewar hakan tayi saurin cewa bai yi ba.

Ita Baaba Mari ta riga ta san za a rina. Komai dangane da zaman Abbati da Hanne ba bakonta bane. Mal. Sa'idu ne ma yanayin nata ya dan bashi mamaki har ya kai ga tambaya.

"Wane irin zama kuke yi da dan uwan naki ne?"

Hanne na jin haka ta jinjina kai da cije lebe. Zuciyarta ta raya mata kila auren Abbati aka yi da 'Yashshafa shi ne iyayen suka zo da kansu don kada ta tada balli. Ido a rufe kuwa ta ajiye tsoronsa a gefe ta soma kuka da fadin maganganu.

"Haihuwa ta Allah ce ba ni na dorawa kaina ba. Tuntuni Baaba Deluwa take son amfani da hakan domin ta hada shi da 'Yashshafa..." Ta sake fashewa da kuka tana jan hanci "ashe sai da ku ka hadasu" 'yar karamar dariyar farinciki tayi da ta tuna wani abu wanda kuma bata barwa cikinta ba "Sai ta shirya, yadda na san ko zan hadiyi Al'Qur'ani ba zan kaffara ba cewa babu soyayyata a ransa na rantse har gwara ni akanta. "

"Bana son zancen banza. Me ya kawo zancen karin aure kuma?" Cewar Mal. Inuwa domin katse soki burutsun Hanne wanda zai iya janyo mata mummunan hukunci a wurin Mal. Sa'idu.

Shi kuwa gogan hannu kawai ya dan daga yace masa ya barta "yaran nan duk abin da suka yi basu da laifi. Tun farko na riga na fahimci zaman nasu babu armashi sai dai ban yi tunanin kawo musu maslaha ba. Idanuna sun da son ta zauna domin maganar abin da ya wuce a baya kada ta sake tashi."

Cikin tashin hankalin tsoron tabbatuwar hasashenta Hanne ta waro idanu tana cewa "Maslahar ce tasa ka bashi 'yarka?"

Rashin da'arta ya kara bawa Mal. Inuwa haushi ya daga hannu kamar zai kai mata mari.

"Za ki rufe mana baki ko kuwa? Idan auren aka yi masa ke kin isa ki kalubalancemu ne? Ko ruwa baki iya bamu ba sai surutan banza. Ko baki auri Abbati ma na zata zamu ci darajar zama yayyen mahaifiyarki"

'Shikenan! Ta tabbata an cikawa 'Yashshafa burinta. Yanzu Gwaggo Deluwa za ta yi yadda take so da Abbati. Karshenta ma tasa ya saketa' tunanin da yazo zuciyar Hanne kenan. A fili kuwa mikewa tayi cike da fitsara domin yau dai babu sauran tsoron Mal. Sa'idu a ranta ta ce

"Da kuna kaunar mahaifiyata da baku sa anyi min irin wannan kishiyar ba" idanunta akan Mal. Inuwa ta kara da cewa "irin wannan biyayyar da kake yiwa Baba Sa'idu wallahi sai...."

"Ke! Hanne? Baki san su waye a gabanki bane?"

Babu wanda ya kula da shigowar Habu sai da ya yi magana. Furucin nasa muguwar harara ya janyo masa daga Hanne. Ta dube shi sama da kasa ta tabe baki.

"Harda su kaza a cin danko? Idan ma kana tunanin kai wa Yaya Abbati gulmar abin da na fada ne to ka kwana da sanin cewa ko sakina ya yi ni ba zan saku ba. Wallahi zama daram a gidan nan ni dashi mutu ka raba."

Alamun tsoro ne ya bayyana a fuskar Mal. Inuwa ya dubi Baaba Mari da damuwa "Kina ganin abin da yarinyar nan take yi kuwa? Ko tana da mutanen boye ne bani da labari?"

Bahaushe ya kan ce a juri zuwa rafi wataran tulu zai fashe. Baaba Mari da bata tanka musu ba ko kadan sai yanzu ta daga kai ta ce "uhmm?" alamun bata ma san me suke yi ba. Yau da ace babu matsalar da ta kunno kai a rayuwar Abbati da har dariya sai tayi domin ko surukarsu wato mahaifiyarsu Mal. Sa'idu da tana raye bata taba yi masa magana irin haka ba. A gidansu kam shi kadai ne ya isa, ragowar jama'ar 'yan bin umarni ne kawai. Sai gashi da ranta da lafiyarta ba a labari ba taga mutuwar bakin Sarkin gida Mal. Sa'idu. Yana zaune gurum ya kasa cewa uffan sai girgiza kai kawai da yake yi.

"Nace ko tana da mutanen boye ne?" Mal. Inuwa ya sake nanata tambayarsa.

Baaba Mari ba shi ta bawa amsa ba. Hanne da ta soma cewa garau take tana tsaka da son murguda baki domin cikar tsiwar ta dakatar.

"Ya isa haka Hanne. Abin da kike gudu ba shi ya faru ba. Dalilin zuwanmu ya zarce batun kishiya ko sakin aure."

Yanayin nutsuwa da haibar Baaba Mari a lokacin da tayi maganar saukarwa da Hanne wata irin kunya da jin nauyi tayi. Ta kalli iyayen nata maza ta sunkuyar da kai da fargabar me zai biyo baya. Ita kanta bata san me ya shiga kanta ya bata karfin gwiwar sakin baki haka ba. Kokarin durkusawa ta soma bada hakurin gaggawa take yi suka ji ana kiran sunanta da karfi da bugu kamar za a balle kofar gidan.

***

Sai da aka kwashi kusan minti goma da Zakiyya taji karar tada mota sannan Qibdiyya ta soma mutsu mutsu. Da sauri kuwa ta kai hannu domin ta dagata sai gani tayi ta soma buge-buge da ihu tana cewa "ka kai ni wurin Daddy na"

Firgicin da ta gani a tattare da ita ya bata tsoro ta tsaya ta kare mata kallo da kyau bayan ta rirrike hannuwan.

"Qibdiyya bude idanunki nice. Mummy ce"

Tarrr ta bude idon ta tabbatar da abin da kunnuwanta suka ji. Ba shiri ta kai 'yan hannuwanta ta rungumo mahaifiyarta tana fashewa da kuka.

"Mummy ki boyeni kada ya sake tafiya dani."

"Waye?" Zakiyya ta tambayeta tana waige waige a dakin.

"Wanda ya gudu dani ya boyeni a gidansa jiya, kuma ya dokeni."

Tsoro ya sake kama Zakiyya. Gabanta na faduwa ta fara tariyo yadda Abbati ya shigo da ita gidan. Kamar an zabureta zuciyarta ta tsinke da mummunan tunani. Irin tunanin da yake zuwa kan kowace uwa a yayinda taga danta ko 'ya cikin yanayi mai cike da ayoyin tambaya. Babu bata lokaci ta dage mata siketa ta kai hannuwanta wadanda tsoro yasa suka yi sanyi kalau ta dubata. Wata irin gigitacciyar kara ta saki da ta tabbatar da abin da tayi zargi ya sami 'yarta. A lokacin bata ma iya tantance yanzu aka yi ko ya dade ba. Abu daya ne dai ta fahimta. Tabbas an raba 'yarta da darajarta tun bata san me duniya take ciki ba. A haka ta sabata a kafada ta fito a guje tana kiran Munzali. Da bata ganshi ba ta kira mahaifiyarta tana kuka amma ta kasa fadin me ya faru. A haka tayi hanyar gidan Abbati tana kiran Hanne.

***

Hanne dasu Baaba Mari babu wanda bai tako zuwa kofar gidan ba saboda karfin kiran da tashin hankalin dake tattare da muryar. Tana bude kofar Zakiyya ta fado ciki bata kula da kowa ba ta kama kokarin bude jikin Qibdiyya.

"Zo ki gani Hanne. An cuceni. An cuci ni Hanne"

Hannunta taji an rike kafin ta kai ga bude jikin. Ta juyo a birkice suka hada ido da Baaba Mari. A lokacin ta kula da mutanen dake cikin falon. Ta san kowa tunda suna zuwa Kirikasamma sosai a lokacin da take auren Munzali. Hawaye ne ya sake jika mata kumatu ta dora hannun Baaban a jikin Qibdiyya.

"Baaba Mari duba ki gani. Allah Yasa ni din ce ban gani daidai ba"

"Daukota mu shiga ciki"

Hanne ce ta dauko Qibdiyyan suka shiga wani daki a kasa aka bar su Mal. Inuwa da tunani.

***

Sai da ta gama shirinta tsaf wanda bai wuce wanka da mulka basilin ba ta nufi dakinsa. A kwance ta same shi ya yi shame-shame a kasan fanka yana jan minshari. Duk shige da ficen da aka dinga yi a gidan tun safe akan batan Qibdiyya ko a jikinsa. Ranta ya sake baci ta cije lebe ta kai hannu ta janye filon. Ba arziki kuwa Alh. Rabi'u ya tashi cikin dimuwar kasa tantance inda yake. Ido da suka hada ne ya sanya shi yin kwafa da wani bahagon tsaki.

"Ki adana rashin mutumcinki zuwa in gama baccin nan don wallahi idan ki ka kunno ni yanzu sai na saba miki. Bar ganin jiya kin min yadda kike so ban tanka ba. Tara ki nake." Yana gama magana ya sake mayar da kai kan shimfida.

Tsaki tayi cike da bakinciki ta ce "Malam ka tashi mu tafi gidan Munzali. Yanzu su Innayo suka dawo an sallame shi yana gida."

A fusace ya tashi zaune ya kai wa katifa naushi "Wohoho Asabe!...Allah dai Ya jikan Innayo ba don ta mutu ba. Ko kusa tarbiyarku ba daya bace. Bata san musu da miji ba balle tsaki. Banda shirmenki ma a ina kika taba ganin namiji yana rawar jiki akan ciwon 'ya'yansa kamar wani dan daudu?"

Asabe bata san lokacin da dariya ta kwace mata ba. Ta daga murya kuwa ta kwalawa Innayo kira. Ba jimawa kuwa ta iso. A tunaninta wani fadan suke yi wanda karshenta ya janyo Alh. Rabi'u ya taba lafiyar jikinta. Da ta gansu kalau sai ta juya za ta koma. Asabe ta yi azamar dakatar da ita ta bata labarin abin da yake faruwa.

"Da satin da ya wuce ne naji yabonki daga bakin Alhaji da nace kila malami ki ka canja."

Murmushi ne ya subucewa Innayo. Asabe kuwa ta hararai Alh. Rabi'u sannan ta ce "wannan magana har zuciyata nake fada miki"

Kafadarta Innayo ta dan tura tana mai cewa "Mu bashi wuri ya shirya sai ku tafi"

Haushi kuwa ya turnuke shi har wuya ganin da gaske 'yar maganar nan ta Innayo tasa ta daina yi masa tijarar da ta fara har tana shirin fita. A da tasu ta zo daya har ta kai suna kulla yadda zasu bakantawa Innayo rai a cikin hirarsu. Amma cikin kankanin lokaci komai yana neman sauyawa. Idan ya bar Innayo ta cigaba da shigewa Asabe ya san za a wayi gari ta karta masa rashin albarka fiye da yanzu. Karshen matsalar ba zai wuce ta hana Munzali bashi kudi ba wamda ko kusa ba zai jura ba. Zai zama cikakken lusari kuwa idan ya bari haka ta kasance.

Dakin Innayo dake cike da 'ya'yanta da wasu cikin jikoki duk sun ji lokacin da Asabe ta kirata. Uwani ma a hanyar fitarta daga dakin suka yi kicibus da ta shigo gidan. Hasiya kuma daga asibiti wurin Abbas suka wutu nan domin jajen batan Qibdiyya. Maimuna ma abin da ya kawota kenan. To dukkaninsu ko gaisuwar kirki basu samu yi da mahaifiyar tasu ba ta fita. Shi yasa da suka ji shiru bata dawo ba sai suka fito duka su biyar din da tunanin tabbas akwai matsala. Da isarsu kofar dakin ne kuma wanda ya yi daidai da sanyo kan Asabe da Innayo zasu fito sai furucin Alh. Rabi'u wanda ke duban Asabe yasa su cin burki.

"Dama na dade da sanin cewa kina da karancin hangen nesa. Banda haka har me ya faru da zai sa ki fara jin maganar Innayo akan tawa? Amma ance jiki magayi, ga ki ga ta nan. Ranar da munafuncinta ya bayyana kansa gareki za ki hankalta."

"Ke kuma" ya juya ga Innayo wadda jikinta ya yi sanyi akan maganganunsa "Kin bi kin cika min gida da zawarawan 'ya'yanki da basa tsinanawa kowa abin azo a gani. Masu takamar kudin cikinsu me suka taba yi miki na bajinta banda wulakanci da raini. Talakawan ne kawai a nanike dake saboda har yanzu suna morarki" ya daga yatsa kurkusa da fuskarta cikin fushi "baki isa ki shiga tsakanina da matata ba saboda haka ki fita idona in rufe."

Yatsan ya sake matsowa dashi kamar zai shigar cikin idonta tayi saurin runtsesu. Alh Rabi'u ya bita da kallon raini sannan ya dubi su Uwani da suka gama shigowa daya bayan daya. Da yake suma din a wuyansa suke tuntuni sai yaga dama ce ta amayar musu da cikinsa.

"Tunda muke dake ko naira dari cikin 'ya'yan nan babu wadda ta taba bani ta neman albarka. Abin ya jima yana ci min tuwo a kwarya sai kace ba jinina ba"

"RABI'U!!!"

Innayo ta kira sunansa da karfi, da kaushin murya da kuma sigar gargadin kada ya dora wata magana daga nan. Su Hasiya ma kowacce 'Baba' take ambata cikin tashin hankali banda Uwani. Ita kadai ta taka har gabansa ta dube shi duba irin wanda ko kusa bai kamata ya gilma tsakanin uba da 'ya ba.

"Mu ne kake zargin ba jininka ba ko kuwa duka 'ya'yanka da ka sakarwa uwayensu ragamar kula dasu tamkar marayun da basu da galihu?,"

"Mahaifin naki kike fadawa haka Uwani? To indai don nice bana son ki shigar min na yafe. Ki ja kannenki ku fita."

Kalaman Salihi ne suka dawowa Uwani ta dubi Innayo da kishiyar kallon da ta yiwa mahaifinta dakiku kalilan da suka wuce. Kwalla ce taf ta cike idanun dattijuwar da ta kawota duniya har ta fara saukowa. A take taji ta kara tsanar kanta da dukkan halayyar da ta gwada mata a shekarun baya.

"Nayi miki alkawari daga yau ba zan kara sabawa umarninki ba. Don Allah ki yafe wa rashin biyayyata ta yau domin idan ban yi ta ba bana jin zan taba yafewa kaina balle in roki gafararki akan abin da ya gabata. Tuni kawai nake son yi masa akan abin da na tabbatar ya sani."

Maimuna, Salima, Zara da Hasiya basu iya boye mamakinsu akan furucin Uwani ba. Asabe kanta sai da ta jinjinawa lokaci da dan Adam yake cewa bai bar komai ba. Yau Uwani ce tayi laushi irin haka a gaban uwar da kowa ya san bata gani da kima.

Innayo kuwa dan murmushi tayi wanda babu wanda ya fahimci ma'anarsa. Ta dai gyada kai alamun lamuncewa Uwani tayi abin da tayi niya ga mamakin dukansu sannan ta sami wuri akan tilon kujerar mai dakin ta zauna.

Kallon baki da hankali Alh. Rabi'u ya yi mata ya ce "kina nufin kin amince ta yi min rashin albarka?"

"Baba"

Sunan a tausashe ya fito daga bakin Uwani. Shi Alh. Rabi'u ma hantar cikinsa sai da ta kada saboda tana bude baki ya tsorata. A iya sanin da ya yi mata ba bata da tsoro balle kunya. Tunda ta iya yiwa Innayo shi waye da ba za ta yi masa ba?

"Naaaa...na'amm?"

"Allah Ya azurtaka da 'ya'ya goma sha uku. Cikinmu wa za ka bugi kirji ka ce ka taba siyawa magani ko da na ciwon kai ne ?"

Shiru ba amsa.

"Rai tara a cikin 'ya'yanka kuma duka mata Innayo ce ta dauki ragamar komai da komai namu har aure. Idan akwai wadda ka sayawa cokalin tafiya gidan miji ka kama sunanta a gaban matanka."

Idanusa kamar 'ya'yan bararriyar gurjiya ya yi tsilli-tsilli dasu ya kasa hada ido da kowa a dakin.

"Banda fitowa daga tsatsonka babu wani abu komai kankantarsa da za ka yi tutiyar cewa ka taba yi mana a matsayinka na mahaifinmu."

"Ya isa haka Uwani" cewar Maimuna saboda tsoron kada tayi rashin kunyar da zata koma ta taba mutumcin mahaifiyarsu.

"Ki barni Maimuna. Ni ba Innayo bace da zan zauna ina hadiyar bakinciki da bacin ran da zai iya haifar min da ciwon zuciya ba. Ba kuma Asabe bace da zan biyewa rashin kulawar miji in sakarwa duniya 'ya'ya ba. Banda shiriya ta Ubangiji ce da tuni munyi qaurin suna cikin gantalallun mata."

A salube Asabe ta ce "nima harda ni Uwani? Na zata tunda mun shirya da Innayo ba sai kin fadi aibuna ba."

Kaza huce kan dami. Maganar Asabe kofa ta budewa Alh. Rabi'u ya hauta da fadan borin kunya.

"Wato ni ta cigaba da fadan nawa kenan?" Ya kalli Uwani a fakaice ya ce "To duk tsiyar mutum sai na daga kafa uwarsa za ta shiga aljanna. "

"Haba dai Baba" cewar Uwani tana murmushi "Fir'auna ma duk kudi da mulkinsa wallahi yana ji yana gani Asiya RA za ta wuce aljanna kuma babu yadda ya iya."

Duk inda bacin rai yake yau ya sarkafi zuciyar Alh. Rabi'u. Abin takaicin ma dariyar da Asabe ta kece da ita wadda tayi sanadiyar murmushin su Zara. Baki yana fitar da kumfa kuwa ya ce "ni kike hadawa da Fir'auna? Innayo kina jin abinda 'yarki take cewa ko? Kina kuma kallon ragowar 'ya'yan naki suna yi min dariya."

Kallonsu tayi tana mamakin har a wannan lokacin ita kadai yake jingina wa su tamkar dasu ta zo gidan.

"Ku shige mu tafi"

Uwani sai cewa tayi "Allah dai Yasa ba wani laifin na kara yi ba. Ni gaskiya ce kawai nake son fada masa a matsayinsa na wanda ya yi sanadiyar kawomu duniya."

Zara tayi saurin karbe zancen da fadin,

"Baba ba komai Uwani take son fada maka ba illa ka sani cewa Allah baya zalunci. Babu ta yadda mutum zai cutar da abokiyar zamansa sannan ya yi zaton idan anje lahira sai an shawarce shi za ta ji dadi. Tsaf za ta wuce aljanna ta bar miji akan layi"

"Dani kike Zara?" Alh. Rabi'u ya ce cike da mamaki. Wato baki dayansu suna ankare dashi kawai sun yi shiru ne duk tsayin shekarun nan. Anya idan ya yi sake ba za su karasa kwance masa zani ba?

Salima ma tunanin gidansu da gashin k'umar da Ale Gambo ya yi mata yasa ta ce "ba kowacce mace bace take da zuciyar yafiya. Idan an fadawa mutum kuskurensa ya kamata ya yi ya karba. Sai ya bayar da hakuri tare da rayawa a zuciyarsa cewa ya daina. Domin duk wani bacin rai ko hawaye komai kankantarsa da miji zai dasawa matarsa ba bisa hakki ba sai an fitar mata da hakkinta."

"Sanin hakki da kyautatawa ke rike aure ba kudi ko talauci ba Baba. Idan neman na kai ne babu wanda ya kai Innayo. Kyawun hali da hakurinta kuwa hatta 'ya'yanmu suna jinjinawa. Amma mun tashi da ganin babu wata mu'amala a tsakaninku sama da kyara da hantara" inji Maimuna tayi maganar idanunta suna ciccikowa da kwalla.

Hasiya ce ta rufe zancen gabadaya da cewa "Baba iyaye su suke koyawa 'ya'yansu tausayi da jinkansu. Innayo tayi iya yinta sai dai ance zama da madaukin kanwa shi ke kawo farin kai. Kamar yadda Maimuna ta ce ne, mun tashi mun san cewa mahaifiyarmu tafi borar mata kaskanci a wurinka. Wannan ya yi sanadiyar kyamarta daga 'yan uwana na haihuwa da ma wadanda ta tayaka sauke hakkinsu ('ya'yan Larai)"

"Ina miki kallon mai hankali ashe duk uwar darin ce ke da Uwani?"

"Ko kusa Baba. Ita fa da a namiji ta zo na tabbata halayenku sai sun yi tagwaitaka"

A kufule Uwani ta ce "Innayo kina jinta fa"

Hasiya ta ce "nima gaskiya zan fada muku kamar yadda ki ka faro. Baba kaga duk wanda ya zama sanadiyar aikin alkhairin wani yana da lada gwargwadon aikin. Haka ma zunubi. Mun riga mun girma kowa yana da littafin ayyukansa. Amma hakan ba zai hana wadanda suka bada gudunmawar aikin ladan ko akasinsa samun rabonsu ba. To ka duba adadin matanka da 'ya'ya...baki dayanmu sai Allah Ya tambayeka game da amanarmu da Ya baka. Baka san rayuwar kowa a cikinmu ba balle ka san ko za ka iya fidda kanka a ranar. Ina jiye maka tsoron komawa ga Allah a wannan yanayin. Kada ka manta duk hawayen Innayo a lokutan da Zara da Uwani suka cusguna mata saboda sun koyi kinta daga wurinka sai Allah Ya saka mata. Kuma..."

Hannu ya daga ya dakatar da ita "ya isa haka! Ba dai Munzali bane ake maganar zuwa duba shi? Zani. A bani wuri na shirya."

A tsakar gida Asabe ta tari Innayo ta ce mata ta zo su tafi gidan Munzali tare. Tayin ya zo mata a bazata. Tabbas ta matsu ta san halin da Qibdiyya take ciki. Satar dan mutum harda baraza akan rayuwa da lafiyarsa abu ne mai ban tsoro. Sai dai sabanin amsa gayyatar da Asabe tayi mata sai ta girgiza kai.

"Ke da Alhaji kadai ya kamata ku je"

Asabe tayi turus tana kallonta kafin ta ce "ni wallahi na dauka mun fara shiri ashe ba haka yake a gun ki ba?"

Dariya ta so bawa Innayo sai ta buge da murmushi.

"Mun shirya mana Asabe. Bana son zuwana yasa Alhaji sake botsare mana a hanya ko a can. Gara ku tafi ku biyun ko a samu ya je yaga halin da dansa yake ciki.

Asabe bata wani gamsu ba. Hasali ma dai tunani ta shiga yi akan ko yadda take hango matsala haka Innayo din ita ma. Sai tayi saurin cewa,

"Kema kina hasashen akwai matsala a gidan ko? Nayi zaton sanin hakan ne ma zai sa ki biyomu domin jin mene ne yake faruwa."

"Ba ayi ciki domin abinci ba kadai. Ku biyun dai ya cancanta ku fara zuwa ku san damuwarsa. Wani sirrin tsakanin uwa da yaranta ko uba ba'a so ya ji. Zuwana zai iya zame muku karan tsaye. Fatana ki jiyo alkhairi irin wanda da kanki ma zaki zo ki bani labari".

BABI NA SHIRIN DA BIYU.

***

Baba Mari bata yi mamakin jin halin da Qibdiyya take ciki ba tunda Munzali ya riga ya fada mata. Yadda Zakiyya ta shiga damuwa ga Hanne duk ta tsorata yasa bata nuna musu ta sani ba, saboda gudun tambayar da bata san amsarta ba. Jikin Qibdiyya da Zakiyya ta so bude musu su gani ta hana. Yawan bude jikin babu alkhairi indai ba gyara zai kawo ba. Hakuri ta dinga basu a yayinda suke ta hasashen abin da ya faru har suka ji karuwar muryoyi a falon. Zakiyya kuwa da zafin nama ta fita da ta tantance ta Munzali a cikin wadanda suka shigo. Ganin ya shigo da wani matashi sai ta hadiye abin da ta so fada.

Fuskarta kawai ya kalla ya gane cewa ta san halin da Qibdiyya take ciki. Ba tare da yi mata magana ba ya gaishe da su Mal. Inuwa. Ya kuma sanar dasu cewa Abbati yana hanya. Tun shigowarsa gidan da yaga motar Buba ya fara tunanin akwai baki daga Kirikasamma. Sai kuwa maigadi ya tabbatar masa da hakan da ma su waye bakin. Kafin ya shiga ciki ya kira shi. Kin dauka ya yi kamar yadda ya yi hasashe, sai kawai ya tura masa sako. Shi kuma bai tashi dubawa ba ma sai da ya tsaya a danja.

Kansa ya sake daukar chaji. Wannan rana ta ki karewa tamkar ita ce ranar wankan da ake cewa ba a boyon cibi. Mika wuya kawai ya yi ga sarautar Allah tare da fatan nutsuwar zuciya ya ziyarce shi a duk sa'ilin da ya tuna wannan ranar a gaba.

Yana shiga harabar gidan ya hango Asabe da Alh. Rabi'u a tsaye suna magana. Ba shiri ya kashe motar ya fito a lokaci guda yana cewa su Mami su biyo shi. Ba don hankula a tashe suke ba da dukkaninsu sai sun yaba da tsarin gidan duk da kasancewarsu masu arziki.

Asabe na ganinsa ta tare shi da tambayar ko Qibdiyya ta dawo.

"Tana ciki na daukota"

Ajiyar zuciya ta saki sannan ta hau sababi da yiwa Shazali mugun fata.

"Abota da wannan la'anannen bata yi muku rana ba Abbati. Amma in sha Allahu yadda ya hanamu sukuni da ya sace Mariya sai ya riski bakincikin da ya ninka namu sau dari"

"Sata? Me yake faruwa ne Abbati?"

Mami Khadija ce tayi magana tana mai yi masa kallon tuhuma. Indai sace Qibdiyya aka yi ai babu mamaki a can aka bata mata rayuwa. A matsayinta na uwa, duk da satar mutum ba abin so bane amma a gareta kofa ce da danta zai iya tsira daga zargin da ake yi masa.

Kallon rashin sani Asabe tayi mata ya hada amsoshin ga baki daya ya basu a jumla guda.

"Mu shiga ciki sai a warware komai da yardar Allah"

Alh. Rabi'u wanda ya kosa da tsayuwar tasu amma tasirin kalaman 'ya'yan Innayo ya hana shi ya magantu ya ce "wanne ne bangaren naka? Maigadinku ya ce duka suna can."

Da hannu ya nuna musu tare da basu hanya su fara yin gaba. Jikin motar ya koma domin taimakawa Suhaib tunda da akwai matattakala kafin a shiga kowane sashe sai yaga Farha ta dawo za ta zauna.

"Muje mana" ya ce bayan Suhaib ya dafa kafadarsa.

"Zan jira ku a nan" ita ce amsar da ta bayar tana dan daure fuska.

Bata son bashi damar ya ce dole sai ta shiga. Ai sam bata ga tsari a shigar masa gida ba alhalin akwai abu a tsakaninsu sannan matarsa da iyayensa kamar yadda taji maigadi na fada masa suna ciki. Gabanta har wani faduwa ya dinga yi saboda tsoron kada Mami ta ce sai ta shiga dole.

Ji ya yi baya son barinta a wurin ya sake bude baki zai yi magana sai Suhaib ya yi belinta don ya gano inda ta dosa.

"Zai dai fi ta jira a wajen"

Kai Abbati ya gyada na fahimta. Ya so ya kalleta su hada ido sai yaji nauyinta ya sake rufar masa. Lallai wutsiyar rakumi tayi nesa da kasa.

Da taimakonsa Suhaib ya shiga falon. Sun sami kowa a zazzaune ana gaisawa. Ganin Baaba Mari a falon ya taimaka wurin ragewa Mami Khadija zulumi. Don ma dukkaninsu babu mai kwanciyar hankalin tsawaita hira sabanin haduwarsu ta farko. Bayan gaisuwar ta tsahirta ne Abbati ya gabatarwa da Mami Khadija da duka wadanda suke wurin.

Zuciyarta kuwa ta tsinke cikin fargabar abin da zai iya samun Lilu. Da ya kula da sanyin da tayi sai ya ce "Mami wallahi ba na tsoron komai don ban aikata ba" iya jinta ita kadai.

Jinjina kai tayi a hankali cikin zuciyarta tana rokon Allah da neman tsarinSa akan wannan musiba da ta tunkaro su. Kwarin gwiwar da yawan jama'ar da suka gani a gidan yasa ta kusa rasawa ne ya dawo mata.

***

Maigadi na shiga bandaki Daddy da Umman Zakiyya suka turo karamar kofar gate din suka shigo. Umman tasu afujajan take tafe da zaninta a hannu ga hawaye ya jike mata fuska. Gidan Munzali suka nufa sai Farha dake cikin mota taga rashin dacewar barinsu su tafi bayan Maigadin ya fadi inda jama'ar gidan suke. Kafin su karasa ta bude motar ta fita ta dan daga murya yadda zasu ji.

"Suna wancan gidan" ta fada tare da nuna inda su Mami suka shiga da Abbati.

Umma ta dawo da sauri ta ce "don Allah rakani baiwar Allah."

"Wancan kofar ce" Farha ta furta da sauri don bata son shiga.

Daddy ya dubeta da shanyayyun idanunsa na 'yan duniya ya ce "ki taimaka ki rakata zan koma in shigo da mota naga maigadin ya fito"

Yawu Farha ta hadiya ta kalli gate din. Tabbas maigadin ta gano yana yiwa dan saurayin da bai fi Lilu ba inkiya da ya zo zai bude masa gate. A gefe guda Umma Lami ta cigaba da sharar hawaye. Ba yadda ta iya dole ta taka kafafunta inda take ganin kamar bai kamata ta je ba. Shi kuma Daddy da yake bai san me ya faru ba ga kyakkyawar fuskar Farha da ta hargitsa tunaninsa tuni ya shigo da motar ya take musu baya. Umma cewa tayi babu lafiya a gidan Munzali. Tunda bai manta yanayin da suka riski gidan da ya kai Zakiyya ba sai bai alakanta abin da barnar da ya aikata ba.

***

"Mu baka fada mana su waye bakin ba."

Alh. Rabi'u ne ya yi tambayar yana mai yiwa Mami kallon kurilla.

Tashi tsaye Abbati yayi ya ce masa "Munzali zai yi muku cikakken bayani" sannan ya yiwa Hanne da iyayensa nuni da kofar dakin da suka fito "mu shiga ciki mu basu wuri."

Wani irin abu mara fasali ne ya sami damar tokare wuyan Munzali da jin furucin Abbati. Gwiwa a sake yana jin jiri na dibarsa ya sami wuri a kusa da Suhaib ya zauna. Falon baki dayansa daga iyayensa har na Abbatin suka shiga cikin rudani. Ba don komai ba kuwa sai kasancewar ba a taba ji ko ganin gilmawar wani abu makamancin wannan a tsakaninsu ba. Ko sallamar su Farha babu wanda ya ji sai idanu da aka kafe Abbati da Munzali dasu.

"Da me kake so naji Abbati?" Munzali ya dago kai yana dubansa ya yi masa tambayar a zuciye.

"Da abin da ka ke jin kai kadai Allah Ya bawa wuyan dauka mana" shi ma ya mayar masa da amsa cikin fushi.

Dama ya san dole ran Abbati ya baci. Amma bai yi zaton abin ya yi masa zafin da zai tona musu asiri a gaban kowa ba. Muryarsa yaji ta karye, kuka na barazanar kwace masa. Idan Abbati ya fita daga rayuwarsa tabbas rayuwarsa za ta tawaya. Rabuwarsu bata da muhalli a kowace mahanga ya dube ta.

Tashi ya yi ya karasa har inda Abbati yake tsaye ya ce "A waje na b'ata maka rai, don me za ka kawo maganar gaban iyayenmu?"

"Saboda su shaida cewa ..."

Katse shi ya yi kafin ya kai karshe ya ce "kalamaina kuskure ne kuma kai ma ka sani. Ashe ban kai matsayin da za ka yafe min idan nayi maka laifi ko da ban baka hakuri ba?"

Yadda murya da yanayin Munzali suka sauya a lokacin da ya yiwa Abbati wannan tambaya sai da ya sanya kwalla zuwa idanun duka matan wurin. Harda Asabe kuwa domin jikinsa ya nuna asalin sallamawa ga abin da yake neman fin karfinsa.

Gorin haihuwa akwai ciwo. Takalmin wanda bai haihu ba baya taba yiwa wanda ya haifa daidai. Shi yasa fahimtar halin da zukatansu suke shiga a lokacin da aka goranta musu yake da matukar wahala. Ciwon yana ninkuwa ne a yayinda gorin ya fito daga bakin wanda kake tunanin matsalarka tashi ce. Shi yasa duk dauriya irin ta Abbati ya kasa hakura. Wani kuskuren yinsa ma babban kuskure ne!

"Fadin abin da yake zuciyarka ba shi ne laifin ba. Zuciyata ta kasa nutsuwa da tunanin kila na saba yi maka wasu abubuwan da suke sa kayi tunanin don ban haifa bane nake aikatasu."

Magana Mal. Inuwa ya so yi sai Mal. Sa'idu ya hanashi. Ya kuma nunawa kowa alama da hannu akan kada su shiga wannan rigimar. Baaba Mari kwalla kawai ta dinga sharewa. Tsaftatacciyar alaka ma ba a rabata da sharin shaidanu daga aljanu da mutane balle kuma tasu. Tausayi suka kara bata ta kuma godewa Allah da bata gaggauta rabasu kamar yadda tayi niyya ba. Maganar da Munzali ya yi a wannan gabar wadda ta tab'a zukatansu ita tayi sanadiyar dawo da zaman na abin da aka yi dominsa tun farko.

Da idanuwansa wadanda suka kada kamar garwashi ya dubesu ya ce "bani da wata kalmar kare kai ko ban hakuri da zan fada maka. Idanuna ne suka rufe dazu har nake ganin kamar ciwon da nake ji baka jin irinsa shi yasa ka kasa fahimta ta. Sai yanzu na gane cewa a cikin komai akwai hikimar Ubangiji. Ya bani haihuwa amma bana cikin mutane masu bin komai cikin lumana domin samun maslaha musamman akan abin da ya shafi wadanda nake so. Sai Ya hadani da kai. Ya baka nutsuwa da hangen nesa domin ka nuna min hanya idan na makance. Abbati wannan bai isheka

dalilin yafe min ba? In kuma ba za ka yafe ba ai ka san cewa baka da ikon rabani dasu Baaba. Saboda haka duk abin da ya shafi Qibdiyya dole ne su sani."

Kallo sai ya koma kan Abbati. Murmushi ya soma yi wanda yake tafe da dariyar farinciki. Ba yace ga kalmar da ta haska masa zuciya ba a zantukan Munzali. Ya dai san kawai komai ya wuce har kasan zuciyarsa.

"Baka ce komai ba?" Munzali ya tsokane shi shima yana dariya.

Hankalin kowa sai ya kwanta har nutsuwa ta maye gurbin tension din da ya gauraye da iskar falon.

Kujerar da Munzali yake shi ma Abbati ya zauna suka saka Suhaib a tsakiya. Da Abbati zai fara yi musu bayani sai murmushin fuskarsa ya bace sai damuwa da alhini.

"Jarabawa ce Allah Ya dora mana irin wadda bamu taba tsammani ba ko a mafarki. An wayi gari an sami wani mara tsoron Allah ya raba Qibdiyya da mutumcinta."

Da wanda ya sani da wanda ya sami labari yanzu baki dayansu sai da suka ambaci kalmar Innalillahi wa inna ilaihi raji'un!

Gumi kamar ruwa a take ya fesowa Daddy. Cikinsa ya kulle yayinda ya fara tunanin hanyar gudu. Yadda yake rarraba idanu yana cilla kai kamar kadangare ne ya dauki hankalin Farha. Ita da shi daga bakin kofa dama suka tsaya. Abbati ne bata son ya ganta shi kuma mara kunyar karyar Munzali yake gudu saboda karonsu na dazu.

Duk wata alama ta rashin gaskiya da firgici ta nuna kanta a tattare dashi. Wannan yasa Farha taji wani abu ya darsu a ranta. Suna jin an fara tambayar waye ya yi sai taga ya juyo da sauri da nufin fita. Ta kalle shi ta tabbatar bata yi kuskuren ganin tashin hankali mara misaltuwa a tare da shi ba. Alamun rashin gaskiya sun dabaibaye fuskarsa ta yadda mutum ba zai fassara tashin hankalinsa da damuwa akan yarinya ba kadai. Ba tare da dogon tunani ba kawai tayi shahada tayi abin da

zuciyarta ta raya mata. Qibdiyya ta kwallawa kira wanda hakan ya yi sanadiyar da kowa ya kallo bakin kofar.

Qibdiyya dake zaune a jikin Zakiyya daga kai tayi ta hango mai kiran da na kusa da ita. Nan da nan tayi mummunar razana. Farha ta dad'a samun yakini akan zarginta. Daddy bai yi aune ba tayi saurin rufo kofar ta rike hannun taki matsawa. Ai da ya fahimci me tayi bai san lokacin da ya yi wasu kwararan taku biyu ya isketa ba.

A wajen Qibdiyya zaman da akayi da zantukan da suke yi babu wanda ta fahimta. Abu daya ne ta sani shi ne yawan tambayar da aka dinga yi mata akan abin da yake mata. Shi yasa tana hango shi ta soma kuka tana cewa

"Ban fada ba Uncle Daddy. Don Allah kada ka yanka min Mummy da Daddy da Papa" ta dubi Munzali wanda ya yi mutuwar zaune da idanuwanta wadanda suke nuni da jigatar da tayi daga jiya zuwa yau ta ce "Daddy kaima ai ban fada maka ba ko? Kaima haka ko Papa" ta kare tana duban Abbati.

"Baki fada ba Mamana" Abbati ya amsa da kyar don magana ma baya son yi. Shi da Munzali da Lilu da uwar gayya Zakiyya duk kofar suka nufo cikin sauri.

Daddy yasa karfinsa zai ture Farha ya fita ita kuma taki sakin hannun kofar.

"Ki bani wuri kafin nayi miki lahani"

Ya yi maganar a fusace yana mai dunkule hannu zai kai mata naushi a inda ya san za ta wahala. Jikinsa ko ta ina rawa yake saboda tsoro. Fuskarsa duk ta canza ta rikice da fargaba. Amma ko gezau taki saki. Tunda Allah Ya kubutar mata da kani tana jin abu na karshe da za ta yi shi ne bayar da gudunmawar kama ainihin mai laifin.

Hannun nasa ya kusa sauka a cikinta don har ta runtse idanu taji shiru. Tana bude ido taga Abbati ne ya rike hannun naushin. Munzali kuma ya sauke masa wani wawan mari wanda sautinsa ya karade falon. Yayinda Lilu ya janyeta zuwa gefe.

Zakiyya kuwa da babu wanda ya kula kujerar dinning table ta kinkimo. Munzali na sauke hannunsa ta rotsawa Daddy kujerar a kansa. Ta gaban kansa inda ya tara wata uwar suma a dukunkune kamar mahaukaci sabon kamu ya dinga tsarto da jini. Durkushewar da yayi da jinin dake zuba basu sa taji sassauci ko digo a ranta ba. Shi yasa ya sake daga kujerar za ta kuma buga masa.

"Kada ki yi kisa 'yar nan. Ki bari a bi komai cikin lumana"

Ashar ta debo za ta saukewa mai ambaton lumana bayan abin da aka yiwa gudan jininta sai tayi ido hudu da Mal. Inuwa. Albarkacin furfura da yaci yasa ta saki kujerar ta kara fashewa da kuka. Ganin yadda falon ya koma da sauri Baaba Mari ta dauke Qibdiyya ta koma dakin da suka fito.

Duk wannan abin da akeyi ashe Lami suma tayi tun yunkurin Daddy na farko wurin fita. Mami Khadija tana tsakar godiya ga Allah da Ya wanke mata d'a tun kafin ayi nisa ce ta fara lura saboda a kusa da ita take zaune. Kanta ta gani ya langabe gefe guda ta rufe idanu. Da hanzari ta tabo Asabe wadda daga gani ta fahimci 'yan uwa ne saboda kamanninsu. Ita kuma da kuka ta hau ihu tana kiran sunan kanwarta.

Da kyar aka samu ta dawo hayyacinta. Tana bude ido ta yunkuro ta zauna kowa yana yi mata sannu. Mutum guda ta nema da ido tayi sa'ar gani, wato Zakiyya. Ta isketa tayi kuka har ta gaji. Fuskar nan ta cabe da hawaye da majina.

"Matso" ta kirata da hannu.

Zakiyya na matsowa kuwa ta cire hannu ta tsinketa da mari.

"Baki da hankali ne Lami?" Asabe ta furta da mamakin wannan hukunci "ga wanda za ki mara can fa" ta nuna Daddy a zaune a kan kafet da jini a fuska.

"Ita zan mara Yaya Asabe. Zakiyya zan fara hukuntawa domin ita ce silar komai."

"Umma ni kuma?" Zakiyya

Mami Khadija na jin haka sai ta mike. Duka 'ya'yanta ma suka tashi. Baaba Mari ma ta ce da Hanne ta samo abinci ta biyota ciki a bawa Qibdiyya.

Umma Lami ta gyara zama ta hanyar sauko da kafafuwanta daga kan kujera ta ce "ina za ku? In kowa zai fita ke Hanne da wannan budurwar..." Ta nuna Farha "ku dawo ku zauna. Abin da zan fada zai iya amfanarku tunda baku wuce shekarun haihuwa ba". Ko ba a fada ba a kallon fuska kawai mutum zai karanto ciwon da yake cin zuciyar dattijuwar nan.

"Zakiyya kin cuceni kin cuci kaninki da 'yar cikinki. Komai lalacewar dan iska a kullum yana kokarin yin abinsa ne a nesa da gida. Ma'ana cikin gidansu ko inda idon sani zai iya gani. Amma yau a dalilin sakacinki irin wannan kwad'on mara dadin ambato ya faru a tsakanin zuri'ata"

Hakuri 'yan dattijan suka dinga bata ta girgiza kai tana cije baki.

"Gado ne kadai Allah bai shardanta tsakanin Daddy da Qibdiyya ba. Banda shi duk wani hukuncin da ya hau wuyan mahaifinta na halacci da haramci shi ma yana kansa. Wane irin hakuri zan yi? Wallahi da ganin irin wannan bakar rana gara ace mijina na kama da mace akan gadona."

Mami Khadija taji gabanta ya fadi domin kalaman karshen sun ratsa ko ina a jikinta. Ji tayi kamar da ita matar nan take.

Zakiyya kuwa cikin kuka ta ce da maihafiyarta "Mene ne laifina Umma? Ta yaya bacin rayuwar Qibdiyya zai zama laifina alhalin ni ba mazinaciya bace?"

Numfashi mai tafe da zazzafar iska mara dadi Umma Lami tayi fashin baki akan bakincikin da ya sark'esu muddin rai.

"Zakiyya kowane bawa bai isa ya tsallake kaddararsa ba ni na san wannan. Na kuma yarda kaddarar yarinyar nan kenan. Matsalar shi ne ke kika zama silar tabbatuwar kaddarar. Akan mutuwar aurenki kin zo kin ce Munzali yana yi miki boye-boye. Don kin matsa da tambaya ya koroki gida. Amma ni nafi tunanin shegiyar kyuya da gandarki ce ta kashe miki aure. Babu abin da yake kayatar dake sama da danna waya, kallo da bacci. Sau nawa Qibdiyya za ta dinga kwala miki kira daga bandaki kiyi ta jera mata ina zuwa akan uzurin banza? Ko kin manta ranar da kika bari har bayangida ya soma bushewa a jikinta saboda bana nan. Sai da na shigo nace miki zai maidota gidan ubanta?"

"Naji ban kyauta ba amma Umma meye hadin laifina da abin da Daddy yayi?"

"Son zuciya. Yawan fadan da nake yi miki sai ki ka mika masa matsayinki na uwa. Daga bata abinci aka koma cire uniform da sakawa (bata san idan bata gida harda tsarki da wanka Zakiyya take saka shi ba). Ko shi ya kawota duniya ai akwai abubuwan da basu dace uba ya yiwa diya mace ba. Kuna son haihuwa amma ba kwa jure raino. Da yawan matan da irin haka yake faruwa da yaransu idan an bi sila baya rasa nasaba da sakaci ko yaya ne (Ban ce duka ba! Mau'du'in labarinmu yana magana ne akan sakacin). Muna cikin zamanin da uba mahaifi yake iya ajiye mutumcinsa ya taki tsatsonsa mace ko namiji. Kinga kuwa halin ko in kula ba na uwa bane. Sai kin yi da dukkan gabbanki ki kuma hada da tsananta addu'a wadda bana jin ke kina ma tunawa da cewa ya kamata ki dinga yiwa 'yarki. A soyayyar baki da daukarta a hoto ki ka fi kauri."

Dukar da kai Zakiyya tayi yayinda kukanta ya kara tsananta. Tabbas mahaifiyarta ta fadi gaskiya. Kuma ita shaida ce cewa indai ta gani sai tayi mata fada akai.

"Baki yi mana adalci ba Zakiyya. Abu irin wannan ya faru amma na rasa kukan me zan yi? Sannan ina ji ina gani dole in cigaba da kwana gida daya da wanda ya yiwa jikata haka tunda nice uwa a gare shi. Duk bacin ran da zan shiga ba zan iya korar shi daga gida ba kada yafi haka lalacewa."

Maganganun Umma Lami sun bawa kowa tausayi harda masu kuka. Musamman Farha da Hanne wadda ta kara tsorata da sharrin kyuya. Daga nan iyayen suka saka baki aka jajantawa juna.

Wadannan zantuka musamman na Umma sun tsayawa Munzali kwarai a zuci. Kansa ya kara dorawa laifin abin da ya faru. Ya kuma gaskata cewa lallai bawa bai isa ya yiwa Mahaliccinsa wayo ba. A lokacin da rayuwa take gara musu, suna tsaka da samun kudi kamar ruwan sama ya aureta bisa umarnin Asabe. Na farko babu soyayya sannan sam aure baya gabansa. Saboda haka ba shi da lokacinta. Tun tana kuka da korafi har ta saba. Waya da tv suka zama abokan hirarta. Ga masu aiki har biyu ya dauko sannan ga kudi baya yankewa. So ya yi ya dauke mata hankali da jindadin duniya. Sai dai bata jima ba cikin rayuwar ba-cas-ba-as ta gaji ta sake kafa masa kahon zuka. Shi ne dalilin sakin. To ashe da wannan sabon na rayuwar da ya koya mata ta tafi. Gashi 'yarsa ce ta kwana a ciki. Shi yasa da ya kalleta yaga yadda take zubar da hawaye ta bashi tausayi.

Kallonsa ya mayar ga Daddy ya hadiyi yawu da kyar.

"Tsakaninka da Allah tun yaushe ka fara bata Qibdiyya?"

Amsar tambayar famin ciwo zata zama shi yasa Abbati ya nemi dakatar dashi.

"Munzali.."

Runtse ido Munzali ya yi ya gyada kai alamun ya hakura da tambayar sai ya canja wata "Me yasa sai ita? Ya aka yi ka iya keta haddin yarinyar da idan kaf matan duniya sun kare ba za ta taba halatta a gareka ba."

"Ku yafe min" ita ce kadai amsar da ya iya hadawa da busassun labbansa.

"Kada ka yaudari kanka. Duk fadin duniya babu wanda ya isa ya yafe maka a madadin Qibdiyya. Ka roki Allah tsahon kwana domin ka roketa da kanka."

Daga wannan bai sake cewa komai ba ya tashi ya bawa su Mami hakuri sannan ya fita daga bangaren. Sam zuciyarsa babu dadi. Yana son ya hada Daddy da hukuma a sauya masa kamanni amma cikin ransa yana jin kamar bai cancanci yin haka ba. A matsayinsa na uban Qibdiyya wanda jirwayen kazantar rayuwarsa yabi 'yarsa ina shi ina ganin laifin wani?

Gwiwoyi a sake Umma da Zakiyya suka tashi zasu tafi. Baaba Mari ta riko hannun Qibdiyya ta damkawa Zakiyya tare da cewa,

"Ki tafi da ita domin yau tafi bukatarki akan kullum"

Da zasu fita ne Qibdiyya ta ce "Papa ina wayar da na baka?"

"Subhanallah" ya furta da sauri don shaf ya manta ta bashi waya ta ce ya kira. Aljihunsa ya laluba ya daukota ya kunna. Cikin sa'a ya samu akwai chaji. Ya duba wurin sunaye yaga 'Alhajina' da wannan ya yi tunanin ko waye kila yana da alaka da mai wayar sai ya kira.

BABI NA ASHIRIN DA UKU.

Da shigar kiran ko dan sautin nan na alamun ta shiga da mutum yake ji idan tana ringing bai kare ba aka dauka.

"Abdul?" Abbati ya ji an ambata da muryar da ake iya gane tana cikin tsananin tashin hankali.

"Ba Abdul bane. Na sami..."

Katse shi Alh. Sadisu ya yi cikin matsanancin bacin rai ya ce "Waye kai? Ina dana? Wallahi duk inda kuke a kasar nan sai an nemo min ku"

Duk inda aka yi shi ma dansa Shazali ya dauka, Abbati ya ayyana a ransa. Tunanin hakan yasa shi kashe wayar ya duka a gaban Qibdiyya ya ce ta fada masa a yanayin da ta baro mai wayar cikin dabara.

"A gidan da Uncle dinnan ya kaini na ganshi. Kuma har ya daukoni zai kawoni gida. Sai Uncle dinnan ya buga masa kai da bango ya yi jini. Sai ya bani ya ce ka kira Daddy dinsa a zo a dauke shi."

Tiryan tiryan ta fada kowa yana ji. Cikin kuka Zakiyya ta roki Abbati da ya fada mata tsakani da Allah me yake faruwa. Ita tunda basu mayar da Qibdiyya gida ba ta san akwai matsala.

Kansa sake daukar chaji yayi. Ya waiga babu Munzali a wajen. Ya dubi su Mami wadanda sai yanzu da hankalinsa ya daidaita ya tuna gamuwarsa da Alh. Tahir. Yawu ya hadiya ya fadi iya abin da zai iya.

"Abokinmu Shazali ne ya dauketa jiya domin ya yi mana barazana ni da Munzali. Daga inda na karbota nake shi yasa ma ku ka ganni haka" ya nuna suturarsa wadda bai san tuni kowa yake tunanin inda yaje aka yamutsasu haka harda yagewa ta wuya ba "Sauran bayanin sai na dawo. Da alama ba ita kadai ya dauka ba."

Wayar da tunda ya katse take faman ruri ya dauka tare da bayar da hakuri.

"Na tsaya neman bayani ne game da mai wayar don ban san shi ba. Ka fada min inda zamu hadu domin zancen ba na waya bane"

"Dole ka ce ba na waya bane mana don kada ayi tracing dinku. Idan kudi ne ka fadi ko nawa kuke so a wuce wurin." Alh. Sadisu ya kare magana cikin fushi yana bubbuga kafarsa daya a kasa. Babu nutsuwa ko kusa a tare dashi. Duk sakan guda gani yake kamar zai rasa dansa har abada.

Shi kuwa Abbati da ya tuna yadda yaji kafin ya dawo gida da Qibdiyya sai ya yi masa uzuri.

"Kayi hakuri. Idan na zo zan yi maka bayani gwargadon abin da na sani."

Wayar a speaker take dama saboda 'yan sanda da suke wurin. Saboda haka da rad'a da inkiya da komai na kwatance suka nunawa Alh. Sadisu abin da suke bukata ya yi. Ya kuwa fada yadda suke so din.

"Ka same ni a gate din makarantarsu Abdul."

"Ina ne?"

"Kada ka nemi ka raina min hankali mana.."

Wani dan sanda ya sake yi masa alama da hannu. Ba don ya so ba ya fadi sunan makarantar da unguwar da take.

Kallon iyayensa da duk wadanda suke wurin Abbati ya yi ya ce,

"Zan je na sami mahaifin yaron"

Mal. Sa'idu ya dube shi da damuwa a fuskarsa ya ce "anya ayi haka kuwa? Daga yanayin maganarku naga kamar kai yake zargi"

"Babu komai in sha Allahu. Bari na canja kaya na je"

Mami Khadija ya sake bawa hakuri da Lilu. Suka yi musabaha da shi da Suhaib sannan suka ce masa zasu koma gida.

"Za ku gane hanya kuwa? Ko za ki biyoni a baya na kai ku sai na wuce daga can?" Ya yi maganar yana duban Farha.

Mami tayi la'akari da halin da ake ciki ta ce "Kada mu wahalar da kai. Idan mun bace hanya zamu kira gidan. Allah Ya rufa asiri Ya kare gaba".

"Babu wata wahala. Makarantar a hanyar take. Sai ma mun wuceta kafin mu karasa gidan"

Baaba Mari ta saka baki ta ce su amince su bishi. Idan ya fadawa mutumin abin da ya sani sai su wuce. Bai kamata a barsu su tafi bayan abin da ya faru ba.

Haka kuwa aka yi. Cikin minti goma Abbati ya kimtsa ya sauko suka tafi. Bai nemi Munzali ba saboda ya san a yau zuciyarsa ko kusa babu dadi. Lilu ne yake jan motar. Farha na gaba su Mami da Suhaib na baya.

Kafin su isa Alh. Sadisu ya kira Abbati yafi a kirga. Wani ya dauka ya ce su yi hakuri yana hanya, wani zubin ya share saboda ransa ya fara baci. Suna isa ya hango motocin 'yan sanda fal a gate din makarantar. A ransa ya ce dan wani babba ne Shazali ya tabo. Wuri ya samu ya yi parking su Lilu ma suka yi a bayansa a waje.

Yana fitowa aka sake kira. Ya kara wayar kenan a kunnensa daga bakin gate din kawai yaga 'yan sanda sun yi masa da'ira. Kafin ya gama sanin me yake faruwa sun fara dukansa. Cikin abin da bai wuce kifta ido da budewa ba suka tura shi cikin motarsu.

Farha bata san lokacin da ta fito daga tasu motar ba da aka fara dukan shi. Lilu ma ya biyota. Haka Mami Suhaib daga baya. Mami ta rasa da wane suna za ta yiwa wannan rana lakabi. Kafin su iso motar da aka saka Abbati tuni tayi gaba. Sauran ne a baya. Farha kuka kawai ta fashe dashi. Lilu ya tsayar da daya daga cikin motocin yana yi musu bayani cewa ba Abbati ne ya dauke yaron ba.

"Yaro ka kama bakinka ko kai ma a tafi da kai wallahi." Wanda ya bashi amsa ya kallo gate din ya ce da direbansu "ga Alhajin nan ya fito muje"

Su Mami suka juya a tare. Alh. Sadisu ne ya fito yana tafiya da sauri kamar zai tashi sama. Ga 'yan kazanginsa da securities da malaman makarantar suna biye dashi a baya.

Kwakkwaran kallo guda Mami tayi masa ta kara sauri tun kafin ya shige motar da aka riga aka bude masa.

"Alh. Sadisu?"

"Don Allah ku rabu dani" ya amsa a fusace don ya gaji da amsa mutane. Burinsa ya gan shi a station din da aka kai mutumin da ya kira shi a waya.

Da ta fahimci da wuya idan zai juyo balle ya kalleta ne ta kara da cewa "Alhaji Khadija ce, Maman Suhaib"

Ai kuwa da saurinsa ya leko kansa ta taga.

"Hajiya Khadija me kike yi a nan?" Ya yi wa direbansa alama da su tafi yana cewa da ita "Za dai mu yi magana daga baya, yanzu ina cikin tashin hankali ne wallahi"

Da sauri ta ce "na sani.Abdul aka dauke ko? Manemin 'yarka ne aka kama yanzu. Ba shi ne ya dauke shi ba"

Kallonta ya yi a tsanake sannan sautin Innalillahi da Farha take ta ambato cikin hawaye ya soma shiga kunnens.

"A mota kuke?"

"Eh"

"To ku biyo mu don Allah."

Suna shiga mota tasa Suhaib ya kira mata Munzali. Ita da kanta tayi masa magana ta kuma umarce shi da ya boyewa su Baaba Mari kafin a san me yake faruwa. Sai

dai tuni hankulan iyayen ya tashi tunda ya amsa wayar ne a gabansu. Suna gama wayar suka nemi jin ba'asi. A dole ya sanar dasu. Haka suka tashi babu wanda ko ruwa ya shiga bakinsa tun zuwansu suka bishi.

A hanya ya kira Alh. Tahir. Yana can gidan Comared har lokacin bai tafi ba. Ya yi bakincikin rashin zuwa da direba gidan saboda har yanzu babu kuzarin tuka mota a tare dashi. Kansa ya rufe ruf ya rasa zaren kamawa tun tafiyar Abbati.

Da yaji kira kamar ba zai dauka ba yadda ya yiwa sauran kiran da suke ta shigo masa. Sunan mai kiran da ya gani ne ya sauya masa tunani. Abokinsa ne da suka hadu ta dalilin ayyukan kwangila. Duk zafin zuciya da kwarjinin da Alh. Sadisu yake yiwa mutane sai tasu tazo daya dashi. Har ta kai suna ziyartar juna a gida.

"Alhaji kaji labarin na shigo Kano ne?" Ya ce da kokarin kawo raha tsakaninsu.

"Kana ina Alh. Tahir? Don Allah duk inda kake ka taho police station din Gadon K'aya. Akwai matsala an sace Abdul kuma muna tare da iyalinka Haj. Khadija."

Satar Abdul din da yaji ta firgita shi. Sai dai ko kusa bata kai kidimar da ya shiga da yaji sunan Mami ba. Ya nemi jin cikakken bayani amma shi ma Alh. Sadisun bashi da abin cewa.

Mukullin motarsa da waya kadai ya dauko ko hula da babbar rigar da ya cire bai tuna ba ya fito. A harabar gidan ya tarar da Comared da Shazali kowa rai a bace suna ta musayar yawu. Comared ya dora masa laifin duk abin da ya faru shi kuma Shazali yana cewa ba zai fita ba sai an bashi kudin da aka alkawarta masa ko ya baza sirrinsu a ahafukan sada zumunta.

"Kai karamin kwaro ne Shazali. Karyar rashin mutumci kake shi yasa har ka sami kwarin gwiwar mayar min da magana. Harma da barazana. Amma yanzu zan tuna maka waye ubangidan kuma waye bawa."

Kira ya kwala da karfi wasu garadan maza biyu suka fito ya umarcesu da su kulle masa Shazali a store din gidan. Da yake jikinsa ya riga ya yi tsami saboda dukan da Abbati ya yi masa sai ya kasa kwatar kansa. Alh. Tahir yana gani aka ciccibe shi aka yi ciki dashi. Da Comared ya nemi jin ina zai je da sauri haka kin fada ya so yi. Sai kuma ya tuna cewa ta dalilinsa ya hadu da Alh. Sadisu. A takaice ma dai yana cikin yaransa na hannun dama. Saboda haka babu bata lokaci ya zayyane masa iyakar abin da yaji daga bakin Alh. Sadisun. Comared ko cikin gidan bai koma ba ya kira direbansa suka tafi tare.

***

Kafin su Alh. Sadisu su iso har an fara dukan Abbati a cell. Lokacin ya daina kokarin kare kansa daga zargin da ake yi masa balle dukan. Irin tunanin Munzali wanda yake ta kwabarsa a kai ne ya shige shi. Kokwonto da tsoron ko tubansu bai karbu ba shi yasa da an toshe kofa daya sai wata daban ta bude ta bakin ciki.

Ba su suka sarara masa ba sai da wani ya leko ya yi musu magana.

"Kai Sergent, ku taho da shi ofishin DPO yanzun nan ana jira"

Suna jin haka sun san cewa Alh. Sadisu ma ya iso. Jiki na rawa saboda kwadayin samun wani abu suka fito. Dukan da suka yi masa ma dama don su burge shi ne in yaji dadi ya yi musu ihsani.

Hankada shi su ka yi har ciki. Tausayinsa ya sake tsirga zuciyar Farha da taga yadda ya koma cikin kankanin lokaci. Fita taji tana son yi daga office din saboda ba za ta iya jurar kallon sa a a cikin wannan yanayin ba. Tana share hawaye suka hada ido sai ya yi murmushi yana yi mata alama da ta bar kuka.

Bai ankara ba yaji an kai masa wata mahaukaciyar a wuya. Yana kici-kicin kwacewa sai saukar duka a gefen idonsa. Farha ta sake saka kuka yayimda Lilu da DPO suke kicikicin kwace Abbati daga hannun Alh. Sadisu wanda yake ta ihun a fito masa da dansa.

Da kyar bayan an rabasu DPO din ya ce da Abbati "Malam ina mai baka shawara da kada ka wahalar da kan ka da mu ka fada min yadda aka yi ka dauke dan Alh. Sadisu da dalilinka na daukarsa"

Zai fara bayar da amsa su Munzali suka shigo suka same su. Hankalinsa ya kara tashi da yaga yadda aka sab'a masa kamanni a lokacin. Wannan abu fa a dalilin dawo da 'yarsa ya same shi. Shi kadai yaga ribar zama da Abbati yayinda Abbatin yake shiga tarin matsaloli tun farkon haduwarsu. Baaba Mari da Mal. Inuwa suka rasa abin cewa saboda tsananin tashin hankali. Mal. Sa'idu ne ya hau bayanin cewa dansa ba zai taba cutar da wani ba balle a kai ga sace shi.

DPO ya tambayi matsayinsu tare da yiwa Sergent din da ya shigo dasu fadan cika mutane a wurin. Jin cewa iyayen wanda suke tuhuma ne sai ya ce lallai a ragu. Office din ya rage daga Alh. Sadisu sai Mal. Inuwa, Munzali (a matsayin mahaifin yarinyar da ta kawo waya) da Abbati. Su Baaba Mari, Hanne da Mami Khadija da su Asabe duka suka koma reception. Mal. Sa'idu kuwa jinjina kai ya dinga yi. Duk takamarsa akan 'ya'yan 'yan uwansa yana ji yana gani DPO ya ce ainihin mahaifin Abbati kadai ake bukata. Wannan ya kara karya lagonsa da yaga ko kara babu Mal. Inuwa ya ce shi ne uban.

Shi Abbati Allah kadai Ya san irin ciwon da kansa, jiki da ruhi suke yi masa a wannan lokacin. Idonsa daya har ya tara jini don ya kasa bude shi sosai. Ya daure ya fada musu iya abin da ya sani

DPO ya bubbuga kan bironsa akan tebur ya sake yi masa wata tambayar.

"To kai me yasa ya dauki taka 'yar? Sannan ina ya kaita har ta hadu da Abdul?"

"Ban san inda ya kaisu ba. Kamar yadda na fada maka ya yi amfani ne da abotarmu ya tafi da ita daga hannun kakarta a asibiti." Abbati ya amsa masa cikin wani irin yanayi na kosawa da komai.

"Wannan bayanin naka bana jin ko alkali ka fadawa zai karbi uzurinka balle ni."

Munzali ya galla wa DPO din harara ya ce "Karya kake so ya yi maka ko me?"

"Kaga DPO a mayar dashi cell mana a dauko Shazali din" Alh. Sadisu ya fada ganin lokaci na tafiya an kasa cimma matsaya guda "idan wani abu ya sami d'ana ku ma da kuke ta jan kafa ba tsira zaku yi ba" ya kare magana yana tashi tsaye. Fita ya yi da waya a hannu yana waya wadda da alama da wani babba cikin 'yan sanda.

DPO din da kansa ya taso Abbati a gaba zai mayar dashi cell. Suna fitowa duka jama'ar da ya zata sun fita waje suka taso lokaci guda. Kowannensu da irin tambayar da yake jefowa domin son jin ko ya kubuta ne.

"Naga alama kana da tarin masoya" cewar DPO ya mayar da hankalinsa garesu "ku bashi shawara ya fadi gaskiya. Wallahi akan yaron nan case din yafi karfin tunaninku. Komishinanmu ma yana hanya kuma ko shi bai isa ya ja da umarnin Alh. Sadisu Nakano ba."

Jiki sam babu kwari Abbati ya dubi DPO din ya ce "iyakar gaskiyata na fada muku. Bani da zabi idan baku yarda ba sama da na cigaba da addu'ar neman taimakon Allah. A cikin kwanakin nan ina cikin jarabawar Ubangiji. Abubuwa suna ta tasowa wadanda suke barazanar rabani da duk wani abu da nake so. Babban burina bai wuce in rufe ido ko da na minti biyar bane idan na farka in ga ashe duka kwanakin nan mafarkinsu nayi."

Sai ga Mami Khadija da Asabe suna share kwalla. Farha ta fita ta sami wani dan dandamali ta zauna tana kuka. Ana dawowa daga rufe shi Alh. Sadisu ya dawo. Munzali ya tari gabansa ya ce shi ya san gidan Shazali.

"Me yasa baka fada ba tuntuni? Officer a hada shi da mutane mu tafi"

Basu bar wurin ba Alh. Tahir da Comared suka shigo reception din.

Mami Khadija da 'ya'yanta suka fara kallon kofa da tarin mamakin me ya kawo shi nan. Tana yin ido hudu da Comared taji zuciyarta ta tsinke. Babu ko tantama abin da suka saba na tara 'yan mata a guest house a kwana ana sharholiya ne take jin

ya hadasu. Takaici ya sake kama ta da ta tuna cewa duba dansu fa suka zo yi amma ya kare da zuwa wurin Comared.

"Ina Abbatin yake?" Ya fara tambayar Munzali.

"Kai kuma waye?" DPO ya tambaya ganin shima nasa hankalin a tashe yake.

Alh. Sadisu ya bashi amsa da cewa abokinsa ne.

Shi kuma Alh. Tahir ya ce da DPO su shiga office dinsa yana da magana.

Alh. Sadisu ya yi saurin cewa "A'a ka bari tukunna. Gidan wani Shazali zamu je Abbati din ya ce wai 'yarsa a can ta hadu da Abdul."

Comared ya ce "Shazali kuma?"

"Ka san shi ne?" DPO da Alh. Sadisu suka yi masa tambayar a jere.

"Kwarai kuwa. Yallabai muje office din naka"

"Comared wallahi ba zan iya sake bata lokaci ba. Ka fadi ko ma mene ne a nan bani da damuwa." Alh. Sadisu ya furta a kagauce.

Alh. Tahir da Comared suka hada ido. Munzali kansa ya tsorata don bai san me zasu ce ba. Jikinsa ya gama sanyi yana jiran a farke musu laya.

"Shazalin nan da ake magana gagarumin kawali ne mai fada a wurin manyan mutane. Yana kai maza da mata duk inda ake da bukata. Bana fata amma indai shi ya dauke Abdul akwai yiwuwar ..."

A hargitse Alh. Sadisu ya ce "kai dakata min nan kada ka karasa wannan maganar banzan da ka dauko."

Baaba Mari, Mal. Inuwa da Mal. Sa'idu sun san waye Shazali da rawar da ya taka a rayuwarsu Abbati. Shi yasa furucin wannan mutumin bai basu mamaki ba. Sun dai kara shiga rudani ne akan dalilin da yasa Shazalin ya dauke Qibdiyya tunda basu sami zama anyi maganar ba.

Cikin lumana DPO ya lallaba Alh. Sadisu da cewa "Yallabai kada muyi saurin katse masa hanzari. Irin wannan abin yana cikin manya manyan matsalolin da muke fuskanta daga makarantun kwana. Lallai zamu je gidan shi Shazali din. Kuma yanzu zan tura mota a taho min da Principal, masu gadi da malaman makarantar tasu."

Gyaran murya Comared ya sake yi ya ce "ina da magana"

"Ina jinka" Alh Sadisu ya bashi amsa rai a bace kamar shi ne Shazalin.

"Ku bani kimanin rabin awa zan kawo muku Shazali har nan."

Alh. Sadisu ya nisa ya ce " kowane sakan guda yana da mahimmanci a gareni. Ni dai na fi son mu rankaya gidan nasa in ga halin da dana yake ciki"

"Ka sanni ba tun yau ba. Abin da ya shafi jininka nima ya shafeni. Ka bani lokacin da na bukata kawai. Komai zai zo karshe in sha Allah. Shazali shu'umi ne. Na rantse maka zai gwammace a kulle shi akan ya fadi gaskiya idan muguntarsa ta tashi."

"To meye alakarku da Abbati da shi wannan Shazalin da ake ta fada?" DPO ya jefawa Comared tambayar da take cin zuciyar kowa.

Alh. Tahir ne ya bashi amsa da cewa "Ni zan baka amsar tambayar nan idan komai ya lafa."

***

Babu wani abu da zai sami bawa face da sanin Mahaliccinsa. A wannan rana taimako ya zo wa Abbati da Munzali a yanayin da basu taba zato ko tsammani ba. Waye zai taba kawowa a ransa cikinsu cewa duk ranar da asirinsu ya tasarma tonowa Alh. Tahir zai zame musu garkuwa? Sai gashi ya zama wata katanga wadda ta tokare bayyanar sirrinsu da tozarcinsu a idon duniya ba tare shi kansa ya shirya hakan ba.

Kamar yadda DPO ya fada, ya tura motoci biyu an taho da duk wani mai kusanci da aji ko hostel din su Abdul daga makarantarsu. Masu gadi ma sai police aka zuba aka taho da su.

Jigum-jigum aka zauna jiran dawowar Comared. Alh. Sadisu kamar zai zare a tsokin lokacin saboda rabin awa ta gota.

Abin da yake faruwa kuwa shi ne da Comared ya koma gida sawa ya yi aka fito da Shazali. Ya kare masa kallo a ransa yana tausaya masa. Indai ta tabbata dan Alh. Sadisu yana gidansa to kashinsa ya gama bushewa. Ta wani fannin ma sune da riba domin duk abin da yake takama dashi na sirrinsu bai isa ta fito dashi ba idan yaje hannu.

"Kayi hakuri. Bai kamata na bari bacin rai ya sani tsare ka ba. Sai dai kana sane da matsayina. Ba zan so duk wani abu da zai shafi mutumcina ba"

"Ina iya tafiya?" Kawai Shazali ya iya tambayarsa saboda ransa ya riga ya gama baci. A gefe guda yana ta tunanin Abdul da ya hada da bango kafin ya fito. Ya rasa dalilin da yasa yake ta fado masa a rai tunda aka rufe shi a daki. Bai sani ba ko don son da yake masa ne har ransa.

Da dingishi ya karasa motarsa ya fice daga gidan. Yana tuki ana biye dashi a baya ba tare da ya sani ba. Motar amittacen yaron Comared ce wanda yasa bin Shazali gida. Shi a nasa zaton ma a can ainihin gidansa da kowa ya sani ne ya ajiye shi. Sai da yaron ya kira ya fada masa suna hanyar wata unguwa mai cikowar mutane da yawan gidajen gargajiya.

"Bishi kawai. Gamu nan a bayanku. Ka kwatanta min inda ku ka bi"

Bai yi mamaki ba don kuwa Shazali ya taba fada masa cewa yana da gida a unguwar inda yake shagalinsa. Suna hanya ya kira Alh. Tahir. Shi kuma ya sanar da DPO da Alh. Sadisu. Nan da nan aka yi ayari aka bisu.

Shazali bai san me yake jiransa a waje ba ya shiga gidansa kai tsaye.

"Abdul na dawo"

Shiru babu amsa. Ya murmusa a ransa yana tunanin ko har yanzu fushi yake saboda yanayin rabuwarsu da zai fita da Qibdiyya.

Yana sanya kafarsa a karshen soron ya hango shi kwance cikin jini a inda ya barshi da zai fita. Rawa jikinsa ya dauka tamkar mazari a yayinda ya duka a kansa yana kiran sunansa cikin sarkewar murya.

"Abbbbbduuu...llll?"

Shiru mai hargitsa tunani ne kadai ya bakunci kunnuwansa. A take duk wani ciwon jiki da yake ji sakamakon dukan da yasha ya kau. Ya dago kan Abdul wanda kasansa babu komai sai jini ya jijjiga shi. Jikinsa gabadaya a sake yake. Fuska tayi fayau saboda rashin jini. 'Na shiga uku' ya dinga ambata a ransa don ko sau daya bai tuna da sunan Sarkin da ke warware dukkan matsala ba.

"Mutuwa kayi?"

Ya yi tambayar da bai sa ran samun amsarta ba. Jinin wajen ya sake kallo wani ya bushe ma. A lissafinsa ya yi wajen awa hudu da barin gida. Cikin sauri-sauri ya tashi ya shiga daki ya dauko duk wani abu da zai iya tunawa wanda zai iya tona masa asiri ya saka a wata jaka. Dama ba wasu kayan kirki yake ajiyewa ba tunda lalatarsa kadai yake yi da kananun yara a wurin. Yaran da ko da zata kwabe a gaba iyakarsu nan gidan wanda ya saya da sunan wani dan uwansa na kauye. Kallo daya ya sake yiwa Abdul ya bude kofar gidan da niyar idan ya tafi ya tafi kenan har abada.

Sai dai me???

Ko minti goma bai yi da shiga gidan ba Comared da motocin 'yan sanda wadanda aka ki kunnawa jiniya suka iso tare da Alh. Sadisu. Ba don an rirrike shi ba ma da tuni ya afka gidan.

Idanun kowa akan kofa. Ga wasu 'yan sandan sun tokare kofar gidan ta yadda ko jinjiri ba zai iya wucewa ta tsakaninsu ba.

Shazali yana bude kofa ya yi ido hurhudu dasu. Cikin dimaucewar tunani ya koma ciki da sauri zai rufo kofar. Sai dai tuni mutum biyu sun riga sun sanya hannuwa sun dannota ciki. Na ukunsu ya tura da kafa. Na karshen kuma ya zura hancin bindiga.

"Idan ka sake yunkurin rufe kofar nan sai na fasa maka kai da harsashi"

Baya ya yi ya daga hannuwansa sama. Ya nemi yawu zai hadiya yaji bakin a bushe. Tunaninsa ya dauke sai hanya da ya bayar domin 'yan sandan su wuce. Abu daya yake takama dashi. Manyan mutanensa ba za su bari ya rayu a kulle ba.

"Ku bani hanya, ku bani hanya."

Abin da yaji ana fada kenan daga kofar gidan. Ya zuba ido domin ganin mai shigowa sai yaga Comared da Alh. Tahir. Budar bakinsa zai yi musu tambayar abin da ya kawosu nan sai ya hada ido da mutumin da ko baka taba haduwa dashi ba a zahiri to lallai an sha gamuwa a TV ko kafafen sada zumunta. Kai hatta muryarsa ba bakuwa bace.

Wani irin sanyi mai hade da zafi a tare suka fara binsa daga tsakar kansa har tafin kafa. Me ya kawo Alh. Sadisu Nakano gidansa?

Shi Alh. Sadisu ba tsayawa ya yi ba. Ciki ya bi 'yan sandan. Yana zuwa ya gansu akan Abdul suna salati. Kirjinsa yaji ya takure. Gumi ya wanke masa jiki. Gwiwa a sake ya durkusa a gaban Abdul ya janyo shi jikinsa. A daidai nan Shazali ya juyo domin ganin me ake yi. Hoton da idonsa ya dauka da kalaman Alh. Sadisu suka kusa sanya shi hadiyar zuciya. Duk da cewa ko uffan bai ce masa ba saboda rayuwar dansa ce a gabansa tukunna.

"Abdul tashi domin Allah kada ka mutu ka barni. Me zan fadawa mahaifiyarka? Me zan fadawa uwayenka? Wace rayuwa ce kuma za ta rage min idan na rasaka? Kai kadai na mallaka. Abdul ka tashi Baba ne da kansa ya zo"

Da kyar da sudin goshi kwakwalwar Shazali ta bude har yaji a ransa cewa muddin ya cigaba da tsayuwa babu abin da zai hana a dauki tasa gawar. Duk fadin kasar nan babu mai tsaya masa ya bar Alh. Sadisu. Mutumin da shugaban kasar dake kan kujera ma babban yaronsa ne a siyasa.

Kofa ya kalla babu ko tunani ya nufeta a guje ya fita. Kafarsa na fita yaji hanya ta kare. 'yan sanda sunfi biyar da suka cafke shi.

Ana kokarin daukar Abdul a ciki Alh. Sadisu ya ce su bari. Da kansa ya dago shi ya saba shi a kafada. Idanuwansa suna zubar da kwallar da rabonsa da yin irinta tun ranar haihuwar Abdul din ya yi ta farinciki. Hanya aka bashi ya fita da shi ya sanya shi a bayan mota. Ya juya da niyar fadawa DPO cewa gida zai wuce sai yaji an kamo hannunsa. Rikon dai babu karfi saboda rashin kuzari.

"Baba.." Abdul ya furta a hankali.

"Alhamdulillah. Ya Allah Ka bani ikon aikata alkhairin da za Ka yi farinciki dani albarkacin raya min Abdul da kayi"

Wannan shi ne furucin Alh. Sadisu kafin cikin gaggawa su bar wurin zuwa asibiti.

'Yan unguwa suna kallo aka jefa Shazali a bayan mota. Wadanda idanuwansu suka taba ganin lokutan da yake kawo yara sannan bakinsu ya bude suka dinga bada shaida.

Sai da aka gama bawa Abdul taimakon da ya dace kafin ayi maganar 'yan sanda. Alh. Sadisu yasa aka duba masa kuma likita ya tabbatar cewa lallai ana amfani da dansa don har ya dauko hanyar gamuwa da cuta. Kansa kuma ya bugu sannan ya zubar da jini. An matukar auna arziki da rayuwarsa bata salwanta ba.

Bayan komai ya daidaita ya bar Abdul tare da matansa ya koma police station. Abin mamaki babu mutum ko daya da ya tafi cikin wadanda suka zo domin Abbati. Ga kwamishinan yan sanda shi ma ya zo. Alh. Sadisu ya fada masa yana so a gaggauta shigar da makarantarsu Abdul da Shazali kotu.

"Ina gudun daukar mataki a hannuna. Ku yi abin da ya dace da wuri kafin a kira ku daukar gawar da hukuma bata bada umarnin kashewa ba"

Office daban aka ware domin sauraron wannan batu. DPO yasa aka fito da Abbati. A reception din Alh. Sadisu ya taresu ya rike masa hannu tare da raba shi a jikinsa.

"Ka yafe min. Da taimakon Allah da jajircewarka akan wanda baka sani ba dana ya kubuta."

Abbati bai ce komai ba. Alh. Sadisu ya juya ya ce idan yana da uwa a wurin nan a nuna masa ita. Mami Khadija tayi murmushi ta nuna masa Baaba Mari. Akan idon kowa ya karasa gabanta ya sauke gwiwarsa daya a kasa.

"Duk wanda ya sanni zai shaida duk zafina bani da girman kai. Ina rokon gafararki akan tozarcin da aka yiwa danki. Wallahi babu mai gane halin da na shiga dazu da wanda nake ciki yanzu sai wanda ya dandana shi. Don Allah ki roka min yafiyar Abbati. Dalilinsa Allah Ya raya min Abdul. Da ya jinkirta ko bai ma kira ba da karshenta bayana ya yanke kenan har abada"

Duk dauriyarta sai da kwalla ta zubo mata.

"Ya yafe maka har abada ba zai kara kallonka da laifin yau ba"

Tunda uwa ta yafe waye d'a da ba zai yafe ba? Tana fada zuciyarsa ta wanke fushinsa zuwa ga fatan kaffara. Munzali ya riko shi domin bashi madogara. Hanne tayi gaba tana kuka zasu tafi. Alh. Sadisu ya dakatar dasu.

"Ina neman alfarma. Don Allah kafin ku tafi ina son ganinka Abbati tare da baban yarinyar nan da Shazali ya dauka"

"Nima ina da magana dasu game da alakarsu da Shazali da satar diyarsu da aka yi." In ji DPO

A wannan lokacin ne kuma Alh. Tahir ya taka rawar da ta shafe tunanin kowa akan laifinsu na baya.

Office din DPO dai aka koma. Alh. Tahir da Comared, Munzali da Abbati sai kuma Alh. Sadisu da DPO din.

"Dazu Alh. Tahir kayi mana alkawarin warware abin da ya hada samarin nan da wancan matsiyacin. Na dawo da tambayar nan ne saboda ina son a hukunta shi akan Abdul da yarinyar wajenku."

"Wani labarin sirri ne wanda jinsa zai iya cutar da mai shi"

Alh. Tahir ne ya yi magana . DPO kuma ya bashi amsa da cewa rashin sanin gaskiya a hukumance zai mayar da Abbati sahun wadanda ake zargi. Wanda a karshe dole shi ma a kai shi kotu.

Basu da zabi. Kofofi sun toshe. Dole su fadi komai da bakunansu yau. Bisa wannan dalilin suka nemi a shigo da iyayensu. Abbati ya ce a hado da Mal. Sa'idu.

Abbati ne ya fara magana yana duban amininsa.

"Ranar wanka ce yau fa Munzali."

"Na sani. Ba a boyon cibi idan ta zo"

"Wadannan sune iyayena" Abbati ya nuna su Baaba Mari, ya dora da cewa "daga Kirikasamma aka turo ni Kano almajiranci. Da karancin shekaru da rashin wayo na zamewa kaina uwa da uba a dalilin haka."

"Ga nawa iyayen. A gabansu na tashi. A cikin gidanmu. Amma daidai banda wurin kwanciya babu abin da zanyi tinkaho dashi a matsayin kulawar uwa da uba."

Shiru akayi. Hankula da kawuna suka karkata garesu a yayin da kowannensu ya bayar da labarin yadda rayuwarsu ta wanzu tun farkon haduwarsu. Baaba Mari tana kuka, Asabe tana tumami. Alh. Rabi'u kuwa kunya tamkar kasa ta tsage ya fada ciki.

"Namiji ya nemi dan uwansa alfasha ce wadda Allah Ya la'anci ma'abotanta. Ya yi fushi da wadanda suka fara ta. Ya kuma gargademu akan koyi da su." Muryar Abbati ta karade kunnuwansu da kaifi.

Munzali ya cigaba da cewa "Mu kuma da ita muka rayu, muka inganta rayuwarmu. Muka yi hajji da umra harma muka kai iyayenmu. Muka yi aure sannan muke kara neman aure. Kuma a ciki muke rainon 'yarmu"

"Da ace iyayena basu turoni almajiranci ba, da ban hadu da Munzali ba. Rashin haduwarmu ina sa rai zai tsameni daga cikin mutanen da Allah Ya tsinewa tun a duniya" wannan karon da kuka Abbati ya karashe maganarsa.

Kafadarsa Munzali ya dafa yana duban iyayensa " da na sami kulawar da ta dace da 'ya'ya bisa koyarwa shari'a, da ban hadu da Shazali ba. Nima da na tsira daga cikin mutane marasa rabo"

Banda hawayen da Asabe da Baaba Mari suke yi, dukkan mazan wurin babu wanda hankalinsa bai tashi ba. Tsigar jikinsu ta tashi.

Abbati ya dubi Alh. Sadisu "kune masu fada a ji a kasar nan. Idan kun kafa doka ina tsammanin za tayi tasiri."

"Doka akan me?"

"Almajiranci. Da farko dai duk musulmi ya san cewa neman ilimi wajibi ne ga mata da maza. To amma duk duniya a arewacin Nigeria ne kadai ake musulunci? Me yasa mu ne kadai muke wulakanta zuri'armu da sunan neman ilimi? Wane irin tunani ne yake shige wa iyaye har su iya turo dan da bai shekara biyar ba ya zamewa kansa gata? A ina yake kwanciya iyaye basu sani ba. Me yake ci? Wadanne ranaku ne ba shi da lafiya? Su waye abokan huldarsa? Mene ne hali da dabi'arsa marasa kyau wadanda ya kamata iyaye su tsawatar? Babu guda da aka sani!"

Munzali ya tausayawa Abbati sai dai shi ma ba wani cikakken bambanci bane a tsakaninsu. Shi yasa yana shiru shi kuma ya karbe ragamar zancen.

"Almajiranci ba shi ne silar lalacewarmu ko ta ragowar dalibai ba. RASHIN MAFADI shi ne yake jagorantar duk wata barna. Yadda almajiri zai iya tashi da gurbatacciyar

rayuwa saboda rashin gata haka dan dake gaban iyayensa idan basu kula dashi ba. A suna ne Abbati yake almajiri amma ni da shi bamu da bambanci sai na wurin kwana. A gidanmu idan ka cire ginin gidan babu wani abu da mahaifinmu yake yi mana na tsakanin uba da da. Hatta abinci sai mun nema. Karatu sai mai ra'ayi ko wanda mahaifiyarsa ta tsaya masa. Kafin na shekara sha biyu mahaifiyata ta fara karbar kudin icce, maggi da mai a wurina. Ina nake samowa ba damuwarta bane." Ya dan numfasa kafin ya cigaba da cewa "da ace makarantun allo anyi su a killace, yaran kamar kowanne dalibi su sami kulawa. Abinci kuma duk malamin da ya bude tsangaya sai ya tabbatar cewa yana da masu girki da wurin kwana. A killace yaran nan daga yawo cikin unguwa da tituna. Da tabbas makarantun allo sun amsa sunansu na cibiyar karantar da Al'Qur'ani da samun nagartacciyar tarbiya. Duk dan da ba a tsarewa cikinsa da lafiyarsa ba muddin iyayensa suna da rai komai talaucinsu sun zalunce shi. Domin duka wadannan abubuwan idon iyaye kadai yana rage radadinsu a zuciyar 'ya'ya."

"Ni duk zuwa da abinci ake turo ni. Almajirai da yawa iyayensu suna yi musu wannan kokarin. To amma waye zai dafa mana? Manyanmu a makaranta da su kansu malaman suna da bukata. Yawanci wanda ya kawoka yana tafiya za ka yi sallama da abincin harma da suturar sawarka. Kwace da rashin tausayin na k'asa ya zama ba komai ba saboda yanayin da muka tsinci kawunanmu." Abbati ya fada idanuwansa suna kan Mal. Sa'idu wanda ya dukar da kai.

"Ba wanda zai dauki nauyin zunubanmu muke nema ba. Kowa ya sayi rariya ya san zata zubar da ruwa. Amma komai yana da sila. Silar da muke fatan a kawar da ita ko masu tasowa a bayanmu zasu sami tsira daga mummunar kaddara. Kamar yadda muka fada, ba almajiranci bane kawai. Hasali ma almajiran suna cutuwa ne mafiya yawan lokuta ta hanyar 'ya'yan da suke gaban iyayensu irina."

(Mai karatu wannan ita ce matsayata game da tura yara almajiranci. Kowa yana da ra'ayinsa na sani. To amma illar dake cikin karatun da aka mayar addini ne ma yinsa tana neman fin alkhairin cikinta. Yaran da uwa take rainon cikinsu ta haifa a wahale ne ake saki suyi ta walagigi kamar ba a san ciwon samunsu ba. Wasu saboda kuruciya da rashin wayo ko sunan garinsu basa rikewa. Sai a shekara biyu yaro bai je gida ba. Duk kuma masu kare irin wannan karatu idan ka duba babu dansu ko daya da zasu iya turowa. Na tabbata iyaye mata da yawa zasu yarda dani akan son a dakile wannan tsohon system din da kullum yake kara tabarbarewa. Duk lokacin da muka yi ido hudu da almajiri sa'annin yaranmu kananu sai mun shiga

damuwa. Saboda ya zama dandalin yada mumanan dabi'un da sai sun baci ake sani. Allah Ya kawo mana mafita ta alkhairi akan duk abin da ya dememu. Amin)

BABI NA ASHIRIN DA HUƊU.

Shiru ne ya ratsa office din na wani lokaci bayan su Abbati sun gama bayaninsu. Baka jin komai sai jan hancin Asabe da saukar numfashin mazan da karfi. Hakika wannan zama ya zama tamkar daukar darasi ne ga dukkanin wadanda Allah Yasa aka yi a gabansu. Kowa ya kalli labarin ta fuskar da ya shafe shi.

Baaba Mari fin karfi ne.

Mal. Inuwa makauniyar biyayya.

Mal. Sa'idu kasa bambance neman ilimi (almajiranci) da bara (rokon abinci, da kudin gabatar da bukatun rayuwa). (Jama'a da yawa sun jahilci kiyayyar da ake nunawa wannan na'u'in karatun domin sun hada shi wuri guda da littafi mai tsarki. Abin da basu gane ba shi ne da makaho, da gurgu, da kuturu da dan malam wato almajiri dukkaninsu mabarata ne. Gyaran da muke nema shi ne a gatancewa yaran da ake turowa karatu ta yadda karatun kadai zasu yi cikin aminci da kulawa. Ita kanta bara tana kashe zuciyar ma'abocinta ne. Kenan tana rage darajar ilimin da suke nema. Duk inda almajiri mai roko yake ba shi da wata kima a idon mutane saboda kullum shi ne hannun karba.)

Asabe sakarar uwa wadda ta biyewa sawun miji wurin banzatar da 'ya'ya.

Alh. Rabi'u irin uban da ake yiwa yawancin hausawa kudin goro da halayyarsa. A haifa a kasa rikewa saboda son zuciya da zalunci. Irinsu da yawa 'ya'yansu lalacewa suke yi kuma su zama silar lalacewar 'ya'yan wasu.

Alh. Tahir magidancin da ya dauka zai ci bulus a tattare da alfashar da ya rayu cikin biyewa zuciya wurin kosar da ita. A yau duk wani tunaninsa ya ruguje. Ashe ita zina ba a cin bulus. Ko ayi a inda zai maka radadi ko aje lahira a girbe shuka. Ko a hadawa bawa duka biyun. Sanin zahirin su Abbati ya firgita shi fiye da zato. Gashi kuma suma bashi da sauran kima a idons.

Alh. Sadisu masu madafan iko wadanda nasu kadai suka sani. Duka matsalolin yau zasu iya zama tarihi idan gwamnati ta saka hannu tayi abin da ya dace. Maimakon haka sai suka zabi amfani da gurbatattun cikin al'umma wurin cimma burikansu na siyasa. Sai gashi daya daga cikin baragurbin ya harbi tilon dansa har ma yana shirin rasa shi baki daya.

*

Da aka rasa mai fara tashi ko kara cewa komai bayan sun yi shiru sai Munzali ya tambaya ko zasu iya tafiya domin yana son ya kai Abbati asibiti.

DPO ya cike takardun da suka dace wadanda suka wanke Abbati daga zargi ya ce zasu iya tafiya.

Gabadayansu tare suka firfito waje. Jikkunan su Asabe a sanyaye. Yayinda wadanda basu san abin da aka tattauna a ciki ba suke ta farinciki.

Kasancewar Hanne tana wurin, Farha bata yi gigin matsowa inda ake ta yiwa Abbati murnar kubuta ba. Amma rashin samun yin hakan ya bayyana tsantsar damuwar da Mami Khadija tayi saurin fahimta a tattare da ita. Tausayi taji ta bata. Tunda bata amsa sunan matarsa ba tabbas bai dace tayi abin da zai sosa ran matar tasa a yanayin da ake ciki ba. A wani bangaren na zuciyarta kuma sai ta shiga wasiwasi akan al'amuran da suka faru a yau. Tabbas idan ta ce babu zargin lauje cikin nadi a game da su waye Abbati da Munzali ta yiwa kanta karya. Babbar damuwarta bata wuce alakarsu da wanda ya sace Qibdiyya da kuma dalilinsa na sace ta ba. Alhalin da kunnuwansu duka sun ji daga bakin Comared cewa kawali ne na kusoshin kasar nan. Abbati ya ce shi almajiri ne amma ji gidansa da irin motocinsu. Shin ko dai su ma kawalan ne???

"Mami?"

Firgigit ta dawo daga duniyar tunanin da take sakamakon tabata da kiran sunanta da Lilu yayi.

"Na bude motar ke muke jira"

Kallon motar tasu tayi taga ashe duk sun shiga bayan sun yi sallama dasu Abbati. Ta shiga baya kusa da Suhaib ta zauna. Sun iso kusa da gate din station din Abbati da ya rufewa Baaba Mari kofar motar Munzali ya tari motar tasu kafin su fita. Saitin tagar gaba inda Farha take zaune ya tsaya amma idanunsa baya suke fuskanta wurin Mami Khadija.

"Mami ku yi hakuri da abin da ya faru dazu da ma damuwar da muka janyo muku yanzu."

Murmushi tayi tana mai kara yabawa da sanyin halinsa.

"Ka bar wannan magana Abbati ta riga ta wuce. Allah Ya tsare gaba. Gara ku samu ku tafi don ka ga likita da wuri."

"In sha Allahu. Nagode..." Ya kallo Suhaib da Lilu ya sake cewa "Nagode"

Farha ce kadai bai yiwa magana ba. Sai murmushi kadai saboda idon Mami. Waje suka yi da motar suka bi bayan Comared wanda yake tare da Alh. Tahir. Kuma shi zai yi musu jagora su koma gida.

A ranar Asabe gidan Lami ta wuce. Bata iya komawa gida ba sannan ba za ta iya fuskantar Munzali ba. Duniyar ce kaf ta daina yi mata dadi. Ta rasa tudun dafawa. Yau ko mashi aka caka mata a zuci iyakar ciwon da za ta ji kenan. Dole bahaushe yake cewa gaskiya tana da daci. Maganganun da taji daga bakin danta basu yi mata dadi ba ko kusa. Amma cikinsu babu karya. Idan Alh. Rabi'u halinsa ne tsallake iyalinsa ya barsu suyi ta kansu da zarar sun fito duniya, ita mene ne nata uzurin? Bata taka rawarta ta uwa a wurin 'ya'yanta ba. Duk wata alamar mace ko uwa ta gari babu a tattare da ita. Kaiconta! Ta ina za ta fara?

Alh. Rabi'u da ya koma gida shi kuma ko runtsawa bai iya yi ba. Dakinsa ya shige ya rufe kofa tun dawowarsa. Gabanin magariba Innayo da su Uwani suka shirya tafiya asibiti dubo Abbas. Aikin nasa karfe bakwai ne da an idar da sallah. Ta cikin dakin ya iya cewa su gaishe su.

Yanayinsa da rashin dawowar Asabe ya sanyata shiga damuwa. Damuwa ba akansu ba. Tunaninta ya tafi kan Munzali da take da yakinin akwai abin da yake faruwa dashi. Da kuma Qibdiyya. Aikin da aka shiga da Abbas ne yasa kowa tsammanin shi ne damuwarta. Shi yasa babu wanda ya dameta da tambaya. Tare dasu Hasiya suka zauna har aka fito dashi suka tabbatar lafiyarsa kalau sannan kowa ya kama hanyar gida.

***

Allah Ya yi dare, gari ya waye. Kowane mahaluki safiyarsa tana zuwa da fuskar da Allah Ya kaddara masa. Wani da dariya wani da kuka. Wani da damuwa wani kuma zuciyarsa fes. Shi bawa har kullum idan yana kwadayin dacewa sai ya zama mai karban rayuwa a duk halin ta zo masa.

A wannan rana wadda ta biyo rana mai tarihi a rayuwarsu Abbati, sun wayi gari da ciwon da jiya ta bar musu. Daga asibitin da Munzali ya kai Abbati, gida suka dawo dukkaninsu. Munzali ya fita ya nemi gidan abinci mai kyau ya sayo musu. Aka taru aka ci kamar ana tura magani. Hanne da Habu kadai ne suka zata shirun nasu yana da nasaba da dukan da aka yiwa Abbati. Ko da suka shishshiga daki domin bawa jiki hakkinsa, babu wanda ya runtsa sai mutum biyun can dai. Juye juye kowa ya dinga yi har aka kira assalatu. Kowa ya tashi kamar jira suke yi. Kafin takwas duk sun hallara a falo.

Zamansu ke da wuya maigadi ya shigo ya fadawa Munzali mahaifinsa yana nemansa. Dan murmushi ya sami kansa da yi domin ya tabbata yau dai neman da yake yi masa na damuwa da lamarinsa ne ba na neman kudi ba. Bai so ace karon farko da mahaifinsa zai damu haka dashi ya kasance akan abu makamancin wannan bane.

Bangaren Abbati ya ce a kawo shi. Ya zo ya zauna suka fara gaisawa da su Mal. Inuwa sai ga Asabe. Kayan jiya ne a jikinta da alamun rashin wanka ma. Tayi wuri wuri da ita gwanin ban tausayi.

"Hanne da Habu ku dan bamu wuri don Allah" cewar Mal. Sa'idu yana mai dubansu da mutuntawa.

Bambarakwai suka ga abin tunda bai saba lallaba dan kowa ba. Habu ya fita waje. Hanne kuma ta haye sama.

Munzali da Abbati suka zazzauna a kasa domin girmamawa ga iyayensu sannan Mal. Sa'idu ya soma magana cike da rauni.

"Ba don wannan al'amari mai muni bane wanda nake fatan daga yau kada a sake tayar da maganar ba, da sai in ce ina son sauran kannena su kasance a wannan zama."

Caraf maganar ta shiga kunnuwan Hanne. Kafafuwanta kuwa suka ci burki a bakin kofar shiga saman daga ciki. Sannu a hankali ta sakaya kofar ta sami wuri ta labe abinta.

Mal. Sa'idu ya cigaba da cewa "Allah shi ne shaida cewa ni Sa'idu ina kaunar 'yan uwana da 'ya'yansu da zuciya daya. A tawa wautar soyayya ce tasa nake juya kowa a gidan a matsayina na babba. Girman kai yasa nake ganin tunda gaba nake da kowa yi min biyayya wajibi ne. Sannan kowa bai san daidai ba sai ni kadai."

Ya dubi Baaba Mari, duba na mai jin nauyin wanda ya sabawa.

"Ki yi min aikin gafara duk da cewa na roka a makare. Tun ranar da ki ka dawo da gawar Sani a bayanki ya dace ace na zauna nayi tunanin halin da na jefamu a ciki. Son zuciya da girman kan da na ambata a baya suka sanya nake jin baki isa na janye kudurina ba. Yin haka tamkar kin yi galaba ne a kaina. Wannan dalilin yasa na kara tamke dammarar juya duk wani abu da kike tunanin kina da iko dashi. Musamman rayuwar Abbati. Sannan magana ta gaskiya, a duk lokacin da ki ka tayar da maganar son sannin sana'ar Abbati, nima ina kwadaituwa da haka. Na kan riski kaina cikin halin tunani da rashin bacci a wadannan lokuta domin nima a tsorace nake. Gudun kada abin da nake gudu ya tabbata yasa bana kaunar jin kina tayar da wannan zancen."

Bayan ya yi shiru Mal. Inuwa ya yi gyaran murya ya ce "laifi ba naka bane kai kadai Yaya. Harda mu da duka wadanda suke da alhakin sanyawa ko hana irin wannan na'u'in karatun. Hakika bana jin akwai wani mai sanya gaba gabas da zai kalubalanci tura 'ya'yan musulmi neman ilimin islama. To amma wannan hanya da

aka biyo ba mai bullewa bace. A da can zan yarda idan aka ce mu iyaye maza muna tura yaranmu ne domin karatun Muhammadiya. Yawancin 'yan kasuwa da masu kudin da ake ji dasu a arewacin kasar nan akwai almajiranci a cikin tarihinsu. Su nemi ilimi su hada da koyon sana'a'o'in hannu komai kankantarsu. Yanzu kuwa babu tantama abin ya koma hanyar gujewa daukar nauyin da Allah Ya dora mana na 'ya'yanmu ne. Muna fakewa a bayan addini muna wulakanta rayuwar yaranmu. Ko babu komai duk mai roko baya daraja da kima a idon mutane. Zuciyarsa mutuwa take wurin jiran a bashi. Sannan ta kangare idan bai samu ba, ya dinga ganin laifin duka duniyar baki daya wurin kin nuna masa tausayi."

Baaba Mari dai bata ce komai ba sai sauraron Mal. Inuwa da Mal. Sa'idu suna bankado rawar da suka taka wurin bata rayuwar Abbati.

Munzali kuma ya tsurawa iyayensa ido. Da ya gaji da shirunsu ya kasa hakuri dole sai da ya yi magana.

"Baku ce komai ba Baba"

Asabe ta dukar da kai cikin jin nauyin kowa. Kunya da bakinciki sun mamaye zuciyarta. Tana mamakin yadda akayi ta makance da son duniya a baya har ta iya aikata wannan danyen aikin na sakaci da rayuwar 'ya'yanta.

"Me zan ce Munzali? Ina cike da kunya da nadama amma hakan ba zai canja komai ba. Laifinmu ni da mahaifinka yafi na kowa yawa a wurin nan. Bamu bar muku komai na tinkaho ba sai yawanku wanda ba don kun yi yunkuri da kanku ba da bai amfaneku da komai ba. Kalmar hakuri kadai bana jin za ta yi wani tasiri wurin rage maka radadin wannan al'amari"

Kalaminta ya zaburar da Alh. Rabi'u ga yin magana tana rufe bakinta.

"Mene ne aibun 'ya'yana? A iya sani na arziki ne yawan haihuwar domin kuwa rana gobe kiyama da irina Annabin Rahama zai yi alfahari"

Sallallahu alaihi wa sallam ya ji falon ya karade da ambata kafin muryar Munzali ta doki kunnuwansa cikin fushi.

"Ina abin alfaharin Baba? Waye cikinmu za ka iya fitarwa ka nuna hankali kwance har ma ka yi zaton za ayi alfahari da shi"

"Munzali meye haka ne?" Abbati ya ce dashi da alamun rashin jindadi.

" Gaskiyar da 'yan uwa, makota, surukai, abokai da mu kanmu 'ya'yansa muka kasa fada masa da wuri zan sanar da shi."

Ya mayar da hankalinsa ga Alh. Rabi'u wanda shi ma kallonsa yake da mamaki. Duk jahilcin da yake tunanin Munzali yana fama dashi bai yi tsammanin zai kasance cikin masu kokonto akan hadisan Ma'aiki ba. Hadisi ma irin wannan da ya dade da karade al'ummar da ya taso a cikinta.

"Baba idan anje lahirar za ka tsame wasu cikinmu ne ka nuna a matsayin 'ya'yanka?"

"Munzali kada ka yi sa6o mana" Asabe ta gargade shi ganin kamar zai saki layi.

"Allah Ya tsareni. Laifukana na baya ma sun isheni. Da yardar Allah ba zan sake afkawa zunubi da gangan ba. Ina dai so in ji shin da wa Baba zai yi alfahirin." Ya soma lissafi da yatsun hannunsa "Da 'yan dakin su Marigayiya A'i wadanda suka butulcewa hannun da ya ciccibi rayuwarsu a lokacin da basu da gata zai yi (Innayo)? Su suka fi morar lafiya da kuruciyarta amma saboda rashin uba tsayayye suka manta alkhairi. Ko Uwani da Zara da suka zabi kyama da tozarci ga mahaifiya kamar Innayo saboda gudun talauci? Ko ni da nafi kowa kazanta? Ko Bature da baka san a gidan wa yake kwana ba? Ko Lawisa dake canja samari kamar hula ta kuma gagara zaman gidanka? Ko Ummakati dake jin kunyar a hadata da ku a matsayin iyaye?"

Alh. Rabi'u shiru ba amsa sai muguwar kunyar da ta mamaye shi. Su Mal. Inuwa kuwa nauyi yasa suka ji ina ma kafin a fara maganar suka fita.

Idanu cike da kwalla Munzali ya dubi Baaba Mari ya ce "ki fada musu babu abin alfahiri a haihuwar da 'ya'ya basu sami kulawa, soyayya da kwab'a ba. Wadannan abubuwan masu saukin samuwa ne tunda babu ruwansu da da kudi ko talauci balle mutum ya dorawa halin rayuwa laifi. Annabi SAW ba haihuwar yuyuyu yace ayi ba. Me zai yi da taron al'ummar da fiye da rabinta suka zabi hanyar shaidan a matsayin tafarkin da zasu bi saboda rashin kulawar iyaye? Da kun sauke hakkina da na 'yan uwana da yake kanku da a yau iyayen Abbati ba suyi kukan fadawarsa harkar neman maza ba."

"Neman maza?" Hanne ta yiwa kanta tambayar a hankali tamkar tana jira wani ya sake fassara mata abin da ta riga ta sani. Ta sake maimaita kalmar tana cije lebe kafin kuma a hankali ta dora hannuwa a ka ta dinga nanata "na shiga uku" tana mai buga kafafunta a kasa a hankali don kada a ji. Matsanancin tsoro da fargabar da suka kama ta basu kawar mata da tunani ta yadda za ta so ta bayyana kanta a garesu kafin ta gama jin komai ba.

"Munzali yawan tada maganar nan ba shi da amfani tunda mai afkuwa ta afku. Ku yafi juna kai da iyayenka a cigaba da addu'a" cewar Mal. Sa'idu wanda hasashen halin da Alh. Rabi'u yake ciki na kunya yasa shi magana.

Shi kuwa Mal. Inuwa sai cewa ya yi "tada zancen akwai amfani Yaya Sa'idu. Ai zaman zubeben kwarya ake. A fitar da komai don kowa ya gane ta inda ya kuskure saboda a ji dadin gyarawa" idanun Munzali ya kalla dake cike da zallar bacin rai da tarin damuwa ya kuma kalli Asabe da Alh. Rabi'u "har yanzu da mu daku bamu makara ba. Dama ce muka samu domin shafe abin da ya faru da yaranmu. Don ko mun ki ko mun so, mu ma muna da namu kason a cikin zunubinsu tunda sakenmu ne sila. Musamman mu iyaye maza."

Asabe ta share hawaye ta ce "haka ne."

Shi kuwa Alh. Rabi'u daure fuska ya yi. Yadda bahaushe yakan ce gaskiya tana da daci to shi ma wannan ba karamin dacinta ya ji ba. Ba kuma ya jin zai bari a cigaba da fadarta balle tayi tasiri a zuciyarsa.

"Dakata Malam wa kake da suna?...wace irin magana ce wannan za ka ce muna da rabo a zunubinsu? Na san lokacin da ya fara ne? Ko ni na aike shi?

"Alhaji mene ne haka kuma?" Asabe ta furta ranta ya soma baci. Ko ba komai mahaifin Abbati bai cancanci irin wannan maganar ta rashin girmamawa ba.

Hararta ya yi kafin ya ce "dama tunda kika fara sauraron Innayo na soma kasa gane kanki. Idan ke kina maraba da a qaqaba miki zunubin irin mutanen Annabi Ludu ni bana so" ya mike tsaye yana baza babbar riga "ban san me ya dawo dani gidan nan ba. Na dai tabbata ba wannan maganar bace don wallahi da ba zan zo ba."

Mal. Inuwa ba shiri ya ce "kayi hakuri ban fada da wata manufa ba"

Munzali cije lebensa ya yi bayan ka karewa yanayin da Abbati ya shiga tunda Alh. Rabi'u ya soma magana. Takaicinsa ya karu da ya fahimci har yanzu akwai sauran gyara a lamarin mahaifinsa.

"Har a yanzu da nake kan siratsi irin wannan na rayuwa ba zan ji ni kamar kowane d'a mai iyaye ba?"

Asabe ta yi saurin cewa "Kada ka dauki maganganun Alhaji cikin fushi ya fada. Ka yafe mana don Allah"

"Kada Allah Yasa ya yafe. Aikin banza. Kaje ka gama iskancinka sannan ka dawo kana neman wanda za ka dorawa alhakin aikin da gabbanka suka aikata."

Su Mal. Sa'idu jiki duka ya yi sanyi. Ana neman gyara ga alamun sake tabarbarewar lamari ya taso.

Idan ya cigaba da sauraron mahaifinsa yana jin tabbas zuciyarsa sai tayi bugawar da take ta shirin yi tunda abubuwan nan suka soma faruwa. Shi yasa ya murje idanunsa ya fadi abin da yake ganin daidai ne.

"Idan ka so Baba ka cireni daga cikin 'ya'yanka. Wannan shi ne kadai nake jin abin da zai rabaka da amsa tambaya akan halin rayuwata..."

"Munzali mahaifinka ne fa..." Cewar Asabe tana jan hannunsa don ya kalleta"

"A suna ba. Na cinye kuruciyata sanda nake matukar bukatarsa ma na rayuwa balle yanzu"

"Munzali" Mal. Sa'idu da Baaba Mari suka kira shi kusan lokaci guda.

"Ku barshi ya nuna min iyakata. Dama can kawunanku yafi gani da gashi ba nawa ba"

"Ka taba yi min wani abu da zan gan ka da kimar da Allah Ya baka ta ubana..."

Da karfi Abbati ya ce "Munzali? Hauka kake ko me? Alhaji ne fa! Zo ka tafi gida gani nan zuwa."

Maganar da Munzali bai karasa ba kenan domin baya jin akwai ranar da Abbati zai saka shi ko ya hana shi ya kuma musantawa. Tuntuben bakin da ya yi akan Qibdiyya yake gudu kada Allah Yasa ya kuma maimaitawa.

Alh. Rabi'u da su Baaba Mari kowa ya ji kuma ya gani cewa Munzali bai bar fadi in fada da babansa ba sai da Abbati ya tsawatar. Hakan ya zama sanadin da Alh. Rabi'u ya sake samun abin aibata dan nasa.

Kujerar da ya tashi ya koma ya zauna a dofane yana kare musu kallo shi da Abbati.

"Ikon Mai Sama. Yanzu Munzali duk fadin wurin nan da jama'ar ciki babu wanda ya isa ya hanaka ka hanu sai wannan almajirin? Ka dubi tsabar idanuna ka dinga cab'a min magana son rai."

"Wallahi Abbati ya isa dani"

"Tabdijan!" Ya dubi su Mal. Inuwa "to Billahillazi da sake. Yaran nan basu tuba ba. Sannan ina tsammanin mu'amalarsu bata sauya ba tun kuruciya. Iya shegenku kuke yi har kwanan gobe." Ya kalli Asabe tana sharbar hawaye "ki adana kukanki don basu cancance shi ba. Alhaki kwikuyo gashi nan ya bi kan 'yarku ai. Shi ne don borin kunya ku ka tara mu a nan kuna karanta mana karya da gaskiya."

"A'uzubillahi" cewar Mal. Sa'idu yana mai duban mutuwar tsayen da Abbati da Munzali suka yi "Alhaji wace irin magana ce wannan? Ana kokarin kawo gyara ya za ka sake jifansu da abin da su da kansu suke neman tsari daga gareshi?"

"Baka ji me yake cewa ba? Wai fa ni yake fadawa cewa Abbati ya isa da shi. Koda yake ba damuwa zaku yi ba tunda wanda ya zaba akan mu iyayensa danku ne."

Asabe kuka kawai take yi. Yayinda Hanne ta sulale a kasa bakin kofar da take labe ta zauna. Wani sashe na zuciyarta yana kokarin karbar zancen Alh. Rabi'u. Domin alal hakika ta dade da rashin son alakarsu duba da yadda komai zasu yi sai sun tuntubi juna. Sutura wannan daidaikun ranaku ne suke bambantawa. Bata ganin kowa sai muryar Munzali da ta karade falon cikin rauni, karaya da bakinciki ya mayar da martani ga zargin da mahaifinsa yake yi musu.

"Ba zan janye kalamaina ba. Abbati ya isa dani. Haihuwata ce kadai bai yi ba amma duk wani abu da ya kamata uwa da uba su yiwa d'a ya yi min. A kuma matsayinsa na ALMAJIRI" Alh Rabi'u ya fuskanta da tambaya "ka taba sanin cewa da ina karami ina yawan fama da ciwon namoniya (pneumonia)? Duk lokacin da ya tashi Abbati ke jinyata. Ita Asabe ai ta sani. Ya nemo kudi ta kazamar hanya ya kaini asibiti. Bata taba son sanin a ina yake nema ba tunda ba ita yake tambaya ba."

"Ke, yaushe aka yi haka ban sani ba?"

Ya tambayi Asabe a zafafe.

"Ban sani ba" ita ce amsar da ta bashi.

"Kun gani ko?" Ya nuna iyayen nasa yana girgiza kai "Abbati ne ya kaini makarantar boko ta yaki da jahilci. Yasa muka koma zuwa makarantar dare duk da mun san cewa mu din masu aikata laifi ne. Sannan tuban da muke hanyar yi shi ne dai sila kuma jagora. Ya yi min komai wallahi. Ya cancanci girmamawa da mutuntawa. Tunda ya ce na tafi gida kuma zan tafi domin wannan almajirin yana da iko da ni" yana kaiwa nan yasa kai ya fita ko waige babu.

"Malam ina neman izinin yin magana"

Abbati ya kai idanunsa ga Baaba Mari ita kuma tana fuskantar Mal. Inuwa. Kai ya gyada mata da sauri sauri don ya san zancenta a kullum abin duba ne.

Asabe da Alh. Rabi'u ta yiwa magana da cewa "Da farko ina son baku hakuri akan duk wani abu da Munzali da Abbati suka yi wanda ya bata muku rai. Abu na biyu kuma ina son tunatar da mu duka cewa zama iyaye ba a ciki da haihuwa bane kadai kamar yadda Munzali ya yi ta nanatawa. Shiriya da 'bata ba a hannun iyaye yake ba. Amma akwai kokari da dagewa. So, kulawa, sawa da hanawa duk namu ne. Su din basu isa su gyara mana 'ya'ya ba. Amma kuma aikatasu yana kosar da zuciya. Yana sanya nutsuwa da kwanciyar hankali domin mutum ya san idan ya koma ga Allah yana da hujjar da za ta cece shi daga azabar tozarta amana."

"Ni wallahi na karbi laifina Maman Abbati. Zanyi duk abin da ya dace domin gyara kuskure na"

"Ki je wurinsa" Abbati ya ce da ita da farinciki.

Tana fita Alh. Rabi'u ya fita kamar zai tashi sama yana faman hardewa da babbar riga.

***

An fi ganin nisan daren da washegarinsa bawa yake da burin aiwatar da wani aikin da dole sai an jira gushewar daren. Haka mutum zai kwana zuciyarsa tana azalzalarsa da son ganin lokaci duk bayan gilmawar hannun agogo. Wani zai iya kwana yana buga tsaki da k'wafa. Yayinda mai wayo yake dauro alwala ya gana da Mahalicci. Idan hakan bai samu ba ayi ta tasbihi da tahmidi ana neman agajin Maiduka wurin ganin safiyar ta zo daidai da burin mai jiranta.

Mami Khadija a wannan dare bayan sun dawo daga ofishin 'yan sanda ko tunanin kwanciya bata iya yi ba. Duhun dare shi ya bawa Alh. Tahir mafaka ya sami damar sabulewa tuhume tuhumen da suke dankare a kokon zuciyarta.

"Ina da magana da kai" ta ce a lokacin da ta ga yana shirin ficewa daga gidan bayan sun kawosu shi da Comared.

"Ba a nan ba Khadija. Ki yi min alfarmar mu jira gari ya waye mu koma Kaduna"

Rokonta yake. Taji hakan a muryarsa ta kuma gani a yanayinsa. Ba don ta so ba ta amince saboda rufin asirinsu tunda akan ce bango ma yana da kunne. Kwana tayi sallah da jan ambaton Allah har aka kira Assalatu. Nan ma bayan tayi sallah tayi wanka gani tayi rana taki fitowa da wuri. Ba ita ta sami salama ba sai da motarsa ta shigo gidan ya nemi da ta fito su tafi.

"Ba zan bar su Farha su taho su kadai ba saboda tukin Lilu"

"Magana zamu yi kawai na dawo dake"

Ta kula gudun rigima yake. Jikinsa ma duk ya yi sanyi. Sannan ga dukkan alamu yadda bata runtsa ba shi ma haka ya kwana. Ba musu ta bishi. Matan gidan wadanda tuni suka karbi uzurin da Suhaib ya basu na jiya cewar Lilu ya bi saurayin

Farha ne ba tare da yiwa Mamin tasu bayanin dalili ba. Shi yasa hankulansu suka tashi. Sai da suka je suka samu 'yarsa aka sace kuma basu dawo ba sai da aka ganta. Shi yasa yau tsokanar Mamin kawai suka dinga yi akan za ta bi mijinta cikin raha ba tare da tayar da zancen jiyan ba. Da zasu tafi har dakin samarin taje ta dauko wayar Danliti dama Suhaib ya cire lock din.

Gidan Comared ya tafi da ita kai tsaye. Suka shiga har falon da Abbati da Shazali suka duku akan boye Qibdiyya.

"Ina ne nan? Me yasa ka kawoni?" Ta tambaya rai a hade tana karewa hargitsin wurin kallo.

Wuri ya nuna mata ta zauna sannan ya bude baki ya fadi abin da yake jin shi ne rufin asirinsa da na su Abbati. Karfin kalaman da ya zube mata sun tafi akan boye laifin matasan ne wadanda zuwa yanzu ya amince da cewa komai na Allah akwai manufa. Wala Allah rufa musu asiri akan yakinin da ya samu na tubansu zai iya rage masa nasa nauyin.

Ya fara da tuna mata shi waye ta fannin mu'amala da mata. Ya cigaba da cewa ya zo gidan ne jiya domin haduwa da 'yan matan sai ya gamu da Abbati.

Katse shi tayi a firgice ta ce "Innalillahi. Kaddai su ma din..."

"Ko kusa" Alh. Tahir ya sami kansa da wani irin karfin gwiwa "kinsan Abbatin ma almajiri ne. Irinsu yawanci babu gata da kulawar babba a kusa. A nan suka hadu da shi wannan Shazalin dake unguwarsu Munzali. Abinka da kuruciya da rayuwar da abinci ma sai ka roka. Bai wahala ba wurin jan ra'ayinsu ya hadasu da manya aka dinga sakar musu kudi suna kasuwanci. Sai da aka bari kudin ya zauna musu sannan aka bijiro musu da irin aikin Shazali na kawalcin maza da mata. Da suka ki amincewa ne fa Shazalin ya dauke musu yarinya. Shi ne abin da ki ka gani jiya"

Mami ta dinga salati da hailala

"To amma kana da tabbas akan basu taba yi ba"

Tunawa yayi da irin rantsuwar da Abbati ya yi da kuma fushin da ya yi akan gara mutuwarsu da su komawa tsohuwar sana'arsu. Sai ya sake zabo kalmomin da zasu kwantar mata da hankali sannan a lokaci guda basu kaucewa abin da ya ji ba.

"Khadija wallahi Abbati bai san ina cikin gidan nan ba da farko. Amma ya yi ta rantsuwa akan gara ya rasa komai akan ya sabawa Mahaliccinsa."

Ajiyar zuciya tayi. Wani abu da ya kwana a wuyanta ya sauka ba tare da ta farga ba. Ta mika godiyarta ga Allah a fili da zahiri da Ya sanya basu cikin masu sabon Allah.

Alh. Tahir shi ma hakan ce ta kasance dashi. Zuciyarsa ta amince da tafiya da sirrinsu Abbati kushewa. Ba komai ya janyo hakan ba kuwa sai ganin cewa izina ce abin da ya faru jiya a gare shi. Kazamin mazinaci irinsa bai isa ya tserewa abin da ya shuka ba. To Amma Allah Buwayi Ya dubi zuciyar uwar 'ya'yan da su kansu Ya kangesu daga zinar. Shin wannan bai ishe shi godiya ba? Da kunnuwansa yaji kalaman tuba da nadamar Abbati. Idan ya hana shi 'yarsa ya san wane irin fasikin za ta hadu dashi? Rayuwarsu curarren zare ne mai wahalar warwara. To amma idan mutum ya nutsu zai gane cewa Allah Shi ne Gwani mai jujjuya lamura domin su dace da rubutun kaddarar allon kowane bawa.

"Ya ganka a nan din?"

Muryar Mami ta sauka a gare shi cike da alhinin amsarsa.

"Ya ganni. Ya kuma alkawarta min ba zasu taba tayar da maganar ba." Wata kwalla yaji ta cika idanunsa ya ce "kinga irin abin da ki ka jima kina fada min duk ya faru ko? 'Ya'yana sun san ko ni waye sannan maneman 'ya'yana ma sun sani"

An dawo inda ya dade yana mata kaikayi. Wayar Danliti ta damka masa bayan ta bude sakonnin da suke musaya shi da Jiddo. Jijiyoyin wuyansa suka tashi suka firfito saboda bakinciki.

Ta fara magana da fada masa zargin da ama yiwa Lilu na bata Qibdiyya. Da tsoron da take kada watarana gangan ta zama gaske. Sai ta koma batun Jiddo

"Tonon asirin wani ba abin kirki bane. Ban taba tunanin yin haka ga kowa ba. To amma ina gudun yadda kaddara ta fada mata nima wata rana za ta zo ta riskeni. Duk wata kamewata da yawan nasihar da nake yi maka ai ba iyawata bace. Ko kadan ban fi karfin Allah Ya jarabceni da aikata wani na'u'i na alfasha ba. Musamman na zina ko danginta wanda kubuce musu yake da wuya. Shi yasa na zabi ka sahale min wannan auren d..."

Mikewa ya yi ba shiri ya ce "Haba Khadija? In kina yiwa Allah ki bar maganar nan zan tuba"

Mami Khadija ta tashi ita ma "Allah Ya haramta zama da fasiki. Aurenmu tuntuni ya dace a raba shi domin in tsira da mutumcina. Zaman nawa me ya haifar banda kwaye maka baya a idon 'ya'yan cikinka?"

"Na tuba"

"Bukata daya ce yanzu ta rage a tsakaninmu. Ina rokonka arziki ka barni in yi maka idda mu rabu a mutumce. Zan yi bakinciki mafi girma da muni ace na mutu ka sanya hannu wurin sakani a makwancina a matsayinka na mijina. Haka kuma zan yi shi ace ina zaman yi maka takaba alhalin baka kasance cikin masu kunyar mummunan aikinsu ba"

Shiru ya yi na dan lokaci maganar ta sami kowace kusurwa a jikinsa ta shiga. Sannu a hankali ya daga kai ya dubeta ya ce,

"Tsanar da ki ka yi min har ta kai haka?"

"Ko kusa. Me zai sa na tsani mijina uban 'ya'yana? Mutumin da ya kyautata rayuwata da ta 'ya'yana da dukiyarsa da soyayya. Kyamar halinka nake yi domin duk dadin mu'amalar mu ta gidan duniya akwai ta lahira. Wadda zata nuna ina

mutum ya nufa bayan an kare wannan gajeruwar rayuwar da bata da tabbas. Ina tsoron kada jindadin more rayuwa yasa in daina ganin aibun laifinka harma zuciyata ta daina yi masa kallon haram."

Kuka take yi. Kuka sosai. Ta durkushe akan gwiwoyinta ta daga hannuwa gareshi. A dimauce Alh. Tahir ya tayar da ita tsaye ya yi nufin rungumeta don lallashi amma ta kame jikinta wuri daya.

Jikinsa ya kara yin sanyi. Yaushe rabonta da amince masa a matsayin miji? Shi kansa ya manta.

"Ki yi shiru"

"Ka taimakeni ka sauwake min."

Kamar wani mahaukaci ya dubeta ya ce "Khadija wallahi zan tuba. Ke na ma tuba. Astagfirullah"

"Don Allah. Ka dubi darajar mai cikakkiyar daraja SAW. Ka raba ko igiya daya ce a tsakaninmu don Allah"

"Nace miki na tuba" ya furta hawaye na sauko masa. Bai taba sanin zafin soyayyarta ba sai a wannan gabar "ta yaya zan rayu babu ke? Ta yaya zan zuba ido ki zama mallakin wani?"

Mami Khadija ta daure ta kamo hannunsa ta rike tamkar suna musabiha.

"Ban san gobe ba. Bani da masaniya akan gaibu. Sai dai ina rokon Allah Sarkin Sarakuna. Idan akwai sauran zama a tsakaninmu, kada Ya bani ikon sake aure har na koma gareshi. Ya baka ikon tuba wanda ya cika dukkan sharudda. Ya tsayar da digadiganka akan siradil mustaqim. Ya tasheka cikin bayin da Ya aminta dasu. Ya

kuma sake hada aurenmu a aljannah. Amma a duniya kam na gama auren nan in sha Allahu."

"Innalillahi wa inna ilaihi raji'un" a gabanta ya durkushe yana nanata wannan kalma sannan da kyar bayan ta soma fitar da rai ya ce "na sake ki saki daya. Don Allahn da kika sa na sake ki kada ki auri wani. Ki jirani. Ko a duniya ko a lahira zan tuba. Wallahi na tuba. Kai...me ya kaini? Wannan wane irin zalunci na yiwa kaina?"

Jikinta ya dauki rawa da jin kalmar sakin. Ta jima tana nema. Ashe duk dauriyar da take tunanin tana da ita bata kai ta kawo ba?

"Ina da gida a Kabala zan baki. Ki jira a gyara takardun in sanya sunanki kafin ki tashi."

"Nagode"

"Batun yara fa? Na san ke zasu bi. Da wuya su zauna a inda nake. Ina nufin ya zanyi in dawo da koda rabin ko kwatan mutumcina a idonsu?"

"Ka tuba. Allah zai yi maka sauran indai dominSa kayi."

Bai san shi dan gata bane kuma asararrarre sai yau. Yau ne ya nutsu ya saurari Khadija. Yau ne kuma igiyar aurensu ta sami targade.

Ya Allah Ka shafe mana kurakuran da suka gabata. Ka hanemu aikata wasu. Amin

BABI NA ASHIRIN DA HUƊU.

Iyalin Innayo sun tashi da alhinin aikin da aka yiwa Abbas. Kowa yana farinciki da jin cewa anyi aikin cikin nasara. To amma duk wanda ya ganshi bayan ya farfado a daren jiya cikin magagin ciwo sai ya tausaya masa. Hasiya tayi kuka tamkar ranta zai fita. Kiran sunayensu yake yana rokonsu da su cire masa ciwon da yake ji. Duka sai gwiwoyinsu suka yi sanyi.

Da wuri 'yan dakin Innayo suka gama shiri zasu tafi dubiya washegari. Hasiya ma man ta taho da sassafe saboda bata yarda ta bar asibitin ba. Da tursasawar Honourable ta taho gida yin wanka tunda nan din yafi kusa da asibitin akan gidansu. Uwani ta riga kowa gamawa. Ta sami wuri ta zauna ta kira Munzali. Muryarsa ta dakushe ba ma a jinsa sosai.

"Kira nayi inji jikin Qibdiyya da naka. Jiya ban wuni cikin kwanciyar hankali ba. Kuma Innayo ta ce akwai sirrin da bai dace mu ji ba ko don mutunta juna shi yasa bamu zo ba".

" 'Baram'barama" cewar Zara dake zaune a dakin tana shayar da diyarta "Hasiya taho ga Metron Uwani tana sakin baki"

"Da yake Hasiyan uwata ce ko? Wai me yasa ku ka raina ni ne?" Uwani ta hau ta da masifa ita kuwa sai dariya.

Tun bayan faruwar lamarin nan sai yau Munzali ya yi dariya. Dariya harda kyakyatawa. Da furucin Uwanin da abin da Zara ta ce duka ya ji. Ya kuma kara kaunar Innayo domin hakika ta karramasu da ta basu damar adana sirrinsu ga mahaifansu kadai. Sai da ya gama dariyar ya ce

"Jiki da sauki. In sha Allahu zan kawota wurinku yau ki dubata sai ki fada min abin da ya dace mu yi."

"Kai ni fa anyi suspending dina. Ranar da muka kai ka ma sai da na barar da girmana wurin roko.Ka kaita na kudi kawai a dubata a sirrance. Irin asibitinmu ai da baki ma za a dinga nuna ni idan na koma aiki. Dama kuma can ba kaunata suke yi ba balle an sami abin gorantawa."

Wata dariyar ya yi sannan ya tambayeta Innayo. A bakinta yaji batun aikin da aka yiwa Abbas. Shi ne ma ta bashi shawarar ko asibitin zai kai Qibdiyya tunda na kudi ne kuma ta yaba da likitocin. Da alkawarin zuwan nasu suka rabu. Ko tashi bata yi ba daga wurin Zara tana ta yi mata tsiya suka ji sallamar 'ya'yan Zaran.

Wayyo dadi! Zara ta kusa sakin jinjirarta saboda tsananin farinciki da taji Salima tana cewa "marhabin da su Maryam, maza ku shiga ciki ki ga kanwarku"

'Yan matan Zara su hudu suka shigo falon Innayo suna ta rab'e-rab'e a jikin bango. Yanayinsu ya nuna sam basu so shigowa ba. Duk da haka Salima ta cije ta dinga cewa

"Ku shiga mana"

Taku daya biyu a daddafe suka sake jan burki. Zara ta taso ta tsaya a gabansu da farincikinta. A zatonta wallahi suna ganinta zasu rufeta don murna. Sai taga sun sake jan tunga an rasa mai fara zuwa jikinta. Wani irin kallo ma suke yi mata mai kama da kyama. Kwala taji ta taho mata ta kuma kasa tareta. Innayo ta kawar da kanta gefe kawai don 'yarta ba karamin tausayi ta bata ba. Sai ta tuna mata da lokutan da ita Zaran take yi mata haka.

Cikin bacin rai Uwani ta daka musu tsawa bayan ta gama karantarsu da kanwarta. A ranta ta kissima irin bakincikin da zata ji idan nata 'ya'yan suka gwada yi mata haka. Ta sake jinjinawa hakurin Innayo.

"Kun wuce jikin uwarku taji duminku kun ji nata ko sai na taso muku?"

Jiki na rawa kuwa suka tafi wurinta amma a bayanta suka labe saboda tsawar Uwani ba don farincikin d'a ya ga mahaifiyarsa ba.

Karamar da yake babu hankali sai cewa tayi "hummm, Mummy ba kya wanka ko?"

Mai bi mata kuma ta ce "ba Aunty ta fada mana a gidansu Mummy ba..."

Mas'uda ce babbar, ta sa hannu ta buge bakin kanwarta tana mai cewa "ba ta ce kada mu fada ba?"

Ta dubi mamanta ta tabe baki "tare da Daddy muke. Ya ce ki zo." Ta kuma ce da kannenta "ku zo mu koma mota"

Salima ta hadiye nata fushin ta ce "ku zo ga kanwarku ku ganta. Sai mu ga da wa take kama"

Maryam har ta fara murna ta soma takawa wurinta sai ta fasa.

"Karaso mana"

"Aunty ta ce kada mu taba komai a gid..."

Mas'uda ta janyo hannunta tana gargadinta "ba ta hanaki surutu ba? Ni ku zo mu tafi kafin mu fara warin talauci"

"Ke???" Uwani ta yi musu tsawa a karo na biyu.

Zara sai kuka. Jikinta har rawa yake. Ta ruga gaban Innayo ta durkusa akan gwiwoyinta.

"Wane mutum Innayo? Waye zai buga kirji ya ce ya zama sanadin hawayen iyayensa kuma ya gama da duniya lafiya? Ki yafe min. Ki yafe daga kasan zuciyarki don girma da isa da tsarkin Mulkin Allah. Nayi miki rantsuwa idan yaran nan suka gwada min abin da nayi miki na sati guda zuciyata za ta buga. Kaicona. Ba zan iya addu'ar cewa Allah Yasa yarana su ji kaina kamar yadda nayi miki ba"

Hawaye Innayo take ita ma. Ta rike hannuwan Zara ta ce "na yafe muku ke da 'yan uwanki tun kafin ku roka. Babu komai a zuciyata game daku sai fatan alkhairi da albarkar rayuwar duniya da ta lahira."

Da hannu ta yafito 'ya'yan tasa suka zauna a gefen mahaifiyarsu. Da har sun fara matsawa don kada jikinsu ya gogi nata Uwani ta watsa musu kallon ku shiga hankalinku. Ana haka Hasiya ta fito daga bandaki daga ita sai daurin kirji. Fiye da rabin jikinta duk kumfa. Bala'i ya ciwota a bandakin na maganganun da suke tashi ta kasa tsayawa tayi wankan a nutse.

"Wace ce Anti?" Ta tambayesu rai a hade.

"Anti Laurat matar Daddynmu" Mas'uda ta bada amsa da sauri saboda tsoron tsawar Uwani. Fuuu....Hasiya tayi waje a fusace.

Innayo kuma ta dubi yaran ta nuna musu Zara "wace ce wannan a wurinku?"

Da yake rabonta da haihuwa bayan tayi ta ruguntsumin kwanika shekara biyar ne, babu wadda bata fahimci tambayar ba a cikinsu.

"Mummy ce" "Mummy" " suka amsa tare.

"Na san kuna zuwa Islamiyya. Mene ne hukuncin masu sabawa iyaye har su sanyasu kuka? Ina Allah zai saka shi?" Tayi tambayar ga manyan.

Maryam da Mas'uda sai da suka zaro idanu a tsorace sannan suka ce "wuta"

Uwani na jin haka hantar cikinta ta tsirga.

"Mu dai mun roki gafara kuma ance an yafe mana ko Zara?"

Zara ta murmusa don idanun Uwani sosai suka bayyana tsoratar da tayi. Innayo ma sai da tayi murmushi sannan ta ce da yaran idan ba wutar suke so ba kada su kara yin abin da zai bata mata rai.

A hankali suka shiga matsawa jikinta. A karo na biyu Salima ta sake nuna musu kanwarsu. Ba bata lokaci suka tafi. Tun suna dan ja baya har suka ware. Ganin haka Innayo ta ce da Zara sai ta tashi tsaye wurin dawo dasu turbar da ta dace. In ba haka ba nan gaba ba za ta iya tankawarasu ba. Kanta ta sake tunawa da yadda tayi ta ta rayuwar. Cikin rashin gajiyawa ta sake bawa Innayo hakuri.

A waje kuma Hasiya ce tsaye akan dakalin gidansu tana fuskantar Alh. Unaisu.

"Saboda ka kara aure sai ku koyawa yara tsanar mahaifiyarsu? Kaga irin kukan da Zara take yi kuwa? Hakkinta ba zai barku ba." ta kare da goge kwallar tausayin yayarta.

Alh. Unaisu ba shi da zabin da ya wuce yin murmushi bayan ta gama magana. Dalili kuwa shi ne tunawa da labaranta da ya kan ji daga Zara tun ma kafin su yi aure. Tana yawan fadin masifar Hasiya musamman idan aka taba nata. Bai taba zaton za ta damu da damuwar Zara ba duba da rashin jituwarsu. A nan dole ya godewa Hajiyan Fatakwal da ta zama sanadiyar komawar Zara gida.

"Dariya ma na baka?" Hasiya ta tambaye shi a hasale da taga yaki magana.

" Yi hakuri Hasiya kuma ina so ki saurareni game da Laurat da kin zuwana"

"Don kana auren yayata bani da hurumin son sanin dalilin karin aurenka. Rashin zuwa kuwa ni ban san me ya hadoku ba. Matsalata shi ne komai lalacewar uwa ko uba babu ruwan dayan wurin dasawa yaran kiyayyar dan uwansa."

Jajirtacciyar mace ce kuma kaifi daya babu karya ya ayyana a ransa. Sannan ya zauna ya yi mata bayannin duk abin da ya faru har zuwa yanzu. Domin kara horar da Zara da karya lagonta Hajiyan Fatakwal ta sanya shi mikawa Laurat uwargidansa yaran. Zaman Zara ne tuntuni yake karya matsayinta tunda ita bata haihu ba. Shi yasa da wannan damar da ta samu ta fito da makirci kala kala tana juya kan

jama'ar gidan. 'Ya'yansa da masu aiki kamar su kwanta mata saboda yadda take kyautata musu. Suka daina ganin girman kowa sai yadda ta ce. Hajiyan Fatakwal na ganin haka ta ce zama bai ganta ba. Da alama da abubuwan da take yi ba wai da kisisina ta dogara ba kadai ba. Shi ne ta ce ya dawo da matarsa tunda yaran ko su yanzu basa gaisarwa sai ta amince.

Tare suka koma ciki. Zara na jin muryarsa gabanta ya fadi. Ta tashi da sauri za ta shige daki. Alh. Unaisu da nasa saurin ya tareta zai karbi jinjirar ta karkace gefe guda tare da rankwafawa da nufin hana shi.

"Bana son sakarci Zara."

Cewar Innayo tana kallon kafafunsa da ya shigo mata har nan da takalma.

Kafar ya bi da kallo shi ma ya koma da baya ya cire takalman. Da ya dawo ya zauna Zara taki mika masa 'yar ta kuma ki kallonsa. Sai ma yaran da ta cewa su shige dakin su jirata.

Shi ma din sai bai bi ta kanta ba. Innayo ya fara gaisarwa sannan ya dora da ban hakuri akan rashin waiwayo iyalinsa.

"Matsayin aurenku nake son sani kafin komai." Shi ne abin da ta ce da shi.

Sai da ta fada ya auna ya ga lallai fa dole ayi tunanin ya daina auren.

"Aure yana nan Innayo. Ku gafarceni akan abin da ya faru" nan ya fada mata abin da ya sanar da Hasiya a waje "zancen da nake muku Hajiya ta ce kada na koma gida ba tare da Zara ba. Ta karbi kuskurenta na hukunta ta ta wannan hanyar akan abubuwan da take ganin halayya ce da bata son jikokinta su koya. Gyara ba zai yiwu da banzatar da matata a cikin halin danyen jego ba."

"Mu kam tsakaninmu da Hajiyarka sai godiya domin kuwa dawowar Zara gida ta haifi d'a mai ido." Inji Uwani.

Innayo sai ta yi musu inkiya da su basu wuri tana mai cewa "gata nan ku sasanta amma babu inda zata tafi yanzu kamar wadda bata da gata" ta kalli fuskar Zara don ta gani shin amsarta ta sami karbuwa ko kuwa son bin miji zai sa ta nuna bacin rai.

Suna hada ido murmushi da alamun godiya ta yiwa mahaifiyarta. Innayo ta cigaba da cewa "yadda ka bamu hakurin wulakanta min rayuwar 'ya da wasa da lafiyarta, zan so Hajiyar taka ita ma ta zo. Zara ta jima tana bata min rai tabbas, amma duk inda bacin raina ya kai akan halayyarta ba zan taba zuba ido ina kallo ana cin zarafinta ba. 'Yar talakawa ce ka aura amma darajarta tafi karfin in baka ita haka sikau kamar kwanakin da suka gabata basu faru ba."

Kai ya gyada tare da cewa "to" da saurinsa. Zai tashi Innayo ta ce a bashi jaririyar.

Zara ta dora masa ita a cinya tana aika masa da mugun kallo. Innayo dauke kai tayi don ko yaya dama ya dace Zaran ta nuna bacin ranta ko don gujewa maimaici idan yaga kamar bata damu ba.

Kurawa yarinyar idanu ya yi har sai da yaji kwalla ta taru.

"Allah Ya baki hakurin jinkirin ganin wannan rana Ummulkhairi. Allah Ya rayaki Yasa ki yi koyi da halin mai sunanki"

Innayo, Uwani, Salima, Hasiya da maijego Zara duk sai da suka yi mamakin wannan irin karamci da ya yiwa Innayo. Wasu cikinsu ma irin Hasiya da Uwani basu zata ya san ainihin sunanta ba. Ita kuwa Zara murmushin da tayi mai hade da dariyar farinciki su kadai suka yi nuni da cewa ta gama yafewa mijinta.

Su Innayo fita suka yi aka basu wuri. Ya kara bata hakuri da nuna mata cewa shi da ita da Hajiyarsa duk sun yi kuskure a baya. Sannan ba a gyara barna da wata barnar.

"Ba jimawa zan yi ba. Ga wannan ki rike. Anjima zan dawo da duk wani abu da ya dace ace nayi tun farkon haihuwar. Na baki dama ki zabi ranar da kike so ayi taron sunanta a gidan nan. Sai anyi za ki koma."

"Na cancanci haka kuwa Daddyn Mas'uda? Laifukana ga mahaifiyata suna da tarin yawa." Ta furta cikin kuka.

"Ki dauki duk abin da zamu yi yanzu a matsayin lallashi da ban hakuri ga Innayo."

"Kai kuma me kayi banda guje min da kayi..?"

"A bar tada zancen gudun nan mana maman Khairi."

Ai kuwa alkunyar da ya kira sunan 'yar tasu dashi ya matukar burgeta har sai da ta sake yin murmushi.

"Nima da laifina sosai. Ban cika masoyi ba tunda ban damu da daidaita tunaninki akan mahaifiyarki ba."

Bayan tafiyarsa Hasiya ta kebe da Zara kafin su tafi asibiti. Maganganun da ta saba yi mata a baya ta kara maimaitawa. Sai dai wannan karon sun sami gurbi mai kyau sun zauna a zuciyar Zara.

"Miji abokin rayuwa ne kuma mahadin rayuwa. Duk wanda Allah Ya zaba miki a matsayin miji, ki sani cewa alakar ta zarce ke da shi da 'ya'yan da zaku haifa. Aure haduwar dangi shida ce. Naki na uwa da uba, nasa na uba da uba, sai kuma abokan arzikinki da nasa. Idan aka sami matsala tsakaninki da guda cikin nasa ko shi da naki, wajibi ne sai ya taba jindadin rayuwar auren mutum. Musamman abin da ya shafi dangi domin su kawaye ko abokan arziki ana iya canjasu. To amma fa duk wanda kika kawo a matsayin makusanci na jini ko na abota, dole ke ce za ki nunawa miji ko shi ya nuna miki mahimmancin dayan a gare shi. Wanda ka mutunta, abokin zamanka ya tayaka mutuntawa. Wanda ka tozarta ko ka wulakanta, wani sai ya fiki ci musu zarafi. Cikin mutanen da na ambata, UWA ita ce tubalin komai. Innayo uwa ce a gareki. Ina fata kin gane me nake nufi."

"Mun gane, kuma mungode."

Tare suka juya suka ga Uwani. Ta karaso ciki ta dubi Hasiya,

"Meye za ki bata shawara ita kadai banda ni?"

"Allah Ya huci zuciyar metiron" cewar Hasiya tana dariya.

"Kin raina ni. Amma muje zuwa. Ba ciki gareki ba? Allah Ya kaimu ranar fafe gora in..."

"Kada ma ki karasa..." Innayo ta shigo cikin dakin ita ma "idan ki ka ci zalin auta rama mata zanyi la'ada waje"

Dakin kaurewa ya yi da dariya kafin kuma su tashi cikin hanzari su cigaba da shirin zuwa asibiti.

***

Tunda Abbati ya san Asabe ta tafi wurin Munzali, Alh. Rabi'u na tafiya ya haye sama. Wanka yake son yi ya dan gasa jikinsa. Dukan da ya sha a police station da fadansu da Shazali sun sa jikinsa yin tsami. Su Baaba Mari ma dakunan da aka saukesu suka shiga. Fito da komai fili da aka yi yasa zukatansu sun sami sukuni. Abin da ya rage yanzu shi ne kawai a tabbatar da cewa sun nesanta daga wannan rayuwa har abada.

Takun Abbati bai sa Hanne yunkurin tashi ba har ya hawo. Gabansa sai da ya yi mummunar bugawa da ya ganta zaune da jajayen idanun da kuka ya rina. Cikin mutuwar jiki ya karasa hawa ya zo gabanta ya zauna shima jingine da bango. Muskutawa tayi ba tare da tunanin komai ba sai kyankyamin abin da taji game da shi.

Sanin cewa za ta iya tona masa asiri bai hana shi yin murmushi mai ciwo ba. Da kansa ya ja jiki ya sake bada tazara a tsakaninsu.

"Zamanki a nan ya nuna min cewa kin ji komai"

"Naji" ta bashi amsa a dakile.

"Ki saki ranki Hanne. Babu sauran bacin rai ko fargabar da ta rage min a dalilin wannan abu. Duk abin da za ki yi ba komai bane illa tishi akan wanda iyayena suka yi. Allah na sabawa, fargabar ko Ya karbi tubana ya danne duk wani abu mara dadi da ya sameni a sakamakon abin nan"

Gashi dai a hankali yake maganar, amma kalamansa ba karamin haushi suka bata ba. Ta tashi tsaye tana masifa.

"Kana nufin bacin raina ba shi da mahimmanci a wurinka? Kodayake dama ba tun yau na san cewa ba ka sona ba."

Tsareta ya yi da ido ya ce "tsakaninki da Allah ke kina so na?"

Bata zata zai yi mata irin wannan tambayar ba. Sai ta sami kanta da bude baki tana rufewa. Shi kuwa bai yi mamaki ba.

"Kada ki tuhumi zuciyata don nima ba zan tuhumi taki ba."

Kuka kawai ta fashe da shi. Ranta a jagule da bakinciki. Abubuwa da dama ne dankare a zuciyarta wadanda suka haddasa mata bacin rai.

Abbati sai ya mika mata hannu. A zatonsa za ta sake nuna kyama. Sai yaga ta miko nata. Ya rike hannunta suka sauka kasa. Baya son sake kwana da komai a ransa. Idan ta kama duk wani nauyi da hakki ya daidaita shi a yau to zai yi domin gobe ta zama goben dake tattare da budewar sabon shafi. Dakin da su Mal. Sa'idu suke ciki ya kwankwasa tare da yin sallama. Mal. Inuwa ne ya amsa don shi Mal. Sa'idu har ya soma gyangyadi. Suna ganinsu tare suka tashi zumbur kowa ya zauna.

"Abbati fada mata kayi?" Mal. Sa'idu ya tambaye shi yana hankalinsa a tashe "me ya kai ka? Wannan sirrin ai tsakaninka da Allah ne"

"Baba ku yi hakuri." Ya rufa mata asiri bai ce tsayuwa tayi ba bayan ance su tashi ita da Habu.

Zama suka yi akan kafet suna fuskantar gadon da su Mal. Inuwa suke kai a zaune. Abbati ya dubi Hanne ya nuna mata iyayensu,

"Tsayin shekarun da muka dauka a matsayin ma'aurata bisa biyayyar iyayenmu bana jin akwai wanda ya taba damuwa da son sanin ainihin bukata da burinki. Yau gashi kin san abu mafi muni a kaina. Ina so ki yiwa kanki adalci a gaban wanda ya hadamu auren nan ki fadi abin da yake ranki"

"Kamar yaya?" Ta tambaye shi saboda kanta ya kulle ta kasa fahimtarsa.

"A wane matsayi ki ka dauki aurena a da da yanzu?"

Sunkuyar da kai tayi. Mal. Inuwa ya ce kada ta cuci kanta suna sauraronta. Kasa magana tayi har lokacin. Sai da Mal. Sa'idu ya hada da jan idonsa mai sa ayi ko ba a so sannan ta magantu a tsorace.

"Na so auren nan duk da cewa hadamu aka yi. Nayi ta kokarin ganin cewa mun zauna kamar wadanda suka yi auren soyayya amma ban samu ba. Babu abin da na nema na rasa a gidan nan. Sai dai kai da nake zamanka duk kokarinka na sauke hakkina bai hanani jin kamar nesa muke da juna ba. Ra'ayi da tsarin rayuwarmu duka ba iri daya bane. Ko hira muke akan abu daya fuskar da muke kallonsa ta bambanta. Shi yasa tun ina kokarin ganin na shawo kan matsalar har na hakura."

"Ba laifinki bane. Laifin rayuwar da nake yi ce wadda ta hanani ganin aibun nawa tsarin. A ganina ci, sha da sutura da sauran 'yan abubuwan da nake yi sun isa su gamsar dake" cewar Abbati.

"To wai ni yanzu mene ne matsalar? Banda tashin hankalin jin mummunan sirrin mijinki kina son rabuwa da shi ne?"

Sunkuyar da kai tayi da sauri. Abbati ya roki Mal. Sa'idu da ya sassauta mata domin tana da damar nuna bacin ranta. Mal. Inuwa kuma ya ce ta fadi abin da take so shi kuma ya yi alkawarin tsaya mata.

"Babu farinciki a cikin gidan nan. Zaman hakuri kawai muke yi cikin wadata amma kowa rayuwarsa daban. Kudin shi ya rikeni har na kai yanzu. Amma tunda na san silar samuwarsa, wallahi gara min rayuwar kauye da nan. Don Allah Baba ina rokon arzikin komawa gaban iyayena. Zamanmu a lokacin da ban san sirrinsa ba ma bai yi min dadi ba balle yanzu?" Ta daga kai a hankali ta kalli Mal. Sa'idu "Baba ku gafarceni. Abin da naji ba zai taba fita daga zuciyata ba. Ba zan iya zama gida daya da Yaya Abbati da Munzali ba. Zuciyata cikin zargi za ta dawwama matsawar zan gansu a inuwa daya. Nayi imani kuma ba zai taba barin Munzali a kan kowacce mace ba."

Kimamin mintuna biyar ne suka wuce kafin Mal. Sa'idu ya ce "Abbati rubuta mata takardarta. Gobe in sha Allahu zamu tafi tare da ita."

Jikinsu duka su biyun ya yi matukar sanyi. Zaman sama da shekara goma duk rashin dadinsa dole mutum yaji wani iri lokacin rabuwa. Rayuwa suka yi babu duka babu zagi. Babu rashin kunya babu fitsara. Sai gidadancin Hanne da wauta da kuma rashin soyayyar Abbati. Amma su biyun babu wanda yake nufin dan uwansa da sharri. Matsalarsu guda ita ce rashin wannan karsashin da zai sa mutum ya shiga ranka ko babu soyayya. A takure suke da juna, kowa yana gwada sauke hakkin dan uwansa a iya damar da Allah Ya bashi. Irin wannan zaman musamman tunda babu yara sai mutum yaji kamar yana kurkuku. Arziki da wadata basa cike gurbin bukatar zuciya na son samun abokin rayuwar da ya dace da ita.

Abbati ya jima da sanin wannan shi ne kuma dalilinsa na amfani da wannan damar wurin sauwakewa Hanne maimakon neman ta zauna. Idan ya zauna da ita yanzu

cutar sai tafi ta da. Domin yanzu aure baya gabansa. Akwai abu mai matukar mahimmanci da ya kamata su fara yi kafin suyi tunanin zama da mata.

***

"Baka ganin dazu kayi amfani da kausasan lafuza akan mahaifinka? A haka kake so ka ja ra'ayinsa wurin sauke akidar da yafi shekara arba'in da biyar a kai?"

Asabe ce tayi maganar tana zaune akan kujera yayinda Munzali ya takure a kasa. A haka tazo ta same shi dama.

"Ki gafarce ni amma ko kalmomi na basu dace ba ina ganin bai kamata ki ga laifina ba."

"Haka ne. Bamu koya muku ba sannan bamu kaiku inda za ku koya ba." Da bai ce komai ba sama da kada kansa gefe ta fahimci amsarta tayi daidai. Tambaya take so tayi masa amma tana tsoron kada su karke kamar yadda ya yi da mahaifinsa. Sai da taga yana shirin tashi ta ce,

"Munzali ka fada min tsakani da Allah wane irin so kake yiwa Abbati. Na san ya kyautata maka sosai. Amma anya saboda wannan dalilin kadai ya dace ka fadawa Alhaji maganganun da ka fada dazu?"

Taune lebensa ya yi gami da rufe jajayen idanunsa. Yana ganin idan bai yi da gaske ba da wuya ya wayi gari saboda zafin zuciya. Me yasa kowa yake yi masa wannan tambayar ne? Ko dai abin da suke zargi game dashi gaskiya ne? Shin mene ne ainihin abin da yake zuciyarsa?

"Zan baki amsa idan na nemota in sha Allahu."

"Munzali?"

"Kiyi hakuri Asabe."

Daga haka ya janyo filon guda daga kan kujera ya ajiye akan kafet ya kwanta a kai. Ko minti goma bai yi vmba bacci ya dauke shi.

***

Da gudu Sauda da Mardiyya suka fito tarbarsu Mami Khadija. Mardiyya harda kukan ganin kafar Suhaib.

"Yaya accident kayi ne?" Ta tsare shi da tambaya tana tattaba kafar.

"Buguwa ce Mardiyya"

Sauda ta ce "Da me?"

"Ku muje ciki" Farha ta katse su tana bin bayan Mami.

Tun tasowarsu daga Kano Mamin ta canja. Su duka sun san wani abu ya faru kuma yana da nasaba da babansu tunda suna tashi aka sanar dasu sun fita tare.

Alh. Tahir bai shigo gidan ba sai bayan la'asar. Yanayinsa ya nuna yana cikin tsananin tashin hankali. Bangarensa ya wuce yau bai tsaya jiran kowa fitowa ayi masa sannu da zuwa ba. Sauda da Mardiyya ne kadai ya san ko ya tsaya zasu iya fitowa.

Sam bai kula da Mama Nasima dake tsaye a bangaren dinning table da tray a hannu ba sai da tayi magana.

"Diya duk gajiyar ce ka shigo haka babu sallama?"

"Uhm" ya amsa kamar baya so yana mai cigaba da tafiya hanyar dakinsa.

"Ina ka wuce ne? Nayi zaton tare ku ka taso dasu."

Maimakon amsa sai ya tsura mata idanu yana kallonta daga sama har kasa. Ya tuna cin mutumcin da suka yiwa Mami shi da ita a dakinsu. Ya kuma tuna cewa ita ta bayar da shawarar a cirewa Mamin mahaifa kuma ya karba. Tirr da Allah wadai ya yiwa kansa. Tabbas yana daga cikin bambancin halittar namiji da mace son tarayya da mutum sama da daya. Hakan iko ne da ayar Ubangiji SWT. To amma shi wane irin mutum ne da bai san kawaici ba? Me zai sa ya yi masha'arsa a cikin gida da matarsa da 'ya'ya? Be tsaya nan ba duk gatan da Allah Ya yi musu na damar karin aure amma yake yawon bin mata kamar bunsuru.

"Lafiya kuwa Diya?"

Muryar Mama Nasima ce ta katse masa tunani. Ya yi firgigit ya dubeta sannan ya ce ta fita ta kirawo Mami Khadija da Jiddo.

"Kayi musu waya mana" ta ce tana dan murguda baki.

"Ki fita ki yi abin da na saka ki kafin na fito daga wanka"

Da wane bakin zai yiwa Mami magana shi da ita a waya?!

Cikin minti ashirin ya gama kimtsawa sannan matansa duk sun hallara a falon. Ya dauko takardu biyu wadanda ya rubuta ya mikawa Jiddo daya, Mami Khadija ma daya. Mama Nasima ta cika fam da ta tabbatar biyu ne.

"Ina tawa? Alhaji me yasa sam baka son yin adalci ne?"

Za ta kara magana Jiddo ta kwarma wani irin ihu wanda ya fita har wurin masu gadi. Ta tashi tana rawar jiki ta kawo masa takardar gabansa ta saketa a kasa.

"Wallahi, na rantse, wallahi babu inda zani." Ta nuna kanta "ni za ka saka? Ni din? Ko don kaga bana haihuwa?"

Da sauri Mama Nasima ta koma ta zauna nata jikin ita ma yana rawa. Ta kalli Mami Khadija a fakaice amma ta kawar da kai don bata ma son sanin me takardarta ta kunsa.

Sai da Jiddo ta gama hargaginta sannan Alh. Tahir ya zaro wayar Danliti daga aljihunsa.

"Ki godewa Allah baki haihu ba don da yau babu abin da zai hanani bawa danki wannan wayar" ya fada yana mika mata.

Hannu ta noke ta ce "wayar waye?"

"Na zata za ki fini sani. Amma tunda da alama kin manta bari na bawa yayarki Nasima ta karanta"

Kafin ya rufe bakinsa ta karbe wayar.

"Whatsapp za ki bude. Ki nemo sunan da aka sa Kaduna account"

Jikinta ya fara sanyi ta nemo sunan. Tana bude chat din gabanta ya yi mummunan faduwa. Ba hirar ta karanta ba. Hoton farko da idonta ya kai gareshi kirjinta ne tsirara da ta turawa Danliti.

"Na shiga uku na" ta furta a dimauce tana kallonsa "wallahi. Kaga ni. Ban san..."

"Adana zancenki don ba zai min amfani ba. Ina fata dai kin tuna waye"

Nan fa ake yinta. Samari nawa ne suka yi irin wannan hirar dasu? Ai ba za su kirgu ba. Don sun fi wadanda tayi mu'amalar zahiri dasu.

Mama Nasima dai jiki sai bari yake. Ta gama firgicewa don ko ba a fada ba ta fara harbo inda jirgin ya dosa. Dama ta jima tana zargin Jiddo tana yawo sai dai bata da shaida ko guda.

Jiddo tasowa tayi tazo gaban Alh. Tahir tana kuka ta fara cewa sharri ne ake son yi mata. Jikinta ne ta yarda amma bata san waye ya dauka har ya tura ba. Rainin wayon nata ya sosa masa zuciya kuwa. Yana son nuna mata bacin ransa sai ya tuna ba shi da wannan hurumin. A takaice ma ya san cewa sakamako ne ya soma girba tun yanzu. Ya ma godewa Allah da ba 'yar cikinsa bace da bai san inda zai tsoma ransa ba. Janye kafarsa ya yi daga rikon da tayi masa ya ce

"Idan kin gama ganin sakarcin naki bani wayar domin ana bukatar amfani da ita wurin gurfanar da Danliti makanike a kotu"

Kiris ya rage ta kwarma ihu lokacin da ta maimaita sunan da karfi.

"Danliti? Kotu? Wallahi ni dai babu ruwana ko me ya yi"

Tsaki kawai ya yi. Bai kara tanka mata ba ya dubi Mami Khadija da Mama Nasima.

"Khadija ga sakin da kika bukata kamar yadda na alkawarta miki zan yi. Alfarmar da na roka ta ki zauna kafin komai ya kammala na gidan kawai nake nema"

"In sha Allah" ta bashi amsa gami da mikewa.

"Me za ki ce da yaran?" Ya tambaya a raunane.

"Idan ka gama ka same mu a falona"

Ficewa tayi abinta don bata bukatar sanin ragowar me zai tattauna da sauran matansa.

Tana fita Mama Nasima ta cigaba da tsuma. Ita dai ta san indai ba mazan da ta sani kafin aurenta ba, babu wani da namiji da za a danganta ta dashi. Daga ranar da ta haifi Mardiyya ta san cewa gantali ba nata bane. Shi ne ta fada neman kudi ka'in da na'in. Laifinta guda a yanzu wanda shi ma tana ganin namiji zai iya saki dominsa. Shi yasa ba bata lokaci ta zamo daga kan kujera ta hau bashi hakuri.

"Me kika yi ke kuma?" Ya ce da dan murmushi. Ya dade da sanin tana yi. Yana dai kawar da kai ne saboda ganin damarsa.

"Kudi" ta ce tana zufa " idan kayi ajiya ina dauka Diya. Ina maka lalube a jaka da walet.

"Tashi ki tafi."

"Ni dai babu sakin ko? Idan ka sakeni ina zani?"

"Babu. Jeki Nasima. Ina bukatar hutu."

Ai ko bai ce ba dole ta fita. Bata son jimawa kada a fito da dalilin sallamarta. Ita da shi duka sun manta da Jiddo dake sharbar kuka. Sai da ta tafi ya ce da ita,

"Duk abin da na saka a bangarenki da wanda na baki ki tattara ki tafi dasu. Wannan shi ne abu na karshe da zan iya yi miki"

***

Su Farha ne zaune a kasa iyayensu akan kujera sun yi jigum. Alh. Tahir ya rasa me zai ce. Mami Khadija sai da ta tabbatar ba zai iya magana ba saboda tsoron halin za zasu shiga sannan tayi magana.

"A matsayinku na musulmai masu hankali na san kun san kaddara. Wannan kaddarar ita ce ta kawo mu wannan rana da aurena da mahaifinku ya kare."

Sauda da Mardiyya suka fashe da kuka. Su Suhaib da suka san dalili su ma babu wanda zuciyarsa bata kadu ba.

"Mami me yasa? Don Allah ku yi hakuri ku koma" cewar Mardiyya.

"Ya Suhaib ba za ka ce komai ba kana jin abin da take cewa" inji Sauda.

Alh. Tahir sai ya hau gumi. Tunaninsa abin da zai ce shi ne dalilin da ya san yaran zasu yi ta tambaya. Mami Khadija ce tayi belinsa da dabaibayin da ya zargowa kansa tun farko.

"Aure zai yi. Kun kuma san cewa ba haramun bane. Wacce zai aura din ce dai nayi rantsuwar ba zan taba zama da ita ba. Yakumbo kuma ta ce tunda har ya yi magana da iyayen yarinyar ita ma bata yarda a janye ba. Rabuwarmu ita kadai ce maslaha a yanzu."

"Wace ce?" Sauda da Mardiyya suka tambaya a tare.

Farha wadda amsar Mami ta farantawa rai domin bata son kannenta su san halin babansu ce ta bada amsa.

"Yumna ce. Kawata Yumna"

Sauda da Mardiyya ko kallon uban basu sake ba suka fice daga falon suna kuka. Mami Khadija ta dubi su Lilu da ko tari basu yi ba ta ce,

"Ina rokon arzikin ku rufawa mahaifinku asiri a wurin kannenku. Fushinsu yanzu na dan lokaci ne zai wuce sabanin idan suka san abubuwan da ku ka sani"

Daga nan ta fada musu zancen tashi da zasu yi bisa umarmin baban nasu. Basu ce masa komai ba suka tashi suka fice su ma.

"Na gode Khadija. Na gode kwarai da gaske. Ina fatan Allah Ya yi miki sakayya da mafificin alkhairi"

Dakinsa ya koma yana tunanin yadda zasu kwashe da iyayensu idan suka ji sakin. Ran kowa zai baci to amma wuyarta a kwana a tashi, komai me wucewa ne.

***

Gwaggo Jummai mahaifiyar Hanne kuma kanwa ga su Mal. Sa'idu ta shiga ta fito don a mayar da aurenta da Abbati abu yaci tura. Sati guda kenan da komawarta gida. Da ta kasa shawo kan 'yarta ta amince a gyara auren sai ta koma wurin yayyenta. Goyon bayan da taga sun bawa Hanne ranar da tazo gidan ya dagula mata lissafi. Abin har ya kaita ga fitowa tsakar gida tana yada magana.

"Anje an gama kullo munafunci an kaso auren 'yata."

Nan da nan tsakar gida da cika ta jama'ar gidan. Dama tun dawowarsu Baaba Mari da fitowar zancen mutuwar auren ake ta kus-kus a kowacce kusurwa. Don ma ita Gwaggo Jummai ba a gidan take ba. Da bakinciki sai ya kusa buga mata zuciya. Da Hanne ta koma gida tayi ta kokarin samun Abbati a waya sai dai bisa umarnin Mal. Sa'idu baya dauka. Yace masa ya bari su zasu yi mata bayani ba tare da tonon asirinsa ba. Suna gudun kada ya fadi wani abin da zai iya darsa mata zargi. Ko kuma ta tilasta masa mayar da auren saboda ganin girmanta. Sai taki zuwa gidan amsa kiran yayanta. Kullum tana faman kiran Abbati. Ga Hanne taki cewa komai. A

takaice ma dai tafi walwala. Ga uban kayan abinci da kudi da ya bata. Zuciyarta fes tunda ta san aurensu kam ko a lahira bata muradinsa. Zaman wa da kanwar yafi mata dadi.

Cikin rumfarsa Mal. Sa'idu ya ce ta dawo su yi magana ta ki.

"Ba zan shigo a ninke ni baibai ba. Ni gabadaya zantukan da kuke yi kai da Yaya Inuwa basu da ma'ana. Ai na jima da sanin Deluwa tana son saka 'yarta a gidan Abbati. Kuna fakewa da rashin haihuwarta bayan ni na san kwadayi ne da hassada."

Deluwa tafa hannuwa tayi don dama itama a matse take da son sanin dalilin sakin. Da canjin da ta gani farat daya a wurin murdadden maigidanta.

"Bana fada da kanwar miji Jummai. Ba don haka ba da kin ji ta wuraren da 'yarki ta gaza har Abbati ya kasa zama da ita."

"Zan saba miki Deluwa" ya fada yana yi mata kallon da yasa ta rufe baki ba shiri. Kanwarsa ya kalla da 'yan ganin kwaf ya ce "rabuwar auren bata da alaka da kowa a gidan nan. Hasali ma 'Yashshafa da kike magana a kanta na riga nayi mata miji"

Deluwa ta san bashi da labarin Sha'aib (Suhaib) na Kaduna. Shi yasa cikinta ya wani murde da taji me yace. 'Ya'yan 'yan uwansa maza da suka rage babu wani mai dan romon da za a sha a cikinsu. Magana ta so yi ya ce tana kara bude baki a bakin aurenta. Haka ta cije lebe ta bar wurin cikin bacin rai.

Tafiyarta ke da wuya Hanne ta shigo. Bata san fitar Gwaggo Jummai ba sai da kaninta ya fada mata. Shi ne ta biyo sawu. Ta iske sun koma rumfar Mal. Sa'idu. Hakuri dai suke ta bata taki yarda saboda har yanzu bata ji kwakkwaran dalili ba.

A yau yawan kallon Hanne ya yi mata rana. Zama tayi ta dubi iyayenta. Mal. Inuwa duk ya fita hayyacinsa saboda tsoron kada karshe Mal. Sa'idu ya rasa zabin da ya wuce fada mata gaskiya. Baaba Mari kuwa dama ko uffan bata ce ba.

"Gwaggo ki yi hakuri. Sakin nan ni na nema. Munje asibiti likita ya ce akwai wani abu a jininmu wanda ya sa da matukar wuya mu haihu tare. Masu irin jininmu basa zama da juna. Shi yasa nake yawan bari. Ya so.mu cigaba da zama. Ni kuma gaskiya ina gudun cinye kuruciyata babu d'a ko daya"

Tunda ta bude baki sai yanzu wani abu da ya tokare wuyan Mal. Sa'idu ya sauka.

A take fuskar Gwaggo Jummai ta koma kalar tausayi. Ta girgiza kai tana cewa "ban san abin haka yake ba. Yaya ku gafarce ni. Tabbas lalura idan ta shafi haihuwa maslaha ake nema. Amma me yasa baki fada min ba?" Ta kare da tambayar Hanne.

Hanne bata yarda ta kwashe laifin karyarta ba. Idan bata gyara zancen ba zasu dade Gwaggonta tana mita. Nuna mata tayi basu dade da yin gwajin ba. Abbati yaki yarda ya saketa da ta nema. Shi ne ya kira iyaye don ayi sulhu. Su kuma suka goyi bayanta.

Gwaggo Jummai ta dinga bada hakuri. Da Baaba Mari ta tashi har daki ta bita tana ta rokon tayi hakuri akan kalaman da ta dinga yi. Ita kuwa da ta san cewa ita ce ta karu da abin da ya faru, da wuri ta nuna komai ya wuce. Bayan tafiyarta ta kira Abbati ta sanar dashi. Ta kuma jaddada masa ya yiwa Hanne godiya sannan ya cigaba da tuba.

***

BABI NA ASHIRIN DA SHIDA.

Zaune yake gaban likita na goma sha uku cikin jerin likitocin da ya ziyarta domin magance matsalarsa. Amsa yake nema don ya san a wane babi zai ajiye lafiyar kwakwalwa da tunaninsa.

Ya gama bayani tsaf akan yadda ya dauki Abbati da zargin da mutane makusantansa suke yi masa kamar yadda ya yiwa sauran likitocin. Ya kare da cewa,

"Bayani nake so a mahanga ta addini. Idan bani da rabon samun rahama ne saboda irin tunanina gara..."

"Subhanallahi" cewar likitan da sauri "Munzali wannan magana taka bata dace da dan musulmi ba. Ni ba malamim addini bane. Amma tabbas har yau ban bar gaban malamai ba. Na kuma godewa Allah da malumanmu na yanzu suka kasance masu ilimin boko wanda yake taimaka musu wurin warware matsalolin da suke tafe da zamani. Idan za ka iya gobe ka zo nan da la'asar. In sha Allah zan kai ka wurin Dr. Abdallah Saraki. Kawu ne kuma siriki a wurin abokina Dr. Huzaifa."

Tun bayan zaman nan da aka yi a gidan Abbati sati biyu da suka wuce, sai yau Munzali ya yi murmushi. Da ya tashi zai tafi likitan nasa ya ce su taho tare da Abbati da iyayensa.

"Hakan ne zai sa kowa ya sami gamsuwa akan amsar da zai baka"

Yana shiga mota ya kira Abbati. A lokacin shi kuma yana cikin ofishin Alh. Sadisu. Kiran na shiga ya dauka da sauri.

"Munzali lafiya dai ko?"

"Lafiya kalau. Kana gida ne?"

"Ina office din Alh. Sadisu ne. Yanzu muka dawo daga duba Abdul"

Munzali yaji kunya ta kama shi. Ba irin lallashi, fada da nasihar da Abbati bai yi masa ba amma kememe ya daina yarda ko zaman minti biyar suyi a wuri daya. Abbati ya yi fushi sosai saboda ya fuskanci akwai abin da yake boye masa. Shi kuma baya son fada saboda a take Abbatin zai soke masa zargin. Gashi zuciyarsa ta riga ta fara rawa akan maganganun iyayensa. Ya zama wajibi ya san me yake ciki.

"Kwatanta min wurin zan zo na same ka"

Minti ashirin ya kaishi. Suka zauna tare da Alh. Sadisu. A yau godiya mai tarin yawa ya sake yi musu sannan ya koma kan batun abubuwan da yaji a police station din.

"Kuna ganin da gaske zaku iya dainawa? Nayi bimcike ance da wahala rabuwa da wannan dabi'ar. Idan Abdul ya tashi a haka ban san yadda zan yi ba"

Munzali bai yi kasa a gwiwa ba ya fada masa shirinsu na zuwa asibiti a Italy. Rashin zuwa a duba lafiyarsu da kuma neman hanyar rabuwa da lalurar har abada ba karamin kalubale bane ga tubansu. Ita wannan dabi'a tana tattare da matsaloli da yawa ga lafiya. Ciki kuwa harda kasa jurewa rashin samun biyan bukata ta inda aka saba. Wannan abu ya kan fi karfin furtawar baki da yakinin zuci. Wani duk dauriyarsa idan abin ya ciwo shi sai ya biya bukatar yake jin dadi.

"Abdul yaro ne. Sake komawarsa ba abu bane mai wahala. Mafi a'ala shi ma ka kai shi asibiti" inji Abbati.

Godiya ya yi musu da zasu tafi da alkawarin tsaya musu a duk lokacin da suke da bukatar taimakonsa.

"Magana nake son muyi Abbati." Munzali ya ce da suka fito waje.

"Dama jikina ya bani tunda ka kira. Ka gaji da yajin ne kazo biko da kanka?"

Da sauri Munzali ya ce "don Allah ka bar amfani da kalmar yaji da biko kamar wasu mata da miji"

Abbati na jin haka ya gano inda matsalar take. Motarsa ya bude suka shiga ya tayar. Gida ya wuce kai tsaye. Yanzu babu kowa daga kuku sai Maigadi. Iya Kande bata dawo ba tun tafiyar Qibdiyya gida.

A waje suka zauna wurin wasu kujeru da 'yar rumfa. Munzali ya fadawa Abbati dukkanin damuwarsa.

"Na san za ka iya cewa ba komai bane. To amma hankalina ba zai taba kwanciya ba. Don Allah gobe ka zo muje wurin malamin."

Kamar uwa da d'a. Tausayin Munzali ya kama Abbati sosai. Don gudun kara masa damuwa sai bai yi masa yadda ya saba ba idan yana cikin yanayi mara dadi. Lokutan da yake yi masa fada ko nasiha da rarrashi har sai ya sauko.

"Allah Ya kaimu goben. Dama nima ina son yi maka magana akan mu nemi fatawa kan dukiyarmu. Goben sai muje masa da komai muji me zai ce."

Munzali ya mike zai shiga ciki. Abbati ya kai hannu zai taba kafadarsa don ya tsaya sai ya fasa.

"Munzali."

Juyowa ya yi fuskarsa duk ta rame kamar ya dade yana ciwo.

"Ina so ka sani cewa ko yaya makomar alakarmu ta kasance gobe ba zan taba barinka ba"

"Ko da ya tabbata wannan kazantar bata barni ba"

"Zama da kazanta fa sai ka so. A matsayin kani kuma amini na daukeka. Banda an riga an dasa maka wani irin tunani a zuciyarka da na fada maka matsayinka a wurina. Yanzu kuwa ina magana za ka iya tsoron kada nace gobe zan kawo sadaki"

Murmushi suka yi a tare sannan kowa ya nufi gidansa.

***

Washegari basu hadu da safe ba. Munzali ya tafi gida dauko su Asabe. Ya sami gidan a cike makil. Larai da su Fati sun zo dukkaninsu kwai da kwarkwata. Gaban Innayo ta zauna ta roki gafararta na rashin kyautawa da tasa 'ya'yanta yi mata. Ta karbi laifinta kamar yadda 'ya'yanta su ma suka karba. Aka yafi juna tare da alkawarin sabunta zumumci.

Hasiya ce kadai bai samu ba. Hakan ya yi masa dadi domin yana jin kunyarta saboda rashin samun sukunin zuwa duba Abbas. Uwani kuwa tana jin muryarsa ta fito ta tare shi a gefe. Mita ta soma yi masa na rashin kiranta da ya ce zai yi domin ta duba Qibdiyya. Hakuri zai bata sai ta kula da ramar da ya yi. Mantawa tayi da fadan ta koma tambayarsa damuwarsa.

"Na manta gidanmu ba irin da bane, da na sani ban zauna abubuwa suna ta damuna ba a cikin kwanakin nan" yace ba tare da wasa a fuskarsa ba.

"Komai mai wucewa ne Munzali. Tunda muka dinke da Innayo kaima kawai ka jira lokaci. Kafin ka farga zaka ga ya koma tarihi. Ko ka bayar dashi ko rike abinka a zuci"

Karfin gwiwa ya samu daga gareta wadda da ita ya yi amfani wajen jajircewa iyayensa suka bi shi.

***

Sheikh Dr. Abdallah Saraki ya saurari jawabin Munzali da Abbati da dukkan nutsuwar da ake bukata daga malami. Labarinsu gabadaya izina ce kuma babban darasi ga iyaye da su kansu 'ya'yan.

(Ni din ba Malamar addini bace. Daliba ce mai koyo har yanzu. Bakin gwargwado ina nazari da bincike kafin na kawo wani batu mai girma cikin labaraina. A nan ma na duba matsayar malamai na kuma hada da tawa fahimtar. Saboda haka idan mai

karatu yaci karo da abin da ya sabawa nasa ilimin, kada a manta cewa wannan labari ne. Abin da ya shafi fatawa a nemi sahihancinsa a wajen maluma. Rabbi Yasa mu dace da khairi duniya da lahira. Amin)

Da Alh. Rabi'u ya ga zai fara magana, hankalinsa kacokan ya mika masa. Yana so yaji malamin ya wanke shi daga abin da Munzali ya ce, wato yana da hannu a cikin lalacewar rayuwarsa.

Dr. Abdallah ya fara jawabinsa da sallama tare da addu'ar bude taro ko wani zama da za a tattauna abu mai mahimmanci. Sannan ya karkare da yiwa fiyayyen halitta salati SAW.

"Da farko zan fara da yaba muku tare da kara muku karfin gwiwa. Duk wanda ya nufi Allah SWT da kyakkyawar zuciya, to ya sani cewa Allah ba zai tab'ar dashi ba. Saboda haka ku cigaba akan niyyarku. Ko a duniya ko a lahira sai kun yi mamakin falala da girman Mahaliccinmu. Zai baku fiye da rokonku. Ya yafe fiye da tubanku domin Shi din gagara misali ne wajen jink'ai da tausayi."

Ya gyara zama saboda su san cewa zancena gaba yana da mahimmanci.

"Munzali ina so kai da iyayenka ku sani cewa tsaftatacciyar soyayya ce tsakaninka da Abbati. Irin soyayyar da Allah SWT Yayi alkawarin inuwar Al'arshi rana gobe kiyama ga ma'abotanta. Wato mutum biyu masu kaunar juna domin Allah Shi kadai."

Munzali ya hau murmushi yayinda Abbati ya dinga kiran sunan Allah a iya a lebbensa.

"Malam baka ji inda ya ce yana son Abbati fiye da kowa ba? Ma'ana fa harda mu. Babu jin nauyi ko kadan yake nuna min cewa yaron nan ya fini a wurinsa." Cewar Alh. Rabi'u yana huci.

Dr. Abdallah ya ayyana a ransa cewa lallai Alh. Rabi'u akwai gagarumin gyara a lamarinsa.

"Aikin sab'o sakamako ne na raunin dan Adam. Shi kuma rauni ana gane shi ne daga zuciya. Idan aka haneta ga barin abin da take so sai ta ce ta kasa. Idan aka umarceta da abin da bata so nan ma ta nuna gazawarta. To da zarar mamallakinta ya biyewa ra'ayinta ba tare da dora shi a mizanin hankali, dabi'a da addini ba, dole nadama ta saukar masa watarana. Alh Rabi'u, ka yi godiya muddin rai ga Allah da Ya bawa yaran nan damar fin karfin zukatansu a lokaci irin wannan. Gurbacewar zamanin nan ta kai ta kawo. An kawata zina ana tallatawa mutane. Tserewa tarkonta wallahi sai wanda Allah Ya azurta da jarumar zuciya. Wadda tana so din kuma tana tsoron mummunar makoma. Zuciya ta ma'abota tsoron Allah da kwadayin rahamarSa."

Asabe ta dinga gyada kai tana yiwa Munzali da Abbati kallon tausayi. Alh. Rabi'u kuwa cikin kosawa ya ce,

"Nifa so nake naji inda aka halattawa baligin namiji kaunar kato kamarsa har ma kake ganin cewa hakan ba laifi bane. Addinin nan bakin gwargwado nima fa na san shi. Maluman zamanin nan banda son zuciya da kwadayin abin hannun masu neman fatawa basu iya komai ba. Sai ayi ta halatta haram don kada ran mai kudi ya baci"

Kunya sosai ta rufe Abbati da Munzali. Asabe ta dinga bawa Dr. Abdallah hakuri. Shi kuwa ko a jikinsa. Mutane irin wannan da wadanda ma suka fi shi nawa ya gani?

"Soyayya tana samuwa ne daga kyautatawa. Babu ruwanta da jini ko alaka. A inda aka samar da ita a nan take samun wurin zama. Ku duba hikimar Ubangijinmu a wurin zamantakewar rayuwa. Da farko Ya sanya soyayyar da a zukatan iyayensa tun yana ciki. Wannan ita ce ainihin sunnar rayuwa game da iyaye da 'ya'ya. Duk wanda Allah Ya bamu mai kyau ko akasinsa. Nagari ko shakiyi sai kaga muna son kayanmu. Har muna jin ciwon hukuncin da mukan yi musu idan sun yi laifi. Su kuma 'ya'ya ana haifarsu ne ba tare da ilimin komai ba. Tunda anyi zuciya da kaunar mai kyautata mata, fuskar da mutum ya nufeta da ita, itama za ta je da kwatankwacinta. Yaro baya sanin wace uwa a gareshi a farkon rayuwa. Shi dai kawai wannan mai kawar masa da yunwa da kula da damuwarsa ita ce mutum a wurinsa. Wannan dalilin yasa wadanda maraici ke riskarsu tun a zanin goyo suke tashi da kaunar marikansu indai an yi musu rikon amana."

Daga nan Alh. Rabi' u ya soma shan jinin jikinsa. Asabe kuma ta soma hawaye.

"Yaran nan sun hadu a lokacin kuruciya. A shekarun da ko iyaye suna kokarinsu sai sun kara sun dage sannan an hada da addu'a. Dalili kuwa shine wannan shekara shabiyu zuwa sama mataki ne na farkon balaga. Lokaci ne da yara suke fara sanin kawunansu. Munzali yana da zuciyar tausayi da jinkai. Amma ya tashi da kishirwa da yunwar kulawa. Wannan shi ma a tsarin halitta zaka ga wani yafi wani cikin yara son kulawa. Wasu yaran tun kuruciya suna son a dinga basu damar yin komai su kadai. Wani kuwa burinsa na gaba ya sanya shi a hanya kullum. Yana son ayi ta ririta shi. In kun duba Munzali da ya san ya taimakawa wani tun kuruciya tabbas shi mutum ne mai raunin zuciya. Duk wanda zai ja shi a jiki shi ne mutum mafi girman kima a idonsa. Ya zo ya hadu da Abbati. Wanda shi kuma bai kasance daga cikin butulun mutane masu manta alkhairi ba. A zamanin nan duk wanda ya kawar maka da yunwa babu ya shi. Kyautatawa junansu a lokacin da ido da sawun iyaye baya garesu shi ya janyo musu shakuwa. Babu ce ta hadasu ba arziki ba balle ace wani yana kwadayin abin hannun dan uwansa. Kune ku ka kora danku zuwa ga mai kaunarsa da zuciya daya. Misalin haka kan faru tsakanin iyaye mata da masu raino. Idan mace ta sakarwa mai raino ragamar komai na danta, watarana sai ta mika hannu ya noke kafada. In ta dauke shi ta karfi ya yi mata ihun da jama'a zasu iya yi mata kallon mai satar yara."

"Tabbas malam kayi gaskiya" Asabe ta furta tana kuka "sakacinmu ya janyo Munzali ya hada Abbati da miyagun mutane. Dole yake kukan cewa ya yi sanadin bata rayuwar Abbati."

"Don Allah ku daina zancen wani ya bata wani cikinmu. Kaddara ce irin wadda bawa bai isa ya kauce mata ba"

Munzali ya kalli Abbati ya yi murmushi. Dama ya san haka zai ce.

"Ni dai duk da haka ka yafe min"

"Nima ka yafe min"

Asabe ta ce "Allah Ya yafe mana baki daya" ta dubi Alh. Rabi'u "Alhaji ka dai ji abin da Malam ya fada. Duka abin da ya ce babu wanda bamu aikata ba. Mu karbi laifinmu kawai mu tuba shi ne maslaha. Wani borin kunya ba namu bane"

"Ke, bana son rashin kunya. Kin sa danki da bare sun kawo ni nan domin a ci min mutumci ne dama?" Ya tashi tsaye yana karkade riga yadda ya saba idan ransa ya baci "tunda bani da amfani a gareku da 'ya'yanku yau dinnan ba gobe ba zan sauwake muku. Kuma ku zuba ido ku gani idan ban auro yara sa'annin jikokina ba. Wadanda zasu karbi irin kulawar da nake baku hannu bibbiyu suna son barka"

Maza irin Alh. Rabi'u masu kafiya, taurin kai, yiwa addini raguwar fahimta da karan tsaye suna daga cikin babbar matsalar arewacin kasarmu. Suna yin ba daidai ba. Sun sani sarai, kuma in an gyara musu sun san kurakuransu. Amma saboda bahagon tunani basa yarda su karbi gyaran. Kuma a haka wani mai zuciya irin tasu zai basu 'ya su aura. Ukubar da za ta fuskanta da sunan aure ba matsalar mijin da uba bace.

"Ba ayi haka ba Alhaji. In zaman nan bai kawo gyara ba ina ganin bai kamata ya kara lalata lamura ba." Dr. Abdallah ya ce dashi. A ransa yana mai cigaba da nazarin hanyoyin karkato tunanin dattijon.

"Na gama zama. Ki sameni a gida idan kun gama"

Abbati ne ya hana shi fita "Alhaji ka zauna ka yi mana shaida akan kudirinmu na gaba. Malam mece ce makomar dukiyarmu a yanzu da muka tuba?"

"A shari'ance dukiya kala biyu ce. Halattacciya da haramtacciya. Tunda kokontonku yana ga son sanin ko dukiyarku ta haram ce to akan ta biyun zamu yi magana. Ita dukiyar haram an kasata biyu. Akwai ta haramci a dalilin abin mallakar mai cutarwa ne kamar giya, naman alade ko mushe. Da kuma wadda ta haramta a dalilin hanyar samuwarta da izini ko babu izinin mai ita. Misali dukiyar da aka sata ko ta bokanci, kwangilar kisan kai, caca, sayar da kayan maye, karuwanci da ribaa. Kun ga irin taku dukiyar ta fado cikin aji daya da karuwanci. To game da wannan nau'in dukiyar wadda ake samu da izinin mai ita amma sanadin samuwarta haram ne, dukkanin malaman mazhabobinmu wato Imam Hannafi, Imam Hanbali, Imam Malik da Imam Shafi'i sun tafi akan cewa wajibi ne a rabu da ita. Ko dai a mayar da ita ga mai ita ko

ayi sadakarta ga mabukata idan babu halin mayarwa. Ibnul Qayyim Aljauzi ma yana cewa a bayar din shi ya fi. Domin a lokacin samunta wanda ya bayar ya amfana da abin da ya biya kudinsa ne duk da cewa abin haram ne. A wani kaulin, Imam Al-Ghazali ma ya ce sadaka, zakka ko Hajji basu wajaba akan wanda duka dukiyarsa ta kasance haramtacciya ba.

Duka maluman nan sun yi duba ne ga ayoyin Alqur'ani da Hadisan Annabi SAW wurin fitar da fatawar. Misali, akwai wani hadisi wanda Imam Bukhari, Muslim, Ibn Majah, Nasa'i, Abu Dawud da Tirmizi duka suka rawaito [an karbo daga Abi Mas'ud Uqbah bin Amr RA cewa Manzon Allah SAW ya haramta kudin cinikin kare, kudin karuwanci da kudin bokanci.] (Ownership of Unlawful Wealth from Islamic Legal Perspective. Badruddin HjIbrahim da Azizah Mohd, 2017)

Hakika ba zan gushe ba wurin yaba muku matuka. Ina kuma yi muku albishir da cewa dukkan wanda ya bar wani abu da yake so domin Allah, to ladan wannan aikin yana ga Allah (Annawawi hadisi na daya). Zaku kwashi rabonku na alkhairi a duniya ko lahira. Ku sani dai cewa wallahi baku yi asara ba."

Kallon juna suka yi suka gyada kai a tare. In sha Allahu ba za su bari son duniya ya rufe musu ido daga barin mummunan alkaba'in da suka jima suna aikatawa ba.

"Akaramakallah akwai wani batu guda daya da ya rage. Ka san wannan abin yana tattare da matsaloli da dama da suka shafi lafiya. Musamman ga wanda ya tasarma barinta. A haka dai bamu da wani ciwo cikin ciwukan da ake dauka ta wannan hanyar. To amma mu dan yi bincike ana samun abin da ya shafi kwakwalwa. Hanyoyin da ya kamata mu bi a likitance domin kauracewa sha'awar da ta kan taso mana saboda sabo. Rashin kulawa zai iya janyo mana rubewa ko fitar tsutsa..." kasa karasawa ya yi saboda takaicin halin da suke ciki.

Abbati ne ya cigaba da bayanin "mun biya miliyoyin kudi ga wani asibiti a Italy wanda suka kware wurin dakilar da sha'awar sake fadawa zunubin. Sannan duk wata lalura da ta shafi lafiya wadda da wuya mu tsallakewa samunta a nan gaba kadan zasu magance ta. Tambayarmu a nan shi ne zamu iya zuwa? Idan bamu je ba Allah kadai Ya san halin da zamu iya tsintar kawunanmu. Sannan bamu da halin sake samun kudin da zamu biya. Duk abin da muka mallaka yanzu hatta waya zamu rabu da ita saboda duka da kudin muka samu"

Iska Dr. Abdallah ya fesar daga bakinsa. Wannan tambaya akwai rudani a cikinta. Ya dubi matasan ya auna duka maganganun da suka yi. Ya tambayi nawa suka biya yaji kudin ba na kusa bane. Bayan nazari ya fada musu abin da yake ganin shi ne mafita.

"Ku je ku nemi lafiyar ku. Domin sai da ita ne kadai zaku iya barin wannan abu har abada. Idan nace ku zauna ban yi muku adalci ba. Bani da halin sama muku irin wannan kudi. Iyakar shawarar da zan baku shi ne ku kiyaye. Kada ku dauki kari akan abin da ku kw san lallai zai isheku iya zamanku a can."

(Wannan ba fatawa bace. Fahimtata ce ba fadin malami ba)

Ragowar bayanin da aka yi shi ne ya dan taba zuciyar Alh. Rabi'u. Ya auna da kwakwalwarsa ba son zuciya ba ya tabbatar duk a kokarin samun lahira Munzali yake wannan abu. Shi kuwa wane irin shaidan ne a kansa da zai sa ya cigaba da riko da mummunar akidar da har mahaifiyarsa ta rasu bata taba goyon bayansa a kai ba?

***

Bayan Wata Hudu

Sannu sannu bata hana zuwa, sai dai a dade ba a je ba. Abubuwa da yawa sun faru a cikin watannin nan ga jaruman labarinmu.

Mami Khadija ta koma hadadden gidan da Alh. Tahir ya mallaka mata ita da 'ya'yanta. Ta cigaba da aikinta cikin kwanciyar hankali. Iyayenta da Yakumbo sun yi fushi har sun sauko. Mardiyya bata yarda an barta ita kadai ba. Kamar yadda suma yaran basu kwashe duka kayansu daga wancan gidan ba. Musamman Sauda da Mardiyya da basa rabuwa. Kullum in basa wannan gidan suna wancan. Jiddo ta dade da tafiya. Gida ta kama mai kyau ta cigaba da shashancinta bisa zugar kawaye. Gidan ya zama dandalin fitinannun mata. Ba a dade ba kuwa suka cinye fiye da rabin kudin da Alh. Tahir ya bata. Tunda bata iya juyasu ba sai bushasha. A halin yanzu ta gamu da ciwon gonoriya. Kuraje manya manya masu dan karen kaikayi da kazamin ruwa sun firfito mata. Ga kudin asibiti ya soma gagararta.

Alh. Tahir ya auri Yumna domin biyayya ga umarnin Yakumbo. Da kuma rufin asirinsa akan abin da Mami Khadija ta fadawa 'ya'yanta. Ya daina bin mata kamar anyi ruwa an dauke. Rayuwarsa babu wani farinciki a ciki saboda rashin Mami da zubar girmansa a idon manyan 'ya'yansa. Mama Nasima ta rage rashin zaman gida saboda tsoron kada ita ma ayi waje da ita. Yumna kuwa babu wannan fadar da take tsammanin samu. Ga kudi ga komai amma mijin bashi da lokacin biye mwa shirmenta.

Lilu ya mayar da hankali akan karatu. Suhaib kafa ta warke ya koma bakin aikinsa. Ayaah tana nan a ransa. Suna yawan gaisawa a waya wadda bata wuce ya gida, jikin Abbas da jarabawarta (a tsarinsa sai ta gama jarabawa zai nemi soyayyarta wadda ya gama nutsewa a ciki). Farha ce ta koma abar tausayi a wurin Mami. A zahiri ta cigaba da gudanar da rayuwarta kamar da. A badini kuwa kewar Abbati tana neman wargaza tuninta. Kara son shi tayi bayan Mami ta fayyace musu komai kamar yadda Alh. Tahir ya fada mata. Ta dai sakaya yanayin haduwarsu da babansu. Sai ta ce wurin abokinsa yaje yaga Abbatin. Wayar duniya ta buga bata samunsa. Tunda tayi na sati ta hakura ta fawwalawa Allah.

A Kano gidan Innayo sai san barka. Kansu ya hadu 'ya'yan suna ta zumuncinsu. Asabe da Innayo ma kamar 'yan uwa. Maigidan ne dai sai a hankali. Yau fari gobe tsumma. Wata dabi'ar barinta yana da wuya. Tuni Zara ta koma gidanta bayan Hajiyan Fatakwal ta zo da kanta sun sasanta da Innayo. Aka yiwa Ummulkhairi taron sunan da ya shiga bakin 'yan unguwa. Da wuya a hadu ayi hira mai tsayi ba ayi zancensa ba. Uwani ma da kanta ta koma. Salihi dawowa ya yi gida kawai ya sameta a falo da Mubasshir suna hira. Yayi murna kwarai da irin canjin da aka samu a tattare da ita. Ya hadasu da Ummule ya musu nasihar zaman lafiyar da kowane magidanci yake yi. Har yanzu dai babu wani abu mara dadi da ya faru gashi har Ummule ta haihu. Uwani ce ta karbi haihuwar tayi komai babu ha'inci a gida. Saura wata daya suspension dinta ya kare. Sannan ba tare da sanin kowa ba sai mijinta ta dauki Zakiyya da Qibdiyya sun je asibiti. Duk wani abu da ya dace ayi Salihi ne ya dauki nauyin biyan kudin. Ita da 'yan uwanta duk sun karbi zancen da yabi bakin kowa na cewa karayar arziki ce ta sami su Munzali. Asabe ta gina zancen akan wanda Mami Khadija tace mata taji a wurin Alh. Tahir lokacin da ta kira tayi musu jaje.

Salima dai aure ya mutu murus. Ale Gambo ya yi rantsuwar idan bata koma ba cikin kayadadden lokacin da ya bata tana da damar sake aure domin babu shi babu ita.

Innayo ta lamunce mata tayi abin da zuciyarta take so. Cikin farinciki don har ta murmure ta ce ta gama zama dashi. Kwanaki kadan da suka wuce ta gama iddarta.

Abbas ya warke ya koma gida. Sauki ya samu don ya fara magana kuma yana tafiya da kansa. Tsakanin su Honourable da Abdulkarim sai tarin godiya. Shi da Ummita soyayya suke yi mai ban sha'awa. Biki saura sati biyu. Ayaah ma ta gama NECO sauran WAEC wadda jarabawa biyu suka rage su kammala baki daya. Anti Hasiya ciki ya fito. Laulayi ya yi sauki sosai. Tana samun riritawa daga mijinta, mahaifiya, 'yan uwa da 'ya'ya. Haihuwa kawai ake jira. Karshen abin farinciki shine kulle Danliti da Shazali da Alh. Sadisu yasa aka yi. Duka malamai da masu gadin makarantar da sukw da hannu su ma an rufe su. Shi Shazali ma a kurkukun bai tsira ba domin kusan kullum sai an yi masa duka.

Tunda Baaba Mari take bata taba samun kwanciyar hankali dari bisa dari ba sai yanzu. Alkawarin Allah Ya cika. Bayan kowanne tsanani akwai sauki tafe. Damuwarta ta shekara da shekaru ta kau. Sauran 'ya'yanta dama basu da matsala irin wadda ta jima tana damunta akan Abbati. Yanzu da komai ya daidaita ta sami nutsuwa.

Mal. Sa'idu ya soke karatun Allah. Sauran 'ya'ya da jikoki duk yasa an dawo dasu gaban iyayensu. Ya kuma aurar da 'Yashshafa ga wani tsohon saurayinta. Deluwa kamar ta hadiyi zuciya. Tana ta mitar yaya zasu yi ida Sha'aib ya zo. Hanne ma ta gama idda har manema sun fara kawo caffa. Ta cigaba da rayuwarta sannan ta rike sirrin Abbati.

***

Wata biyu kenan Abbati da Munzali suna karbar treatment akan hanyoyin tsira daga komawa tsohuwar rayuwarsu. Kafin su taho duk wani abu da suka mallaka sun damka shi a hannun Dr. Abdallah Saraki. Zunzurutun kudi da kadarori. Sutura da takalma kadai ne basu bayar duka ba. Amma hatta zobe da agogo basu bari ba. Motocinsu sun sayar. Gidan ma a satin aka sami mai saya. Sauran abin da basu kammala ba suka bar masa amanar sayarwa. Cikin kankanin lokaci aka dinga gina rijiyoyin burtsatse a kauyukan da suke tsananin bukata. Aka biyawa marasa lafiya da yawa kudin asibiti. Kudi ya zaga inds ya kamata. Dr. Abdallah ya taimaka musu kwarai wurin sauke nauyin da yake wuyansu. Hankulansu kwance a inda suke. Wayoyin hannunsu ma shi ya saya musu kafin su tafi.

Bayan tafiyarsu Alh. Sadisu ya neme su a waya shiru. Sai ya tuntubi Alh. Tahir. Shi ma bai san inda suke ba. A wurin Mami Khadija ya sami numbar Baaba Mari. Takanas ya tafi Kano inda suka hadu shi da Alh. Sadisu suka kirata. Ta hadasu da Mal. Inuwa shi kuma ya faygace musu halin da ake ciki.

"Alhaji da zuciya daya nake kaunar yaran nan. Idan suka dawo kana ganin zasu yarda in saka su cikin siyasa? Ba wai 'yan banga ko makamancin haka ba. Ina so in daga su a idon duniya. Su fara da zama PA dina ko Secretary. Ta yadda duk inda nasa kafa muna tare. A hankali har a sansu wata rana idan muna raye in daga hannuwansu a zaben manyan mukamai" Alh. Sadisu ya ce da Alh. Tahir bayan sun koma gidan Alh. Sadisun.

"Nima nayi tunanin janyo su aikin kwangilata. Amma ina gudun kada su ki amincewa saboda yarana da suka nema a baya. Sannan bani da wani mutumci a tunani a idanunsu. Dama auren zai yiwu da naji dadi. Musamman na Farha." Shi ma Alh. Tahir ya fadi nasa kudirin. Jari zai basu mai tsoka da zai ishesu tsayuwa akan kafafunsu. Amma kuma Alh. Sadisu zai bawa "ina gudun kada su ki karba. Ko kuma su ga kamar nayi ne da wata manufa"

"Hakika haduwarka da yaran nan izina ce garemu baki daya Alh. Tahir. Duba ka gani yadda rayuwarka ta canja. Ina fada ba don izgilanci ba. Yadda ka rabu da harkar mata haka idanuna suka bude na rabu da duk wani abu na haramci a siyasata. Don gani nake kamar hakki ne ya kama Abdul. Kuma naga fa'ida domin na kara samun masoya. Kwarjinin da nake fata na kara yinsa ba tare da na bawa kowa tsoro saboda cin zali ba."

***

Garin Parioli wanda yake cikin babban birnin Italy wato Rome shi ne inda ake da babban masallacin kasar. Saboda girmansa zai iya daukar masallata dubu goma sha biyu a lokaci guda. A daya daga cikin wuraren alwalar maza Abbati da Munzali ne suke alwala. Sun cika burinsu na ziyartarsa kafin su bar kasar. Abbati sanye yake da shudin wando da shudiyar shet wadda ya dorawa jacket sea green. Munzali kuwa bakin wando ne da polo shet ruwan madara a jikinsa. Su biyun sun yi kumari sosai. Ashe duk yadda jikinsu yake wannan abu yana tsotsesu basu sani ba. Sai yanzu suka kara zama cikakkun maza masu cikar kamala. Kowanne ya ajiye gashi a fuska

wanda ya kara musu haiba. Alwala suke Munzali yana ta rawar dari. Abbati da ya gama ya koma gefe yana yi masa dariya.

"Nace maka ka k'ara riga akan ta jikinka amma ka dage wai da alamun rana a waje. Yanzu kuma ka zo ka sani a gaba kana makyarkyata kamar wanda ya kulla abota da DJ"

Munzali ya ciko hannu da ruwa zai watsa masa ya kauce yana kara yi masa dariya. A hasale Munzali ya ce,

"Ka dai ji kunya. Wai a matsayin wa na kake amma ka kasa sadaukar min da rigar sanyi. Sai surutu kake min kamar ..."

Kunnensu Abbati ya kamo yana cewa "ban hanaka rashin kunya ba?"

Munzali ya karkace kai saboda zafi yana magiya "me yasa baka san wasa bane. Don Allah ka saki kada kayi min kunne daya"

Zungure masa kai Abbati ya yi sannan ya cire rigar ya mika masa.

"Minti talatin zata yi a jikinka ka bani"

Da farinciki Munzali ya karba ya saka suka shiga masallacin domin yin sallar azahar.

Da suka idar hotuna suka dinga dauka domin tarihi. Ba su suka tafi ba sai da suka yi sallar la'asar. Lokacin jacket din ta koma jikin Abbati. Kowa minti talatin din yake ya bawa dan uwansa. Suna ta atishawa. Abbati ya yi ta mita. Munzali yana tunzura shi da cewa don kada ya barshi da jinya ne ma fa yake karbar aron rigar sanyin. Da zasu tafi addu'a kowannensu ya yi. Kusan abu daya suke roko. Cigaba da samun rufin asiri akan abin da ya gabata na rayuwarsu. Samun sana'ar yi sai kuma kowa ya yiwa dan uwansa fatan samun abokiyar zama tagari ba tare da sanin dayan ba.

Ranar da zasu tafi a airport dukkaninsu dokin ganin Qibdiyya suke yi. Sabo da rigima kamar yara harda fadan waye zai fara daukarta.

"Bayan ma yau baka kira mana ita ba" Abbati ya harari Munzali.

Zama suka yi akan kujerunsu daga jikin juna a jirgi sannan Munzali ya ce "na fada maka kashe min murya Zakiyya take yi. Sai ta kusa cinye kudin da surutu. Kai kuma ka wani dage ba za ka dinga kiranta ba sai kace surukarka"

"Ka sani ko ayi kome?"

Seatbelt din da yake kokarin sakawa ya saki ba shiri ya kalli Abbati.

"Kome a ina? Ni nace maka ina son aure ne ko kuwa ina son Zakiyya?"

Abbati ya ce "ko daya. Aure dolenmu ne Munzali. Indai ba so kake iyaye su sake fara zargin ko mun koma ruwa ne. Ba don na san mun rabu kenan dasu Diamond girl dinka ba ai da ita zan ce ka aura. To amma kaga babu wadda ya dace ka zauna da ita kamar Zakiyya. Ita ce ta haifi Qibdiyya. Ita ta san me ya faru da ita. Ita ce kuma zata san hanyar hana maimaici."

"Shawara ce kake bani?"

"Eh"

"Kana ganin akwai alkhairi idan aka daina rabawa Qibdiyya hankali?"

"Tana bukatar tsayayyen gida da uwa da uba."

"To kai yaushe za ka yi auren?"

"Wa yake ta tawa? Da Hanne tana nan da yanzu bakina alaikum. Yanzu kuwa dole in nema can nesa da gida."

Zancen Farha ya so yi masa amma ya fasa saboda baya son yi masa fami.

"To Allah Ya kawo tagari. Amma ka daina zancen Hanne baiwar Allah. Ni na san ko kadan baka sonta. Shi yasa kana samun dama ka sallameta" cewar Munzali yana dariya.

Shi ma Abbatin dariya ya yi yace "Cutar juna muke kawai. Tana jin haushina ina jin nata."

Jirgin na shirin tashi suka kira Dr. Abdallah, Alh. Sadisu wanda yanzu yake yawan kiransu sannan kowa ya kira iyayensa. Munzali kadaran kadahan suka gaisa da babansa. A hakan ma sun sami cigaba ne a alakarsu saboda jajircewar Munzalin.

***

Tafiyar awa biyar da minti hudu ce ta kawosu Nnamdi Azikiwe International Airport Abuja. Suna fitowa daga ciki mota tazo ta daukesu kamar yadda Alh. Sadisu ya ce musu ya bada umarni da suka yi waya.

"Zai kai ku hotel. Gobe zan zo garin ganin party chairman. Sai mu juya jibi tare. Ina fatan hakan ba zai zama takura a gareku ba"

Wannan shi ne abin da ya fada musu a wayar. Cike da girmamawa suka yi masa godiya. Da zasu fita daga motar bayan sun isa hotel din kudi direban ya basu a envelop.

"Yallabai ya ce ku rike kafin ya iso"

Suka sake yin godiya sannan kamar lokacin tasowarsu duk da dare ya yi sai da suka kira iyayensu. Cikin daren suka tattauna yadda zasu yi idan Alhaji Sadisu ya zo musu da wani abu da zai iya bata musu rayuwa. A yanzu sun hankalta suna matukar tsoron shigewa masu kudi. Babu dangin Iya babu na Baba. Watakila wani abin ake nema a garesu.

Washegari sai bayan isha Alh. Sadisu ya iso. Tare suka je suka ci abinci. Dakinsa a hotel din yace su biyo shi. Gabansu ya fadi amma suka daure.

Yana zaune a kan kujera suna kasa a gefensa ya yi musu magana.

"Na san cewa zukatanku suna cike da tambayoyi da fargabar manufar janyoku da nayi a jiki. Dom Allah ku kwantar da hankalinku. Ko babu komai ceton rayuwar Abdul da ku ka yi ya isheni dalilin son saka musu da abin alkhairi. A dalilinku ya sami sauki har ina shirye shiryen tura shi kasa mai tsarki da biyu cikin iyayensa mata. Sai ya yi a kalla shekara guda yana karatun addini zai dawo gabana ya karasa sakandire. "

Murna suka taya shi yaji dadi kuwa

"Magana ta gaskiya labarinku ya tsaya min a zuciya. Ban taba ganin almara irin wannan ba. Giyar kudi bala'i ce. Musamman ga matasa irinku wadanda kuruciya take diba. Yaran yanzu zasu yi komai domin kudi. Sai gaku na hadu daku zahiri ba labari ba. Kun bude min ido da kusanto da tunanin lahira a dukkan lamurana. A takaice rayuwata duka na canjata kuma duka kune sila. Wannan yasa na daukarwa kaina alkawarin ba zan bari ku tagayyara ba. Rashin abin yi da rashin kudi a hannun wanda ya saba rikewa ba karamar jarabawa bace. Tsananin rabo da tsoron Allah ne kadai zai dakushe zukatanku daga tunanin hanyoyin samun kudi ko ta wace siga. Saboda haka idan kuna da ra'ayi ni Alh. Sadisu Nakano nayi muku alkawarin muddin ina raye da rai da lafiya, zan yi iya yina domin ganin kun zama wasu ababen misali da alkhairi a cikin al'ummarmu. Ina burin duniya ta amfana da alkhairin da nake da yakinin Allah Ya wanzar muku sakamakon mika wuya gareShi. Me ku ka ce?"

Basu ce komai ba sai kwalla. Ikon Allah akwai ban tsoro. Duka duka awanni nawa da suka wuce ne suka zauna suna tunanin yadda zasu yi da rayuwarsu yanzu? Sai gashi mafita tazo daga inda basu tsammani.

Alh. Sadisu ya yi murmushi "in dauki shirunku a matsayin amincewa?"

"Alhaji ko za ka bamu zuwa gobe domin mu shawarci iyayenmu"

"Ka cika babba Abbati. Dama gaggawa daga shaidan take. Ku yi shawara da duk wanda ya dace. Fatana Allah Yasa ku bani damar zame muku uwa da ubs a siyasance. Da yardar Allah ni daku babu mai yin nadama."

Dr. Abdallah suka fara kira. Ya ce idan sun shigo Kano gobe su zo su same shi a gida. Da makomar tattaunawarsu da shi zasu yiwa iyayensu bayani. Daga nan su nemi amincewarsu.

Direban da ya daukosu daga airport shi ne ya kuma zuwa daukarsu. Alh. Sadisu ya sanar dasu cewa zasu tsaya a Kaduna zai ga abokinsa kafin su wuce. Haka suka jera suna biye dashi a baya.

***

Suhaib, Farha, Lilu, Sauda da Mardiyya ne suka fito daga wani babban shopping mall wanda yake makwabtaka da ofishin Alh. Tahir. Mami Khadija ya kuma roka akan burinsa na daidaitawa da yaran. Tayi musu magana harma da fada akan lallai su cire abin da yake ransu su kyautatawa mahaifinsu.

"Shi kadai gareku. Ba zai yiwu don ya auri Yumna kowa ya dauki gaba dashi ba. Duk alkhairinsa gareku bai kyautu ku manta ba saboda wani abu guda daya da bai sabawa shari'a ba"

Fadan a gaban kannensu ne. Su manyan sun san me take nufi. Hakuri suka bata tace to tana so bishi office su nuna masa komai ya wuce. Da yake kullum cikin kokarin janyosu jiki yake suna yakicewa sai kowa yaji babu dadi. Shi ne Suhaib ya ce su fara zuwa kowa ya sayi gift guda daya su bashi.

Sauda da Mardiyya sai tsalle da murna. Ji suke kamar sun dade basu ga Abbansu ba. Kowa ya yi kewarsa. Harda Suhaib kuwa.

Abbati da Munzali a hadadden reception din office din suka zauna suna hira. Alh. Sadisu ya shiga wurin Alh. Tahir ba tare da sun san wurinwa ya zo ba. Yana ciki suna tattauna makomar rayuwar yaran. Niyarsu sai sun gama magana sannan Alh. Sadisu zai kirasu ciki domin su sami fahimta da Alh. Tahir. Yana so su dauke shi a matsayin makusancinsu.

Waya suke yi da Qibdiyya ta cikasu da surutu mai bude kofar ya hangameta. Basu dago sun kalli su waye suka shigo ba koda suka ji ma'aikatan dake wucewa suna ta yi musu maraba.

"Oga yana tare da bako." Wani masinja ya fada musu.

"Bari mu jira shi a nan" Suhaib ya nuna kujerun reception din.

Kafin su karasa duka su biyar din sun ga su waye a zaune. Farha ji tayi kamar zazzabi zai kama ta. Kujerar farko ta gabanta ta dafa yayinda Suhaib da Lilu suka karasa gabansu.

Earpiece ne a kunnen Abbati yana kallon video din Qibdiyya

BABI NA ASHIRIN DA BIYAR.

***

48

Zaune yake gaban likita na goma sha uku cikin jerin likitocin da ya ziyarta domin magance matsalarsa. Amsa yake nema don ya san a wane babi zai ajiye lafiyar kwakwalwa da tunaninsa.

Ya gama bayani tsaf akan yadda ya dauki Abbati da zargin da mutane makusantansa suke yi masa kamar yadda ya yiwa sauran likitocin. Ya kare da cewa,

"Bayani nake so a mahanga ta addini. Idan bani da rabon samun rahama ne saboda irin tunanina gara..."

"Subhanallahi" cewar likitan da sauri "Munzali wannan magana taka bata dace da dan musulmi ba. Ni ba malamim addini bane. Amma tabbas har yau ban bar gaban malamai ba. Na kuma godewa Allah da malumanmu na yanzu suka kasance masu ilimin boko wanda yake taimaka musu wurin warware matsalolin da suke tafe da zamani. Idan za ka iya gobe ka zo nan da la'asar. In sha Allah zan kai ka wurin Dr. Abdallah Saraki. Kawu ne kuma siriki a wurin abokina Dr. Huzaifa."

Tun bayan zaman nan da aka yi a gidan Abbati sati biyu da suka wuce, sai yau Munzali ya yi murmushi. Da ya tashi zai tafi likitan nasa ya ce su taho tare da Abbati da iyayensa.

"Hakan ne zai sa kowa ya sami gamsuwa akan amsar da zai baka"

Yana shiga mota ya kira Abbati. A lokacin shi kuma yana cikin ofishin Alh. Sadisu. Kiran na shiga ya dauka da sauri.

"Munzali lafiya dai ko?"

"Lafiya kalau. Kana gida ne?"

"Ina office din Alh. Sadisu ne. Yanzu muka dawo daga duba Abdul"

Munzali yaji kunya ta kama shi. Ba irin lallashi, fada da nasihar da Abbati bai yi masa ba amma kememe ya daina yarda ko zaman minti biyar suyi a wuri daya. Abbati ya yi fushi sosai saboda ya fuskanci akwai abin da yake boye masa. Shi kuma baya son fada saboda a take Abbatin zai soke masa zargin. Gashi zuciyarsa ta riga ta fara rawa akan maganganun iyayensa. Ya zama wajibi ya san me yake ciki.

"Kwatanta min wurin zan zo na same ka"

Minti ashirin ya kaishi. Suka zauna tare da Alh. Sadisu. A yau godiya mai tarin yawa ya sake yi musu sannan ya koma kan batun abubuwan da yaji a police station din.

"Kuna ganin da gaske zaku iya dainawa? Nayi bimcike ance da wahala rabuwa da wannan dabi'ar. Idan Abdul ya tashi a haka ban san yadda zan yi ba"

Munzali bai yi kasa a gwiwa ba ya fada masa shirinsu na zuwa asibiti a Italy. Rashin zuwa a duba lafiyarsu da kuma neman hanyar rabuwa da lalurar har abada ba karamin kalubale bane ga tubansu. Ita wannan dabi'a tana tattare da matsaloli da yawa ga lafiya. Ciki kuwa harda kasa jurewa rashin samun biyan bukata ta inda aka saba. Wannan abu ya kan fi karfin furtawar baki da yakinin zuci. Wani duk dauriyarsa idan abin ya ciwo shi sai ya biya bukatar yake jin dadi.

"Abdul yaro ne. Sake komawarsa ba abu bane mai wahala. Mafi a'ala shi ma ka kai shi asibiti" inji Abbati.

Godiya ya yi musu da zasu tafi da alkawarin tsaya musu a duk lokacin da suke da bukatar taimakonsa.

"Magana nake son muyi Abbati." Munzali ya ce da suka fito waje.

"Dama jikina ya bani tunda ka kira. Ka gaji da yajin ne kazo biko da kanka?"

Da sauri Munzali ya ce "don Allah ka bar amfani da kalmar yaji da biko kamar wasu mata da miji"

Abbati na jin haka ya gano inda matsalar take. Motarsa ya bude suka shiga ya tayar. Gida ya wuce kai tsaye. Yanzu babu kowa daga kuku sai Maigadi. Iya Kande bata dawo ba tun tafiyar Qibdiyya gida.

A waje suka zauna wurin wasu kujeru da 'yar rumfa. Munzali ya fadawa Abbati dukkanin damuwarsa.

"Na san za ka iya cewa ba komai bane. To amma hankalina ba zai taba kwanciya ba. Don Allah gobe ka zo muje wurin malamin."

Kamar uwa da d'a. Tausayin Munzali ya kama Abbati sosai. Don gudun kara masa damuwa sai bai yi masa yadda ya saba ba idan yana cikin yanayi mara dadi. Lokutan da yake yi masa fada ko nasiha da rarrashi har sai ya sauko.

"Allah Ya kaimu goben. Dama nima ina son yi maka magana akan mu nemi fatawa kan dukiyarmu. Goben sai muje masa da komai muji me zai ce."

Munzali ya mike zai shiga ciki. Abbati ya kai hannu zai taba kafadarsa don ya tsaya sai ya fasa.

"Munzali."

Juyowa ya yi fuskarsa duk ta rame kamar ya dade yana ciwo.

"Ina so ka sani cewa ko yaya makomar alakarmu ta kasance gobe ba zan taba barinka ba"

"Ko da ya tabbata wannan kazantar bata barni ba"

"Zama da kazanta fa sai ka so. A matsayin kani kuma amini na daukeka. Banda an riga an dasa maka wani irin tunani a zuciyarka da na fada maka matsayinka a wurina. Yanzu kuwa ina magana za ka iya tsoron kada nace gobe zan kawo sadaki"

Murmushi suka yi a tare sannan kowa ya nufi gidansa.

***

Washegari basu hadu da safe ba. Munzali ya tafi gida dauko su Asabe. Ya sami gidan a cike makil. Larai da su Fati sun zo dukkaninsu kwai da kwarkwata. Gaban Innayo ta zauna ta roki gafararta na rashin kyautawa da tasa 'ya'yanta yi mata. Ta karbi laifinta kamar yadda 'ya'yanta su ma suka karba. Aka yafi juna tare da alkawarin sabunta zumumci.

Hasiya ce kadai bai samu ba. Hakan ya yi masa dadi domin yana jin kunyarta saboda rashin samun sukunin zuwa duba Abbas. Uwani kuwa tana jin muryarsa ta fito ta tare shi a gefe. Mita ta soma yi masa na rashin kiranta da ya ce zai yi domin ta duba Qibdiyya. Hakuri zai bata sai ta kula da ramar da ya yi. Mantawa tayi da fadan ta koma tambayarsa damuwarsa.

"Na manta gidanmu ba irin da bane, da na sani ban zauna abubuwa suna ta damuna ba a cikin kwanakin nan" yace ba tare da wasa a fuskarsa ba.

"Komai mai wucewa ne Munzali. Tunda muka dinke da Innayo kaima kawai ka jira lokaci. Kafin ka farga zaka ga ya koma tarihi. Ko ka bayar dashi ko rike abinka a zuci"

Karfin gwiwa ya samu daga gareta wadda da ita ya yi amfani wajen jajircewa iyayensa suka bi shi.

***

Sheikh Dr. Abdallah Saraki ya saurari jawabin Munzali da Abbati da dukkan nutsuwar da ake bukata daga malami. Labarinsu gabadaya izina ce kuma babban darasi ga iyaye da su kansu 'ya'yan.

(Ni din ba Malamar addini bace. Daliba ce mai koyo har yanzu. Bakin gwargwado ina nazari da bincike kafin na kawo wani batu mai girma cikin labaraina. A nan ma na duba matsayar malamai na kuma hada da tawa fahimtar. Saboda haka idan mai karatu yaci karo da abin da ya sabawa nasa ilimin, kada a manta cewa wannan labari ne. Abin da ya shafi fatawa a nemi sahihancinsa a wajen maluma. Rabbi Yasa mu dace da khairi duniya da lahira. Amin)

Da Alh. Rabi'u ya ga zai fara magana, hankalinsa kacokan ya mika masa. Yana so yaji malamin ya wanke shi daga abin da Munzali ya ce, wato yana da hannu a cikin lalacewar rayuwarsa.

Dr. Abdallah ya fara jawabinsa da sallama tare da addu'ar bude taro ko wani zama da za a tattauna abu mai mahimmanci. Sannan ya karkare da yiwa fiyayyen halitta salati SAW.

"Da farko zan fara da yaba muku tare da kara muku karfin gwiwa. Duk wanda ya nufi Allah SWT da kyakkyawar zuciya, to ya sani cewa Allah ba zai tab'ar dashi ba. Saboda haka ku cigaba akan niyyarku. Ko a duniya ko a lahira sai kun yi mamakin falala da girman Mahaliccinmu. Zai baku fiye da rokonku. Ya yafe fiye da tubanku domin Shi din gagara misali ne wajen jink'ai da tausayi."

Ya gyara zama saboda su san cewa zancena gaba yana da mahimmanci.

"Munzali ina so kai da iyayenka ku sani cewa tsaftatacciyar soyayya ce tsakaninka da Abbati. Irin soyayyar da Allah SWT Yayi alkawarin inuwar Al'arshi rana gobe kiyama ga ma'abotanta. Wato mutum biyu masu kaunar juna domin Allah Shi kadai."

Munzali ya hau murmushi yayinda Abbati ya dinga kiran sunan Allah a iya a lebbensa.

"Malam baka ji inda ya ce yana son Abbati fiye da kowa ba? Ma'ana fa harda mu. Babu jin nauyi ko kadan yake nuna min cewa yaron nan ya fini a wurinsa." Cewar Alh. Rabi'u yana huci.

Dr. Abdallah ya ayyana a ransa cewa lallai Alh. Rabi'u akwai gagarumin gyara a lamarinsa.

"Aikin sab'o sakamako ne na raunin dan Adam. Shi kuma rauni ana gane shi ne daga zuciya. Idan aka haneta ga barin abin da take so sai ta ce ta kasa. Idan aka umarceta da abin da bata so nan ma ta nuna gazawarta. To da zarar mamallakinta ya biyewa ra'ayinta ba tare da dora shi a mizanin hankali, dabi'a da addini ba, dole nadama ta saukar masa watarana. Alh Rabi'u, ka yi godiya muddin rai ga Allah da Ya bawa yaran nan damar fin karfin zukatansu a lokaci irin wannan. Gurbacewar zamanin nan ta kai ta kawo. An kawata zina ana tallatawa mutane. Tserewa tarkonta wallahi sai wanda Allah Ya azurta da jarumar zuciya. Wadda tana so din kuma tana tsoron mummunar makoma. Zuciya ta ma'abota tsoron Allah da kwadayin rahamarSa."

Asabe ta dinga gyada kai tana yiwa Munzali da Abbati kallon tausayi. Alh. Rabi'u kuwa cikin kosawa ya ce,

"Nifa so nake naji inda aka halattawa baligin namiji kaunar kato kamarsa har ma kake ganin cewa hakan ba laifi bane. Addinin nan bakin gwargwado nima fa na san shi. Maluman zamanin nan banda son zuciya da kwadayin abin hannun masu neman fatawa basu iya komai ba. Sai ayi ta halatta haram don kada ran mai kudi ya baci"

Kunya sosai ta rufe Abbati da Munzali. Asabe ta dinga bawa Dr. Abdallah hakuri. Shi kuwa ko a jikinsa. Mutane irin wannan da wadanda ma suka fi shi nawa ya gani?

"Soyayya tana samuwa ne daga kyautatawa. Babu ruwanta da jini ko alaka. A inda aka samar da ita a nan take samun wurin zama. Ku duba hikimar Ubangijinmu a wurin zamantakewar rayuwa. Da farko Ya sanya soyayyar da a zukatan iyayensa tun yana ciki. Wannan ita ce ainihin sunnar rayuwa game da iyaye da 'ya'ya. Duk wanda Allah Ya bamu mai kyau ko akasinsa. Nagari ko shakiyi sai kaga muna son kayanmu. Har muna jin ciwon hukuncin da mukan yi musu idan sun yi laifi. Su kuma 'ya'ya ana haifarsu ne ba tare da ilimin komai ba. Tunda anyi zuciya da kaunar mai kyautata mata, fuskar da mutum ya nufeta da ita, itama za ta je da kwatankwacinta. Yaro baya sanin wace uwa a gareshi a farkon rayuwa. Shi dai kawai wannan mai kawar masa da yunwa da kula da damuwarsa ita ce mutum a wurinsa. Wannan dalilin yasa wadanda maraici ke riskarsu tun a zanin goyo suke tashi da kaunar marikansu indai an yi musu rikon amana."

Daga nan Alh. Rabi' u ya soma shan jinin jikinsa. Asabe kuma ta soma hawaye.

"Yaran nan sun hadu a lokacin kuruciya. A shekarun da ko iyaye suna kokarinsu sai sun kara sun dage sannan an hada da addu'a. Dalili kuwa shine wannan shekara shabiyu zuwa sama mataki ne na farkon balaga. Lokaci ne da yara suke fara sanin kawunansu. Munzali yana da zuciyar tausayi da jinkai. Amma ya tashi da kishirwa da yunwar kulawa. Wannan shi ma a tsarin halitta zaka ga wani yafi wani cikin yara son kulawa. Wasu yaran tun kuruciya suna son a dinga basu damar yin komai su kadai. Wani kuwa burinsa na gaba ya sanya shi a hanya kullum. Yana son ayi ta ririta shi. In kun duba Munzali da ya san ya taimakawa wani tun kuruciya tabbas shi mutum ne mai raunin zuciya. Duk wanda zai ja shi a jiki shi ne mutum mafi girman kima a idonsa. Ya zo ya hadu da Abbati. Wanda shi kuma bai kasance daga cikin butulun mutane masu manta alkhairi ba. A zamanin nan duk wanda ya kawar maka da yunwa babu ya shi. Kyautatawa junansu a lokacin da ido da sawun iyaye baya garesu shi ya janyo musu shakuwa. Babu ce ta hadasu ba arziki ba balle ace wani yana kwadayin abin hannun dan uwansa. Kune ku ka kora danku zuwa ga mai kaunarsa da zuciya daya. Misalin haka kan faru tsakanin iyaye mata da masu raino. Idan mace ta sakarwa mai raino ragamar komai na danta, watarana sai ta mika hannu ya noke kafada. In ta dauke shi ta karfi ya yi mata ihun da jama'a zasu iya yi mata kallon mai satar yara."

"Tabbas malam kayi gaskiya" Asabe ta furta tana kuka "sakacinmu ya janyo Munzali ya hada Abbati da miyagun mutane. Dole yake kukan cewa ya yi sanadin bata rayuwar Abbati."

"Don Allah ku daina zancen wani ya bata wani cikinmu. Kaddara ce irin wadda bawa bai isa ya kauce mata ba"

Munzali ya kalli Abbati ya yi murmushi. Dama ya san haka zai ce.

"Ni dai duk da haka ka yafe min"

"Nima ka yafe min"

Asabe ta ce "Allah Ya yafe mana baki daya" ta dubi Alh. Rabi'u "Alhaji ka dai ji abin da Malam ya fada. Duka abin da ya ce babu wanda bamu aikata ba. Mu karbi laifinmu kawai mu tuba shi ne maslaha. Wani borin kunya ba namu bane"

"Ke, bana son rashin kunya. Kin sa danki da bare sun kawo ni nan domin a ci min mutumci ne dama?" Ya tashi tsaye yana karkade riga yadda ya saba idan ransa ya baci "tunda bani da amfani a gareku da 'ya'yanku yau dinnan ba gobe ba zan sauwake muku. Kuma ku zuba ido ku gani idan ban auro yara sa'annin jikokina ba. Wadanda zasu karbi irin kulawar da nake baku hannu bibbiyu suna son barka"

Maza irin Alh. Rabi'u masu kafiya, taurin kai, yiwa addini raguwar fahimta da karan tsaye suna daga cikin babbar matsalar arewacin kasarmu. Suna yin ba daidai ba. Sun sani sarai, kuma in an gyara musu sun san kurakuransu. Amma saboda bahagon tunani basa yarda su karbi gyaran. Kuma a haka wani mai zuciya irin tasu zai basu 'ya su aura. Ukubar da za ta fuskanta da sunan aure ba matsalar mijin da uba bace.

"Ba ayi haka ba Alhaji. In zaman nan bai kawo gyara ba ina ganin bai kamata ya kara lalata lamura ba." Dr. Abdallah ya ce dashi. A ransa yana mai cigaba da nazarin hanyoyin karkato tunanin dattijon.

"Na gama zama. Ki sameni a gida idan kun gama"

Abbati ne ya hana shi fita "Alhaji ka zauna ka yi mana shaida akan kudirinmu na gaba. Malam mece ce makomar dukiyarmu a yanzu da muka tuba?"

"A shari'ance dukiya kala biyu ce. Halattacciya da haramtacciya. Tunda kokontonku yana ga son sanin ko dukiyarku ta haram ce to akan ta biyun zamu yi magana. Ita dukiyar haram an kasata biyu. Akwai ta haramci a dalilin abin mallakar mai cutarwa ne kamar giya, naman alade ko mushe. Da kuma wadda ta haramta a dalilin hanyar samuwarta da izini ko babu izinin mai ita. Misali dukiyar da aka sata ko ta bokanci, kwangilar kisan kai, caca, sayar da kayan maye, karuwanci da ribaa. Kun ga irin taku dukiyar ta fado cikin aji daya da karuwanci. To game da wannan nau'in dukiyar wadda ake samu da izinin mai ita amma sanadin samuwarta haram ne, dukkanin

malaman mazhabobinmu wato Imam Hannafi, Imam Hanbali, Imam Malik da Imam Shafi'i sun tafi akan cewa wajibi ne a rabu da ita. Ko dai a mayar da ita ga mai ita ko ayi sadakarta ga mabukata idan babu halin mayarwa. Ibnul Qayyim Aljauzi ma yana cewa a bayar din shi ya fi. Domin a lokacin samunta wanda ya bayar ya amfana da abin da ya biya kudinsa ne duk da cewa abin haram ne. A wani kaulin, Imam Al-Ghazali ma ya ce sadaka, zakka ko Hajji basu wajaba akan wanda duka dukiyarsa ta kasance haramtacciya ba.

Duka maluman nan sun yi duba ne ga ayoyin Alqur'ani da Hadisan Annabi SAW wurin fitar da fatawar. Misali, akwai wani hadisi wanda Imam Bukhari, Muslim, Ibn Majah, Nasa'i, Abu Dawud da Tirmizi duka suka rawaito [an karbo daga Abi Mas'ud Uqbah bin Amr RA cewa Manzon Allah SAW ya haramta kudin cinikin kare, kudin karuwanci da kudin bokanci.] (Ownership of Unlawful Wealth from Islamic Legal Perspective. Badruddin HjIbrahim da Azizah Mohd, 2017)

Hakika ba zan gushe ba wurin yaba muku matuka. Ina kuma yi muku albishir da cewa dukkan wanda ya bar wani abu da yake so domin Allah, to ladan wannan aikin yana ga Allah (Annawawi hadisi na daya). Zaku kwashi rabonku na alkhairi a duniya ko lahira. Ku sani dai cewa wallahi baku yi asara ba."

Kallon juna suka yi suka gyada kai a tare. In sha Allahu ba za su bari son duniya ya rufe musu ido daga barin mummunan alkaba'in da suka jima suna aikatawa ba.

"Akaramakallah akwai wani batu guda daya da ya rage. Ka san wannan abin yana tattare da matsaloli da dama da suka shafi lafiya. Musamman ga wanda ya tasarma barinta. A haka dai bamu da wani ciwo cikin ciwukan da ake dauka ta wannan hanyar. To amma mu dan yi bincike ana samun abin da ya shafi kwakwalwa. Hanyoyin da ya kamata mu bi a likitance domin kauracewa sha'awar da ta kan taso mana saboda sabo. Rashin kulawa zai iya janyo mana rubewa ko fitar tsutsa..." kasa karasawa ya yi saboda takaicin halin da suke ciki.

Abbati ne ya cigaba da bayanin "mun biya miliyoyin kudi ga wani asibiti a Italy wanda suka kware wurin dakilar da sha'awar sake fadawa zunubin. Sannan duk wata lalura da ta shafi lafiya wadda da wuya mu tsallakewa samunta a nan gaba kadan zasu magance ta. Tambayarmu a nan shi ne zamu iya zuwa? Idan bamu je ba Allah kadai Ya san halin da zamu iya tsintar kawunanmu. Sannan bamu da halin

sake samun kudin da zamu biya. Duk abin da muka mallaka yanzu hatta waya zamu rabu da ita saboda duka da kudin muka samu"

Iska Dr. Abdallah ya fesar daga bakinsa. Wannan tambaya akwai rudani a cikinta. Ya dubi matasan ya auna duka maganganun da suka yi. Ya tambayi nawa suka biya yaji kudin ba na kusa bane. Bayan nazari ya fada musu abin da yake ganin shi ne mafita.

"Ku je ku nemi lafiyar ku. Domin sai da ita ne kadai zaku iya barin wannan abu har abada. Idan nace ku zauna ban yi muku adalci ba. Bani da halin sama muku irin wannan kudi. Iyakar shawarar da zan baku shi ne ku kiyaye. Kada ku dauki kari akan abin da ku kw san lallai zai isheku iya zamanku a can."

(Wannan ba fatawa bace. Fahimtata ce ba fadin malami ba)

Ragowar bayanin da aka yi shi ne ya dan taba zuciyar Alh. Rabi'u. Ya auna da kwakwalwarsa ba son zuciya ba ya tabbatar duk a kokarin samun lahira Munzali yake wannan abu. Shi kuwa wane irin shaidan ne a kansa da zai sa ya cigaba da riko da mummunar akidar da har mahaifiyarsa ta rasu bata taba goyon bayansa a kai ba?

***

Bayan Wata Hudu

Sannu sannu bata hana zuwa, sai dai a dade ba a je ba. Abubuwa da yawa sun faru a cikin watannin nan ga jaruman labarinmu.

Mami Khadija ta koma hadadden gidan da Alh. Tahir ya mallaka mata ita da 'ya'yanta. Ta cigaba da aikinta cikin kwanciyar hankali. Iyayenta da Yakumbo sun yi fushi har sun sauko. Mardiyya bata yarda an barta ita kadai ba. Kamar yadda suma yaran basu kwashe duka kayansu daga wancan gidan ba. Musamman Sauda da Mardiyya da basa rabuwa. Kullum in basa wannan gidan suna wancan. Jiddo ta dade da tafiya. Gida ta kama mai kyau ta cigaba da shashancinta bisa zugar kawaye. Gidan ya zama dandalin fitinannun mata. Ba a dade ba kuwa suka cinye fiye da rabin kudin da Alh. Tahir ya bata. Tunda bata iya juyasu ba sai bushasha. A halin

yanzu ta gamu da ciwon gonoriya. Kuraje manya manya masu dan karen kaikayi da kazamin ruwa sun firfito mata. Ga kudin asibiti ya soma gagararta.

Alh. Tahir ya auri Yumna domin biyayya ga umarnin Yakumbo. Da kuma rufin asirinsa akan abin da Mami Khadija ta fadawa 'ya'yanta. Ya daina bin mata kamar anyi ruwa an dauke. Rayuwarsa babu wani farinciki a ciki saboda rashin Mami da zubar girmansa a idon manyan 'ya'yansa. Mama Nasima ta rage rashin zaman gida saboda tsoron kada ita ma ayi waje da ita. Yumna kuwa babu wannan fadar da take tsammanin samu. Ga kudi ga komai amma mijin bashi da lokacin biye mwa shirmenta.

Lilu ya mayar da hankali akan karatu. Suhaib kafa ta warke ya koma bakin aikinsa. Ayaah tana nan a ransa. Suna yawan gaisawa a waya wadda bata wuce ya gida, jikin Abbas da jarabawarta (a tsarinsa sai ta gama jarabawa zai nemi soyayyarta wadda ya gama nutsewa a ciki). Farha ce ta koma abar tausayi a wurin Mami. A zahiri ta cigaba da gudanar da rayuwarta kamar da. A badini kuwa kewar Abbati tana neman wargaza tuninta. Kara son shi tayi bayan Mami ta fayyace musu komai kamar yadda Alh. Tahir ya fada mata. Ta dai sakaya yanayin haduwarsu da babansu. Sai ta ce wurin abokinsa yaje yaga Abbatin. Wayar duniya ta buga bata samunsa. Tunda tayi na sati ta hakura ta fawwalawa Allah.

A Kano gidan Innayo sai san barka. Kansu ya hadu 'ya'yan suna ta zumuncinsu. Asabe da Innayo ma kamar 'yan uwa. Maigidan ne dai sai a hankali. Yau fari gobe tsumma. Wata dabi'ar barinta yana da wuya. Tuni Zara ta koma gidanta bayan Hajiyan Fatakwal ta zo da kanta sun sasanta da Innayo. Aka yiwa Ummulkhairi taron sunan da ya shiga bakin 'yan unguwa. Da wuya a hadu ayi hira mai tsayi ba ayi zancensa ba. Uwani ma da kanta ta koma. Salihi dawowa ya yi gida kawai ya sameta a falo da Mubasshir suna hira. Yayi murna kwarai da irin canjin da aka samu a tattare da ita. Ya hadasu da Ummule ya musu nasihar zaman lafiyar da kowane magidanci yake yi. Har yanzu dai babu wani abu mara dadi da ya faru gashi har Ummule ta haihu. Uwani ce ta karbi haihuwar tayi komai babu ha'inci a gida. Saura wata daya suspension dinta ya kare. Sannan ba tare da sanin kowa ba sai mijinta ta dauki Zakiyya da Qibdiyya sun je asibiti. Duk wani abu da ya dace ayi Salihi ne ya dauki nauyin biyan kudin. Ita da 'yan uwanta duk sun karbi zancen da yabi bakin kowa na cewa karayar arziki ce ta sami su Munzali. Asabe ta gina zancen akan wanda Mami Khadija tace mata taji a wurin Alh. Tahir lokacin da ta kira tayi musu jaje.

Salima dai aure ya mutu murus. Ale Gambo ya yi rantsuwar idan bata koma ba cikin kayadadden lokacin da ya bata tana da damar sake aure domin babu shi babu ita. Innayo ta lamunce mata tayi abin da zuciyarta take so. Cikin farinciki don har ta murmure ta ce ta gama zama dashi. Kwanaki kadan da suka wuce ta gama iddarta.

Abbas ya warke ya koma gida. Sauki ya samu don ya fara magana kuma yana tafiya da kansa. Tsakanin su Honourable da Abdulkarim sai tarin godiya. Shi da Ummita soyayya suke yi mai ban sha'awa. Biki saura sati biyu. Ayaah ma ta gama NECO sauran WAEC wadda jarabawa biyu suka rage su kammala baki daya. Anti Hasiya ciki ya fito. Laulayi ya yi sauki sosai. Tana samun riritawa daga mijinta, mahaifiya, 'yan uwa da 'ya'ya. Haihuwa kawai ake jira. Karshen abin farinciki shine kulle Danliti da Shazali da Alh. Sadisu yasa aka yi. Duka malamai da masu gadin makarantar da sukw da hannu su ma an rufe su. Shi Shazali ma a kurkukun bai tsira ba domin kusan kullum sai an yi masa duka.

Tunda Baaba Mari take bata taba samun kwanciyar hankali dari bisa dari ba sai yanzu. Alkawarin Allah Ya cika. Bayan kowanne tsanani akwai sauki tafe. Damuwarta ta shekara da shekaru ta kau. Sauran 'ya'yanta dama basu da matsala irin wadda ta jima tana damunta akan Abbati. Yanzu da komai ya daidaita ta sami nutsuwa.

Mal. Sa'idu ya soke karatun Allah. Sauran 'ya'ya da jikoki duk yasa an dawo dasu gaban iyayensu. Ya kuma aurar da 'Yashshafa ga wani tsohon saurayinta. Deluwa kamar ta hadiyi zuciya. Tana ta mitar yaya zasu yi ida Sha'aib ya zo. Hanne ma ta gama idda har manema sun fara kawo caffa. Ta cigaba da rayuwarta sannan ta rike sirrin Abbati.

***

Wata biyu kenan Abbati da Munzali suna karbar treatment akan hanyoyin tsira daga komawa tsohuwar rayuwarsu. Kafin su taho duk wani abu da suka mallaka sun damka shi a hannun Dr. Abdallah Saraki. Zunzurutun kudi da kadarori. Sutura da takalma kadai ne basu bayar duka ba. Amma hatta zobe da agogo basu bari ba. Motocinsu sun sayar. Gidan ma a satin aka sami mai saya. Sauran abin da basu kammala ba suka bar masa amanar sayarwa. Cikin kankanin lokaci aka dinga gina rijiyoyin burtsatse a kauyukan da suke tsananin bukata. Aka biyawa marasa lafiya da yawa kudin asibiti. Kudi ya zaga inds ya kamata. Dr. Abdallah ya taimaka musu

kwarai wurin sauke nauyin da yake wuyansu. Hankulansu kwance a inda suke. Wayoyin hannunsu ma shi ya saya musu kafin su tafi.

Bayan tafiyarsu Alh. Sadisu ya neme su a waya shiru. Sai ya tuntubi Alh. Tahir. Shi ma bai san inda suke ba. A wurin Mami Khadija ya sami numbar Baaba Mari. Takanas ya tafi Kano inda suka hadu shi da Alh. Sadisu suka kirata. Ta hadasu da Mal. Inuwa shi kuma ya faygace musu halin da ake ciki.

"Alhaji da zuciya daya nake kaunar yaran nan. Idan suka dawo kana ganin zasu yarda in saka su cikin siyasa? Ba wai 'yan banga ko makamancin haka ba. Ina so in daga su a idon duniya. Su fara da zama PA dina ko Secretary. Ta yadda duk inda nasa kafa muna tare. A hankali har a sansu wata rana idan muna raye in daga hannuwansu a zaben manyan mukamai" Alh. Sadisu ya ce da Alh. Tahir bayan sun koma gidan Alh. Sadisun.

"Nima nayi tunanin janyo su aikin kwangilata. Amma ina gudun kada su ki amincewa saboda yarana da suka nema a baya. Sannan bani da wani mutumci a tunani a idanunsu. Dama auren zai yiwu da naji dadi. Musamman na Farha." Shi ma Alh. Tahir ya fadi nasa kudirin. Jari zai basu mai tsoka da zai ishesu tsayuwa akan kafafunsu. Amma kuma Alh. Sadisu zai bawa "ina gudun kada su ki karba. Ko kuma su ga kamar nayi ne da wata manufa"

"Hakika haduwarka da yaran nan izina ce garemu baki daya Alh. Tahir. Duba ka gani yadda rayuwarka ta canja. Ina fada ba don izgilanci ba. Yadda ka rabu da harkar mata haka idanuna suka bude na rabu da duk wani abu na haramci a siyasata. Don gani nake kamar hakki ne ya kama Abdul. Kuma naga fa'ida domin na kara samun masoya. Kwarjinin da nake fata na kara yinsa ba tare da na bawa kowa tsoro saboda cin zali ba."

***

Garin Parioli wanda yake cikin babban birnin Italy wato Rome shi ne inda ake da babban masallacin kasar. Saboda girmansa zai iya daukar masallata dubu goma sha biyu a lokaci guda. A daya daga cikin wuraren alwalar maza Abbati da Munzali ne suke alwala. Sun cika burinsu na ziyartarsa kafin su bar kasar. Abbati sanye yake da shudin wando da shudiyar shet wadda ya dorawa jacket sea green. Munzali kuwa bakin wando ne da polo shet ruwan madara a jikinsa. Su biyun sun yi kumari sosai.

Ashe duk yadda jikinsu yake wannan abu yana tsotsesu basu sani ba. Sai yanzu suka kara zama cikakkun maza masu cikar kamala. Kowanne ya ajiye gashi a fuska wanda ya kara musu haiba. Alwala suke Munzali yana ta rawar dari. Abbati da ya gama ya koma gefe yana yi masa dariya.

"Nace maka ka k'ara riga akan ta jikinka amma ka dage wai da alamun rana a waje. Yanzu kuma ka zo ka sani a gaba kana makyarkyata kamar wanda ya kulla abota da DJ"

Munzali ya ciko hannu da ruwa zai watsa masa ya kauce yana kara yi masa dariya. A hasale Munzali ya ce,

"Ka dai ji kunya. Wai a matsayin wa na kake amma ka kasa sadaukar min da rigar sanyi. Sai surutu kake min kamar ..."

Kunnensu Abbati ya kamo yana cewa "ban hanaka rashin kunya ba?"

Munzali ya karkace kai saboda zafi yana magiya "me yasa baka san wasa bane. Don Allah ka saki kada kayi min kunne daya"

Zungure masa kai Abbati ya yi sannan ya cire rigar ya mika masa.

"Minti talatin zata yi a jikinka ka bani"

Da farinciki Munzali ya karba ya saka suka shiga masallacin domin yin sallar azahar.

Da suka idar hotuna suka dinga dauka domin tarihi. Ba su suka tafi ba sai da suka yi sallar la'asar. Lokacin jacket din ta koma jikin Abbati. Kowa minti talatin din yake ya bawa dan uwansa. Suna ta atishawa. Abbati ya yi ta mita. Munzali yana tunzura shi da cewa don kada ya barshi da jinya ne ma fa yake karbar aron rigar sanyin. Da zasu tafi addu'a kowannensu ya yi. Kusan abu daya suke roko. Cigaba da samun rufin asiri akan abin da ya gabata na rayuwarsu. Samun sana'ar yi sai kuma kowa ya yiwa dan uwansa fatan samun abokiyar zama tagari ba tare da sanin dayan ba.

Ranar da zasu tafi a airport dukkaninsu dokin ganin Qibdiyya suke yi. Sabo da rigima kamar yara harda fadan waye zai fara daukarta.

"Bayan ma yau baka kira mana ita ba" Abbati ya harari Munzali.

Zama suka yi akan kujerunsu daga jikin juna a jirgi sannan Munzali ya ce "na fada maka kashe min murya Zakiyya take yi. Sai ta kusa cinye kudin da surutu. Kai kuma ka wani dage ba za ka dinga kiranta ba sai kace surukarka"

"Ka sani ko ayi kome?"

Seatbelt din da yake kokarin sakawa ya saki ba shiri ya kalli Abbati.

"Kome a ina? Ni nace maka ina son aure ne ko kuwa ina son Zakiyya?"

Abbati ya ce "ko daya. Aure dolenmu ne Munzali. Indai ba so kake iyaye su sake fara zargin ko mun koma ruwa ne. Ba don na san mun rabu kenan dasu Diamond girl dinka ba ai da ita zan ce ka aura. To amma kaga babu wadda ya dace ka zauna da ita kamar Zakiyya. Ita ce ta haifi Qibdiyya. Ita ta san me ya faru da ita. Ita ce kuma zata san hanyar hana maimaici."

"Shawara ce kake bani?"

"Eh"

"Kana ganin akwai alkhairi idan aka daina rabawa Qibdiyya hankali?"

"Tana bukatar tsayayyen gida da uwa da uba."

"To kai yaushe za ka yi auren?"

"Wa yake ta tawa? Da Hanne tana nan da yanzu bakina alaikum. Yanzu kuwa dole in nema can nesa da gida."

Zancen Farha ya so yi masa amma ya fasa saboda baya son yi masa fami.

"To Allah Ya kawo tagari. Amma ka daina zancen Hanne baiwar Allah. Ni na san ko kadan baka sonta. Shi yasa kana samun dama ka sallameta" cewar Munzali yana dariya.

Shi ma Abbatin dariya ya yi yace "Cutar juna muke kawai. Tana jin haushina ina jin nata."

Jirgin na shirin tashi suka kira Dr. Abdallah, Alh. Sadisu wanda yanzu yake yawan kiransu sannan kowa ya kira iyayensa. Munzali kadaran kadahan suka gaisa da babansa. A hakan ma sun sami cigaba ne a alakarsu saboda jajircewar Munzalin.

***

Tafiyar awa biyar da minti hudu ce ta kawosu Nnamdi Azikiwe International Airport Abuja. Suna fitowa daga ciki mota tazo ta daukesu kamar yadda Alh. Sadisu ya ce musu ya bada umarni da suka yi waya.

"Zai kai ku hotel. Gobe zan zo garin ganin party chairman. Sai mu juya jibi tare. Ina fatan hakan ba zai zama takura a gareku ba"

Wannan shi ne abin da ya fada musu a wayar. Cike da girmamawa suka yi masa godiya. Da zasu fita daga motar bayan sun isa hotel din kudi direban ya basu a envelop.

"Yallabai ya ce ku rike kafin ya iso"

Suka sake yin godiya sannan kamar lokacin tasowarsu duk da dare ya yi sai da suka kira iyayensu. Cikin daren suka tattauna yadda zasu yi idan Alhaji Sadisu ya zo musu da wani abu da zai iya bata musu rayuwa. A yanzu sun hankalta suna matukar tsoron shigewa masu kudi. Babu dangin Iya babu na Baba. Watakila wani abin ake nema a garesu.

Washegari sai bayan isha Alh. Sadisu ya iso. Tare suka je suka ci abinci. Dakinsa a hotel din yace su biyo shi. Gabansu ya fadi amma suka daure.

Yana zaune a kan kujera suna kasa a gefensa ya yi musu magana.

"Na san cewa zukatanku suna cike da tambayoyi da fargabar manufar janyoku da nayi a jiki. Dom Allah ku kwantar da hankalinku. Ko babu komai ceton rayuwar Abdul da ku ka yi ya isheni dalilin son saka musu da abin alkhairi. A dalilinku ya sami sauki har ina shirye shiryen tura shi kasa mai tsarki da biyu cikin iyayensa mata. Sai ya yi a kalla shekara guda yana karatun addini zai dawo gabana ya karasa sakandire. "

Murna suka taya shi yaji dadi kuwa

"Magana ta gaskiya labarinku ya tsaya min a zuciya. Ban taba ganin almara irin wannan ba. Giyar kudi bala'i ce. Musamman ga matasa irinku wadanda kuruciya take diba. Yaran yanzu zasu yi komai domin kudi. Sai gaku na hadu daku zahiri ba labari ba. Kun bude min ido da kusanto da tunanin lahira a dukkan lamurana. A takaice rayuwata duka na canjata kuma duka kune sila. Wannan yasa na daukarwa kaina alkawarin ba zan bari ku tagayyara ba. Rashin abin yi da rashin kudi a hannun wanda ya saba rikewa ba karamar jarabawa bace. Tsananin rabo da tsoron Allah ne kadai zai dakushe zukatanku daga tunanin hanyoyin samun kudi ko ta wace siga. Saboda haka idan kuna da ra'ayi ni Alh. Sadisu Nakano nayi muku alkawarin muddin ina raye da rai da lafiya, zan yi iya yina domin ganin kun zama wasu ababen misali da alkhairi a cikin al'ummarmu. Ina burin duniya ta amfana da alkhairin da nake da yakinin Allah Ya wanzar muku sakamakon mika wuya gareShi. Me ku ka ce?"

Basu ce komai ba sai kwalla. Ikon Allah akwai ban tsoro. Duka duka awanni nawa da suka wuce ne suka zauna suna tunanin yadda zasu yi da rayuwarsu yanzu? Sai gashi mafita tazo daga inda basu tsammani.

Alh. Sadisu ya yi murmushi "in dauki shirunku a matsayin amincewa?"

"Alhaji ko za ka bamu zuwa gobe domin mu shawarci iyayenmu"

"Ka cika babba Abbati. Dama gaggawa daga shaidan take. Ku yi shawara da duk wanda ya dace. Fatana Allah Yasa ku bani damar zame muku uwa da ubs a siyasance. Da yardar Allah ni daku babu mai yin nadama."

Dr. Abdallah suka fara kira. Ya ce idan sun shigo Kano gobe su zo su same shi a gida. Da makomar tattaunawarsu da shi zasu yiwa iyayensu bayani. Daga nan su nemi amincewarsu.

Direban da ya daukosu daga airport shi ne ya kuma zuwa daukarsu. Alh. Sadisu ya sanar dasu cewa zasu tsaya a Kaduna zai ga abokinsa kafin su wuce. Haka suka jera suna biye dashi a baya.

***

Suhaib, Farha, Lilu, Sauda da Mardiyya ne suka fito daga wani babban shopping mall wanda yake makwabtaka da ofishin Alh. Tahir. Mami Khadija ya kuma roka akan burinsa na daidaitawa da yaran. Tayi musu magana harma da fada akan lallai su cire abin da yake ransu su kyautatawa mahaifinsu.

"Shi kadai gareku. Ba zai yiwu don ya auri Yumna kowa ya dauki gaba dashi ba. Duk alkhairinsa gareku bai kyautu ku manta ba saboda wani abu guda daya da bai sabawa shari'a ba"

Fadan a gaban kannensu ne. Su manyan sun san me take nufi. Hakuri suka bata tace to tana so bishi office su nuna masa komai ya wuce. Da yake kullum cikin kokarin janyosu jiki yake suna yakicewa sai kowa yaji babu dadi. Shi ne Suhaib ya ce su fara zuwa kowa ya sayi gift guda daya su bashi.

Sauda da Mardiyya sai tsalle da murna. Ji suke kamar sun dade basu ga Abbansu ba. Kowa ya yi kewarsa. Harda Suhaib kuwa.

Abbati da Munzali a hadadden reception din office din suka zauna suna hira. Alh. Sadisu ya shiga wurin Alh. Tahir ba tare da sun san wurinwa ya zo ba. Yana ciki suna tattauna makomar rayuwar yaran. Niyarsu sai sun gama magana sannan Alh. Sadisu zai kirasu ciki domin su sami fahimta da Alh. Tahir. Yana so su dauke shi a matsayin makusancinsu.

Waya suke yi da Qibdiyya ta cikasu da surutu mai bude kofar ya hangameta. Basu dago sun kalli su waye suka shigo ba koda suka ji ma'aikatan dake wucewa suna ta yi musu maraba.

"Oga yana tare da bako." Wani masinja ya fada musu.

"Bari mu jira shi a nan" Suhaib ya nuna kujerun reception din.

Kafin su karasa duka su biyar din sun ga su waye a zaune. Farha ji tayi kamar zazzabi zai kama ta. Kujerar farko ta gabanta ta dafa yayinda Suhaib da Lilu suka karasa gabansu.

Earpiece ne a kunnen Abbati yana kallon video din Qibdiyya na zuwa sabuwar makaranta wanda tasa mamanta tura musu a lokacin. Munzali ne ya daga kai da yaji alamun ana tahowa gabansu. Mamakin dake fuskarsu Suhaib shi ne a tasa. Da hannu ya zunguri gefen hannun Abbati. Yana daga kai idanunsa a bangaren hagu suka sauka. Duniyar sai ta tsaya cak. Numfashinsa ya dinga fita da sauri da sauri da yayi tozali da Farha.

Jikinsa nauyi ya yi masa saboda bai san me zai ce mata ba. Akwai tarin tambayoyi da ma bayani da zata bukata wanda bashi dasu. Kwanciyar hankalinsa daya shi ne sanin cewa Alh. Tahir ya rufa musu asiri.

Yana can duniyar tunani da kallonta har Munzali suka gama gaisawa dasu Suhaib. Ya rike hannun Lilu yana cewa "ka gafarceni. Kunya ta hanani nemanka."

"Komai ya wuce. Naga message dinka tun lokacin" Lilu ya bashi amsa da fara'a.

Sauda ta turo Mardiyya gaba don su gaisa tana ta nokewa.

"Diamond girl da Hasanarta kuna lafiya? Ya kwana biyu?"

Sama sama suka amsa, hankulansu sun karkata ga Abbati da ya yi mutuwar zaune ga Farha tana takowa wurinsu a hankali. Har ta iso Abbati bai dauke idonsa daga gareta ba. Tana zuwa gefen Munzali taje ta tsaya tayi masa sallama.

"Don Allah ko za ka iya bani wuri in zauna kusa da dan uwanka?" Ta nuna inda yake zaune kusa da Abbati.

Idanu ya dan ware ya ce "na'am?"

Idanun Abbati basu bar kanta ba duk da taki juyowa.

"Hoto nake so a daukemu" ta furta a dake. Hannunta ne ma ya soma rawa wurin kokarin bude jaka domin ta dauko wayarta. Idan ta kama dan karfen budewar sai ta kasa juya shi yadda ya dace. Saboda dauriyarta ta kusa karewa.

"Bashi wannan" Abbati ya mika mata wayarsa ko earpiece din jiki bai cire ba.

Ta mika hannu ta karba kanta a kasa bata yarda sun sake hada ido ba. Lilu ta mikawa don hannunsa tuni ya yo gaba. Ta koma ta zauna a inda Munzali ya tashi.

"Ya Farha"

Ko da wasa bata yi yunkurin amsa kiran da ya yi mata iya jin kunnuwanta ba don ta san muryar ta bace. Daga kai tayi kawai aka yi dace shi ma ita din yake kallo. A haka Lilu ya daukesu hoton suna yiwa juna kallo mai cike da sakonni kala kala.

Ana dauka ta mika hannu ta karbo masa wayarsa. 'Yan uwanta da Munzali suna ta kallon ikon Allah. Numbarta ta soma sakawa sai gani tayi sunanta ya fito baro-baro a jikin screen din.

(Ya Farhata)

Kwalla mai zafi ya sauko mata kowa yana gani tasa hannu ta dauketa. Cikin whtsapp dinsa ta shiga ta bude sunanta ta tura hoton da suka dauka sannan ta mika masa. Yana karba ta haye sama.

Su Mardiyya suka bi bayanta da sauri. Office din Alh. Tahir taje. Ta bude da sallama ta fada kai tsaye. Yana ganinta ya tashi ta iso ta rungume shi sai kuka. Lilu ya rike baki a hankali ya ce "see love"

"Me ya sameta?" Alh Tahir ya tambayi su Suhaib hankalinsa a tashe.

Amsar ya gani da idonsa da isowar su Abbati kofar office din.

Alh. Sadisu ya saki murmushi "Munzali me ku ka yi mata?"

"Babu ruwana fa. Aikin Abbati ne."

Abbati yaji kamar yana kan k'aya a inda yake. Ta daina kukan amma ko fuskarta baya hangowa.

Alh. Tahir dadi kamar ya yi yaya. Farincikin da ya rasa na watanni ya samu da ganin yaransa. Gashi alamu sun nuna Farha da Abbati suna son juna har lokacin. Alfarma ya roki Alh. Sadisu akan su je gidansa kafin su wuce.

"Abba da alama mun kusa shan biki a gida" Sauda ta ce tana tafa hannuwa.

Aka yi dariya sannan kowa cikinsu ya mikawa Alh. Tahir kyautar da ya kawo masa. Bawan Allah sai yaji yana neman yin kuka. Sauda da Mardiyya ya rungume don kada a gane suka fita tare.

Idan Abbati da Munzali sun yi mamakin sabon gidan da suka gani na Alh. Tahir sam basu nuna ba. Mami Khadija tasa mai aikinta ta kawo musu lemo da ruwa sannan ta fito. Ita kanta taji dadin sake ganinsu Abbati.

"Shikenan sai kuka bace Munzali?"

"Dawowarsu kenan kasar tun bayan faruwar wannan abin" Alh. Tahir ya bata amsa.

Bayan tambayoyin yaushe gamo, Sauda da Mardiyya kadai aka sallama daga falon sannan Alh. Tahir ya sake nanata abin da ya fada a gabansu.

"Alh. Sadisu ne ya basu shawarar barin kasar har kura ta lafa. Dukiyar da aka basu kuma sun tattara komai sun mayar ga masu ita. Shi ne suka gujemu a tunaninsu zumunci zai kare tunda yanzu basu da komai."

Wannan abu ya kara tausayinsu ga su Mami Khadija.

"Bawa bai taba yi domin Allah Ya tabe ba. Ba kowa zai iya abin da kuka yi ba Abbati. Mara tsoron Allah ne kadai zai gujeku"

Dama tunda Alh. Tahir ya kirata a waya ya fada mata zai kawo nan shi ne tasa aka kara abinci.

Falon cikin gidan tasa Lilu ya shigo dasu Munzali domin su ci abinci. Alh. Tahir kuma ya ce zai tafi da Alh. Sadisu don gujewa kananun magana kamar yadda Mami ta ce. Harda direbobin zasu tafi. Idan suka gama zasu dawo su daukesu su wuce.

Mai aiki ce tayi jigilar kai kayan abincin falo. A ciki kuma ba babba ba yaro an hadu ana bawa Mami Khadija labarin hoton Farha da Abbati. Ita da tayi hoton ma sai yanzu kunya ta rufeta. Dariyar da Mami Khadija tayi ne yasa "Mami sharri ne fa. In akwai su nuna miki."

"Lallai ma Ya Farha. Bari naje na karbo wayarsa" inji Lilu uban gayya.

Suhaib ya janyo hannunsa "dawo gadanga abinci zasu ci"

Falon Mami Khadija ta tura mazan. Su Mardiyya ta saka su aikin hada fruitsalad sannan ta tsare Farha a daki.

"Na jima rabona da ganinki cikin yanayi irin wannan na zallar farinciki Farha." Kai Farha ta sunkuyar. Mami ta cigaba da cewa "bana so ki zura jiki da yawa. Tun haduwar farko na lura Abbati yana da hankali. Na tabbata faruwar wannan lamari ne ya koresu. Kin ji ance basu da komai yanzu. Sai dai nayi imani tunda Alh. Sadisu yake bibiyarsu he has a plan for them. Abbanku ma ya ce akwai abin da ya shirya. Tambayata a nan Farha za ki iya zama da Abbati sabanin yanda kike zatonsa?"

Idan tayi shiru tabbas za ta kwari kanta. Sannan bata kasance cikin masu zurfafawa da naci ba tare da neman zabin Allah ba.

"Ina addu'a sosai Mami. Sai gashi na ganshi a wurin da ban taba zato ba. Indai kin yarda dashi in sha Allah zan iya zama dashi.

Cikin farinciki Mami Khadija ta ce "Alhamdulillah. Abbanku ne ya ce na tambayeki kafin su dawo don yana so a yau a tsayar da magana guda."

Da gudu Farha ta bar dakin saboda kunya. Dakinta ta shiga tayi sallah ta sake gyara fuska. Tana gaban mudubi taji kira ya shigo. Haka kawai jikinta ya bata Abbati ne. Da ta duba kuwa sai taga bakuwar namba. Sake kira aka yi still taki dauka. Sai ma haushi da taji cewa yana da nambarta amma bai taba kira ba. Fitowa tayi daga dakin suka kusa karo da Lilu. A ranta tace dama ya saba rawar jiki idan ya gansu.

"Yauwa dama ke nake nema. Wai ya ce ki fito ku yi zance"

Bakin Lilu ta rufe da sauri ta waiga hanyar kitchen. Ai kuwa masu aikinsu biyu suna wurin kuma sun ji. Ga Sauda da Mardiyya. Sai suka hau yi mata dariyar shakiyanci.

BABI NA ASHIRIN DA BAKWAI.

49

Bakin Lilu ta rufe da sauri ta waiga hanyar kitchen. Ai kuwa masu aikinsu biyu suna wurin kuma sun ji. Ga Sauda da Mardiyya. Sai suka hau yi mata dariyar shakiyanci.

Falon ta nufa zuciyarta tana dukan uku uku. Tana yin sallama Abbati ya ajiye cokalin hannunsa ya bita da ido. Munzali ya hada ido da Suhaib sai kawai suka tashi. Ya zo bakin kofa ya juyo ya kalli plate dinsa wanda ya cinye abincin tun kafin shigowarta.

"Abbati ban koshi ba fa. Na dawo na karasa?"

Jinjina kai Abbati ya yi rai a bace. Munzali ya rasa lokacin yi masa haka sai a gaban Farha. Bai san lokacin da harare shi tare da gargadi ba.

"Kada ka bari na tashi Munzali"

"Za ki iya da wannan mafadacin? Ko dai za ki koma ciki ni na karasa cin abincina?" Munzali ya sake zolayarsa kafin ya fita da sauri da Abbati ya yunkura zai tashi.

Kujerar farko idan an shigo Farha ta samu ta zauna. Abbati sai ya ajiye nasa plate din akan tray ya taso ya dawo ta kusa da ita. Yana kallon alamun takura a tare da ita. Ta hade yatsunta tana ta wasa dasu.

"Ya Farha"

Tsigar jikinta tashi tayi saboda yadda tayi kewar sunan a bakin wanda ya furta shi.

"Uhm"

"Ina neman alfarma. Farha-ta nake son magana da ita. Wadda ta sauke min alkawarin da nayi na daukar hoto da ita"

"Me yasa kake nemanta bayan baka damu da ita ba?" Ta furta a raunane.

Yana ji ya san ranta ya baci da shirunsa. Dole ya rarrasheta in yana son ta fahimce shi.

"Bana bukatar fada miki matsayinki a wurina. Amma ina so ki sani cewa zuciyata bata taba samun hutu ba tun ranar da na fara ganinki"

"Ta yaya zan yarda bayan kai kadai kake yadda kake so. Lokacin da ka ga dama kawai kake nemana" tayi maganar cikin zubar hawaye.

"Ki yi hakuri. Nayi zaton hakan shi ne mafi alkhairi saboda halin da muka tsinci kanmu ni da Munzali"

Sai ya kara bata tausayi. Ta dube shi da hawayen idanunta "kana ganin ya dace kai kadai ka yanke hukunci akan abin da ya dace ba tare da jin ta bakina ba?"

Idanunta dake cike da kwalla ya fara kallo sannan duka fuskar da kuka ya fara kumburawa. Wani abu mai girma ya sake motsa zuciyarsa. Sonta da burin mallakarta a matsayin matar aure ya mamaye tunaninsa. A cikin nutsuwa ya ce mata,

"Kiyi hakuri Ya Farha. Farha-ta. My Angel. Zan iya kiranki Angel ko?" Ya marairaice murya.

Da wadannan kalaman ya tarwatsa tunaninta. Zuciyarta ta kara cika da tsaftatacciyar soyayyarsa.

"A'a" ta bashi amsa kai tsaye.

"Me yasa?"

"Saboda ban sani ba ko nan da kwanaki kadan zan sake nemanka na rasa"

Murmushi ya yi ya ce "na hakura. Zan jira ranar da za ki kirani da kwatankwacin wannan sunan. A lokacin na san kin shirya karbar Abbati."

Dan muskutawa ya yi ya ce "Zamu iya magana a gaggauce kafin su Abba su dawo?"

Da ka ta amsa. Abbati ya dauko mata zancen abin da ta sani. A kasan zuciyarsa yana bakincikin boye mata ainihin labarinsa. Sai ya tuna cewa ko babu tsoron rasa

soyayyarta bai kamata ya dinga kwayewa kansa baya ba. Takaicinsa sai ya rage na sanya mahaifinta da duk masu son rufa musu asiri yin karya.

"Rayuwata ta koma baya. Bana ajin irin mazan da suka dace su kiraki matarsu. Wannan ne dalilin da yasa ban kara nemanki ba"

"Angel" ta ambata a can ciki don da kyar ma yaji. Cike da annashuwa kuwa ya kalleta.

"Na'am"

"Kada ka sake guduwa!"

Daga haka ta tashi ta fita. Ba jimawa Munzali ya shigo. Sai kuma su Alh. Tahir suma suka dawo.

Fitar da Munzali ya yi yasa Sauda ta kira masa Mardiyya. Sun sami wuri sun zauna ya yi amfani da rufin asirin da babanta ya musu ya fada mata duk abin da ya faru. Ba tare da jan zance ba ya ce,

"Baki cancanci soma rayuwar sadaukarwa da kuruciyarki ba. Zan cigaba da kasancewa tare dake a matsayin dan uwa. Amma ina so ki cigaba da normal rayuwarki har muga ikon Allah"

Kuka yaga tana son yi ya ce "kada mu yi haka dake. Ba datse alakarmu nayi gabadaya ba. Ina bukatar lokaci. Bayan abin da ya faru da Qibdiyya yanzu zamu daidaita da mamanta. Ki yafe min bacin lokacin da nayi miki"

"Nagode Ya Munzali" Mardiyya ta kirkiro murmushi. Karancin shekaru basu sa ta kasa fahimtarsa ba.

Su hudu suka zauna a falon. Alh. Tahir ya fara da tambayarsu game da 'ya'yansa. Kai tsaye Munzali ya ce ya janye.

"Bayan duk abin da ya faru ina ganin ya dace na dawo da matata da muka rabu. Zan cigaba da daukar Mardiyya kamar kanwata. Allah Ya kawo musu miji nagari.

"Kai fa Abbati?"

Kai a kasa ya fada musu yana son auren Farha amma ba yanzu da bashi da komai ba. Ya kuma san cewa ta jira shi ba karamin son kai bane. Rasata kuma is not an option.

Manyan dariya suka yi. Sun riga sun gane halin da yake ciki. Alh. Tahir ya ce idan ya je gida ya bawa mahaifinsa nambarsa don ya kira suyi magana. Sauran abubuwan da yake tsoro kuma Ya barwa Allah.

Da suka tashi tafiya Mami ta sake fitowa. Su Suhaib ma har mota suka zo, Farha ce kadai bata fito ba. Kunyar da rashinsa yasa ta iya ajiyewa dazu ita ce ta dawo bayan samunsa.

***

Ko akwai, ko babu, indai dangi suna da yawa kuma da hadin kai to kuwa da wuya idan uzurin juna ya tashi a ji kunya. Cikin 'yan watannin nan da aka sami wadatar farinciki da kyautata zumunci a gidan Alh. Rabi'u, 'yan uwan sun dauki juna da matukar mahimmanci. Abu ya zo akan gaba. Za ayi bikin Ummita da Murja. Kowa ya zage damtse. In baka yi bani wuri. Da talaka da mai kudi babu wanda bai kawo wani abu domin a saka a dakin amaren ba. Abdulkarim yaso sakar musu kudi sosai amma sam Honourable yaki yarda. Wanda aka yi ma ya isa. Kada su zama marasa tunani. Sannan dole su kiyaye mutumcin 'yarsu.

Munzali ne ma ya dinga jin ba dadi. Zasu aurar da 'ya'ya amma duk abin da ya saya rabin kudin Abbati ne ya bashi cikin wanda Alh. Sabi'u ya basu.

"Banza, akan haramtacciyar dukiyar kake ta kunkuni tun jiya ko? Idan kana so sai na kai ka inda aka sakaya Shazali ku gana"

Kukan kura Munzali ya yi ya tashi zai cakumo shi sai ga Qibdiyya ta shigo.

"Daddy me za ka yiwa Papa?"

"Maballi ne ya shake shi zan gyara masa" Munzali ya ce da sauri.

Abbati da Asabe dake zaune a falon nata suka kwashe da dariya. Tare suka fito daga gidan da Asabe da Innayo a bayan mota. Sai Qibdiyya akan cinyar Munzali. Abbati ya jasu zuwa wurin da ake taron kamu.

Taro ya yi kyau sosai. Da aka bukaci uwar amare ta fito domin kai 'ya'yanta kan shimfidar da aka tanada domin kamu duka 'ya'yan Larai sai cewa suka yi Uwani taje. Ta tashi cikin farincikin da bata taba ji ba ta rungumosu a jikinta har wurin. Da ta dawo ta zauna Hasiya ta dan tabota ta ce,

"Metiron kuka kika yi ne?"

Uwani ta maka mata harara bayan ta karewa wajen kallo ta tabbatar babu wanda yaji.

"Bani da lokacinki yanzu. Nan da wata biyu zaki ga Metiron Uwani a gabanki ra'ayil aini."

Jikinsa Hasiya tuni ya yi sanyi. Tsokanar da ta fara ta hadiye ta tsurawa katon cikinta kallo. Can dai ta kasa daurewa ta riko hannun Uwani.

"Don Allah da ciwo sosai yadda ake fada? Taba wuyana ki ji. Wallahi zazzabi ke neman kamani"

Uwani ta tuntsire da dariya. DJ na cewa uwar amarya ta fito ta janyo hannun Hasiya filin rawa tana jujjuyata. Innayo ta kallosu su biyar, da su Ummakati da Fati duka suturar jikinsu iri daya, sun yi kyau. Karo na farko da wani zai gansu ya ce jininsu guda.

Cikin aminci aka yi taro aka gama. Washegari daurin aure. Ranar ne kuma Suhaib da Lilu suka zo. A masallacin daurin auren suka hadu dasu Abbati. Munzali ya yi murna da suka karbi gayyatarsu.

"Ba dole ba. Idan naki zuwa Ya Farha da Ya Suhaib zasu iya tsireni" Lilu ya ce yans dagewa Abbati da Suhaib gira.

Munzali ya ce "ban gane ba. Abbati dai na san an gama da zuciyarsa. Suhaib ne dai sai ka bani haske"

" 'Yarka ce Ayaah"

Munzali sai murna. Suhaib ya ce to dai gaskiya kada su bata masa show. Su yi shiru a jira su daidaita.

"Ashe a jaririn mataki kuke. To ga Romeo nan sai ka tambaye shi satar amsa" cewar Munzali da shakiyanci.

"Allah Ya tsareni da zama Romeo. Shi da bai dorar da soyayya ba. Ka dai kirani ...."

"Wa?" Suhaib, Lilu da Munzali suka tambaya.

Abbati ya tashi ya barsu yana cewa duk basu da kunya sun raina shi.

***

Da kaiwa baki abinci Munzali ya samu ya tura Ayaah wurin Suhaib. Tayi kwalliya mara hayaniya wadda ta fiddo da kyawunta. Tray din hannunta lemuka ne da ruwa a kai. Tana tafe wurin da Munzali yace mata ya bar mota tana yangar 'yan mata. Suhaib ne kadai a motar yana ta dariyar yadda take fama tura baki a dole kayan sun mata nauyi.

" 'Yan mata na tayaki ne?"

Bata kula dashi ba sai murya taji. Dama kuwa ta gama fushi don ya ce mata ba zai zo bikin ba. A saman boot ta ajiye ta murguda baki cike da shagwaba.

"Bana so."

"To tsayuwar me kike a nan?"

"Saurayina nake jira" ta amsa tana waige waigen baya.

Suhaib ya dauki lacasera mai sanyi ya bude ya sha kadan sannan ya ce "Har ya bani tausayi"

"Wa?"

"Saurayin naki mana. Zai kwashi tsiwa. Gashi ma ba sonsa kike ba?"

Ayaah ta daure fuska. Fushi take dashi maimakon ya bata hakuri ya zauna tsokanarta.

"Inji wa yace bana son sa?"

"Inji wanda kike so"

Kusan faduwa Ayaah tayi don dama inda take tsaye dan tudu ne mara fadi.

Sannu Suhaib ya ce mata da ta gyara tsayuwa a gefensa.

"Na zata kin fara sona ne fa kamar yadda na dade da sonki"

Kunya da farinciki suka rufeta ta ce "Ni wallahi..."

"Ke me?"

"Me yasa kace ba za ka sami zuwa ba?"

"You are not serious. Amsar abin da na fada miki kenan?"

Rufe idanu tayi da tafukan hannunta ta ce "kunyarka nake ji"

Girgiza kai ya yi don ba haka yake son ji ba "ya batun amincewa ko babu? Dazu Baba yake fada min ya dage bikinki sai yaron da ya zaba miki ya dawo daga cirani."

Yana kallonta duk ta fara rikicewa

"Kin tuna ni kuma kin ce kada ma nace ina sonki a baya ko?"

"Lokacin ma fa wasa nake? Kace masa..."

Dariya taga yana yi shi yasa ta kasa karasa magana. Yana kiranta ta dinga sauri ga takalminta mai tsini.

****

A yau cikin hukuncin Allah aka daura auren Auwal (Abbati) da Farha, Munzali da Zakiyya da kuma Suhaib da Haajara (Ayaah). Bikin ya zo wata biyu daidai bayan Hasiya ta haifi santaleliyar 'yarta wadda aka radawa suna Aisha kamar yadda Innayo ta roka.

Anyi biki na masu ilimi da aji. Alh. Sadisu ya tsaya tsayin daka a matsayin uban angwaye. Iyayensu basu da abin cewa sai godiya da addua.

Kamar yadda ya yi alkawari ya basu aiki a jikinsa. A gefe guda sun soma kasuwanci kuma suna ganin alkhairi. Sun kara gaskata zancen da ake cewa Na Allah baya tabewa. Rabon kwado kuma baya hawa sama.

Zakiyya dai auren a bazata yazo mata. Munzali wanda yake jin zai iya sadaukar da komai domin Qibdiyya ya je gidansu wata daya kafin bikin ya yi magana da Gwaggo Lami. Ya fada mata taja kunnen Zakiyya saboda ko kusa ba zai dauki sakaci da rayuwar 'yarsa da wasa ba. Daddy kuma wanda ya koma hostel saboda tsangwamar Gwaggo da kiyayyar da Zakiyya ke nuna masa ya ce a fada masa ko da wasa kada ya yi gigin zuwa inda yake da sunan ganin yayarsa. Bai kulleshi ba saboda kawai yana ganin shi ma mai laifi ne.

A gefe guda ya auna yaga da wahala idan ya auro wata ba za ta gorantawa Qibdiyya wataran ta ce kanin babarta ya bata ta ba. Ya kuma san wannan abin ne yasa Abbati cewa ya dawo da Zakiyya.

Kafin magariba amare duk sun shiga dakunansu. Gidan Abbati yana Farm center, na Munzali yana Lodge road. Dukkaninsu cikin gidajen hayan Alh. Sadisu wadanda suke apartments ya basu daidai su zauna. Ya nuna musu cewa lokaci kuma ya yi da zasu koyi rayuwa su kadai domin samun damar kulawa da iyalansu.

Ayaah kuma Kaduna aka kaita. Gidanta babu nisa da na Mami Khadija. Shima na Alh. Tahir ne. Suhaib ya yi mata alkawarin cigaba da karatu kamar kannensa.

SHEKARA KWANA

Baaba Mari, Innayo, Asabe da Mami Khadija suna zaune a tsakar gidan Alh. Rabi'u. Yau ake yinin bikin Salima da wani abokin Alh. Unaisu.

Baaba Mari tana dauke da Maama (Khadija) 'yar wajen Suhaib da Ayaah. Akan cinyar Innayo kuwa Auwal din Munzali da Zakiyya ne. Mami Khadija kuma ta goya sarkin rigima Sa'id din Abbati da Farha. Asabe kuma tana ta kai kawo wurin kaiwa baki abinci.

UWA UWACE...

Tammat Bihamdulillah